🌺 *HAMDAH* 🌺
*WASA FARIN GIRKI!!*✍🏻

*NA*
*RASHEEDA S DIRECTOR*

_(Book 3)_

_(Bismillahirrahmanurrahim.) Alhamdulillah ina yiwa Ubangiji buwayi gagara misali godiya da ya kuma bani iko a karo na uku nakuma dawowa domin kawo muku cigaban labarin HAMDAH ina rokon Allah ya bani ikon kammala shi lafiya👏🏻_

(Afwan a karshen book 2 nasaka (After 1 year)
I'm so sorry typing ero ne👌🏻 )

Littafin na siyar wa ne ki biya ki karan ta.
domin biyan kuɗin littafin sai ka-ki tuntuɓi wannan number 08034690723

🅿️1

Bayan wani lokaci.
Tuni ai kin hajji ya karato gamasu niyya tuni aka fara shirye-shiryen tafiya ai kin hajji. kan kace me kasar Saudiyya tacika tayi makil da al'ummar Musulmi.
yanzu bama samun wani zama kullum muna hanyar zuwa bautar Ubangiji, ba dare ba rana kullum Bappa na tasani gaba  wani sa'in tare muke tafiya da su Naseem da Nasmah,wani sa'in kuma na barsu wa Mammaa mahaifiyar Ukhtee kawata da nayi anan cikin masarautar Saudi jika ga Masarautar Saudi. dan tare muke tafiya da Ukhtee ita kuma Mammaa ciwon kafa ke damun ta bana bazata samu daman fita afara aikin hajji da itaba.
acewar ta sai an zurfafa ibada sosai kan lokacin Abdul Malik yayan Ukhtee da yake karatu can jami'ar Madina yashigo zai fita da ita gurarren ibada a kan keken zama irin na masu ciwon kafa.

kasan cewar na yaye su Nasmah kuma suna cin komai gashi sun saba da matar sosai, shi yasa wahalar su ta ɗanyi min sauki ko zamu fita ban cika tafiya da suba....
cikin yarda da buwayar Ubangiji aka kamla ai kin hajji na wannan shekaran lafiya.★
tuni mahajjata suka fara komawa kasashen su,nan muma muka fara shiri damin ko mawa kasar mu.
ana gobe jirgin mu zata ɗaga. tun safiyar ranar jama'ar dake cikin masarautar sukayi ta zuwa sallamar mu. duk wan da yazo sai ya nuna baison tafiyar mu wasu ga fuskokin su wasu kuwa sai sun kai ga furtawa. Ukhtee da Mammaa da tun safiyar ranar muke tare da su a side ɗin mu, suka tirje wai sam sai dai Bappa  ya barni a nan, ai ko nan kowa yace ya barni shi ya tafi bayan wani lokaci sai na koma.
ni dai dariya kawai nake binsu da shi, sai dai zuwa yanzu jikina yayi sanyi ganin yan da Ukhtee take kuka.
bilhakki ta rungume Nasmah tana faɗin bazan tafi ba.
Bappa ko ido yake binsu da shi cike da mamakin ganin zunzurutun kauna gun waɗan nan larabawan.
ana cikin haka kiran Mahmoud ya shigo wayar Bapp.
nan yake sanar wa Bappa yasami masaniya daga shugaban kasar mu anfara duk ayyukan dana lissafa kuma bazai ɗau wani lokaci ba insha Allah za'a gama,
Bappa yayi fatan alheri kana yakashe wayar.
koda naji labarin daga bakin Bappa nayi matukar mamaki dan ni har yau ganin abun nake kamar wasa bazai yiwu ba.
Bappa ya mai da hankalin sa kan mutanen da suke cikin parlour'n, abun da ya lura shine suna matukar son ba'i musamman wata kabilar, bugu da kari wan da Allah ya ɗaukaka a cikin su, babu garin da zai waye wasu daga wasu unguwanni daban-daban wasu kuma daga ɗan garuruwan dake gefen gari basu shigo ganina ba, na zamo abun kallo da hira a gurin su, haka zasuyi ta hotuna da ni da su Naseem.
numfashi Bappa ya sauke ganin gabaki ɗayan su kalma guda suke nanatawa..
dun dole Bappa ya amsa musu badun yaso ba da sharaɗin zasu sako ni a jirgi nan da ɗan kwanaki kaɗan.
ai kuwa ihun murna Ukhtee ta sake ta rungume ni tana sunbata. gaba ki ɗaya parlour'n yakaceme da murna...
washegari da misalin karfe 4 na asuba jirgin su Bappa ya ɗaga suwa kasar mu ta gado wato Nigeria★.
kafin ya tafi sai da yayi ta min nasihohi da jan hankali mai ratsa jiki..
tun da Bappa ya koma kusan kullum sai munyi waya ta wayar Ukhtee har da su Inna wuro.
Alhmdllh bazan ce komai ba game da zamata anan cikin masarautar Saudi batun samin kula da tarairaya ni da ƴaƴana kuwa ba'a magana...

A can kasar Nigeria cikin garin Bauchi state.

Na'ima ce da kawar ta Raliya,tafe cikin mota suka ɗau hanyar wani asibiti dake nan cikin G.R.A wan da shine Na'imar ke zuwa awo.
Raliya ke jan motar Na'ima na zaune a gefen mai zaman banza.
Raliya ta ɗan muskuta ta dubi kawar tata kana ta mai da idanun ta kan titi tare da faɗin
"Aminiya yanzu yanda kika tsaran nan kina ganin hakan zai yuwu kuwa baza'a sami wata matsala ba dai ko?".
Na'ima tasauke numfashi tare da gyara zaman ta cikin karfafawa da gaskata muradin ta tace
"Kada ki damu aminiya Nice fa Na'ima baza'a sami wata matsala ba tabbas zai yiwu zai yiwu, yau ɗin nan kuwa zan haihu, Raliya ina cikin haɗari dole ne kawai na ai watar da hakan, kinsan kuwa jiya da daddare muna kwance da SALEEM yaɗaga rigata yana duban cikin yace shi har yanzu baya ganin garman cikin ciki wata 7 amma har yanzu bai taso ba,
kin san me yafi firgitani kuwa?".
tayi tambayar tana duban Raliya.
Raliya ta girgiza kai cikin takai ci taci gaba da faɗin
"Aminiya sunan wancan ɓatacciyar yarin yar, ya kira min har da min misali da ita, wai lokacin da take da ciki bai cika wata huɗu bama amma yaɗan taso".
ido Raliya ta waro tace
"What! ya akayi har ya iya tunota? to gaskiya kawata kada kiyi wasa".
Na'ima cikin damuwa da bakin cikin tuno da HAMDAH da SALEEM yayi tace
"Shiyasa nake son bin duk wata kofar da zaibi ya tuno da wancan banzar ɓatacciyar da ko a muce ko a raye oho, duk wata kofar zanbi na toshe duk da nasan bayida wani kataɓus, ko da ya tuno tan ma, amma ni kwata-kwata bana son na rikajin kwatankwacin irin sunan ta a bakin sa,
bakiji abun da boka yace min ba, yana son yara sosai hakan zai iya yin tasiri wajen rika tuno ta da ita da abun da ke cikin ta duk da hakan ba wani abun damuwa bane amma ni dai sam bana son jin kalmar sunan ta kan laɓɓan sa,
to ko yau da safen nan ma muna kwance dashi yaɗaga rigata yana shafa cikin yace wai anya abun da ke cikin nan yana da lafiya kuwa shi baya ganin yana girma,
nace masa ai jikina yabi Allah ya taimaka ma ina da tumbi,ke nifa kullum a narka abinci nake aciki na in kika ga abincin da nake ci yanzu wai dun kawai tumbi na ya kara girma,
yanzu Raliya cikin nan wata 7 ne yana daf da shiga wata 8 yazama dole na ɗau mataki in ba hakaba komai zai iya ɓaci,
kin ga wancan hatsabibiyar kanwar tasa Rafee'at ranar da muka haɗu a gidan su har habai ci take min wai mai cikin tuwo, ni har na fara zargin ko ta gane ne".
Raliya ta saki dariya har tana dukan sitiyarin motar tana faɗin
"Ai wannan Rafee'at ɗin shegiyar gaske ce sai ana taka mata burki".

dai-dai nan suka isa get ɗin asibitin, hon Raliya tayi mai tsoron bakin get ɗin yawan gale musu get.

a gefe in da aka tanada dan ajiye motoci suka faka suka fito suka nufi cikin sibitin.
kofar wani office direct suka nufa tare da yin knocking,
daga cikin office ɗin aka basu izinin shigo wa.

wanda ke cikin office ɗin yana zaune cikin shigar likitoci yana ganin su ya washe baki tare da faɗin.
"A'a manyan kasa kune tafe?".
cikin fari da ido Raliya taja kujerar da ke fuskantar sa ta zauna tana faɗin.
"Kanana dai ai kune manyan kuna zaune AC na ratsa ku kuɗi na shiga yadda yakamata me yamuku saura?".
Na'ima ma kujerar taja tazauna kana suka shiga gaisawa,
suna ɗan taɓa hira da dariya sakanin su da kagan su kasan tabbas sunyiwa juna farin sani.
Dr Mukhtar Lawan abokin su Na'ima ne sosai abota ne na tun a makaranta duk kanin su gar tasan garne, duk wani iskanci da sheke ayar da sukayi lokacin suna makaran ta tare sukeyi, har kuma yanzu wani kullin tare suke tufke shi. acikin su shine kaɗai yaɗan maida hankali kan karatu har yake cin moriyar karatun da yanzu yake a matakin Dr, asibitin mallakin sa ne wan da mahaifinsa yagina masa bayan zamowar sa Dr.
duk hirar da suke Dr Mukhtar idanunsa a kan Raliya,yakafe kirjin ta da ido  wan da ɗinkin rigar jikin ta ya bayyanar da nonuwan ta kusan rabi a waje.
fiki-fiki yayi da ido cikin yanayin shiga tarkon Raliya yadubi Na'ima kana yace
"Na'ima kawarki Raliya takini fa taki na ganta kwata-kwata yanzu ko waya na kirata muɗan haɗu taki ta bani da ma mu haɗu, sabo da tasami manya wan da suka fimu bata hurɗa da mu".
yakarashe maganar da mai da idanunsa kan Raliya wacce tadaɗa bankaro kirji tana wani fari da ido.
dariya Na'ima tayi tace
"Kai haba aminiya ai ko ba komai dai zakizo wannan haɗaɗɗen office ɗin kiɗan rika ɗebe maba kewa."
fuska Raliya ta yamutsa cikin salon kwarewa a harkar bariki takuma bankaro kirji yayin da yatsarta guda ke saman wuyan ta tana ɗan yawo da shi  har zuwa kirjin ta, ta saman nonuwan ta,ido ta kanne a kansa kana tace.
"Dr kenan ku abun naku ai sai a hankali in ka shirya yanzu Na'ima ta wuce ta bamu guri amma yanzu zaka ajiye min rabin miliyan anan shima ɗin dai-dai azo sallama ne".
tanuna saman table ɗin gaban sa.
ido ya waro da karfi ya furta
"500k ai ko ai kina na wata guda bai kai rabin miliyon ba".
dariya duka suka saka.
Dr Mukhtar yace
"Ina kinji ko Na'ima kawar ki tafi karfi na sai dai mugani kawai mu latse baki, ko za'a ɗan taimaka min naɗan lallasa ne basai ciki ba iya waje kawai". yakarasher maganar da dariya haɗe da tsigar zolaya.
baki Raliya ta taɓe tana faɗin
"Yanzu dai muyi abun da yakawo mu, Dr muna da damuwa fa".
Na'ima ta karɓi zancen da faɗin
"Kwarai kuwa Dr akwai matsala".
yace "Wani damuwa kuma ai ni a tunani na yanzu bakuda wata sauran ragowar damuwa ke Na'ima da kike da SALEEM a hannun ki".
"A'a Dr gaskiya da saura nasame shi kam amma da saura  munaso mukuma samin shi sosai

yazamo nawan da gasken gaske".
zaman ta ta gyara da kyau ta daɗa fuskantar shi kana tace
"Dr yau nazo haihuwa".
ido yawaro yace
"Haihuwa kuma antaɓa haihuwar da ba ciki?". yafa da dariya
sai kuma yakuma sakin dariyar shakiyyanci
yace "To ai cikin naki baikai na haihuwa ba tukun".
wani goron numfashi ta sauke kana ta daɗa gyara zaman ta da kyau tace "Dr tunani na kenan ranar da cikin nan zaikai na haihuwa, ace ciki yayi wata tara yaya zanyi narasa yanda zanyi, rabon da naji wani abu yasani shiga damuwa irin haka na mance, Dr taya zanyi nasami ɗa kune manya aikin kune kunfimu sanin yadda za'ayi".
jakar hannunta ta aje gefe kana taɗaura hannayenta biyu kan teburin gaban su sannan tacigaba da faɗin.
"Ko nawa ne zan biya har idan nima bukatata zata biya".

Ɗan shiru yayi yayin da yake ɗan juyawa kan kujerar da yake kai, sannan yasauke numfashi kana yace
"Gaskiya wannan buka taki babbace a gaskiya yanzu samin ɗa a cikin asibitin nan da kamar wuya, yanzu an saka matakan tsaro iri-iri, kinsan kwanaki fa munyi ta shari'a da wasu mutane wan da mukayi musu canjen ɗa,munyi ta samin matsala dan ma allah ya rufa asiri,
amma mezai hana tun da kince kinason ɗan cikin gaggawa kije gidan marayu, gidan marayu yakamata kije, akwai wan da suka haifi ƴaƴa zaki iya samin wan da yau ma ta haifa ta yar aka samu aka kai shi gidan marayun,
to inaga kije ki ɗauka a can ɗin zaifi".
kai Raliya ta jinjina alamun gamsuwa da shawarin nasa tace
"Eh gaskiya hakan ma kawai za'ayi gidan marayun zamuje mu samo ɗan acan kagama babu wanda ya isa ya zarge mu, sukuma hukumar gidan marayun zamusan yadda zamuyi da su tun da akwai ƴaƴan banki".
Shiru Na'ima tayi yayin da ta zurma cikin tunani naɗan wani lokaci kana ta ce
"To shike nan amma kuna ganin baza'a sami wata matsala ba ko?, dan nifa bana so maganar tafita naso ace munyi shi anan sakanin mu basai ansako wasu ciki ba".
Dr Mukhtar yace "Ai samun ɗa a gidan marayu shine kawai mafita kuma rufin asiri, tun da jakar ku na cike da makullin kulle bakin wasu ai an gama,
idan mukace a nan ne zamu samu to za'a iya samin matsala dan har yanzu asibitin nan idon hukuma yana kansa sun saka ido sosai suna jiran suji wani abun yakuma fita su sami mafakar hujjojin da suka tara, wan da naki bada damar hujjar tasu tayi aiki idan da kuɗi meye bazamuyi ba".
ido Raliya ta kanne tace "Wai wan da kayiwa ai kin nan nawa ne yabaka haka?".
wani munafukar dariya yayi kana yace
"Miliyan 10 tabani kuma ko wani wata ina ɗaukar albashi daga gurin ta".
"Bayan 10 million tana kan baka wani kuɗin kuma?".
Na'ima tayi  maganar da fuskar mamaki.
yace "To ai kin wasa nayi mata kaɗan fa yarage yataɓa nawa aikin dan ma Dad yatsaya da

gaske kan lamarin, canjin ɗa ai bakaramin kasada bane, jigo na canza mata da shi ɗa na miji na musan ya mata da mace, to kuɗin wasa suke samu a kasar nan 10 million wani kuɗi ne agurin su,
duk wata 300k nake ɗau ka a gurin ta tukuicin godiya."
dariya suka sheke da shi cikin muryar dariya Na'ima tace
"Kai Mukhtar wlh bakada dama shine ko ɗan salalan nan babu."
"Haba wani salala ke me zakiyi da kuɗi yanzu kinada jakar kuɗi a gefen ki, kinada ABDALLAH IDRIS ABDALLAH me kuma zakiyi da kuɗi, ai nine abun a taimaka dan ko Raliya kuɗin da take samu bani samun irin sa".
mikewa Na'ima tayi tana faɗin
"Kace dai bazaka bamu ba kawai musan in da muka ajiye ka, aminiya tashi mutafi gidan marayun nan yanzu ba'a bori da sanyin jiki".

zai yi magana sai kuma yayi shiru sakamakon hayaniyar da yaji ke ɗan tashi daga can waje da alama a cikin parlou'n asibitin ne in da mutane ke zama dan jiran ganin likita.
wata nurse ce ta shigo bayan tayi knocking an bata izinin shigowa,
ɗan rusunawa tayi tace "Sir gawasu sun zo da alama haihuwa ce sai dai basuzo da kayan haihuwa ba, nace sukawo kuɗin kayan haihuwar sunce basuda kuɗi,nace to su koma suzo da kuɗi sunki tafiya, kuma yara ne dukan su nayi ta tuhumar su ina iyayen su sunyi shiru na ce suje su kira babba san nan su taho da kayan karɓar haihuwa ko kuɗin kayan tunda akwai anan sunki tafiya,kuma da alamu labour take sosai zata iya haihuwa cikin mintuna kalilan gasu can zaune a parlour sunki tafiya."
Dr yace "Yara kuma? akira su su shigo."
tace "Okay sir."
tajuya da sauri ta fita, jim kaɗan suka shigo,
tana gaba ƴammata biyu na biye da ita ɗaya da ciki rukuku ɗayar kuma tana tallafe da ita, sanye da uniform ajikin ta. da kaga mai cikin da alama nakuda take sosai dan sai tauna baki da yarfe hannu take tana ta faman zubda kwalla da faɗin "Wayyo nashiga uku."
Dr yadubi wacce suke tare da mai cikin yace
"Me yake faruwa wace matsalar ke tafe da ku?."
tace
"Haihuwa tazo shine na rako ta."
Na'ima da Raliya kuwa ido suka zubawa yaran wan da akalla shekarun su bazai wuce 16 ba.
Dr Mukhtar yace
"Ke kaɗai kika rakota haihuwar ina iyayen ku?".
shiru yarinyar tayi tana duban mai cikin da sai daɗa shiga yanayin nakuda gadan-gadan take.
sai kuma ta dubi likitan cikin rauni tace
"Iyayen ta suna gida nima kawai tazone tace narako ta asibiti."
ɗan shiru Dr mukhtar yayi idanunsa a kansu kana yace
"To ina mijin ki?." yayi maganar idanunsa akan mai cikin.
duk kanin su shiru sukayi sai raba ido suke, ido ya kure su da kyau yakuma faɗin "Nace ina mijin ta? ita kaɗai zata taho haihuwa babu wani babba ko shi mijin baisan haihuwar yataso bane kirashi a waya yanzu yazo dan bana karɓar haihuwa sai an ajiye kuɗi an kuma sa hannu tukun".

Cikin kame kame ƴarrakiyar tashiga faɗin
"Um..um mijin..ta..mijin ta."
sai kuma tayi shiru. duban mai labour ɗin yayi da kyau yace
"Kirawo mijin ki yanzu yazo kice masa bazamu karɓe kiba har sai yazo."
kasa tayi da kanta batare da tace komai ba sai hawayen da ke cigaba da sauka a idon ta, girgiza kai yayi kana yace
"Ba miji kenan wannan ciki ba uba baya da uba ko?".
da sauri ƴar rakiyar ta gyaɗa kai tana tsilli-tsilli da ido kamar an tare ɓera kana cikin in-ina tace
"Wlhy likita tsautsayi aka samu bata da miji, kuma yanzu iyayen ta sun kore ta da sukaga tana labour sun ce tafita musu a gida taje can ta haihu ba a gidan suba,
shine tazo gidan mu nikuma naga kamar zata mutu shine na rakota asibiti, dan Allah likita ka taimaka mata."
gaba ɗaya suka zuba musu ido. wani murmushi Raliya ta sake.
ido Na'ima ta bita da shi dan tasan ma'nar murmushin nan nata tace
"Aminiya sabon shiga harka ko?". baki Raliya ta taɓe tare da faɗin
"Oh yaro man kaza har yaushe zakayi sake irin haka ta kasance, ka ɗaukar wa kanka wahala shi ba mai uba ba wahalarka a banza, uban titi da bazai kalleka cikin halin labour yace ma sannu ba, tuni ban wanke shi na zubar ba in ma yasami shiga kenan mttss".
taja wani dogon tsaki tare da faɗin
"Kara mar ƴar iska bata san yan da zatayi iskancin bama."
Dr Mukhtar da Na'ima kasan cewar suna kusa ne suna juyo duk abun da take fata akasin su da suke tsaye a sakiyar office ɗin.
Dr Mukhtar yayi murmushi tare da faɗin
"Ko zaki sata a hanya ne idan ta sauke kayan dake jikin ta".
harara ta dalla masa tare da kuma jan wani gajeren tsaki.
Dr Mukhtar ya mai da duban sa kan yaran sannan yace
"To a gaskiya bazamu karɓi haihuwar ba, na ɗaya babu kuɗin karɓar haihuwa sannan babu wani babba a tare da ku, bazamu karmi haihuwar ba saboda gudun matsala, bugu da kari kuma ɗan bashi da uba,
muzo mu karɓi haihuwa wani abu ya faru azo a dakatar min da asibiti gaskiya yanzu na daina irin wannan kasadar gaskiya kuje kawai kuje wani asibitin."

Da sauri Na'ima da Raliya suka juyo a tare tare da yiwa junan su
kallon-kallo, sai kuma da sauri Na'ima ta juyo gun Dr tace
"Dr a taima musu a karɓi haihuwar ni zan biya kuɗin duk wani ɗawai niyar da za'ayi ni zan biya, zan kuma tsaya wajen ganin ba'a sami wata matsala ba, aje a kaita labour room."
kai Dr Mukhtar ya jinjina kana yace
"Okay." yadubi nurse ɗin yace
"Akai ta labour room.
tace "Okay sir." tajuya da sauri tana faɗin "Kubiyo ni."
suka fita dukan su mai labour'n da kawar tata.

suna fita da sauri Raliya ta dubi Na'ima zatayi magana Na'ima tayi saurin soma yiwa Dr mukhtar magana.
"Dr irin su ne idan suka haihu suke kashe ɗan, har idan akabar ta ta tafi bazataje wani asibitin ba wani gun zataje ta haihu ta kashe ɗan, ko kuma ta jefar da shi to ni ina son abun da zata hai fa har idan na miji ne."

Dr mukhtar yayi wani dariya tare da faɗin
"Ai tun ɗazu na fahimci hakan ai tun da naga kuna wannan kallon-kallon Na'ima Raliya bakuda kyau sai an haɗa da wanka, ai na san hali tun a makaranta har idan kukayi wannan kallon-kallon to wata tsiyar za'a kulla."
dariya suka sheke da shi suka tafa kana shima ya miko hannu suka tafa da shi dukan su.
zaman sa zagyar da kyau sannan yace
"To meye kaso na a ciki?."
Na'ima tace "Kana da kaso mai tsoka yanzu dai kaje ka bata kulawa ta haihu kuma kayi fatan namiji zata haifa, yau nima zan haihu."
yace "kwarai kuwa har an shiga dake labour room".
dariya suka saka dukan su.
Nan sukayi ta wasu magan ganun su sakanin su batare da ni naji ko fahimtar me suke nufi ba..

Bayan awa uku, kukan jariri ne ya soma tashi daga cikin labour room, Na'ima da Raliya da har yanzu suna zaune a office ɗin Dr Mukhtar suka wani saki murmushi, lokacin da sakon Dr Mukhtar yashigo wayar Raliya wato tex message yana sanar musu da abun da aka haifa, ciki murmushin mai kunshe da ma'anoni da dama Raliya tace
"Kai sannu Na'ima kin sauka lafiya kai gaskiya haihuwa akwai wuya kinsha fama yau."
itama wani dariya ta sake cikin kware wa a zunzurutun makirci da hatsabiban ci tace
"Na haihu yau ni Na'ima gaskiya haihuwa a kwai wuya".
darika suka kuma shekewa sukatafa.
Dr Mukhtar da yanzu shigowar sa office ɗin bayan ya amshi haihuwar, zama yayi kan kujerar sa yana faɗin
"Gaskiya yau ba sauki oga SALEEM ya haihu um wayaga oga SALEEM da ɗa abun ba sauki hhhhh".
"Shima yazama baba ni kuma mama".
Na'ima ta faɗa tana wani faɗi.
nurse ce tayi knocking tashigo taɗan dukar da kai tana faɗin
"Sir an gama kimsa komai sai dai har yanzu tana bledin, munyi iya kokarin mu bai tsaya ba ko zaka zo ka duba ta."
kai ya girgiza kana nurse ɗin ta fita da sauri,
a tare Na'ima da Raliya suka mike ganin Dr shima ya mike sukabi bayan sa.
dukan su suka shiga ɗakin da aka tanada domin haihuwa.
nan da nan yasoma baiwa yarin yar taimakon gaggawa ganin yan da jini ke fita a jikin ta, batare da ɓata lokaci ba tadawo cikin hayyacin ta ,jinin kuma ya tsaya.
jaririn da nurse's suka gyara shi suka kunshi cikin ɗankwalin mahaifiyar sa sai musu-musu da

kuka yake ga dukkan alama niman abinci yake,
nurse ta ɗago shi ta maso gaban gadon da mamarsa take, wan da a ƴan min tunan da ta sami kanta bayan Dr yabata taimakon da ya kamata har ta iya mikewa tazaune.
tamika mata shi tana faɗin
"Ga abun da kika haifa nan kuma da alama niman abinci yake gashi bakuzo da flas ba, bare a bashi ruwan zafi ya sha."
kin karbar sa tayi sai kukan da ta fashe da shi.
kawar ta da suka zo tare ita ta karɓi ɗan tashiga jijjiga shi, wayar ta dake cikin aljuhun wandon makarantar jikin ta  yasoma kara alamar shigowar kira,da sauri takai hannunta guda ta cusa cikin aljuhun wan donta,
 ɗaya hannun kuma ta gyara rukon jaririn da kyau ta zaro wayar.
 ido ta waro kan screen ɗin wayar murya cike da tsoro tace
"Mama." sai kuma da sauri taɗaga kiran takai wayar kunnen ta tare da yin sallama.
ɗan shiru tayi sai kuma tace
"Mama gani nan dawowa an tashi ne bansami abun hawa ba shine yasa na tsaya".
tana sauke wayar da sauri tadubi kawar tata tace
"Mama ce takira ni taga lokacin tashi yayi har yanzu ban koma gidaba, bayan ko makarantar ma banje ba,ni sai yanzu ma na ga agogo tun ɗazu lokacin tashi yayi, tofa zantafi gida yanzu yaya zamuyi ina tsoro kada Baba yadawo yasamu ban dawo ba,
kema zaki tafi gida ba kawai tun da yanzu kin haihu? muje na rakaki gidan ku nima sai na wuce gida,
karfa Mama tasa yayu na su biyo ni kin san fa in nakai wannan lokacin sawa take aje a nimo ni".
tana maganar ne cikin tsaro sosai.
itako mai jego kuka kawai take takasa cewa komai.

Dr yace "A'a taya za'ayi ta tafi yanzu bayan yanzu ta dawo hayyacin ta,sai mun daɗa ganin yanayin jikin nata kafin mu sallame ta, yanzu kam ma allurar da akai mata zai fara ai ki in tayi bacci ta farka mukaga yanayin karfin jikin ta sai mu sallame ta, yanzu dai ke kije tun da ke a na kiran ki."
to tace da sauri ta mika mata ɗan,
yanzu ma kin karɓar ɗan tayi.
Raliya ce ta karɓi ɗan a hannunta tace
"To kije kawai."
ai ko tafita da sauri.
bayan fitar ta Dr Mukhtar ya dubi yarinyar yace
ta kwanta ta sami bacci, a hankali ta gyara kwanciyar ta,su kuma suka fita suka koma, office ɗin sa.
suna zama Na'ima tace
"Bani ɗan na ganshi."
Raliya ta mika mata kyakkyawa fari kuwa da shi, sai dai yaron bashida girma ɗan kankani ne hakan kuwa bazai rasa nasaba da rashin samun kulawa da ya kamata tun aciki ba.
takafe shi da ido tana wani irin murmushi tana ɗan jijjiga yaron.

after 4 hr.
hakan kuwa yayi dai-dai da farkawar yarinyar da ta haihun a bacci, alhmdllh taji karfin jikin ta kwarai.
nan tanimi tafiya gida nurse tazo ta sanar wa Dr yace taje ta kira ta.
tare nurse ɗin suka shigo da yarin yar,ya nuna mata kujera ta zauna kana yacewa nurse ɗin taɗan basu guri, nan ta fita tajawo musu kofa.
duban yarinyar yayi kana ya ce
"Inane gidan ku".
cikin kame-kame tashiga faɗin
"Um..um..gidan mu gidan mu."
sai kuma tayi shiru.
da kyau yakuma duban ta sannan ya ce
"Bana son wani ɓoye-ɓoye nasan wannan ɗan bashi da uba cikin shege ne dan haka kawai tan bayar ki nake ki bani amsa inane gidan ku?."
kwalla ta matse tare da mutsutstsike yatsun ta kana ta soma magana,
"Gidan mu yana..yana Unguwar Bakaro".
kai ya jinjina yace
"A Bakaro kike?."
ta gyaɗa kai, Raliya ta jinjina kai kana ta ce
"Ah to shikuma uban ɗan a ina yake shima a Bakaron yake?".
tace Eh.
"To yan zun ina zakije keda ɗan idan kika fita daga nan?".
Raliya tayi mata tambayar tana dubam ta, shiru tayi tare da musutssuke yatsun hannunta.
Dr Mukhtar yaɗan tsura mata ido kana yace
"Yanzu ina zaki kai ɗan idan aka baki shi?."
kuka tafashe da shi tana faɗin
"Wlh idan na tafi da shi gida yan kani za'ayi wlh iyayena sun ce sai sun yanka ni yanzu ma in na koma gida nasan suka na za'ayi idan na tafi da shi zasu yanka ni".

kuka take sosai tana faɗin zasu yanka ta,
Na'ima kuwa carap tayi tace "To ni zan rike miki ɗan ni ina son shi nasan idan kika fita yaddashi zakiyi ko ba haka ba?".
tafaɗa tana duban ta.
da sauri yarin yar ta gyaɗa kai tace
"Wlh in natafi da shi gida ne za'a yanka ni in naje dashi gida ne."
Na'ima ta ce "To ya isa, in kika je da shi gida ne za'a yanka ki idan kika fita da shi daga nan kuma yaddashi zakiyi to ni ina son shi zan rike shi".
hannu ta saka ta buɗe jaka ta ciro kuɗi masu yawa gudan dubu-duba ne a ɗaɗɗaure ɗauri uku,wacce a kalla ko wani ɗauri guda yakai 100k ta mika wa yarin yar tana faɗin
"Karɓa in kinje kya nima abun da zaki rika ci wan da yakamata masu jego suci, ba sai kin jira iyayen ki sun yi miki ba tun da nasan cewa bayimiki zasuyi ba, da ma ace ɗan da uba ne tun da bashi da shi kuwa ba mai saurarar ki, gashi sai kije kiyi jego shikuma ɗan ina son shi zan rike shi, dan bazan iya zuba ido ina gani azalinci ɗan da baiji ba baigani ba ku mutane kurika jin

tsoron Allah, ɗan da bai san komai ba aje a jefar da shi ko a kashe shi."
da sauri yarin yar ta mika hannu ta karɓi kuɗin har hanunta na rawa ganin yawan kuɗin, kana ta yimusu godiya ta mike da sauri ta fita,
har takai bakin kofa Na'ima tace
"Idan kikaje gida aka tanbaye ki ina abun da kika haifa sai kice yana ina?."
"Ya mutu tun a ciki!."
tayi maganar cike da karfafawa tana daɗa dunkule makudan kuɗin da ta bata.
murmushi Na'ima tayi tare da faɗin "Da kyau." da sauri yarin yar tayi waje ta haye abun hawa ta wuce gidan su cikin zillumi da tsoro..
bayan fitar yarinyar Raliya da Dr Mukhtar suka tuntsire da dariya, cikin muryar dariya Dr Mukhtar yace
"Kin ji Na'ima har da ɗan guntun wa'azin ta wai ku mutane kurika jin tsoron Allah tun da kin samu a sama ai dole kijefo wa'azi ciki hhhhh."
"In da kuɗi meye bazan samu ba kai bakaji takashe ɗan nata tun a ciki ba, wannan kuma ni na haifa."
tayi maganar tana leko fuskar yaron da yake baccin sa.
Dr mukhtar ya gyara zama tare da sauke numfashi sannan ya ce
"To yan zu ya za'ayi ne?."
tace "Dr ni da na haihu kuma me yazaunar da ni a nan a kaini labour room mana."
dariya ya sheke dashi Raliya ma dariyar tayi tana faɗin
"Ai kuwa mai jego a gado yakamata a same ta a kwance ba'a zaune a office ɗin likita ba."
nan suka mike suka nufi labour room bayan sun gama shirya duk yan da abun zai tafi.
suna shiga ta haura gado ta kwanta, tayi shame-shame kamar wacce ta haihu da gaske.

Waya Na'ima ta mikawa Raliya tace
"Kirashi a waya".
Raliya ta amsa ta danna number SALEEM......!

Mommyn Twins ce

🌺 *HAMDAH* 🌺
*WASA FARIN GIRKI!!*✍🏻

*NA*
*RASHEEDA S DIRECTOR*

_(Book 3)_

Littafin na siyar wa ne ki biya ki karan ta.
domin biyan kuɗin littafin sai ka-ki tuntuɓi wannan number 08034690723

🅿️2

Wayar tayi ta ringing har ya yanke bai ɗaga ba, ta dubi Na'ima tace
"Bai ɗaga bafa. "
ta ce "Sake kiran shi kin san shi ai murɗaɗɗen mutum ne idan baiyi ra'ayi ba bazai ɗaga ba yanzu haka wayar tana kusa da shi ɗagawar ne dai baiga dama ba."
kuma kiran nasa tayi namma har ya yanke bai ɗaga ba, sai da ta kirashi har sau uku a na huɗu ne ya ɗaga.
ganin ya ɗaga kiran takai wayar kunnen ta tare da faɗin
"Asslamu'alaikum SALEEMA Raliya ce muna asibiti da Na'ima tahaihu."
SALEEM dake zaune a office yana ta tarkasa ƴan kayakin sa dan locin tashin sa yayi har ya wuce ma, ƴan wasu aiyuka ne suka tsaida shi. yamike zumbur yana faɗin.
"Haihuwa kuma? yaushe cikin nata yakai na haihuwa cikin ya fita kenan?."
yajero tanbayar da alamun hankalin sa a ɗan tashe yake.
ta ce "Eh haihuwa ce ba fita cikin yayi ba sai dai bakwaini ta haifa ɗa na miji."
numfashi yasauke jin akasin abun da yake zato,shi gaba ɗaya jin lamarin na bazata ya mantar

da shi zata iya haifar cikin tun da yakai wata bakwai, ya ce
"Ina jaririn yake yanzu yana cikin wani hali yana dai lafiya ko?."
"Eh gashi can a cikin kwalba."
katse wayar yayi batare da yace komai ba, Na'ima da take jin duk abun da yake faɗa kasan cewar tasa wayar a amsa kuwa ne ta ce
"Lallai ma wannan wato shi ta jaririn yake bazai fa taɓa sauyawa duka ba."
dariya Raliya tayi tare da faɗin
"SALEEMA kenan miskili kafi mahaukaci ban haushi bafa zai sauya ba dan kuwa a jinin sa yake."

SALEEM na kashe wayar, wayar Mamie ya kira, zaune Mamie take da su Aunty Rafee'at Aunty Jaleela da su Ummi kiran sa ya shigo.
bayan sun gaisa yake faɗa mata Na'ima ta haihu.
"Haihuwa." Mamie tafada da karfi
kana ta ce "Wani irin haihuwa ciki wata bakwai." ya fuskanci yanayin da yashi ga lokacin da Raliya ta sanar masa da haihuwar shi Mamie ta shiga yanzu.
yace "Eh ta haihu bakwaini ta haifa tana asibiti ma yanzu."
"To Allah ya raya." Mamie ta faɗa a takaice tare da kashe wayarta.
gaba daya hankalin ƴan cikin parlour'n yakoma kan Mamie, Ummi ce da sauri tace
"Wa ta haihu Na'ima ce?".
Mamie tace
"Wai haka, wai ta haihu". Mamie ta faɗa tana taɓe baki.
Ummi ko baki ta washe tana fadin
"Ikon Allah, kaji ikon Allah ko to Allah dai yasa abun da aka haifa nacikin koshin lafiya".
baki Mamie takuma taɓewa tare da faɗin
"Ina kuwa zai zama cikin koshin lafiya ciki wata bakwai sai dai yabada wahala dai".
a ɓangaren Aunty Jaleela ma fuska ta yamutsa tana faɗin
"Gayyan wahala dai ciki wata bakwai ai ba arziki."
"Ina kuwa arziki duk uban iyayi da cikin ashe dai rabin halitta za'a haifo ba arziki."
Aunty Rafee'at ta faɗa, tana tura ɗankwali gaban goshi.
duk kanin su in ka gansu babu wani mai farin ciki da jin daɗin haihuwar, akasin Ummi da fuskarta ke ɗauke da annuri bakin ta ya kasa rufuwa sai faɗi take
"Kai masha Allah Allah dai ya raya mana."

mikewa Ummi tayi tana cigaba da faɗin
"Kai masha Allah zamu wuce asibitin ba yakamata mu tafi asibitin yanzu".
Mamie ta kawar da kai gefe tare da faɗin
"Ummi'n Fauzan ni gaskiya ba yanzu zanje asibitin nan ba gaskiya inaga kamar ina da abun yi, ai dare yayi yanzu ga magriba yakawo kai."
Ummi ta girgiza kai tana faɗin
"Kai Mamie'n Nusaiba yakama ta dai muje yanzu ace babu wani nashi a can gaskiya baiyi ba."
fuska Aunty Rafee'at takuma yamutsawa tana faɗin "Um ni kamma kucire ni a tafiyar dan yanzu Abba'n Adeel zaizo ya ɗauke mu."

dakuwa Ummi tayi mata tare da faɗin
"Maza tashi kushirya ke Jaleela tashi maza muje".
Aunty Jaleela da tazo har wuya ta kwaɓe fuska kana tace
"Ni wlh ina ji ma kamar kar inje dan nima Daddy'n Fadeel nasan zai zo yanzu."
haɓa Ummi ta rike tana sallallami da kyar dai ta tirsasa musu ta samu suka fita, suka nufi asibitin bayan sun sanar wa su Abbu.

A asibitin suka tadda SALEEM shima isowarsa kenan a tare suka shiga cikin asibitin.
direct ɗakin hutu suka nufa in da nurse tayi musu jagora zuwa ciki,take sanar musu da cewa an mai da Na'ima can domin ta huta.
nan suka tadda Na'ima kwance tana ta sauke numfarfashi Raliya na tsaye a kanta tana ta yi mata sannu.
da sauri Ummi ta matso in da take tana faɗin
"Sannu sannu kinji Na'ima, kin sami kanki kalau?".
dakyar ta buɗe baki cikin yanayin mutum yasha wuya murya can kasan makoshi tace
"Lafiya lau."
Mamie ko kallo ɗaya tayi mata kana tace mata Sannu.
namma da kai ta amsa.
Aunty Rafee'at kam ko kallo bata ishe taba, Aunty Jaleela ce ma a sama tace mata sannu ita ma.
Ya SALEEM da ya naɗe hannu a baya yana tsaye tagurin kafafun ta yadan dubeta kana yace "Ina yaron yake?". Raliya tace "Yana can ansashi a kwalba.
kai ya jinjina cikin yanayin nan nasa, ya maida duban sa kan nurse ɗin da ta yimisu jagora yace "Muje a nuna mana in da yake, ina Dr yake?".
ta ce "Yana office".
fita sukayi duka har da Raliya,
Raliya tayi saurin shigan office ɗin Dr tare suka fito da shi, ya mikawa Ya SALEEM hannu suka gaisa ba yabo ba fallasa Ya SALEEM ya amsa masa gaisuwar, kana ya gaida su Mamie sannan ya wuce dasu ɗakin da aka ajiye jaririn wan da yake karkashin kulawar na'urori..

Can suka hango jaririn cikin kwalba
wan da ake saka jariran dabasu kai watannin haihuwa ba, yanata wutsul-wutsul da kafafunsa.
murmushi Raliya tayi a kasan ranta dan ganin shirin su yana tafiya yan da ya kamata.
da sauri Ya SALEEM ya karasa jikin kwalbar yana leka cikin kwalbar.
su Ummi ma gaba ɗayan su suka karaso jikin kwalbar,
Ido Mamie ta kurawa jarijin da ake kiran sa da bakwaini gashi dai ba wani girma yake da shi ba ɗan kankani ne, sai dai yanayin sa da wayon faskarsa ya girmi na bakwaini.
kai ta girgiza tare da juyawa ta kalli likitar tace
"Wannan shine bakwaini an ya ma kuwa anyi lissafin cikin nan dai dai ko dai tara ne an ɓata lissafin kaga yaron da wayon sa."
da sauri Raliya tace
"Bai cika tara ba bakwai ne ai ko jiya ma sai da mukayi lissafin watannin da ita, yau kuma sai ga haihuwa kingan shi ai ɗan misilili da shi".

Ummi tace "Ai kuwa gashi ɗan kankani irin su idan suka tashi girma sai an gansu dan sai anci tuwo an koshi kafin a iya ɗaukar su".
Ya SALEEM kam duk baya jin su dan ya gama shagalta da kallon yaron wai shine yau da ɗa, wannan ɗan nasa ne, wani murmushi yayi a kasan ransa wan da har sai da yabayyano kan fuskarsa.

Aunty Rafee'at data kafe yaron da ido tarr sai lokacin tayi magana.
"Wai wannan yaron shine bakwaini gaskiya wannan baiyi kamada bakwaini ba sai dai in ku kuka ɓata da lissafin".
tayi maganar cikin gatsali.
wani kallon sama da kasa Raliya ta bita da shi. Aunty Rafee'at ma irin kallon ta wasa mata tare da girgiza kai tana cigaba da yi mata wani kallon shekeke, sannan ta juya ta fita a cikin ɗakin bayan ta gama ai kawa Raliya kallo masu cike da ma'anoni da yawa..
ko minti 30 basuyi a asibitin ba Mamie tace sutafi, haka dai suka fita suka koma gida.

Haushi da bakin ciki kamar Na'ima tayi yaya, wai ace kalar gaisuwar da surukar ta zata yi mata kenan, babu wani gaisuwa mai nuna tausaya wa babu wani nuna farin cikin samo mata jika da tayi.
Raliya tace "Ni da ɗina da ke gajen hakuri dan Allah kibar wannan maganar kiyi shiru, ke kam dai ba kin haihu ba ina ruwan ki da su, wan da kika haifa masa ne idan ya miki zakiji zafi,ina ruwan ki da su ba wa ɗan su kika haifa ba, can ta matse musu ke meye damuwar ki, kinga wannan shegiyar yarinyar
zan nuna mata ni ƴar bariki ce cikakkiya ma kuwa ciki da waje na,
wai shegiyar Rafee'at ɗinnan kinga wani kallon da take min,
kinga wani kallon da take min kuwa, zan nuna mata halina bata sanni bane."
Na'ima tace "Him in dai wannan Rafee'at ɗin ce ta wuce sammanin ki, wannan yarin yar da kike gani nima inada cikin ta kuma zanyi maganin ta, zan je musamman gurin boka domin yamin maganin ta,
zatagane da ni take rabu da ita mance da ita dan wlh sai ta gane kuskuren ta."

Jin an murɗa handle yasasu yin shiru da zancen nasu,
Na'ima ta gyara kwanciyar ta kamar ɗazu, ta daɗa marairace fuska da shagwaɓe fuska.
ya karaso bakin gadon yadube ta kana yace
"Ya jikin?". cikin makirci da salon iya kirsa tace
"My SALEEM kaga ɗan mu ko,ya bani wahala yaron nan,
ɗan ka yabani wahala My SALEEM da kyar na iya haifo shi."
gefen fuskarsa ya shafo tare da naɗe hannun sa ɗaya a bayan sa,
"Ɗa na."
yafaɗa a kasan zuciyar sa yayin da yake jin wani abu yana tsarga masa mai kama da farin ciki, can karkashin kasan zuciyar sa kuwa, jin wani abu mai nauyi yake yana kokarin tasowa sai kuma yanayi biyun suka shiga kokawa da junan su, yayin da farin cikin ya danne wancan nauyin da yake jin nauyin sa na yau yafi na kullum. har sai da yakai hannu ya dafe kahon zuciyar sa.

daga Na'ima har Raliya ido suka zuba masa ganin yan da ya dafe kirjin sa da karfi tare da rumtse idanunsa,
wani abu ne ya gilma masa cikin duhuwar kwayar idanunsa da suke a rufe, wani irin bugawa kirjin sa yayi kamar an fizgi zuciyar sa, sai yarika ganin wasu abubuwa guda uku masu haske suna yi masa yawo cikin ido yayin da bugun zuciyarsa ya tsanan ta, dai-dai lokacin da yaga abun suna daɗa tunkaro sa tamkar suna tahowa gare sa,
a zahiri kuma idanunsa a buɗe. sai kuma a sannu suka rika yin nesa dashi sai da sukayi nesa dashi sosai kana duhu takuma gilmawa sakanin su.
cikin tsananin karfi ya ware idanun sa, jin muryar Na'ima tana faɗin
"Ya dai My SALEEM?".
hannayen sa biyu ya cusa cikin sumar kansa kana ya burzar da wani huci mai zafi daga bakin sa
"I'm sorry."
ya faɗa tare da juyawa yabar ɗakin da sauri, yayin da yake jin zuciyar sa naciga da yi masa nauyi, acikin ƴan kwanakin nan hakan yana yawan faruwa da shi akai-akai, musamman in ya kwanta bacci yarika irin wannan mafarkan kenan, sai yari ganin haske guda uku suna dumfaro shi sai sunzo daf da shi sai su bashi baya yayin da duhu kuma zatazo ta mamaye hasken. abun da yake gani cikin mafarkin sa shi ke kokarin zuwa masa a zahiri, to ko bacci yafara a tsayen har ya fara mafarkin?.
yarika jefowa kansa tambayoyin da bashida amsar su..

Bayan sa Na'ima tabi da kallo cikin takai ci, a tunanin ta ɓarin jiki zaiyi idan yaji ta haihu, idan yaga ɗan kuma murna zai yi ba adadi, sai kuma gashi sai wani shashshan kamshi yake,batare da ya nuna farin ciki da hakan ba.

A can kuwa bayan komawar su Mamie suna tare a parlour kowa na faɗan albarkacin bakin sa. Mamie kam sam taji wannan ɗa bai kwanta mata a rai ba,
kwata-kwata taji ɗan baya cikin ranta, tana yi masa wani irin kallon da ita kaɗai tasan ma'anar sa.
Aunty Rafee'at fuska ta yamusa ganin su Fauzan da Nusaiba na ta murna wai matar Ya SALEEM ta haihu zasu sha suna tace
"Dalla kurufa mana baki, ni wallahi wannan ɗan ma kwata-kwata bai min ba wlh ya ɗauko jinin uwar sa, ni bai min kama da bakwai niba haka bakwaini yake,sau nawa nake ganin ƴaƴan da ake haifarsu wata bakwai sai ace wai wannan ɗan wata bakwai ne, to can ta matse mata sai taje ta ta fama taje can tayi ta haifar bakwaini ita ta sani".
kai Mamie ta girgiza.
Aunty Jaleela tace
"Ai wlh nima Aunty Rafee'at ɗan baimin kama da ɗan bakwai ba, sai dai idan ko sun ɓata lissafi ko kuma wani munafurcin ta ke kullawa ciki yafi wata bakwai tace bakwai to meye amfanin hakan, meye na cewa ciki wata bakwai bayan tasan cikin yafi bakwai ɗin".
Ummi ko cemusu tayi
"To ku in ban da abun ku ta yiwu ta ɓata da lissafin ne in mutum ya ɓata da lissafi kam shi zai rika lissafi kuma alhalin ba haka bane, ai ba wani abu bane kakan iya ɓata da lissafi, kuma ai

ana iya haifar wata bakwai yayi rai me lafiya ma yatashi har yafi ɗan wata taran kwari da kuzari, kar ku mance fa a asibiti ta haihu in ba bakwai ba taya za'ayi a sashi a kwalba likitan ai yafiku sanin me yake, Allah dai ya rayashi da imani".
"To amin".
cewar su dakaji amin ɗin kasan baikai can kasar zuci ba...

Bayan kwana uku
tun da sukaje sau ɗaya basu kara zuwa ba sai ranar da ta cika kwana uku shima da kyar Ummi tasa Mamie suka koma asibitin, anan suka tadda ƴan gidan su Na'ima, nan ma basu wani jima ba suka baro asibitin.
satin su Na'ima biyu a asibitin, zaune suke da kawar ta Raliya Na'ima ta dubeta tana faɗin
"Kai Raliya wlh nagaji da zaman asibitin nan haka,
wai shin dole ne sai mun yi wata biyu a asibitin nan, dole wai saimunyi wata biyu wlh nagaji da zaman asibitin nan, wai dole ne har sai ɗan yacika wata tara kafin mu koma gida, gaskiya asan yan da za'ayi kije ki sami Dr asan yan da za'ayi gaskiya, wlh nagaji da zaman asibitin sati fiyu fa ina nan,gaskiya kije ki same shi asan yan da za'ayi nakoma gida."
Raliya tace
"Gaskiya nimafa nagaji da sintirin yau asibiti gobe asibitin nan,kullum kenan mutum na hanyar zuwa asibiti alhalin duk kanin ku lafiyar ku lau, jariri yana nan yana shan madarar sa ke kina nan kina narkar abincin ki,
nikam mafa inada wasu a hannu wlh ina da wan da na karɓi kuɗin su, akwai wan da na karɓi kuɗin sa na kwana uku gashi nan ko wuni ɗaya bamuyi da shi ba, sakanina da shi da daddare mu kwana  shi da yaso muje Abuja muɗan shana,
gaskiya bari naje na samu Mukhtar asan yanda za'ayi ki koma gida, nasamu naje su fanshi kuɗin su".
ta karashe maganar tana mikewa tsaye ta fita ta nufu office ɗin Dr.

Bayan Raliya sun gama tattaunawa da Dr Mukhtar yace
"To gaskiya akwai yadda za'ayi zata iya komawa gida abisa ita ta tirsasa tagaji da zaman Asibitin, nikuma sai na bada wasu shawarwarin da zata ɗauru akai bayan ta koma gidan".
nan suka tsara yan da abun zai tafi.
a ranar da yamma suka sami sallama suka koma gida, bayan shariɗoɗi da shawarwarin da Dr ya bata a gaban ƴan uwan ta da kuma gogan wato SALEEM.

Tun da suka koma gida yaron kullum a kwance yake idan akazo barka ma sai tace ba'a ɗau kar sa sabo da likita yace, kada a rika yawan sa masa hannu, sai dai azo a ganshi a kwancen kawai  acikin bargon da kullum yake dukunkune a ciki.
haka tayi ta rainon ɗan da masu da ita da ɗan ma'aikatan ta da kuma ƴan uwan ta, koda waɗan da suke kanta sukaga nonon ta ba ruwa basu kawo komai ba sai cewa sukayi ai dama gaka wasu matan suke sai an nimi magani.
tuni aka nemo maganin wanke nono da ku ma ruwan nono, kan kace me ruwan nono yakawo tashiga shayar da ɗa.

lokacin da suka cika wata biyu,wato ɗan yacika wata tara kenan washegari tahaɗa wani gagarumin taro.
biki irin na masu ji da naira, biki akayi na gani na faɗa naira tayi kuka, ranar SALEEM katuwar saniya ya yanka da katon rago,
yaron yaci sunan baban Na'ima.
ko da taji sunan da ya raɗa masa sam bata so ba dan taso yayi wa babansa ne takwara.
yace mata shi halacci yayi mata yasa wa ɗan sunan mahaifin ta.
ranar kuwa kaɗan ya rage Raliya suyi faɗa da Aunty Rafee'at kan cewa da Aunty Rafee'at tayi yaron ma ko kama da su baiyi ba duk da kuwa girman da yake ta karawa,amma ko alamar kama da su bayayi sai dai in ya ɗauko zuriyar uwar sa dan ko kama da uwar tasa ma baiyi ba.
shike nan kawai suka kama zasuyi faɗa, wai akan me yasa Aunty Rafee'at zatace haka ai duk wan da yaga ɗan yaga SALEEM, dan kuwa farin SALEEM ɗin ma ya ɗauko tun da kuwa yayi kama da uban sa ai ba sai yayi kama da dangin uban sa ba. cikin masifa da bala'i da tsagwaran bariki Raliya take maganar.
Aunty Rafee'at ma kuwa bata yi mata da sauki ba tayi mata wankin babban bargo.
Allah ma ya taimaka Ummi tazo sunan ita ta raba faɗar. ta kora Aunty Rafee'at da Aunty Jaleela tace duk su tafi an yafe musu sunan, dan ganin abun na daɗa girma dan har Aunty Jaleela tashiga faɗar....

After 1 year

Acan kasar Saudi

Da sauri na fito daga cikin bedroom cikin hanzari jin kiran da Ukhtee take kwaɗa min, abakin kofa mukayi kiciɓus da ita, fuska na kwaɓe ganin tana yi min dariya
"Ni gaba ɗaya kin firgita ni na ɗauka wani abun ne".
nayi maganar cikin harshen larabcin da nake ɗan tsinta a gurin ta.
murmushi tayi tare da ruko hannuna
tace "Zo ki gani ga ɗan'uwan ki yazo shi yace nayi mishi magana da ke".
tayi maganar ne cikin yaren ta da kuma yanayin da zan fahimta, dan yanzu ba laifi nakan fahimci abun da ake faɗa da larafci har nakan iya ɗan gwamusa wa wajen yin magana da bashi da tsawo mafi sauki.
ta janyo ni muka nufi parlour.
turus nayi ganin wan da yake zaune a parlour'n su Naseem da Nasmah sun zagaye shi sai zuba masa surutu suke.
sai kuma nayi murmushi tare da karasowa cikin parlou'n ina faɗin
"La Uncle Mahmoud kai ne yaushe ka zo?".
dan yanzu kunyar kirashi da sunan sa nake.
shima murmushin yayi yana faɗin
"Ban jima da isowa ba,Naseem yace min kina bacci da zaije ya taso kine nace a'a yabar hajiya

ta huta".
baki nawashe ina zama kan kujera jin abun da ya faɗa
nace "Uncle Mahmoud kenan wai hajiya, hajiya kuma".
yace "Eh mana hajiya kai, taya za'a taso hajiya a bacci lokacin tashin ta baiyi ba ai dai gara abar hajiya tayi bacci da kyau da kyau".
dariya kawai nayi kana nace
"Sannu da zuwa ya hanya? yasu Bappa da Inna wuro da Fatu".
yace "Hanya lafiya lau, sai dai badaga gida nake ba, amma dai Duk suna Lafiya".
Naseem da Nasmah suka mike a jikin sa sukabi bayan Ukhtee aguje sukayi side ɗin Mammaa.
janyo table ɗin da ya ɗaura system ɗin sa a kai yayi, yajuyo shi ta gabana yana faɗin
"To hajiya komai fa ya kammala, shiya sa ma na dako musamman tun daga Nigeria zuwa nan na sarnar miki ki kuma ganewa idonki, ba sai an kira ki a waya an sanar miki ba."

Ido na kurawa system ɗin, ganin bidiyoyi sunata bayyana cikin system ɗin, masu ɗauke da tamfasa-tamfasan gidaje wane a turai motoci gidajen mai masallatai makarantu haɗe da kamfanoni da dai sauran su.
cikin tsananin mamaki na dubeshi nace
"Wannan fa Uncle Mahmoud?".
nayi tambayar ina nuna cikin system ɗi. yace "Ah ai kin ki ya kammala wakilci a ka naɗa ni domin a kawo miki kiganewa idon ki musamman nataso domin shi".
da ɗin bin mamaki nakuma kallon hotunan dake bayyana kan system ɗin kana na maida dubana gareshi nace
"Waɗan nan ɗin?."
yace "Kwarai kuwa sune,nakine sun kammala yanzu ke kawai muke jira ki koma abubbuɗe su, sannan kuma ba a gari ɗaya akayi su ba a state da dama ne nacikin kasar mu Nigeria, ga jerin sunayin garirruwan da akayi gine ginen a cikin sa".
ya daddanna system ɗin,sai ga sunayen garuruwan sun bayyana da kuma abubuwan da akayi a kowa ni garin.
yace "Kin ga yanzu zaki koma Nigeria a dai-dai dan kullum sai Bappa yayi maga, yanzu ma yace mu dawo tare sai dai ni bagida zan koma ba zan wuce Uganda tare da abokan aiki na, akwai wani abun da zamuje muyi a can".
kai na jinjina dan nifa har yau ganin abun nake kamar wasa nace
"Him..Him.."
kasa magana ma kawai nayi sai Him. nake ta faɗa ina kallon ikon Allah,yayin da nakeyi wa Ubangiji buwayi gagara misali tasbihi a can kasar zuciya ta.
rufe system ɗin yayi kana yace
"Kin ga abubuwa yan da suka kammala ko, ko mai masha Allah, yanzu wani suna kike ganin za a sakawa kamfanoni da gidajen mai dai duk sauran kaddarori, wani suna kike ganin ya dace a saka musu, domin idan akaje yin katin gayyata da sanarwa ayi amfani da wannan sunan, da zai zamo shine sunan duka kaddarorin".
Shiru nayi yayin da na saka yatsa na guda kan kuma tuna nayi sama da ido na alamun tafiya duniyar tunani, tare da ɗan kyafkyafta idon.
kana nayi kasa da idon cikin washe baki nace

"Yauwa na tuno sunan da nake so a saka masa *HAM'NAS*".
nayi kaganar cikin zakuwa ina cigaba da washe baki.
yanayin yadda nake maganar sai da ya bashi dariya ya ce
"To meye ma'anar *HAM'NAS* ɗin kuma".
fuskata narufe da tafin hannuna cikin muryar dariya haɗe da zakuwar jin yadda na haɗa kalmomin suka tafi normal nace
"Kaga ma anar sa, HAM sunana ma'ana HAMDAH, NAS kuma Naseem and Nasmah".
dariya sosai ya sake yana faɗin
"Kaga yarin ya mai basira, tabbas wannan suna yayi kuwa ba shakka *HAM'NAS* Co Fitroleum Nigeria Limited *HAM'NAS* Intranational School Of Science And Technology *HAM'NAS* Store Complex *HAM'NAS* Clinics *HAM'NAS* International Hospital, Eh ba shakka lallai sunan yayi *HAM'NAS* Allah ya taimaka yayi jagora".
tsabar zakuwa kasa kuma  cewa komai nayi sai baki na da yakasa rufuwa..★
A ranar da yamma Mahmoud ya wuce Uganda........★

Mommyn Twins ce

HMD

🅿️3

Yau juma'a babban rana, ranar da duk kanin al'ummar musulmi suke farin cikin zuwan sa, al'ummar Annabi suna ta kai komo hada-hada da shirye-shiryen tafiya masallaci domin sallar juma'a.
da sauri Ummi tafito daga cikin bedroom ɗinta sanye da mayafi akanta, fuskarta ɗauke da yelwataccen annuri, da ka ganta kasan tana cikin matsanancin farin ciki. da sauri ta nufo bakin kofa,
lokacin Fauzan yasako kansa da gudu kaɗan yarage yayi karo da Ummi,
Ummi ta ce "Kai Fauzan bazaka rika yin abu cikin nutsuwa ba ko."
baki ya washe yana waigen bayan sa da faɗin
"Yau wa Ummi direba yadawo daga masallacin nace masa yafito da mota zai kai ki unguwa."
yana maganar yana waigen bayan sa yana wurga hannu alamun zakuwa, sarai Ummi tagane shi so yake ya bita dan tun kan afita a sallah yake fita dubo direba ko yadawo, dan ko masallacin shi baije ba dan ko da tace masa yaje masallaci cewa yayi wai shi a gida yau zaiyi sallah.
fita Ummi tayi tana faɗin
"To naji."
bayan ta yabi da sauri yana faɗin
"Ummi nima zan biki Ummi dan Allah kije dani kin ga wancan Juma'ar da ɗayan wancan juma'ar bakije da ni ba, akwai bashin tafiya unguwa biyu da bake je da ni ba."
"Tafican da alla kai ko ina za'aje sai an je da kai kai mata ne, da Nusaiba zamuje kai sai ka jira idan Abba ko Abbu'n ku suka dawo sai kayi musu rakiyar."
kafa yashi bubbugawa yana biye da ita a baya tare da faɗin
"Ummi nikam dai kije dani ina ranar da Nusaiba kuka je."
suna isowa tsakar gidan Mamie da Nusaiba suna fitowa,
dagudu Fauzan yaje in da suke yaruko hannun Nusaiba da take gyara mayafin ta da ta fito dashi rike a hannu tsabar sauri, jan ta yayi kusa da Mamie yana faɗin
"Allah yau bazaki je ba dani za a je Mamie rike min ita kar ki sake ta sai nashi mota mun tafi."
Mamie tace To cikin muryar dariya ganin yan da ya janyota tana torjewa kamar masu kokawa,
Ai ko Mamie na rike ta yajuya a guje yayi gun mota yana dariya da faɗin
"Yarinya yau badake za a je ba agida zaki zauna."
kukan shagwaɓa tasake tana jan hannunta dake rike a hannun Mamie tana faɗin
"Ai wlh dani Ummi zata tafi da kai namace ce sai ka rika bin mata unguwa, Mamie sake ni kuma sai na maka duka."
yana isa jikin motar ta zille a hannun Mamie tarufa a guje suka kama rige-rigen shiga mota. tana faɗin
"Da kai mace ce kuma ai Ummi tace dani zata rika zuwa unguwa."
"Allah baki isa ba yaukam dani za a tafi ai sau uku ana tafiya dake unguwa ni ba a tafiya da ni sai naje."
yayi maganar yana shigewa cikin motar a guje, itama shigewa tayi ta ɗaya barin tana cewa
"Bazan taɓa zama a gida ba sai dai kai ka zauna."
Ummi kam baki ta rike tace

"Oh yaran nan sai shegen son yawo duk in da mutum zai je sai kun bishi kamar jakka."
dariya Mamie tabisu da shi.
da sauri direba yafito yabuɗe wa Ummi kofa tashiga, da sauri Nusaiba ta dawo gefen ta yazamo sun sata a tsakiya.
sunata yiwa junan su gwalo direba yaja motar suka fita bayan Mamie tayi musu a dawo lafy.

koda suka haura titi direba ya juyo ya dubi Ummi yace
"Hajiya ina zamu fara zuwa?."
yayi tambayar ne dan yasan rana irin ta yau wato ranar ko wata juma'a Ummi tana fita zuwa asibitoci kan titi in da mabarata suke zama dakuma masallaci in da  mabarata suke zama, domin basu sadaka a kowace ranar juma'a, dan haka yake da tabbacin wannan fitar ma zuwa guraren zasuyi dan iwar haka suke fita.
Ummi tace "Babban masallaci zamu fara zuwa."
yace "To Hajiya." nan yajuya akalar tafiyar izuwa babban masallaci.
suna isa direba yagyara parking a gefe, Ummi tafito rike da jakarta, yayin da Fauzan da Nusaiba suka rufa mata baya,
ta isa in da mabarata suke jere a bakin masallacin, ta buɗe jakarta tarika ciro kuɗi tana raba musu, tana bin kowa layi-layi tana mika musu sadaka.
duk wanda ta mika masa sai ya kwararo mata addu'a da fatan samun biyan bukatun ta na alkhairi ga mahaliccin ta.
duk wan da ta bawa idan yayi mata wannan addu'ar sai kaga ta saki wani murmushi tare da fatan tabbatu war hakan acikin zuciyar ta.
akasin da da idan sunyi mata addu'ar saboda raunin dake zaune cikin ruciyar ta har sai ya kai ga tayi kukan zuci, tana ji ina ma Ubangiji yakarɓi addu'o'in nasu da wanda take hana idanun ta bacci acikin kowani dare, ya kare mata ɗiyar ta a duk in da take.
gaba ɗaya yau ɗin nan ta tashi ne cikin farin ciki da jin daɗi tana jin kanta cikin wani irin farin ciki mara misaltuwa, wan da ita kanta batasan na mene ne ba.

Haka tarika binsu tana raba musu cike da shauki da jin daɗin da yagama baibaye zuciyar ta, har sai da ta tabbatar da kowa ya samu, kafin ta koma cikin mota tana jin su suna daɗa bin ta da addu'o'i mai kara mata nutsuwa da kwanciyar hankali.
daga masallacin kuwa titi-titi suka fara bi in da mabarata ke zama suma tarika mika musu sadaka. kana suka wuce asibiti, har sai da kuɗin da ta fito dashi yakare kafin tacewa direba su koma gida....

*(a can kasar Saudiyya cikin masarautar Saudi)*

Da sauri nafito daga cikin bathroom  ina gyara gashin kaina dana wanke yazubo ya rufe min fuska har bana iya ganin hanya,
cikin hanzari na nufi gaban mirror karamar towel in dake rike a hannuna na naɗe shi a kaina ina

tsane ruwan dake ɗiga daga gashina.
kana na ɗau na'urar dake busar da gashi nabusar da gashin, batare da  ya bushi duka ba, nabaza shi ta baya domin iska yakarasa busar da shi.
zama ta na gyara na ɗau mai nasoma shafawa a jikina.
daga cikin mirror nake hango su Ukhtee ita da su Naseem sun sata a tsakiya sai surutu suke zuba mata, suyi da hausa su gwama da larabci abun ka da kwakwalwar yaro sukam tuni suka fini ji da iya mayarwa ma.
kai na jinjina a raina nake cewa
"Kai waɗan nan yara da surutu suke ko surutun wa suka ɗauko?."
ko ɗazu dasuke ta zuwaba Mammaa surutu sai cewa tayi wai ni suka gado, niko ina nake da surutu irin haka.
idan kaji maganar su kamar wan da sukayi shekaru huɗu wan da ko shekara uku basu cika ba saura wata huɗu nan gaba.
nayi murmushi kawai tare da girgiza kai, ganin Naseem yajuya fuskarta gareshi in zayi magana Nasmah ma haka.
wai su in zasuyi magana ala dole sai mutum na kallon bakin su in bai kallaba sun rika juyo da fuskar shi kenan.
wayan Ukhtee ne yashiga kara taɗago wayar tana dubawa kana ta maida duban ta gareni, daga cikin mirror'n muke kallon juna,
ganin ta mai da kallon ta kan wayar namike da sauri dan nasan ni ake kiran ganin yan da tayi zuruu tana kaloon wayar tawani langwaɓar da kai,
da sauri na isa bakin gadon, ina faɗin
"Bappa ko?". kai ta gyaɗa tare da mika min wayar, na amshi wayar na ɗaga kiran tare da kara wayar a kunne.
"Assalamualaikum Bappa." daga cikin wayar Bappa yace "Ke HAMDAH  me kike yi ne har yanzu baki shirya ba."
da sauri nace "Ina kan shiri Bappa yanzu nafito daga wanka ina kan shirin, ina shafa mai ne yanzu." yace "Kada fa ki tsaya wani dogon shafe-shafe kisaka kaya kawai kada jirgi ya tashi ki rasa jirgi kada ki tsaya shiririta irin na rannan."
"To Bappa yanzu zan gama".
nakashe wayar ina mai jin wani farin ciki. wan nan karon bazan yi wasa ba kamar na wata guda da ya wuce, haka nayita lalawai har jirgi yatafi a bun sa, wannan karon kam ba Bappa kaɗai keson komawa ta ba ni kai na inason komawa kasata, hankali na gaba ɗaya yakoma kasata yanzu.
ina so najini a cikin ta, ba naganni cikin kasata kaɗai ba, ina so naganni cikin ahalina duk da nasan hakan ba abu mai sauki bane, har idan Abba bai sauka daga fushin da yake dani ba.

Mika mata wayar nayi ina kokarin juyawa, wani kiran yakuma shigowa.
murmushi nayi ganin Bappa ne yakuma kiran, da safiyar nan kiran sa na shida kenan kan nayi sauri kada jirgi yatafi.
"Hello Bappa". nafaɗa ina kai wayar kunne na, muryar sa na jiyo yana faɗin
"Kada ki ɓata lokaci dai kinji ko, kisaka kaya kawai kada ki rasa jirgi ki hanzarta."
nace "To Bappa."

na sauke wayar na mika mata da sauri na koma gaban mirror, a gaggauce nakarasa shafa mai sai pauda da man baki.
na mike da sauri na isa bakin gado in da dama nan nacire kayan da zansaka na aje na ɗauka na sa, dan sai da na shirya su Naseem da Nasmah kafin na shiga wanka, shiyasa shirin yayi min sauki.
tun da Bappa yakira waya nalura da yanayin Ukhtee gaba ki ɗaya yanayin ta ya sauya tayi wani ziruu da ita,
kai na kawar dan bana son muhaɗa ido da ita, dan yanayin nata zai iya sa jikina ya mutu.
cikin hanzari na kammala saka kayana,
ina cikin sa kayan ban kai ga gamawa ba Bappa yakuma kira.
Nan ma kuma faɗin nayi sauri yace, cikin hanzari na kammala saka kayan.

Na dubi Naseem da Nasmah ina faɗin
"Kutashi muje ko." ido
Naseem ya kura min yayin da hannayen sa biyu ke dafe da kuma tun sa kana ya ce "Mommy mataiyaci amuje?".
Nasmah ma tace "Tayan kaya amuje ko Mommy?." kai na girgiza musu nace
"Ba siyan kaya ko masallaci zamu je ba, kasar mu zamu koma can kasar mu in da aka haife mu."
ido yaran suka ware suna kallona kana Naseem yakuma cewa "Mommy kasar mu in da aka haife mu?."
yy maganar yana zura yatsarsa cikin baki alamun mamaki irin na yara.
kai na gyaɗa masa tare da ruko hannunsu ina faɗin "Kutashi muje." dan nasan idan nabi na surutun su sai mu makara anan har Bappa yakuma kira.
Ukhtee kuwa tuni idanunta suka kawo
ruwa kan kace me hawaye yafara sauka,
hannunta na rike cikin rauni tare da girgiza mata kai dan nima idanuna sun  fara tara kwalla.
cikin harhaɗa larabci nace
"Dan Allah Ukhtee kar kisa jikina yayi san yi, baga waya ba zamurika  magana ai tafiya ba mutuwa bace ai dai bamu rabu ba tun da akwai waya zamu rika gaisawa, bakin ce zaki zo kasar mu ba?."
kai ta  gyaɗa min alamar Eh nace
"To dan Allah kada ki karya min guiwa da tafiyar kizo muje kin ga Bappa sai kira yake."
jiki a sanyaye ta mike.
koda muka fito parlour sai gani nayi babu akwatin kayan mu in da nafito da shi na ajiye ɗazu bayan nagama shirya mana kayan mu.
nan Ukhtee take sanar min direba ne yashigo ya ɗauka.
koda muka fita farfajiyar masarautar, a tsaye jikin mota muka tadda direba da alamu mu yake jira.
da sauri na juya na nufi side ɗin su Ukhtee dan yiwa Mammaa sallama,
narika bin part-part na masarautar ina yi musu sallama duk in da na shiga sai na fito da ƙwalla dan suma da kwallar suke rako ni,haka narika bin side mafi kusa da mu ina yi musu sallama dan idan nace zanbi na nesa da mu sai na kusan sai na ɓata lokaci mai tsawo ban gama ba.

daga karshe nashiga can cikin masarautar in da lokacin da mukazo aka canza diamonds  ɗin nan aciki.
direct cikin katafaren parlour wan da aka kawata shi da adon zinari mai matukar ɗaukar ido muka shiga,  adalin shugaba na zaune a mazaunin sa na alfarma, yayin da Alkur'ani ke gaban sa yana bita cikin nutsuwa. a gaban sa muka rusuna, cikin ladabi nayi masa barka da war haka,kafin nakuma cewa wani abu ya ɗaura hannunsa a kai na yana yimin fatan isa kasata lafiya, nayi mamakin yan da yasan abun da ya kawo ni dan ni a zato na bai san da tafiya ta ba.
naji daɗin addu'o'in da yayi min kwarai da gaske, na mike cikin jin daɗi yayin da jikar sa wato Ukhtee ta rufamin baya, bayan itama ta gaishe shi, gaba ɗaya cikin parlour'n suka shiga yimin fatar isa gida lafiya ina amsawa da amin har muka fita.
a jikin mota na tadda su Mammaa cikin matukar bege kowa sai hawaye yake har sai da suka sa hawaye na ya karu.
direba na ganin mu yayi saurin buɗe motar yariko hannun su Naseem yasa su cikin motar, rungume juna mukayi da Ukhtee muka saki kuka a tare, gaba ki ɗaya gurin hawaye suke babu mai iya rarrashin wani,
zame jikina nayi cikin sauri nashige cikin mota, direba yatada motar.
motocin da suke jere a gaban mu guda uku sai wasu biyu a bayan mu,
motar farko mai tambarin masarautar haɗe da jiniya, shi ya fara fita, kafin biyu suka bi bayan sa sai kuma motar da muke ciki.
motoci biyu da suke bayan mu suma suka biyo mu, kamar dai ranar da muka shigo masarautar sai gashi yauma a haka muka fita.
muna isa airport batare da ɓata lokaci ba muka shige cikin jirgi, nan motocin suka juya.
bada jimawa ba jirgin ta ɗaga...

Bayan wasu ƴan awanni jirgin mu yasamu sauka cikin yar dar Allah da buwayar sa, cikin babban birnin tarayya Abuja da ke cikin kasata ★NIGERIA★.
bayan saukar jirgen da kamar minti 15 fasinjojin ciki suka fara sauka.
da sauri ganin Naseem da Nasmah sun mike kan kace me sun rufa da gudu sunyi bakin kofar fita in da mutane keta sauka,
cikin hanzari na rufa musu baya da sauri ina faɗin
"Kai kutsaya fa kar kuje ku faɗi."
ai ko da gudu suka fara sauka daga matattakalar jirgin suna dariya.
bayan su nabi ina dariya ganin inda suke sauka cap-cap-cap daga matattakalar kamar zasu kefe kasa ina cigaba da faɗin.
"Zaku faɗi fa kutsaya."
kan kace me sun sauka kasa, sauri na kara ina sauke kafata kan shinfiɗaɗɗiyar kasan kasata abun alfahari na ƙasata Nigeria, naja wani irin numfashi tare da shakar daddaɗan iskar dake kaɗawa acikin ƙasata.
ganin suna kokarin cigaba da gudun nayi hanzari na ruko su tare da faɗin
"Idan yaro ya faɗi yayi min kuka zan kara masa."
baki suka washe cikin kyakyata dariya Naseem yace
"Mommy baya mu faɗi ba." goshin sa na dungure nace "Zaku faɗi mana in zaku faɗin zaku sani ne wan nan gudun da kuke ai sai dai kuji ku a kasa kuzo nan ku tsaya."

na janyo su gefe guda.

Daga can gefe guda
da sauri aka buɗe wata motar da suke jere ɗan nesa da mu, wasu mutane biyu suka fito da sauri suka karaso in da muke, sannu da hanya sukayi min, na amsa ina kokarin janyo su Nasmah mu matsa gefe, daya daga cikin su ya mika min waya, kallon wayar da yake mika min ɗin nayi kana na mai da duba na kansa,
kai ya ɗaya tare da faɗin
"Ana maga na." ya fada yana kallon kan screen ɗin wayar, a hankali na sake Nasmah dake rike a hannun dama ta na amshi wayar, shikuma yayi saurin ruko hannun ta yaɗan matsa gefe kaɗan in da ɗayan mutu min ke tsaya ya harɗe hannu da bakin gilashi a aidon sa,
a sannu nakai wayar kunne na tare da yin sallama, daga cikin wayar akace
"Barka da isowa kasa Nigeria ki bisu su isa da ke masauki."
ɗan shiru nayi kamar naso nagane muryar mai maganar, sai kuma na sauke wayar batare da nace komai ba na mika masa wayar.
a hankali na soma tafiya suna biye da ni har gurin mota, da sauri ɗayan ya buɗe min murfin motar muka shiga in da tuni suka saka jakar mu cikin motar.
jere motocin suka fita kamar yan da aka kawo mu airport a can kasar Saudiyya.
muna fita daga cikin airport ɗin muka ɗau hanya, shiru nayi cikin motar ina raba ido cikin ƙasata yayin da zuciya ta ke kunshe da ɗin bin farin cikin gani na cikin ƙasata, ina jin wani farin ciki tabbas ƙasata abun alfahari na ne.
munyi tafiya mai nisa kafin muka isa wani katafaren hotel, hotel ne irin wan da manyan kusoshin kasa suke sauka a cikin ta...

Awani haɗeɗɗen ɗaki aka sauke mu sai da suka rako mu har bakin kofar room ɗin kafin suka juya, wan da ke rike da jakar mu kuma yashi ga ya ajiye, kana ya miko min waya yace "Ana magana." na amshi wayar a raina nake faɗin
"To yanzu kuma ina zai kuma cewa na bisu."
a sannu nakara wayar a kunne na sai jin muryar Bappa nayi yana faɗin
"HAMDAH sannun ku da hanya ya gajiyar hanya."
washe baki nayi dajin muryar Bappa da sauri nace
"Laaa Bappa mun iso lafiya kalau Bappa kana ina?."
nafaɗa ina washe baki cike da murna jin muryar Bappa da nayi yace
"Kuhuta ku kwanta ku huta sosai ina nan zuwa."
nace "To Bappa." na mika masa wayar ina cigaba da washe baki, mutumin ya fita tare da jamin kofa, numfashi na sauke tare da bin ɗakin da kallo, na isa bakin gado na zube bakin gado, in da tuni Naseem da Nasmah suka haye gadon sai salle suke.
kokarin tuɓe kayan jikina nake dan so nake naɗan watsa ruwa, naji ana knocking mayafi na naɗauka na mayar jikina, na mike na nufi kofar na buɗe ma'aikacin hotel ɗin nagani tsaye rike da babban tray, baya naja na bashi hanya yashigo ya dire try ɗin kan table kana yafita na mai da kofar narufe na murza key.
na dawo bakin gadon na tuɓe kayana nashige bayi,
wanka nayi sosai nafito na tuɓe su Naseem suma nayi musu wan kan.

bayan na shirya su nima na sauya kaya, kana na zuba mana abinci mukaci.
muna gama ci muka koma gado...

bayan haka da kamar awa 2 akayi knocking na mike naje na buɗe, ɗaya daga cikin mutanen da mukazo tare nagani tsaye yace
"Madam kun kammala zamu iya tafiya?".
kai na gyaɗa masa, juyawa nayi dan kiran su Naseem sai ganin su nayi a bayana suna kokarin fita daga ɗakin,
mutumin ya ruko hannunsu nikuma na koma na ɗau mayafi na nabi bayan sa muka fita..
tun daga bakin get ɗin da muka iso na fahimci banki muka zo dan gashi a rubuce (First bank) buɗe baki nayi a raina nake faɗin "To me mukazo yi a banki." bakin na rufe jin yana faɗin "Bismillah fito muje ko." sai lokacin na lura ashe ma har sun fita har ya buɗe marfin ɓarin da nake ban sani ba, a hankali na zuro kafafuna waje na fito.
direct cikin bankin muka shige batare datsaida mu ko bincike ba, akasin jama'ar da nagani tsaye bakin bankin an tsaida su an hana su shiga.
tun da nashiga cikin bankin aka bani gurin zama ban motsa ba, duk wani cike-cike da kai kawo wasu suke tayi su da wan da mukazo da su, sai dai abun da yakamata ni nayi da kaina shine nake tashi naje nayi, awa 1 da zuwan mu aka kammala komai aka bani ATM,
muna fita daga bankin zato na masauki za'a maida mu sai ganin mu nayi a get ɗin wani banki, shima kusan mintunan da mukayi a bankin da muka baro mukayi a nan ɗin kafin muka kammala, nan ma da ATM ɗin bankin muka fita. ina mai jin mamakin kuma zuwan mu wannan bankin.
mamaki na bai karu ba sai da nakuma sin tar kaina cikin wata banki, wunin ranar muka kare ta a bin bankuna dan sai da muka je banki biyar kuma duk wan da mukaje da ATM ɗin sa muke fita..
sai yamma liss muka dawo masaukin mu, a gajiye na zube bakin gado in da ɗaya daga cikin mutanen da muka tafi da su yashigo da su Nasmah, wata laidar dake rike a hannunsa ya mika min yana faɗin
"Gashi ance na baki."
bin laidar nayi da kallo kana namika hannu na amsa shiku yafita,
zamata na gyara tare da zuba ATM ɗin da suke hannuna kan table ɗin gabana.
a sannu nashiga buɗe laidar dan ganin abun da ke ciki,
kwalayen wayoyi ne har guda biyu nagani ciki a sannu na ciro su ina jujjuyasu, rabon da narike waya haka a hannuna a matsayin nawa har na mance, sai kuma cikin hanzari nashiga buɗesu dan tun ban ciro su ba wayoyin suka tafi da ni, da sauri na ciro cazar wayoyin duka namike cikin hanzari naje na saka su a cj, ina saka wa kuwa suka nuna min acike suke, da sauri na dawo in da na tashi na kunna wayoyin, ai ko ina kunna wa sai ji kake ɗuɗut-ɗuɗut alamun shigowar message alert akai-akai.
ido na kurawa musu ganin alat ne na kuɗi suke ta shigowa, na bankunan da muka buɗe ɗazu, ido na zubawa sarautar Allah ganin kuɗaɗen da suke ta shigowa ni bama zan iya kiyaste adadin su ba.
sai da naji wayoyin sunbar kara kafin nashiga latsa su, contacts nashiga da sauri sai gani nayi babu number ko ɗaya, jiki a sanyaye nake kallon wayar, abu na farko da ya fara zuwar min

shine lokacin da Abbu ya siya min waya yasaka min number family na aciki,haka narika bin lambobin ƴan'uwa na ina kiran su.
 hawayen da yagangaro kan fuskata na share ina mai jin kewar ahalina, a sannu na mike na isa in da jakata yake na buɗe naciro number Ukhtee da ke rubuce a takarda, na saka cikin wayat kana na dannan mata kira,
tana ɗaga wa dajin nice mai kiran atare muka saki ihun murna.
hira mukayi tayi da ita har magriba kafin na mukayi sallama...

Kasan cewar ina fashin sallah gado na haye nayi kwanciya ta cike da kewar ahalina daya baibaye ni lokaci guda...
washe gari da rana Bappa ya iso Abuja, nayi murna matuka da ganin sa har nake jin wani ɓari na kewar ahalina dana kwana dashi ya yaye da ganin sa.
isowar sa ba da jimawa ba muka bar cikin hotel ɗin har da kayan mu.
wani katafaren gida mai matukar kyau da tsaruwa gida ne babba wan da girmansa yakai ya kawo tsarin sa gwanin burgewa, a bakin ramɓasheshen get ɗin gidan motar gaban mu ya tsaya, wan da mutanen da suka ɗauko mu a airport da wan da muka haɗu dasu a banki jiya dakuma wasu karin mutun biyu  da yau nafara ganin su, sune acikin motar, motar da muke ciki ke biye da su, sukayi hon, abakin get ɗin ramɓasheshiyar gidan........★

Mommyn Twins ce

HMD
WASA FARIN GIRKI!!!✍🏻

_(Book 3)_

🅿️4

Asannu a ka wangale tamfatsetsen get ɗin gidan, motar gaban mu yakusa ciki, a hankali direban dake jan mu ya danna hancin motar cikin gidan, a tsakiyar farfajiyar gidan duk suka faka motocin, a sannu na zuro kafafuna waje, "Ya ilahi ya littahi".
abun da na furta kenan lokacin da na dai-dai ta tsayuwa ta a cikin gidan, bin gidan nashiga yi da ido har ina wai ga gefe da gefe na.
gaba ɗaya gidan da tsaruwar sa yatafi da ni, tsaruwan gidan yawuci misali komai an tsarashi a inda ya kamata yana ajiye a in da ya dace,gida ne babba mai ɗauke da part har huɗu, daga gefe can gabar da gidan side ne guda ɗaya sai kuma gefe ta hannun dama shima side ne guda sai kuma gefen hagu shima side ɗaya, sai dai ƴan madaidaita ne ba wasu manya ba.
daga tsakiyar gidan kuwa wani side ne na musamman wan da yazamo sauran side ɗin sun sashi a tsakiya shi kam gini ne mai hawa ɗaya babbane ya tsaru iya tsaruwa, daga saman side ɗin har kasan sa yaji ado da gilasai masu ban mamaki an kawata shi tamkar a turai,daga kasa kuma an zagaye shi da wasu flaw's masu matukar kyau da ɗaukar ido,
gaban side ɗin wani shinfiɗaɗɗiyar swimming pool ne wan da aka kawatashi da rubber grass malaye har bakin kofar shiga side ɗin.
gefe can kuma parking space ne ɗauke da lafiyayyun motoci da suka kai guda uhu a cikin sa,

daga farin shiga gidan kuma gefe da ɗakin mai gadi masallaci ne shin fiɗaɗe agun,
sai kuma ɗakuna guda ɗai-ɗai a jere guda uku a gefe da masallacin ta can.

Maganar Bappa naji yana faɗin
"Muje ciki ko HAMDAH." da sauri nadawo daga duniyar kallon gidan dana tafi, da murmushi kan fuskarsa dan ganin yan da na tafi gaba ɗaya na shagalta  da kallon gidan.
 na ce "To Bappa". a hankali nabi bayan su side ɗin da ke gefe ta hannun dama muka nufa a hankali nake taka kafata ina cigaba da baza ido cikin gidan har muka isa cikin side ɗin.
masha Allah ɗan madaidaicin side ɗin ya tsaru matuka.
side ne mai ɗauke da 3 bedroom ko wanne da banɗaki a cikin sa, ɗan madaidaicin parlour haɗe da dinning
da kitchen da komai da komai, an tsara komai yan da yakamata duk wani abun bukata an tanadar babu abun da babu.
ɗakunan cikin parlour'n muka rika shiga wan da komai akwai hatta gadon ɗakunan duk da shinfiɗar su, sunsha lafiyayyun bedsheets.
bayan mungama zagaye cikin side ɗin gaba ɗaya, muka fita ɗayan side ɗin dake gefen hagu muka shiga, shima kamar wancan side ɗin yaji komai. kowa sai faɗin masha Allah yake, nidai kasa magana nayi sai binsu nake inata baiwa idona abinci sabo da gaba ɗaya yanayin tsarin gidan yatafi dani.
daga nan ɗaya side ɗin dake can gabar da gidan muka nufa, shima tsaruwan sa da tsarin sa kamar sauran part biyun nan,
koda muka fito daga cikin part ɗin baki na washe nadubi Bappa dake ta faɗin
"Kai komai yayi masha Allah komai fa yayi yadda yakamata". baki nakuma washewa ina faɗin
"Kai wlh Bappa gidan nan Allah yayi kyau kaga fa nan irin wancan can ma irin wancan kai tsarin gidan yayi kyau komai iri ɗaya, sai dai kawai kalolin kayan cikin sune daban-daban".
dariya Bappa yayi kana yace "Da gaske gidan yayi kyau ko?."
"Wlh kuwa Bappa." nafaɗa da sauri ina cigaba da washe baki, shima dariyar ya kuma yana girgiza kai kana muka rufawa mutanen baya in da suka nufi wannan kayatacce rantsatstsen babban side ɗin nan dake a tsakiyar gidan wan da yazamana da sauran side ɗin sun sashi a tsakiya.
a hankali muka isa bakin kofar da sauri ɗaya daga cikin mutanen ya isa bakin kofar side ɗin wan da yake na glass ya ɗaura hannunsa gefe kan wasu madannai ya daddanna sai ga glass ɗin yafara bada sauti ɗan baya yaja kana ya dubeni yace
"Bismillah Madam ɗan zo ki tsaya a nan."
ya nuna min kan step ɗin da yasauka akai wan da saika haura kansu kafin ka isa bakin kofar,step ne guda uku, nuna kai na nayi alamar ni?. yace "Eh." a hankali na matso na haura kan step ɗin, daga in da yake yamika hannunsa yakuma danna wasu lambobin kana yace na ɗaura hannuna kan nan yanuna min wani ɗan zagaye da hoton yatsu, a sannu nakai hannuna na dai-dai ta yatsuna kan zanen yastun, nan yafara bada sauri ɗit-ɗit sai kuma yakuma danna wata lambar data fito mai alamar Okay. nan take kofar tazuge gefe ai ko da sauri na ɗaga hannuna.
ya juyo yana duba na kana yace
"Madam wannan kofar special ne mai amfani da zanen yatsune mutum ɗaya ke amfani da shi,

sai kuma wancan". yanuna wata kofar dake gefe ya isa gurin muma mukabi bayan sa,ni dai cikin rashin fahimta nake jin sa, yace
"Shi wannan common door ne kamar yanda aka sani kowa zai iya amfani da shi."
ya murɗa handle ɗin kofar yabuɗe muka shiga ciki.
sai gamu mun bayyana cikin wata katafaren parlour ya ilahi ya lilahi, har bansan san da na furta "Kai! amma wannan duk yafisu kyau!".
nayi maganar cikin hakikance gaskiyar abun da ke cikin zuciya ta wan da maganar fitowa kawai tayi,
Bappa ko karamar dariya yayi tare da jijjiga kai.
suma sauran dariya suka bini da shi, nan muka fara kusawa cikin katafaren parlour'n, baki da hanci gaba ɗaya na buɗe wajen kallon katafare kayataccen parlour'n, faɗan tsaruwar sa da misalta tsarin parlour'n ma ba zai misaltuba, yaji kayan alatu da more rayuwar duniya tsaruwan sa ya zarce sauran side ɗin da muka shiga babu haɗi ko kaɗan.
bedroom ɗin dake cikin parlour'n muka rika shiga ɗaya bayan ɗaya, bedroom ne zafafa har guda huɗu masu ɗauke da tsalatsalan bathroom,
daga gefe da parlour'n kuwa katon dinning area ne sai kitchen babba a gefe.
sama muka hauwa wan da shi kanshi step ɗin haurawan sama abun kallo ne domin kuwa shima an kawatashi na musamman.
wow masha Allah shima tsarin saman kamar kasan sai dai banbancin kalolin kayan dake cikin su, kalar kujeru da labulayen bedroom and parlour kasan white and ash da ɗan ratsin lemon-green. saman shima 4 bedroom ne a cikin sa kalan kayan bedroom and parlour'n kuma white and sky-blu.
Antsara komai yadda yakamata sai tashi da sassanyan kamshi mai haɗe da kamshin sababbin kaya yake.
kai gidan ya haɗu fa nidai bakina yakasa rufuwa wajen kallon tsaruwan gidan, bayan mun gama zaga lungu da sako na saman muka gangaro kasa anan muka yada zangon mu cikin parlour'n kasa.

Kowa sai yaba kyau da tsaruwar gidan yake, ɗaya daga cikin mutanen yadube ni kana yayi gyaran murya sannan ya ce
"Madam komai yayi ko? komai ya miki wannan gidan yayi miki? kokuma mu isa wani gidan?."
kallon sa nayi cikin rashin faminta sai kuma na maida dubana ga Bappa danaji yana faɗin
"Duk da dai bataga sauran ba amma ga yanda take ta washe bakin nan ai ba a magana."
da sauri nace "Bappa gidan..". bai bari na karasa ba yace "Gidan ki wannan gidan duk girman ta nakine akwai kuma ire-iren su suna nan".
ido na waro kamar a mafarki nakejin zancen, "Wannan ya miki?". mutumin yakuma jefo min tambayar, kai nashiga gyaɗawa da sauri sai kuma naruko hannun Bappa ina faɗin
"Eh wlh yayi-yayi Allah Bappa gidan yamin kyau sosaiiiii".

Dariya Bappa yayi yace "To sake min hannu kada ki ɓala".
ai ko sauran mutanen ma suka rika dariyar ganin yan da nake washe baki ina jijjiga hannun Bappa, Naseem da Nasmah dariya suka rikayi suna tsalle jikin Bappa kamar wan da sun san abun da ake.

Mutumin yacigaba da faɗin
"To masha Allah wannan side ɗin shine naki a yanda aka tsara ginin gidan, sauran kuma ke kikasan yan da zakiyi da su, yanzu mu zamu koma mubarki ki huta zamu dawo zuwa gobe, domin sauran baya nai."

Sukayi mana sallama suka fita, suna fita, na dubi Bappa ina waro ido nace
"Bappa wai da gaske wannan gidana?". Bappa yayi murmushi tare da faɗin "Daɗina da ke akwai shirme." hannu nashiga tafawa ina faɗin "Kai wlh gidan nan yayi min mugun kyau." ya ce "To sai ki goyashi kuta yawo tun da dai naki ne." ido na waro tare da sa dariya nace
"Bappa gidan zan goya?." kanshi ya jinjina yana murmushi.
rungume Naseem da Nasmah nayi cikin tsananin farin ciki, sai kuma na sake su.
da sauri nace "Bappa ina su Inna wuro da Fatu?."
yace "Suna can ruga". nace "Bappa shine bakazo da su ba kace su dawo nan  suzo mu zauna da su a nan, kaji Bappa."
nafaɗa ina jijjiga hannun sa, "Kaji Bappa kace su zo". nakuma faɗa ganin yayi shiru bai ce komai ba,
yace "A'a HAMDAH su zauna acan zan koma ai nima".
ido nakuma warowa da karfi nace "Bappa ni kaɗai za'a barni a wannan gari gudan, da ni kaɗai zan zauna a gidannan ai dani daku zamu zauna."
nayi maganar ina nuna cikin parlour'n  "Tap Allah bazan iya zama ba dan Allah Bappa kace su dawo nan, wannan gidan ai tsoro zai rika bani ni kaɗai a cikin sa, kaji Bappa?."
nafaɗa ina bubbuga kafafuna a kasa. "To babu damuwa zasu zo amma ba yanzu ba."
na ce "Bappa sai yaushe." ya ce "Bari dai mana a gama Hajiya HAMDAH."
dariya yake bani in naji ance Hajiya HAMDAH, ai ko na washe baki,
yace "To meyasa bakisa hakorin hajji ba acan?."
"Kai Bappa,hhhh to zan sa in na kuma komawa."
"Allah ya kai mu ai kamar yanzu ne shekara zata kuma zagowa Allah ya nuna mana cikin masu rai da lafiya."
yayi maganar yana mikewa tare da cigaba da faɗin
"To ni bazanje masallaci gashi ana ta kan kiran sallah, mutumin zo muje muyi sallah".
da sauri Naseem ya mike ya roko hannunsa suka fita.

Da sauri na mike inata daɗa waigen cikin parlour'n inshiga wan ɗakin in fita inshiga wancan haka narikayi, daga nan kuma naja hannun Nasmah muka haura sama ina faɗin
"Bari naje na zaɓi bedroom ɗin da yafi min."
koda muka haura ɗakunan duka na shiga kana nazaɓi ɗaki ɗaya, nan cikin bedroom ɗin nabuɗe bathroom ɗin sa na shiga mai girma da tsaruwa kamar ɗakin kwana.
kayan jikina na tuɓe duk da ban jima da yin wanka ba nacika ruwa cikin basin nashige ciki, lumshe idanuna nayi ina jin daɗin ruwan na ratsani, najima sosai a ciki kana na wanke jikina da sabulu mai sanyin kamshi da nagani cikin bathroom ɗin, sannan nafito.
Na sami Nasmah gaban mirror ta ɗauki janbaki sai murkawa take a bakin ta.

dariya nayi ina faɗin
"Oh wannan yarin ya ke kam akwai ki da son janbaki".
itama baki ta washe tana cigaba da kwaɓula janbakin a bakin ta.
da sauri na sauka kasa akwatin kayan mu na janyo nadawo ɗakin, a sannu na isa gaban wardrobe dan na shirya kayan ciki, ina buɗe wa ido na ware cikin wardrobe ɗin ganin kaya ashake a ciki, kama daga kan leshi atamfa material shadda dogayen riguna iri-iri, sai dai ba a ɗinke suke ba,a hankali na zaro ɗaya daga cikin dogayen riguna wan da suke jere gefe guda masu kyan gaske, na dawo gefen Nasmah na zauna, kana na sauya kayana da dogon rigar nan...

Tsabar farincikin da nake jin kaina ciki yau bazai misaltuba, muna zaune har su Bappa suka dawo muka sauko parlour'n kasa muna ɗan taɓa hira dakuma kallon tv.
duban Bappa nayi sai kuma kamar an zabure ni na mike ina faɗin
"Bappa ina zuwa."
sama na haura in da na aje karamar jakata ta hannu na ɗauko na buɗe jakar naciro wayoyin da jiya aka bani wan da tun da na kunna su nakuma kashewa najefa cikin jakar, dakuma ATM ɗin da jiya aka bani su a banki, nadawo in da Bappa suke da sauri nace
"Kagani Bappa jiya mutanen nan suka ɗauke ni sukayi ta kaini bankuna sukayi ta buɗe min account, muna dawowa kuma suka bani waɗan nan wayoyin ina kunna su kawai Bappa kaga kuɗin da sukayi ta shigowa  kawai kuɗi sunata shigowa cikin accounts ɗin".
nayi maganar ina wawwaro idanuna alamun tsantsar mamaki.

Murmushi Bappa yayi irin nasu na manya kana yace "HAMDAH kenan ai kuɗin kine yake shiga cikin asusun bankin ki, duk wani abun da kikaga yake faruwa duka, duk waɗannan mutane dasuke ta zirga-zirga da ɗawainiya da ke, duk umurnine daga sama, duk kanin su an ɗaurasu ne jagora akan lamarin, shiyasa kikaga duk waɗan nan abubuwa suke faruwa duk abun da kikaga sunyi umurnine, sunce min ma gobe idan Allah yakai mu za'a fara kai ki guraren da akayi ayyuka wato guraren kaddarorin ki, kije ki gaggansu gobe za'a fara tafiya shiyasa sukace kihuta yanzu."
kai na jinjina alamun gamsuwa, ikon Allah abun kamar a mafarki yake zuwar min.
knocking ɗin da ake ne yasani mike wa nanufi kofar da nafi zaton tanan ake knocking ɗin, na isa jikin kofar na buɗe,
wani nagani tsaye rike da basket har guda biyu a hannunsa, ɗan risinar da kai yayi alamun girmamawa kana ya ɗago yayi min barka da warhaka, na amsa kana yace min order ne daga hotel ɗin su akace yakawo nan gidan, kai kawai na girgiza kana nabashi hanya yawuce ciki.
dinnig table ya isa ya aje kayan abincin kana yayi mana sallama yafita.
muna nan zaune a parlour sai wajen la'asar mukaje mukaci abincin, daga nan Bappa yakuma fita domin zuwa Masallaci shida Naseem.

Washegari da safe kamar yan da mutanennan suka ce zasu zo suka iso,
suna zaune a parlour nikuma ina ciki domin kimsa su Naseem, ina gama kimsasu muka sauko nan muka ɗunguma.
yau munsha yawo kaman kaman domin kuwa tundaga unguwar muka fara, wani gida mukaje

sakanin sa daɗan rata da gidan da muke ciki, sannan  muka wuce wasu unguwanni biyu duk kanin su da gidaje ɗai-ɗai, wan da an gama musu komai suna kulle,suka nunnuna min dakuma tabbacin nawa ne, nasha mamaki kwarai daganin manyan gidajen wai kuma a matsayin nawa.
daga nan wani tsalelen gidan mai muka je tun daga can nahango ( *HAM'NAS Co Petroleum Nigeria LIMITED* ) wan da aka rubuta da manyan harufa a saman gidan man, tunga nesa zaka iya hango shi ɓaro-ɓaro.
idanuna na lumshe tare dayiwa Ubangiji buwayi gagara misali tasbigi a kasan raina kana na buɗe,

Mun zaga gidan man na yaba da tsarin sa kwarai yana rufe ne ba'a fara aiki da shi ba, daganan kuma wasu gidajen man mukaje har guda uku duk masu ɗauke da ( *HAM'NAS Co Petroleum Nigeria LIMITED* ) daga nan muka kuma zuwa asibitoci suma masu ɗauke da sunan ( *HAM'NAS International  HOSPITAL* )
suma asibitotin guda uku a gurare daban da ban manyan gaske, sai dai duk a kulle suke anzuba kayan aiki komai da komai acikin su sai dai ba'a fara ai ki da suba.
daganan kuma makarantu da kamfanoni muka nufa duk kanin su da tambarin *HAM'NAS* International School Of Science's And Technology, *HAM'NAS Store Complex's su ma duk  ba'a fara ai ki da suba. sai kuna masallatai manya guda uku anzuba komai a ciki suma ba'a fara amfani da su ba.

Zuwa yanzu kam nidai komai ganin sa nake kamar almara nafara yarda kan cewa komai da gaske ne, sai yamma muka dawo gida, mun dawo a gajiye suke faɗa min cewa muhuta nan da kwana uku sai mu fara tafiya guraren kaddarorin dasuke garurruwa nesa da nan, nace to Allah ya kaimu..

Damin Bappa narikayi nace nidai yasa su Inna wuro da Fatu suzo kafin mutafi nan da kwanan ukun,
yace a'a abarsu tukun ba yanzu ba,
haka dai dole yasa direba yaje ya taho da su dan na tubure a la dole sai an kawo su, ko da direba zaije ɗauko su nace yace musu kada suzo da komai, dan cikin side ɗin dana matsawa Bappa sai ya zabi ɗaya daga cikin side ɗin gidan wan da zasu zauna ciki, akwai kaya komai na bukata sai suzo suyi amfani dashi abun da babu sai a karo musu kamar kayan sawa shi da babu a sauran side ɗin.
hakan kuwa a kayi ranar da su Inna wuro sukazo murna kamar nayi yaya, suma agefen su ba'a magana, na rungume Fatu inata murna, tarika ɗaukar su Naseem cikin tsananin farincikin kuma ganin su.
a ranar ma Uncle Mahmoud yazo har da matarsa da yaran su, dan su anan Abuja suke gun ai kin sa.
nan muka wuni da su wunin ranar yayi min daɗi matuka, sai narika jin su tamkar wani ɓari ga ahalina,
ganin su yaɗan rage min kewa da begen family na.

Yau asabar hakan yayi dai-dai da kwanaki ukun da zamuyi tafiyar, da sassafe muka ɗauki

hanyar suwa Kano, motoci biyu muka tafi dasu motar mu ni da Naseem da Nasmah dakuma Bappa,sai ɗaya daga cikin jagororin ke zaune a gefen direba, ɗaya motar kuma mutane huɗu ne a cikin ta suna gaba muna biye da su.
mun isa cikin garin Kano da misalin ƙarfe 12:30pm sai da muka tsaya mukayi sallah kafin muka nufi inda zamu,
gidajen mai muka fara ziyarta kafin asibitoti dakuma kamfanoni.
bamufi awa biyu a cikin Kano ba muka ɗau hanyar Kaduna a kaduna muka kwana, washegari muka nausa Katsina.

Sati biyu muka ɗauka muna yawon zuwa garuruwa ganin in da aka zuba ayyuka, masha Allah duk garin  da mukaje daga gwamnatin su muke samun tarba da karɓa mai muhimmanci, daga karshe muka biyo garin Bauchi,
lokacin da motar mu tashiga cikin Bauchi state, tashin hankalin da nashiga bazai misaltuba, wani irin tashin tsikar jiki da sanyi mai matukar shiga jiki su suka ziyarce ni, wani irin ɓari da kakkarwa nasomayi lokaci guda har hakorana suna garuwa da juna, sai kuma wani masifaffen zufa yashiga keto min, hankalin Bappa yayi musifar tashi ganin halin dana shiga lokaci guda, cikin tsananin tashin hankali jin bakon yanayin daya ziyarce ni lokaci guda tamkar ƙwaƙwalwa ta zata fashe jin wani irin abu mai matukar nauyi da kara ya dankare min a kai, kunnuwa na tamkar ana busa wani irin busa mai matukar kara da firgitar wa, da karfi nakai hannuna na toshe kunnuwana cikin matukar jin  azabar dake kokarin tarwasa min rayuwa nashiga faɗin
"Bappa mu tafi Bappa kace musu kada mu tsaya Bappa mutafi wayyo Allah na".
kaina nashiga juyawa da karfi jin  yan da zabar da nakeji na karuwa nan take nanimi tunani na na rasa.
cikin ɗaga murya ganin numfashi nakokarin barin jikina Bappa yace
"Direba yi hanzari mufita a cikin garin nan yi maza da sauri!".
gudu direba ya kara bai tsaya ba sai da muka fita a garin, gabaki ɗaya, hankalin kowa yayi masifar tashi ganin halin da nake ciki,
Bappa ko karatun Kur'ani yasoma yanayi yana tofa min, hankali na bai dawo jikina ba har sai da mukabar eriya'n Bauchi gaba ɗaya.
A hankali narikajin abun da nake jin na sassauta har ya washe.
numfashi Bappa ya sauke tare da saida karatun da yake, kai ya girgiza tare da faɗin
"Kai mutum abin tsoro ne Allah kashiga sakanin nagari da mugu akwai hisabi ranan gobe kiyama".
  yadubeni da kula yace
"Sannu ko HAMDAH".
kai na girgiza yace "Me kike ji yanzu?". nuna masa kaina nayi da hannu dan shi ke yimin ciwo sosai.
"Zai bari insha Allahu".
yayi maganar tare da buɗe tafukan hannunsa yasoma karanto Suratul (Khafi) aya goma na farkon surar haɗe da ayatul Qursi'yu ya tofa kana yashafamin a kan. cikin yar da da buwayar Allah naji ciwon kan na sauka.

Ko da muka shiga jahar plateau state, farkon shiga garin  Jos NARKUTA. wasu zafafan kwalla

ne suka gangaro kan fuskata tuno da Mama mai awara, da sauri nayi yinkurin yin magana a tsaya amma abun mamaki sai naji harshe na yayi min mugun nauyi gaba ɗaya jikina ya sake babu alamar karfi tattare da ni, abun da na fahimta tun lokacin da nayiwa Bappa maga shigar mu Bauchi zan kuma wata maganar naji na kasa, har kuma yanzu ina jin yanayin...
da daddare muka shiga Abuja, da kyar da taimakon Bappa na iya sauka cikin mota muka shiga ciki.
Inna wuro ta firgita da ganin yanayi na, ko da Bappa yayi mata bayanin abun da ya faru, hankalin ta yayi masifar tashi, yace ta taimaka min naje na kwanta, shikuma yafita can ya dawo da ɗan karamin ƙwarya da magani a ciki yabawa Inna wuro yace
"Kibata tasha babu komai insha Allah zata ware garin ne kwatakwata basa so tashiga sai dai tayi nesa da shi sun mance cewa Allah baya bacci".
Inna wuro tace "Ikon Allah wannan irin shiga sakani sai sakayyar Ubangiji".
ko da Inna wuro ta bani maganin inasha bada jimawaba bacci yaɗauke ni, ranar a kaina ta kwana, Fatu kuma tana tare da su Naseem a ɗaya ɗakin dake kusa da nawa.
washegari kuwa cikin yarda da buwayar Allah namike garau...
muna tare a parlour ni Inna wuro Fatu dan har lokacin basu koma side ɗin suba, labarin garuruwan da mukajejje narika basu ina washe baki da faɗin
"Allah Inna wuro bakuga abubuwan yan da sukayi kyau ba kai har da garin da ban taɓa zuwa ba".
nayi maganar ina washe baki, dariya suka rika min, nan
Bappa yashigo ganin jikina shima yazauna mukayi ta hira....

bayan kwana biyu

Mutane biyu daga cikin jagororin nan suka zo su da wasu mata guda biyar sukace na zama a cikin su wan da zasu rika yi min ai ki,
mata ne irin wan da suke karkashin paundation, irin waɗan da mazajensu suka sake su dakuma wan da mazajensu suka rasu, akan ɗauke su ai ki irin gidajen masu kuɗi ɗin nan, a cikin su na zaɓi guda uku dasukafi kwanciya min a rai, kana nace zan gwada ai ki da su.
ɗaya na ɗauke ta a matsayin mai kula da su Nasmah dakuma kula da tsaftar side ɗin,
na biyun kuma mai girka abibci, sai kuma ɗayar na turawasu Inna wuro ita zata rika kula da tsaftar side ɗin su dakuma girkin su.
nan suka kuma gabatar min da masu maza wan da nazo nasame su a cikin gidan, direba sai mai baiwa fulawa ruwa shi zai rika wanke mota, sai mai gadi dakuma mai kula da tsaftar farfajiyar gidan gaba ɗaya.
mun zauna da su na ɗan wani lokaci na fahimci mutane ne masu kirki da rukon amana.

Haka rayuwa tacigaba da tafi, tuni akayi bikin buɗe masana'antu da masallatan nan manyan shuwagabannin Nigeria sun halacci torurrukan sun kuma bada gudummawar su kwarai da gaske wajen ganin an ɗibi ma'aikata masu inganci.

Bayan wani lokaci

Tuni aka damkamin ragamar duk wasu kaddarori na ni nake bada umurnin ayi da kuma kar ayi, har kuma yanzu muna tare da jagororin nan su suke sanya ido kan ganin komai yatafi dai-dai. tuni nasa aka baiwa Fatu uniform a ɗaya daga cikin makarantu na, dan dama acan rugar ma tana karatun ta tacigaba a nan.

Zaune nake a parlour ina dudduba jerin sunayen mata da matasan da nasa a ɗiba, a karkashin paudasion ɗina domin basu tallafin wasu kuɗaɗen da zai jamusu jari domin dogaro da kansu, matasa hamsin da kuma mata hamsin,na tura da kuɗaɗen tallafin izuwa asusun *HAM'NAS* paudasion.
a hankali na mike tsaye tare da yin mika haɗe da salati, wayoyina na tattara haɗe da sabuwar system ɗina, na haura sama,
kan bedside na ajiye su kana na haye gado dan bacci nake ji, ina so nayi baccin kafin su Naseem su shigo dan suna can side ɗin su Bappa.
har na kwanta na tuna da akwai maganar da nake so muyi da Bappa kan wani Company na murza karfe da ake gina shi a Lagos,
mikewa nayi na fita dan ina so muje ziyarar gani da ido acikin satin nan.
da gudu Nasmah ta shigo tana faɗin
"Mommy kin ga Naseem ko jai camin jiji".
Naseem shima dagudu yashigo yana binta da abun yana dariya, Fatu na biye da su tana dariya da faɗin "Naseem kabari kar ka sa mata".
da sauri nakarasa sauka kan step na rungumo Nasmah dake falfala gudu kamar zata kife kasa nace "K.......!★

Mommyn Twins ce

5

"Kai Naseem me zaka sa mata kai ka bari zata faɗi fa kabari."
nayi maganar ina ɗago Nasmah cak na rungume ta a jikina, shiko dariyar yake yana matsowa in da muke ya ɗaga hannun sa sama tare da yin ɗagelgel da kafa, yana washe baki,
na ce "Idan ka zo nan sai na mare ka, zo kagani zo ka samata kagani,
dariya sosai yarika yana faɗin
"Mommy dan tamata ne dan ta mata wannan."
"To ka samata kagani sai na maka bulala."
kiran Talatu mai kula dasu nashiga yi ina faɗin
"Talatu zo ki kaishi wa ɗawisu ta cakwaɗe shi tun da dai shima sa mata jiji zaiyi."
Talatu ta iso da sauri tana faɗin
"Ayi hakuri Hajiya kar a kaishi wa ɗawisu zata cake shi, zo nan Naseem kada kasa mata ko, so kake a kaika wa ɗawisu ta cake ka,zo ko ɗan lele na mene ne zaka sawa Nasmah ɗin?."
ɗan karamin tafin hannunsa da ya dunkule ya buɗe kaɗan ya nuna mata kana ya kuma dun kulewa yana cigaba da dariya, "Lalala shine zaka sa mata?."
cewar Talatu tayi maganar haɗe da dariya, kai ya gyaɗa yana washe baki, duban Fatu nayi ina faɗin
"Wato Fatu keda Naseem kuke sawa Nasmah ta abin tsoro ko? to bazata sake wasa da ku ba."
dariya Fatu tayi tare da faɗin
"Allah Adda HAMDAH kin ga bansan in da yasamo ba kawai ganin sa nayi ya  shigo da shi a hannunsa,malam buɗe takarda ne fa."
 "Au malam buɗe takarda ne ya ɗauko shine yake so ya sa mata to bari yagani sai an kaishi wa ɗawisu shima, shine baki karɓa ba ko Fatu kika tayashi tsoratar da ita."
"Allah Adda HAMDAH binshi nake na karɓa shine yagudu."
Talatu ta ɗauke shi tabuɗe hannunsa taciro abun tana faɗin
"Kawo shi nan a yasar da shi kada ka saka mata kaga tana jin tsoro, kaima kada ka sake ɗauka a hannun ka."
tana rike da hannunsa tafita waje ta yasar da shi kana suka dawo ciki.
karaso wa cikin parlour nayi na zauna kan kujera tare da zaunar da Nasmah kan cinya ta, na dubi Fatu nace
"Fatu Bappa na ciki ne?."
tace "A'a yafita". sai kuma ta turo baki gaba tare da faɗin
"Adda HAMDAH nifa wannan sunan Fatun nace ki dai na faɗin shi, Fatun nan fa a can Ruga ne fa ake kiran Fatun nan tun da yanzu mutum yazo birni har yanzu ayi ta ce mishi wani Fatu, gaskiya Adda HAMDAH ni wlh na canza suna Fatu  ai duk su Inna wuro ne suka wani lankwasa min suna yaya Mahmoud dake shi a birni yake ai Fatima yake cemin,haka jiya wata ƴar ajin mu tana ta min dariya wai ni Fatu, aradun Allah na canza suna ko a ajin mu ma na faɗa na canza suna".

dariya muka tuntsire da shi, Talatu tace
"To Fatu man yan gari me kike so ace miki kenan?".
"Ai sunana da yawa masu daɗi ma, Nana, Fatima, Faɗimatu, Faty Zarah duka gasunan masu daɗi sai a rika cewa mutum wani Fatu kamar rugo".
nace "To lallai kam kamar kin sani da ma kam wannan sunan bai dace da ke ba yanzu dai kawai Faty za'a rika ce miki."
tace "Yauwaaa Adda HAMDAH Faty wlh yama fi amma kuna ta cemin wani Fatu kamar rogo".
"Hhhhh Faty kenan Allah bakida dama".
tace "Yauwa Adda HAMDAH gashi kin iya faɗin sunan dai-dai mai daɗi".
kai kawai na girgiza ina dariyar ta.
tace "Zo muje muyi wasan mu o Nasmah."
nace "O'o kuje bazata biku ba kuje kusata kuka bazata biku ba kam kutafi ku."
"Allah bazan barshi yasa mata ba". fuskata na kawo dai-dai fuskar Nasmah nace
"Zaki bisu?". kai ta gyaɗa "To muje daga gun na duba ko Bappa ya dawo".
nafaɗa ina mikewa na direta kasa tare da ruko hannunta muka nufi side ɗin su Inna wuro.
a parlour muka tadda Inna wuro Bappa bai dawo ba sai na zauna muna ɗan taɓa hira da ita.
muna nan zaune har Bappa ya shigo yazauna muka cigaba da hirar da shi, acikin hirar nake yi masa maganar yace kwarai kuwa ya dace kam aje domin a ganewa ido, in yaso satin sama sai a je, duk da akwai idanu da yawa akan lamarin. nace "Toh Allah yakai mu."
muna zaune sai ganin Naseem mukayi ya kin kimo school bag ɗin Faty, a tsakiyar parlour'n ya zauna ya tuttuɗe littatafan cikin jakar kasa ya ɗauki littafi guda ya buɗe yana ta gwalaɓe wai shi yana karatu.
dariya duka muka saka, Faty ko da gudu ta mike taje ta tattari litattafan ta tana ta faɗin
"Kai kasan meye a ciki ka iya karatu ne".
Inna woro tace "To ai karatun yake baki gani ba".
cikin muryar dariya nace "Um karatu yake ko gwalaɓe har da wani mike kafa kamar mai karatun gaskiya."
"Ah to gaskiya za'a saku a makaran ta tun da har ka iya ɗauko littafi kazauna ka buɗe kana karatu".
cewar Bappa yana yi masa dariya.
"Wlh Bappa nima dama ina so a turasu makaranta amma a sona sai sun cika shekara uku da rabi, amma gashi nan bakin su ya buɗe kawai sutafi yanzu."
Bappa ya jinjina kai kana yace
"Kwarai kuwa ya kama ta kam tun yanzu, tun da ga bakin su nata kan buɗe wa a kai su makaranta yakarasa buɗewar a can"....

A cikin satin akayi musu komai da komai nashiga makaranta, sai dai wata makarantar daban badaga cikin nawa ba, dan *HAM'NAS* International School Of Science Of Technology. suna da nisa saka nin mu, duk da dai shima makarantar da aka sasun yana da ɗan nisa sai dai baikai su nisa ba,
Islamiyar da a kasasu kuma anan unguwar tamu yake.
ranar da zasu fara zuwa kuwa zo kaga murna wajen su, da misalin karfe 7 na safiya Talatu taga

ma shirya su tsaf, Zulai kuma ta shirya musu lafiyayyen breakfast ɗin su.
ina rike da hannun su muka fito in da Talatu ke biye da mu rike da school bag ɗin su da baske, parking lot muka nufa, tun kan mukaraso Yakubu direba dake goge mota yayi hanzarin buɗe marfin motar, cike da ladabi yaɗan duka yana faɗin
"Barka da safiya Hajiya."
"Yauwa barka." nafaɗa cikin ɗan jin nauyin yan da suke yimin idan zasu gaida ni, duk kanin ma'aikatan gidan sun girme min nesa ba kusa ba wasu ma sun haife ni sun juya,nakan ji nauyi a duk san da sukayi min irin wannan gaisuwar.
Nasmah naɗaga nasaka ta cikin motar, Naseem kam cemin yayi shi da kan sa zai shi, Talatu tayi dariya tana saka musu school bag ɗin cikin mota tace
"Naseem iyayen rigima kai bazaka bari a saka ka ba da kan ka zaka shi ka girma ashe".
kai ya gyaɗa yana gyara zama tare da faɗin
"Eh nagima da kaina naciga."
tace "To babban zance ke kuma Nasmah yaushe zaki girma?". Nasmah ta cuno ɗan karamin bakin ta gaba tace "Gobe dan gima ai".
murmushi nayi tare da shafa gefen suskar ta nace
"Au ke sai gobe zakiyi girman naki?". kai ta gyaɗa tana murmushi, kansu na shafa dukansu nace
"To sai an dawo ayi karatu sosai kunji".
sukace to. direba yaja mota ina ɗaga musu hannu suma suna daga min
mai gadi yawangale get suka fita..

Kwana uku kullum cikin ɗoki suke zuwa makarantar ranar na huɗu kuwa ɗoki tafara kare wa, ina kwance sai ga Nasmah ta shigo da gudu ɗaure da ɗan karamin towel ɗin wankan su tahaye gado ta ɓoye a baya na  tana faɗin
"Ni bajan je school in ba."
zanyi magana sai ga Naseem shima da wandon uniform ajikin sa babu riga, sai muryar Talatu daga bakin kofa tana faɗin
"Kai Naseem kazo nakarasa saka maka kayan".
mikewa nayi zaune ina faɗin
"A'a  yaya ne tsaya mana". ai kan kace me shima ya ɗale gadon
cikin cuno baki gaba Nasmah ta daɗa laɓewa jikina tana faɗin
"Ni Mommy bajan je School in ba".
ido na waro ina duban Naseem shima da yake faɗin
"Nima bayan jeba".
kai na  langwaɓar gefe nace
"Oh yanzu wa School ɗin kuke gudu ne, bazaku je ba kuma, yaushe ne kuka fara zuwan da har zaku fara fashin sa?, kuna ji ko kuzo ku je makaranta".
kafaɗa suka make alamar o'o, rungumo su nayi dukan su ajikina ina murmushi kana nace
"Ina kallon da mukayi jiyan naaan na sojojin naaan, to waye meson zama irin su a cikin ku?".
da sauri Naseem ya mike a jikina yana washe baki tare da nuna kanshi yana faɗin
"Nine-nine". "Yau wa to har in kana son kazama soja to ko sai kaje makaranta, kaje makaranta kayi karatu sosai daga nan zaka zamo soja, in kuma baka so to kazauna kawai a gida ina baka

so kazama sojan zauna abin ka kada kaje School".
kai yashiga girgizawa da sauri yace "A'a a'a Mommy ina so to danje School in nine toja".
"Yauwa to kada ka sake cewa bazakaje School ba dan soja baya fashin School, Nasmah ta kefa? baki son zama sojan ne?."
da sauri tace "Ina to." nace "To ke bama soja zaki zama ba Dr Nasmah ce a nan, ina kina so kizamo likita kirika yiwa mutane allura."
ta gyada kanta da sauri, nace "Yauwa kinga in kikaje makaranta kikayi karatu da yawa to zaki rika yiwa mutane allura".
kuma gyaɗa min kai tayi da sauri tun kan in karasa maganar, murmushi nayi ina shafa kansu.
kallon kofa nayi tare da ɗaga murya nace
"Talatu kawo musu uniform ɗin su saka".
daga can bakin kofar in da take tsaye ta waje ta amsa da to kana taturo kofar tare da sallam, nakarɓi uniform ɗin nafara sakawa Naseem rigar sa wan da shi dama ta saka masa wandon shine yagudu,gyara masa zamar rigar nake ina faɗin
"Um kaga soja wannan yaro zai iya rike bindiga in ya girma ya zama soja".
baki yarika washewa yana ɗaɗɗaga kafaɗa da faɗin "Nine toja ai nine toja". "Ai kam ga sojan gasken gaske".
a haka nagama kimsashi
kana nasakawa Nasmah ita ma inata faɗin mata itace Dr zata rika yiwa mutane allura.
nariko hannun su muka fito parlour nan muka iske Zulai da kayan break ɗin su, Talatu kuma ta ɗauko musu School bag ɗin su, muka nufi parking space, da murna suka shige cikin motar Naseem sai faɗi yake
nine toja, Nasmah kuwa ta dube ni tace "Mommy ni meye?". kumatun ta naja nace "Kece Dr me yiwa mutane allura".
sai washe baki suke cike da murna direba yaja motar suka tafi.

Wani sati na gewayo wa muka fara shirin tafiya ziyarar gani da ido nan muka ɗauki hanyar zuwa Lagos,
sai dai wannan karon bantafi da su Nasmah ba saboda School, ni da Bappa da wasu jagorori biyu muka tafi, mun isa Lagos lafiya awani kayataccen hotel akayi mana masauki, mun isa yau washegari muka nufi Company da ake ta kan ginashi tamfatsetsen Company wan da girman sa ya kai ya kawo, an kai ni gurare da dama acikin sa an nunnuna min, masha Allah komai yayi saura kaɗan a kammala.
a gajiye muka koma masaukin mu kansan cewar da kafa akayi ta yawo damu acikin Company'n.
kayan jikina na tuɓe nashiga baya na watsa ruwa kana nafito na sauya kaya na haye gado dan na ɗan huta, waya ta na ɗauka na laluɓo lambar Talatu bugu ɗaya ana biyu ta ɗaga, da sallama bayan mun gaisa nace
"Ina mutanen naki?". tace "Gamu nan muna tare da su a parlour muna kallo, ungo Naseem karɓa ga Mommy tana magana."
tasaka masa wayar a kunne,
"Mommy da mu biki kijo jike da mu".
murmushi nayi jin muryar Naseem nace "To zan zo naje da ku, kuna karato sosai ko?".

kai ya gaɗa, Talatu tace "Ka amsa da baki ai bata ganin ka". yace "Eh." "To a dage sosai, bawa Nasmah wayar." ya mika mata Nasmah tace
"Mommy kina ina, damu biki kije da mu".
nace "Nasmah to zan dawo nazo naje da ku kinji."
"Mommy yaushe zaki jo?."
"Gobe zan dawo naje da ku kinji". to tace, haka sukayi ta zuba min surutu da gwalaɓen su ni ma ina biye misu kun kai minti 30 a haka daga bisani na kashe wayar.
na gyara kwanciya ta dan bacci nake ji.
kwanan mu uku a Lagos muka juya Abuja.

Yau asabar ba makaranta muna tare da ƴaƴana a parlour munata sharholiyar mu cikin farin ciki da jin daɗe, duban daular da nake ciki a rayuwa da nake yin ta yan zu nayi, Allah yabani duniya ya ɗaga ni ya ɗaukaka min daraja ta, a lokacin da duniyar ke kokarin suɓuce min a lokacin da rayuwa ta tazomo tamkar kwai a cikin tray, wan da yazamo  baki-baki saura kiris ya suɓuce kasa ya tarwatse.
numfashi na sauke lokacin da tunanin Inna ta ya zomin, wasu zafafan kwalla ne suka zubo min, Allah sarki Inna ta tabbas na yarda wani hanin ga Allah baiwa ce, ya ɗauke ta a lokacin da nake tsananin bukatar ta arayuwa ta, lokacin da duniya ta juya min baya lokacin da narasa madafar dafawa lokacin da na gwammaci mutuwa ta da rayuwa ta.
ya ɗaukaka darajata abayan bata nan ya azirtani da arziki mai tarin yawa, wa zai iyayin duk wannan in banda *RABBUSSAMAWATI WAL'ARDI*.
Allah sarki Inna ta Allah yakai haske kabarin ki ya sa mutuwa yazame miki hutu.
wasu kwallan nakuma sharewa lokacin da na kuma tunawa da wata uwar wato Mama mai awara, Allah sarki rayuwa
ta cito ni lokacin da duniya tafara wasan kwallo da ni, matar data jajirce wajen ganin an ceto rayuwa ta gun haihuwa, da awancan lokacin bata samo kuɗin da za'a min cs ba wata kila da yanzu na mutu da ni da su duka aciki, tarike ni tamkar ɗiyar da ta haifa a cikin ta. lokacin da tayi nisa wajen ceto rayuwa ta sai ta tsuɓuce min.
sai gashi yau Bappa yamaye gurbin su, yazame min uba kuma uwa,  ya jajirce yatsaya kan lamari na yazamo silar isata matakin danake yanzu, matar sa ta zame min uwa ƴaƴan sa suka zame min yan'uwa.
Rungume su Naseem nayi a jikina ina jin wani irin kuna, rumtse idanuna nayi da karfi jin kaina yana wani irin tsara min, lokacin da tunanin abun da yayi silan rabani da ahalina yashiga yimin yawo a kwakwalwa da zuciya ta. zunbur na mike nashige bedroom ɗina, sam bana son narika tunawa da hakan duk ranar da na tuna nakan kwana cikin kunci da bakin ciki da matsanancin ciwon kai, dan ranar zan kwana ina kuka.

Zubewa nayi kan kado nakife fukata jikin pillow, kai na rika juyawa ina ta fafutukar son na mance da tunanin, amma ina sai daɗe tahomin yake, da karfi cikin karaji narika faɗin
"Wlh Allah Abba ban taɓa ai kata zina ba, Ya SALEEM ba wani ɗa na mijin daya taɓa sani na mace bayan kai, duk da karancin shekaru na Inna ta ta tsoratar dani haɗe da kyamatar dani illan dake cikin zina, Ya SALEEM kai ka sanar dani mene ne aure, a lokacin da kuma nasan mene ne auren akayi min kagen zina aka kuma sheganta min ƴaƴa, bazan taɓa aikata zina ko

da ace bani da aure bare ina da shi ɗin."
wani irin kuka ne ya tsuɓuce min, na kankame jikin pillow'n ina cigaba da kuka mai tsanini.
nakai tsawon awa guda ina kukan kana da kyar na sai-saita zuciya ta na baiwa kai na da kai na hakuri, kana nagyara kwanciya ta wan da ba bacci nayi ba, sai tulin tunani daban-daban.
har yamma ina nan kwance, ganin tunani yana kokarin kassara ni sai na mike nanufi side ɗin su Bappa,
a can na iske su Naseem, har dare muna can sai wajen bayan sallar isha kafin muka koma side din mu.
zuwa lokacin kam naji saukin damuwa ta kwarai dan su Inna wuro sun yaye min shi da hirarsu mai ɗebe kewa.

Washegari Lahadi ma ban yarda na zauna a side ɗi na ba da sassafe na wuce part ɗin su Inna wuro acan mukayi breakfast, a nan nawuni muna hirar mu cikin jin daɗi.

Yau Monday da misalin karfe 7 narako su Nasmah har sai da naga tashin su kafin na koma ciki, ina gama abun da zanyi nawuce side ɗin su Bappa, ina shiga bayan mun gaisa Bappa yake cemin
"Dama yanzu nake da shirin niman ki, kan ai kin masallacin nan ne harfa an rigada an gama shi, wan da aka bashi kwangilar jiya yake sanar min da cewa an gama."
da murmushi sosai kan fuskata nace
"Kai masha Allah kai amma dai ai kin yamin sauri wlh."
Bappa yayi murmushi tare da faɗin
"In dai da kuɗi a kasa komai cikin sauki yake zuwa, in dai da kuɗi ai komai mai sauki ne Allah dai yaba da ikon cin jarabawar da yayi dan shi kanshi arziki babban jarabawa ne, yakan kai mutum wuta yakan kaishi aljanna, kuɗi kamar takwabi yake idan kayi jahadi da shi shigar aljanna mai sauki ne idan ka ai kata ɓarna da shi shiga wuta mai sauki ne, Allah yasa mudace."
Amin Amin. duk muka amsa da shi
cikin washe baki nace
"Bappa masallacin nan fa nagina ne saboda Inna duk ladar arika kai mata kabarin ta, shima asibitin da yanzu ake gina shi idan a ka gama komai kyauta za'a rika yi duk ladar arika kai mata cikin kabarin ta".
"Masha Allah masha Allah".
abun da Bappa da Inna wuro suka rika faɗa kena.
Bappa yace "Ubangiji Allah ya tabbatar mana da hakan Allah yajikanta da rahama ya kai mata dukkanin ladan kabarin ta ya kyautata namu bayan nasu, kai sannu HAMDAH kinyi tunani kwarai da gaske Allah ya saka miki da mafificin rahama."
Amin. nace ina mai jin sanyi da daɗin addu'ar da yake min.

Muna nan zaune a parlour ban ankara ba sai gani nayi karfe 12 har da ɗori,
wayata na ɗaga da sauri ina faɗin
"Ikon Allah lallai guri babu wuya dubi 12 har ta gota an yama Yakubu yadawo kuwa bari dai na kirashi naji."
nayi maganar ina laluɓo lambar sa, wayar tayi ta ring bai ɗaga ba, nakira yakai sau biyar bai

ɗaga ba, na sauke wayar ina faɗin
"Oh to ya ajiye wayar a ina ne shi ga lokacin ɗauko su Nasmah daga School yayi, gashi nayi ta kiransa bai ɗaga wayar ba."
Bappa yace "Ko ina ya aje wayar to shi, ina yaje haka ayi ta kirashin baya ɗaga wa".
nace "Wlh ɗazu ne na ai keshi gidan Hajiya Firdausi matar ministar Bukar, akwai wasu kayan da tayi min tallar su wan da tayi odar su daga jamani, to sun yi min na tura da kuɗin to ɗazu take faɗa min direban ta baya nan ko zan turo nawa direban ya amso min, shine na tura shi to gashi har yanzu bai dawo ba nayi ta kiran shi ma bai ɗauka ba".
nayi maganar ina kuma ɗaga wayar nakuma niman lambar sa.
Hajiya Firdausi matar ministan Abuja ne,
na yar da idan Allah yayi maka rufin asiri babu irin mutanen da bazaka gani ba ka kuma yi tarayya da suba,
ire-iren irin waɗan nan matan manya muna hulɗa da su sosai wasu sun girme min nesa ba kusa ba, wasu ma sun haife ni sun juya amma haka muke cuɗan ya da su.

Mikewa nayi da sauri ganin na kuma kiran sa har sau biyu nan ma bai ɗaga ba, nace "Bappa bari naje kawai na ɗauko su har yanzu bai ɗaga wayar ba, kar suyi ta jira kasan mutumin ka yanzu haka yana kan musu rigimar zai dawo gida".
Bappa yace "Maza hanzarta kam ga guri nata kan tafiya".
da sauri nafita ina shiga side ɗina  mayafi kawai na yafa dan dama a kimtse nake na ɗau ɗaya daga cikin makullen mota da suke cikin drower, da sauri na sauka na nufi parking space.
kana nashiga motar nayi wa motar key, tun kafin na karaso bakin get maigadi ya wangale min get yana fadin "Adawo lafiya".

Saboda yanayin gosulo na bata lokaci sosai a hanya dan har karfe ɗaya ta cika har ta ɗan gota, kafin nan na isa makarantar su.
tun kafin nakaraso get ɗin makarantar, na zubawa kofar makarantar ido sosai dan ganin wasu yara rike a hannun wani mutum "Kamar su".
nafaɗa a file, nayi saurin isowa gurin, da mamaki nazuba musu ido ganin  suɗen ne, yana rike da su suko sai washe baki suke,
shikuma mutumin yana ta tafiya da su yana nufar wata mota dake fake taɗan can gefe da get ɗin makarantar, yayin da yake ta girgiza kai alamun yana jin surutun da suke ta zuba masa.
cikin hanzari na isa gefe nafaka  cike da mamakin ganin nufar motar yake gadan-gadan na ɓalle marfin mota na fita da sauri, cikin hanzari nasoma bin bayansu ina faɗin
"Kai Naseem Nasmah!, malam ina zaka kaisu kuzo nan ku wuce mutafi".
mutumin bai juya ba sai su yaran ne suka juyo sai kuma suka kawar da kansu suka juya suka cigaba da tafiya suna cigaba da zuba masa surutu.
da sauri nasha gaban su gani yan da suka batsar kamar basu sanni ba nace
"Kai ina muku magana kuna jina ina zakuje kuwuce mutafi malam ina zaka kaisu?".
sai sannan mutumin yaɗan dukar da kansa dai-dai tsawon su kana yasoma magana
"Kunsan ta ne?." batare da yaɗago ko ya dube ni ba ya ce "Ke a ina kika sannu bamu hanya mu wuce."
ido na waro cike da mamaki jin abun da yafaɗa tare da mamaita kalmar nasa

"Nasan su? nasan su fa kace, da alla malam ka sake su ina magana kana cigaba da tafiya da su."
gefe na ya gota batare da yace komai ba ya karasa jikin motar nima da sauri na rufa musu baya ina cigaba da faɗin
"Kai malam ina tambayar ka ina zaka kai su wai kana tambaya ta nasan su ne, ni zaka tambaye ni nasan sune, tambaya ta kake nasan su? dalla kasake min yara muwuce,ina ne zaka dasu kake nufar cikin mota da su?,
idan baka sake suba yanzu-yanzu zan kira maka hukuma anan."
baiyi magana ba sai mika hannun sa yayi yabuɗe marfin motar, yaɗau ko kwalin chocolate yaciro chocolate guda huɗu yabawa Nasmah biyu ya baiwa Naseem biyu kana yace
"To ga tsarabar ku kuci wannan yanzu, wannan kuma sai kusa a aljuhu."
yafaɗa yana cusa musu wani chocolate ɗin cikin aljuhun wandon su.
da mamaki nake kallon su ganin yan da sukayi tamkar basu sanni ba, sai murna da tsalle suke suna faɗin
"Ye am bamu da yawa ye am bamu da yawa."
cikin takaici nakai hannu zan fisge chocolate ɗin, da sauri mutumin ya janye su gefe kana yaɗago kansa tare da zuba idanun sa cikin nawa,
wani irin dirrr naji a cikin jikina tamkar jan wutan lantar ki.......!

Mommyn Twins ce

Yan da idanun sa yasarkafu cikin nawa haka babu zato ko sammani shi yasani shiga yanayin, sai kuma na gyara tsayuwa ta da kyau, wani kallo yake bina da shi daga sama har kasa kana yace
"Na ɗauka kafin kiran hukuma ihu zaki yi ta yi kitara jama'a kice ga ɓarawo yazo satar yara, ke ba'a yi miki ihu ba har ke zaki wa wani ihu? karfe nawa ne yanzu wai wannan lokacin ne lokacin zuwa ɗaukar yara a makaranta,abar yara can kowa ya watse sai su kaɗai a cikin makaranta, sabo da baki san abun da kike yi ba an turaki ɗaukar su kin tsaya kin ɓata lokaci a hanya kina damuwar ki wata kila ma kinbi gidan kawayen ki kin gama sharholiyar ki,
kafin nan kika zo wai ke a hakan kinzo ɗaukar su a makaranta, karfe nawa yanzu?. karfe nawa ne yanzu?!".
yakuma nanata tambayar, yana maganar ne ida nunsa a kaina da kuma alamun jaddada tambayon da yake jefa min,
gashi dai maganar cikin faɗa yake yin sa amma lamɓansa a hankali suke motsawa.
dogone yana da faffaɗar kirji da zubin kakkarfan maza, fuskarsa na ɗauke da ɗan siririn saje wan da ya zagaye fuskar nasa har zuwa ɗan gemun sa da bai wuce rabin kamu ba, irin gemun da gayu suke bare.
baza a kirasa da fari soll ba sanna kuma ba baki bane, hasken sa dai-dai.
kwantaccen gashin kansa baki sitif yasha gyara mai tsamtsi da tsulɓi sai wani yal-yal yake, sabo da iskar dake kaɗawa.

Kaina nakawar gefe tare da murguɗa baki nashi a wanne zai zauna yana wani masifa to ina ruwan shi ne ma.
ɗan rutsunawa yayi yarage tsawon sa dai-dai tsawon yaran kana ya dubi ko wannen su yace
"Idan kunje gida kuce wa Mommyn ku kada a sake turo Aunty ku ta ɗauko a School a rika ai ko me wayo yarika ɗauko ku, wan da bazai barku kuyi ta shan wahala a nan ba, kunji ko?."
kai suka gyaɗa suna ta faman shan chocolate "Yauwa to kuje gida sai gobe zan kawo muku wani chocolate ɗin, kada ku man ta in kunje gida kufaɗa wa Mommy kada a kuma turo wannan Aunty'n naku ɗaukar ku a School a aiko mai wayo."
yayi maganar yana yi musu alama da suje in da nake yana binsu da murmushi,
ido na waro cikin masifa nabuɗi baki zanyi magana, dai-dai lokacin mota ta faka gefen mu, da mugun gudu, Yakubu direba yafito da sauri ya iso in da muka yana faɗin
"Ranki shi daɗe Hajiya wlh gosulo ne yatsare ni tun ɗazu babu ta yan da zanbi na koma da baya na canza wata hanyar, gaba da baya motoci suka sani a tsakiya,jibi kumatu na har mari nasha dana nimi in juya dan na canza hanya, Hajiya a gafarce ni, wlh gosulo ne, ita kuma wayar sam na mance jiya da zankwanta bacci nacire ta a kara yau har gari yawaye kuma ban mai da kararta ba, Hajiya ayi hakuri da Allah."
maganar yake tamkar zai zuba guiwowin sa a kasa yana tafa bayan hannun sa a cikin ɗaya tafin hannunsa alamun roko,
banyi magana sai juya wa nayi nanufi gun motar dana zo da ita, dan wannan mutumin yakure ɓata min rai.

Muryar Yakubu naji yana faɗin
"A'a ranka shidaɗe ina wuni barka da warhaka."

bude motar nayi nashige ciki batare da naji amsa gaisuwar da yake yi masa ba.
sai juyawar sa nagani yamatsa jikin motar sa yana kokarin bude marfin gidan baya, da sauri a ka buɗe gidan gaba wani ya fito cikin hanzari yarigasa kai hannu jikin kofar yabuɗe, kana yaɗan ja dabaya ya bashi hanya yashige motar ya mai da murfin ya rufe, kana shi kuma yakoma mazaunin direba yaja motar sukayi gaba.
Yakubu yakamo hannun su Naseem ya kawo su motar da nake yabuɗe gidan baya yasaka su, yace
"Hajiya bari na rufe wancan motar sai na kaiku gida a wannan na hau abun hawa na dawo na ɗauki wanca ɗin."
yajuya da sauri ya nufi in da motar da yazo da ita yake, fita nayi nakoma baya in da su Nasmah suke, yana kulle motar yadawo yashiga mazaunin direba yaja motar.

Munbar harabar makarantar da ɗan nisa kana na juyo na dubi su Nasmah dasuka gama kwaɓe jikin su da chocolate, ganin ina kallon su sai Nasmah ta miko min na hannuta tace
"Mommy akici". cikin masifa nace "Ai sai kun sha duka ba kun iya kwaɗayi ba bakusan mutum ba kuka ma binsa, waya sani ma ko mai satar mutane ne yayi gaba da ku wata kila ma badun na iso da wuri ba da yanzu yayi gaba da ku, yaje yayi kuɗi da kanku,
idan kuka kara ganin mutum baku sanshi ba kuka bishi sai na zane ku, bare har ya baku abu ku karɓa sai na yanke hannun ku, yajaku mota zaiyi gaba da ku Allah ya so ku ai da kuna can Allah kaɗai yasan halin da kuke ciki, badun na iso da wuri ba, ɗan rainin hankali wai arika ai ko mai wayo yarika ɗaukar ku to ina ruwan sa ma daku tukun, mttsss." nayi maganar tare da jan tsaki.
baki Naseem yawashe cikin ɗan sallen murna daga zaunen da yake yace
"Ai Daddy yace dai caya mana mota."
wani irin faɗuwar gaba naji da ya ambaci sunan Daddy da sauri nace "Kai Naseem waye kuma Daddy?." Nasmah ce ta caɓe zancen da fadîn
"Daddy daya bamu chocolate yace dai cayamin jigi haida mota da chocolate da yawa."
da karfi jin yan da zuciyata ke tafarfasa kai na ke sara min nace
"Kai ya isa! idan na kara jin kalmar wani Daddy a bakin ku sai na fasashi, ku bani chocolate ɗin nan."
nafaɗa ina karɓe chocolate ɗin hannun su na zuge glaas ɗin motar nayi wurgi dashi.
maganar Yakubu najiyo wan da tashin hankalin da nashiga ciki yanzu sama-sama nake jiyo shi yana faɗi
"Hajiya ai shi wannan mutumin bamai satar yara bane mutumin kirki ne, shine Ahmad Tijjani Sabil mai kamfanonin nan wan da ake nuna shi agidajen talabijin, ai ko ɗazu dana kawo su makaranta na tarar da motar kamfanin shi tana sauke kujeru dawasu kayan amfani na makaranta,ai kin sa kenan yana da yawan taimako kuma taimakon sa yafi yawa a inda yara suke."
"Ahmad Tijjani Sabil."
na mai-mai ta sunan a raina ina ta son tuna in da nasan sunan, sai a lokacin na tuna ɗazu da safe ake labarai a kansa a gidan tv anan nataɓa jin sunan.
Naseem yace "Ai nima Daddy yace dai taya min mota in tuka akaina."
cikin tsawa nace "Ban ce kada naji wani ya kara min maganar wani Daddy anan ba?, rufamin

baki idan ka kara sai na fasa ma baki bari ka gani."
Yakubu kuwa ci gaba da zuba yake wan da ma gaba ɗaya hankali na baya cikin motar da jikina gaba ɗaya.

Muna komawa gida nakira *HAM'NAS* Store Complex nace a kawo min motar wasan yara guda biyu da wasu kayan wasa, batare da ɓata lokaci ba motar ShopRite ɗin ya iso, a ɗakin kayan wasan su aka jibge musu,
ihun murna suka sake ganin motocin cikin tsallen murna Naseem yace
"La iyin motan da Daddy yace dai taya mana babba."
da sauri na mike daga kan kujerar da nake zaune cikin ɗakin kayan wasan su, hannayen su duka na riko nadawo na zauna, inajin zuciya ta na min mugun ɗaci da kuna a duk san da naji sun furta kalmar Daddy a bakin su,
duban su nayi dukan su nace
"Kuna ji ko Naseem Nasmah?, shi wancan mutumin ba Daddy'n ku bane baku sanshi ba kuma ku bakuda Daddy, nice Mommy'n ku kuma nice Daddu'n ku bakuga na siya muku mota ba, idan kuka sake faɗar Daddy bazan sake siya muku mota ba, kuma zan sa akwashi waɗan nan ma a tafi dasu, baku da Daddy nice Daddyn ku kunji ko?."
kai suka gyaɗa nace "To maza kuje kushiga motar ku." ai ko da sauri suka ruga in da motar suke suka shiga,
ina tare da su a ɗakin sai zaga ɗakin suke a cikin motar, suna dariya.
numfashi nasauke ganin suna cikin farinci sosai, Nasmah ta danna motar ta motar tatafi tsuu zata garu da jikin garu-bango da sauri na mike na tafi da gudu na taro ta, na ciro ta ciki ina faɗin
"To ya isa haka muje kuyi wanka kuci abinci sai kuma anjima zan sa afito muku da shi can tsakar gida kuyi wasan acan."
nayi waje da su.

Yau Juma'a da wuri Talatu tagama yi musu shirin makaranta, narako su har sai da motar kaisu makaranta yafita kafin na juya a hankali, gaba ɗaya yau jikina baya min daɗe a hankali na isa bakin swimming pool na cire takalmata gefe na zauna bakin swimming pool ɗin na zura kafafu na ciki, a hankali nake motsa ruwan da kafata ina ɗan lilashi ciki, wasu hawaye ne masu ɗumi suka zubo kan fuskata banyi kokarin sai da su ko danne zuciya ta daga abun da take jiba, tun jiya nake jin kai na cikin yanayin ina so nayi kuka ko zanji sassaucin abun da nake ji cikin zuciya ta, sai dai ban sami damar yin kukan ba saboda su Naseem, sam bana so nasaka musu rauni cikin zuciyar su, dan aduk san da irin wannan damuwar ta taso cikin zuciya ta zama nake a ɗaki nayita kuka, aduk san da sukaga ina kuka sun rika tambaya ta me ya same ni idan nayi shiru ban basu amsa ba ko nace musu babu komai suma sai su fashe da kukan su rungume ni muyita kukan.
tabbas ina ganin rauni da damuwa aduk san da hakan tafaru agare su, duk da kuwa kasan cewar su yara wan da basu san komai ba, amma nasan akwan atashi idan hakan yaci gaba da faru zasu tashi da abun a ransu,
nasan ɗaci da kunar dake tattare da kuncin ganin UWA cikin damuwa game da ɗan ta, dan kuwa shike hanani sukuni a koda yaushe.
wasu hawaye ne masu zafi da kuna suka cigaba da wanke min fuska cikin jan sheshsheka

nashiga faɗin
"Ummi na kizauna gidan Abba Ummi bazan taɓa yafewa kai na ba har idan nayi sana diyyar barin ki gidan Abba, Ummi na zancigaba da yin nesa dake har idan hakan zai sa ki cigaba da zama gidan Abba."
kuka sosai ya kwace min cikin muryar kukan nacigaba da faɗin
"Abba wlh ban ai kata zina ba ban taɓa ai kata zina ba, Abba zan cigaba da yin nesa daku har idan hakan zaisa Ummi na tacigaba da zama agidan mu, bana so nayi maraicin uwa batare da tabar duniya ba,
Abbu Mamie Ya Masa'ud Auny Rafee'at Aunty Jaleela Nusaiba Fauzaun, kewan ku da begen ku yana hanani sukuni,kullum da ku nake kwana cikin raina, shin haka kuma kuke kewata ina son ku ko da yaushe ina tare da ku a cikin zuciya ta,
ku yar da dani wlh ƴaƴana ba shegu bane, wlh Allah ban taɓa zina ba,
Allah sarki Inna ta da kina nan da kin faɗa musu kalar tarbiyyar da kikayi min wan da ko da agidan karuwai zan zauna bazan yi iskanci ba, bazan yi ba, bazanyi ba,
Ya SALEEM Ya SALEEM Ya SALEEM me na tare muku kai da matar ka meyasa zaka rabari da *MAHAIFIYA TA* karabani da ahalina me nayi muku, me yasa zaka sheganta min ƴaƴana tsaftatattu ka dan ganta su da wani uba wan da bansan ko waye shiba,
duk hakan na menene da har sai ka kazanta min ƴaƴa? ƴaƴa na ba kazan ta bane kamar yadda ka faɗa ƴaƴana tsaftatattu ne bazan taɓa yafe maka Ya SALEEM bazan yafe maka b...."

Kuka ne yaci karfi na nakifa kaina da guiwa na nayi ta kuka kamar raina zai fita.
najima sosai zaune a gurin ina ai kin kuka, mai cike da kuna da bakin ciki. da kanshi hawayen ya tsaya badun na tsai da shi ba, sai dai kukan zuci danake, a hankali na mike cikin matsananciyar ciwon kai wan da dakyar nake iya buɗe idona duka sabo da zafin ciwon kan, na nufi ciki.
direct bedroom na shige kana shiga bathroom wanka nayi nafito na sauya kaya na zo na kwanta bakin gado,
karatun Alkur'ani na kunna cikin wayata a hankali nake bin karatun, a sannu narika jin zuciya ta tana samin salama da nutsuwa, a hankali narika jin bacci na fizgata ta, na lumshe idanuna.
can cikin baccin da ya ɗauke ni da nisan ta baifi na minti 20 ba.
najiyo muryar su Nasmah, da gudu suka haye gadon suna faɗin
"Mommy mun dawo Mommy mun dawo."
ida nuna na rumtse da ɗan karfi dan har lokacin kai na bai bar yimin ciwo ba,
mike wa zaune nayi jin sun zube a jikina na ɗago su ina faɗin
"Wai har kun dawo? amma dai ba'a tashi ba ko."
nayi maganar ina duban agogo, karfe 12 har da rabi,nayi mamakin gani in da lokaci yatafi har haka, ranar yau karfe 12 saura suke dawowa har sun dawo anyi musu wanka an sauya musu kaya.
lallai najima ina kuka har ban san lokaci yatafi har haka ba, tausayin kaina ya kamani, ɗan guntun kwallar da ke kokarin sauka a idona ɗaya nayi saurin kai yatsata na tare shi kana na gyara zama ta ina faɗin
"Ashe dai lokacin tashin naku yayi, to yaya karatu yau ansha wasa ko."
nayi maganar ina shafa kansu.

baki Nasmah ta washe ta mike tsaye a kangadon tace
"Mommy yau Aunty'n mu tayi mana haka."
tarike kugu tare da girgizawa, dariya nayi ina faɗin
"Au kice yau Aunty rawa tayi muku."
"Ba haka bane haka ne".
Naseem yafaɗa tare da mike wa yarike kugu yasoma tsalle.
ido na ware nace "Kai kuce yau kunsha rawa." cikin tsallen yace "Eh ai hadda chocolate ma."
tsai da tsallen da yake yayi sai kuma ya dira a godon da gudu yafita sai gashi ya dawo da School bag ɗin sa, a tsakiyar gadon ya zazzage School bag ɗin sai ga Chocolate masu yawa haɗe da littattafan sa sun zubo,
da mamaki nace
"Yau kuma Talatu kayan zaki tacika muku a jakar."
nakai hannu na ɗibo chocolate dasuka kai guda biyar kala daban daban, ga kuma wasu a gaban sa, da ɗan mamaki nake kallon su dan asanina babu kalar waɗannan chocolate ɗin acikin kayan cime-cimen su kalar nasu ba irin wannan bane.
"Kai Naseem a ina ka samo waɗan nan chocolate ɗin?."
nayi maganar ina duban sa, da sauri Nasmah tace
"Nima akwai nawa." ta dira agadon da gudu tayi waje, Naseem ko bai bani amsa ba sai kokawar buɗe laidar chocolate ɗin yake.
ta shigo da school bag ɗin ta itama ta zazzage, nace
"Kai wai waya baku wannan abun haka, Talatu Talatu."
nashiga kwaɗawa Talatu kira dan na fara tunanin ko rikici sukayi mata gun shirya su tabuɗe wani katon ɗin chocolate ɗin daban.
Naseem da yakai Chocolate ɗin baki ya kutsura yana ɗaga kafaɗa alamun yana jin daɗin abun yace
"Daddy yace mucinye wannan duka dai kaya mana wani."
"Ai yace idan ka kaiɓa min baye kaya maka ba ni de bani da yawa."
cewar Nasmah tana kai wan da ta ɓare baki.

Ido da baki na waro da mamaki tuno wan da suka taɓa kiran sa da Daddy a makarantar su nace
"Wani Daddy mutumin nan ko?, a ina kuka san shi dan gidan ku da har zaku rika ce masa wani Daddy."
Naseem daya cika chocolate a bakin sa yace
"Ai Daddy yace  kuma dai jo ya auke mu ya kai mu can guyin kifi babba."
cikin tsawa nace  "Bana ce muku kada wani yasake baku abu ku karɓa ba? ashe bakuji ba so kuke nazane ku ko?, bana ce muku nice Daddyn ku nice Mommy'n ku ba, shi ba Daddy'n ku bane, baku san shiba shima bai sanku ba, bakuda Daddy nice Daddy'n ku, kuna jina dai ko?."
 nariko kunnuwan su ina jijjigawa a hankali, suka gyaɗa kai.
shiru nayi tare da komawa na jingina bayana da jikin gado jiki a sanyaye nashiga maganar zuci
"Kuhi hakuri ƴaƴana ni zan cigaba da zame muku uwa kuma uba a duniyar na."
jin kwalla nakokarin zubomin nayi saurin dakatar dashi...

A ranar nasa aka kawo musu chocolate dawsu kayan makulashe aka kara kan wan da yake

gida.
washegari ranar asabar bamu wuni a gida ba yawon guraren shakatawa muka tafi, ni Faty Naseem Nasmah da kuma Talatu, sai direba. sai yamma muka dawo niki niki da kayan makulashe, washegari ranar Lahadi ma muka kuma fita, shima sai yamman muka dawo a part ɗin su Inna wuro muka yada zango sai bayan isha muko koma side ɗin mu, ai ko muna shiga su Nasmah suka ɓingire da bacci.
koda gari ya waye dakyar nata da su Talatu ta tafi da su dan yimusu wan ka da shirin makaranta, dan tare jiya muka kwana da su.
kamar kullum na rakosu muna ɗagawa juna hannu suka fita.
ina komawa ciki wanka nayi nashirya cikin les copie colour da ɗan ratsin gold ajiki,
da misalin karfe 10 da rabi nasauko kasa da mayafi akai na sai ƴar karamar jaka mai ɗauke da wayoyina da wasu ƴan kuɗi dana saka ciki,
dinning area na nufa, in da na tadda Zulai tagama shirya komai na breakfast, a ɗan gaggauce nayi breakfast ɗin, ina yi ina duba agogo, dan fita zamuyi da Bappa zuwa asibitin da ake ginawa dasunan Inna ganin yan da ai kin ke tafiya, ina saurin ne dan jiya nace mishi karfi goma da rabi zamu tafi nasan kuma yanzu haka yagama shiri ni yake jira.
koda na fita a kofar masallaci dake ta nan cikin gida na taddashi zaune, na karaso in da yake tare da gaida shi, daga nan muka shige mota muka nufi asibitin.
masha Allah asibiti yayi kyau saura kaɗan a kammala aiki, bamu bar asibitin ba sai wajen karfe 12:20pm nacewa Yakubu muwuce makarantar su Nasmah mu ɗauko su.

Abakin get ɗin makarantar Yakubu ya faka mota yafita da sauri yana faɗin
"Bari naje na fito da su". yayi cikin makarantar da sauri, muna nan zaune can yafito da sauri kamar zai kife kasa yakaraso gefen da nake yace
"Hajiya wai an zo an ɗauke su."
ido na waro da mamaki nace "Wa yazo ya ɗau kesun bayan kai muna tare da kai ina ce kai ne me zuwa ɗaukar su."
Bappa yace "Zancen banza kai wani direban akayi musu sabo ne da zaizo ɗaukar su? ko dai bakaji abun da suka faɗa da kyau bane?."
yace "Wlh haka mai gadin yafaɗa Bappa."
da sauri Bappa ta buɗe motar yafita ai ko nima da sauri nafita narufa masa baya har ina haɗawa da sassarfa.
babu kowa cikin makarantar sai mai gadi da masu kula da tsaftar makarantar sai shara da goge-goge suke, hankali tashe Bappa ke tambayar mai gadi, mai gadin yace
"Ai ko minti goma basu da tafiya ba duk ɗazu muna tare da su anan da wasu ɗaliban mota tazo tafaka nan bakin get suna ganin motar suka zuba a guje zuwa gurin motar suna murna, da naso hanasu dan ganin ba ɗaya daga cikin irin motocin da ake zuwa ɗaukar su da shi bane, to ganin yan da suke ta murna sukayi gun motar a guje yasa nayi tunanin ɗaukar su a kazo, dama badaga gida akazo ɗaukar su ba!."
maigadi yakarashe maganar yana buga kirji.
Yakubu da gumi yafara keto mishi kamar zai fashe da kuka yace
"Ina ni ke zuwa ɗaukar su kuma gani a gaban ka sai kuma hajiya wata rana,ko mutumin yasako irin fuskata ce ya zo."

Bappa yace "Amma kuwa abun da mamaki amma ya kamata lokacin da kaga ba ɗaya daga cikin motocin da ake zuwa ɗaukar su da shi bane yazo kama yayi kaje kaga ko waye ne,amma wani abun mamakin da kace wai sun je gurin motar da gudu kuma suna murna to ko wani ne daga gida yazo ɗaukar su tun da sun san mun fita har da direba?."
ni dai kasa magana nayi sai ɓari da jikina yake cikin matukar tashin hankali tuni idanuna suka kawo ruwa kan kace me hawayen suka fara sauka.
murya na rawa Yakubu yashiga tafa hannu da salati yana faɗin
"Dama ance yanzu masu garkuwa da mutane sun canza salo akwai wani abun da suke yi sai dai kaga mutum na ta binsu kamar ya sansu harsu tafi da shi, wayyo Allah Naseem da Nasmah ko dai sune."
cikin gwalalo ido mai gadi yace
"Wayyo Allah nashiga uku wayyo ai kina shikenan dama ance idan aka sami matsala to abakin ai kina, ashe dama tsarin da masu garkuwa da mutane suka fito dashi kenan? shi yasa yarannan sukayi ta tsalle kamar doki suka ruga in da motar take, ashe jansu ake taciki kamar kuran karfe."
ɓarin jikina ne yakaru yayin da zuciya ta ke bugawa da karfi gudun hawaye na yakaru.
Bappa yace "Kai ya isa haka Falyakum khairan au yasmuq, in sha allahu babu abun da zai faruku muje gidan mugani wata kila daga gida ne akazo aka ɗauke su tun da sunsan bama gidan."
yadube ni yana cigaba da faɗin
"Kice Innalillahiwa'inna'ilaihirraji'un."
kalmar nashiga nanatawa kana muka juya gun mota, muka bar maigadin nan tsaye yana ta rafka salati dafaɗin shikam yau yasan ai kin sa yazo karshe har in sace yaran akayi.
acikin mota Bappa yarika zuba addu'o'i yakuma hanani kukan danake shirin yi yace nayi ta faɗin Innalillahiwa'inna'ilaihirraji'un.
a haka muka isa gida.

Muna isa Yakubu yayi hon maigadi ya wangale get yana kokarin wucewa parking lot nace
"Ka sauke mu anan."
dan gani nake kamar motar bata tafiya da sauri tsabar tashin hankali.
tun kan ya dai-dai ta parking muka fito daga motar maigadi yakaraso yana mana sannu batare da dukkanmu mun amsa ba Bappa yayi saurin cewa
"Wayaje ya ɗauko su Naseem a makaranta a cikin ku?."
maigadi yace "Gaskiya babu wan da yaje ɗauko su dan tun da kuka fita ma babu wan da yafita, yau kam sunsha zama a makaranta Yakubu  yayi hanzarin zuwa ɗauko su."
"Innalillahiwa'inna'ilaihirraji'un an ce anzo an ɗauke su kuma kace ba wan da yafi tun fitar mu an sace su kenan."
nayi maganar tare da fashewa da kukan da Bappa ketasa ni danneshi, nacigaba da faɗin
"Ina suke ina suka shiga waya ɗauke su.".
maigadi ya walalo ido tare da faɗin
"Iye! ansace su!."
Bappa yace "Ka tabbatar da babu wan da yafita."

yace "Wlh babu wan da yafita tun fitar ku ina bakin get ɗin nan........!

Mommyn Twins ce

7

HMD WASA FARIN GIRKI!

Littafin na siyar wa ne kibiya ki karan ta my no 08034690723

Mai gadi yashiga jan hanci yanaci gaba da faɗin "Sam babu wan yafita ai da nasani dana shiga ciki naje na karɓi makullin mota naje na ɗauko su ai, na ɗan iya mota ba sosai ba amma da wasu su ɗauke su gara ni naje a haka na ɗauko sun, wasu matsiya tane masu niman jaraba suka ɗauke su, duk tai makon da akewa mutane baiyi musuba har sai sun haɗa da sata, wayyo Allah Naseem wayyo Nasmah, ashe da rabon ragowar shayi da nama gobe bazan shaba, kullum sai sun kawo min na haɗa da nawa duk na  kallame."
zuwa yanzu tashin hankalin Bappa yafara bayyana  yashiga faɗin
"Kanu innalillahiwa'inna'ilaihirraji'un Allahumma ahjirni fi musibati²."
bakina na toshe da tafin hannuna jin kuka mai sauti yana son suɓuce min najuya ina kokarin barin gurin Bappa yakira sunana najuyo ina hawaye yace
"Je ki zauna kada ki ɗaga hankali sosai na tabbata zasu kira kuma bazasu cutar da su ba dan kuɗi suke bukata za'a kuma basu babu komai."
kai kawai na gwaɗa najuya nasoma tafiya, maigadi yabiyo ni yana cigaba da jan hanci yace
"Anyi bako Hajiya."
 ban iya juyowa ba bare nabashi amsa Bappa ne yace "Ina bakon?." yace "Gashi can a mota yana shigowa kuma kuka shigo,"

"Wanene?." cewar Bappa, yace
"Gashi can cikin mota ai da naso hanashi shiga ganin baiyi kama da irin waɗan da za'a dakatar ba shine na barshi ya shigo."
yayi maganar yana nuna wata mota dake fake gefe a farfajiyar gidan.
Bappa ya girgiza kai kana ya soma tafiya yana faɗin.
"Ana cikin wani hali ta ya za'ayi a saurari wani bako."
Cikin matukar da muwa da tashin hankali nake tafiya, "Me zaisa su ɗauke su in dai kuɗi ne akan su ɗauke su  ni da sun faɗa min ko nawa ne zan basu, me yasa suka zaɓi su cutar da yaran da basujiba basu gani ba.
wlh Allah sai yabi musu kadin su tun suna ciki ake cutar dasu da zaluntar su, har suka fito duniya."
wasu zafafan kwalla ne suka rika wanke min fuska bana ko iya ganin gabana, tunani na ɗaya awani hali suke yanzu..
Bappa har ya wuce motar da mai gadi yace masa bako ne ciki, sai kuma ya dawo sanin da yayi kan cewa bako rahama ne,
gilashin motar ya kwankwasa, a hankali aka zuge glass ɗin.
cikin matukar mamaki Bappa ke lallon mutumin da waɗan da ke tare da shi, yana zaune a mazaunin direba waya na rike a hannunsa yana ta faman latsawa, Nasmah na zaune a gefen sa tasaka kanta jikin kafaɗar  sa tana ta cin chocolate, Naseem kuwa na zaune a gefen mai zaman banza rike da waya a hannunsa yana buga game yana kuma taunar chocolate.
cikin tsananin matukar mamaki Bappa ke cigaba da kallon mutumin da mamakin ganin sa tare da su Naseem,
tabbas bazai taɓa mance wannan fuskar ba, mutumin daya samar musu da ingantaccen ilimi a rugar su,mutumin da ya yayi ruwa yayi tsaki wajen ganin an cafke ƴan ta'addan da suke shiga rugar su suna kaɗa musu shanukai su kashe musu makiyaya.
cikin girmamawa mutumin yashiga gai da Bappa, Bappa ya amsa fuska ɗauke da annuri yana yi masa kallon sani, shiko mutumin ga duk kan alamu bai gane shiba, cike da al'ajabin ganin su tare da su Nasmah Bappa yace,
"Ikon Allah kai ne nan tare da su Naseem da muke zaton ko ƴan garkuwa da mutane ne suka ɗauke su."
da sauri Bappa ya juya yana faɗin
"HAMDAH taho gasu nan."
cak naja na tsaya dai-dai lokacin dana ke kokarin ɗaura hannuna jikin kofar side ɗina, najuyo da sauri, magana Bappa yaci gaba dayi yana nuna cikin motar.
"Gasu nan cikin mota Allah yayi ikon sa."
dagudu na nufo gun motar ina share hawaye na da bakin mayafi na,
ina isa gun motar nawuce gaban Bappa da sauri batare da duban cikin motar ba duk da glass ɗin motar a sauke take, hankali na nakan murfin motar dana saka hannu ina kokarin buɗe motar sai jin ta nayi a rufe, da sauri na ɗago karaf idanun mu ya haɗu da juna, da mamaki nake kallon sa sai kuma nan take naji raina ya ɓaci,
mutumin da yace wai arika turo mai wayo yarika ɗaukar su Naseem a school ba ni ba, wan da kuma suke kiran sa da Daddy yayi ta tara musu chocolate kamar sun zama shazumame sar kin shan zaki.

fuska na ɗaure tamau ina duban su Nasmah nace
"Ku sauko nan!." nayi maganar cikin tsawa da zare idanuna.
Bappa yaɗan matso yana faɗin
"Wlh mun shiga tashin hankali sosai da akace wani mota daban yazo ya ɗauke su ba ɗaya daga cikin motocin gidan nan ba, mungama zaton masu garkuwa da mutane ne, suka ɗau ke su."
kai ya jinjina tare da yin murmushi wan da yayi sana diyyar bayyanar kyakkyawar dimple ɗin fuskar sa, batare da yayi magana ba ya kai hannu ya buɗe marfin motar, baya na ɗan ja kaɗan ya buɗo marfin, ya zuro kafafun sa waje, Nasmah dake gefen sa yaɗago ta cak yafito da ita ya aje ta kasa, kana asannu yafito daga cikin motar,tsayuwar sa ya gyara kana yaɗan sunkuya jikin kofar yamika hannu cikin motar Naseem ya rike hannun nasa yaɗago shi cak yafito da shi, sai da ya ajiye Naseem kasa kana ya ɗago da murmushi yace.
"Idan za'a cigaba da barin su har kowa ya watse a makaranta ba'a je ana ɗaukar su kan lokaci ba to kuwa zasu iya fuskantar hakan,domin su masu garkuwa da mutanen babu ta in da basa nan."
kai Bappa ya jinjina cike da gamsuwa da maganar sa kana yace
"Tabbas kuwa, Allah yashiga sakanin nagari da mugu."
a kufule nace
"Babu ranar da ba'a zuwa ɗaukar su kan lokaci in ban da ranar da nayi ta kiran Yakubu bai ɗaga ba, sai kuma yau, yau ɗin ma ai bawani makara akayi ba tun da karfe 12:50pm muka isa makarantar kuma karfi 12 da rabi ake tashin su, kuma tun kan ɗalibai su watse mai gadi yace aka ɗauke su, to ashe dai ba'a makara zuwa ɗaukar su, ana zuwa ɗaukar su tun shabiyu ajira su har sai an tashe su a ɗauko su a dawo da su, babu wani ɓata lokaci a zuwa ɗaukar su, kai kuwuce mushiga ciki!."
nayi maganar cikin haɗa haushi biyu zuwa uku, akan me zaice ba'a zuwa ɗaukar su kan lokaci. sannan kuma wace dalilin ne yasashi zuwa ɗaukarsu ina ruwan shi dasu dakuma rayuwar su, yasa nayi kuka da tunanin ansace su ne. sannan ganin yan da yaran suka manne masa sai kiran sa da sunan dana hanasu suke.
tun da nafara maganar idanunsa  akaina yayin da yake shafa sajen fuskar sa, kafaɗa yaɗaga kana yace
"Kinyi kokari, kiyi wayon sanin hakan tukun dan da kaɗan kikafi yaran wayo."
ido na waro amma lallai mutumin nan yana da rainin wayo karo na biyu kenan da yake cemin wai bani da wayo, yaran dana haifa yake cewa wai dakaɗan nafisu wayo. wani kallo na watsa masa tare da murguɗa baki nace "Allah yasa wayon suka fini, mece ce matsalar ka?."
nayi maganar tare da kuma murguɗe baki.
Bappa yace "Um to hakane kam amma ana zuwa ɗaukar su akan lokaci sai dai ɓacin rana, amma akiyayen shiyafi, mun gode sosai, in sha Allahu za'a kara azama wajen zuwa ɗaukar su."
hannunsu na fizgo ina faɗin
"Kuzo ku wuce ina magana kuna tsaye."
najanyo su fuuu muka nufi ciki anan na barsu shi da Bappa, cikin haushin jin Bappa yana saurarar sa, har shi zai gwada wa mutane yan da zasuyi da rayuwar su, ina ruwanshi, irin mutane masu shegen shishshigi kan abun da bai shafe su ba.
sai da muka shiga parlour kafin na sake hannun su, na zauna kan kujera, ina duban su sukam

ma ko a jikin su sai wata tsafgar su suke.
kunnuwan ko wannen su na rike naɗan murɗa da karfi, suka haɗa baki wajen cewa "Wayyo Mommy."
nace "Sai na sinke kunnen har idan baku dai na abun da na hana kuba, wato duk hanaku da nake tayi bakuji ba ko shine yau abun naku yagirma har da binsa, kunsan shi ne? baku san mutum ba kukama binsa har da shiga motar sa, ina kuna so a yanka kanku ne?."
kai suka girgiza da sauri tare da faɗin
"A'a-a'a Mommy." nace "To ban hanaku ce masa Daddy ba bana ce muku ku bakuda Daddy nice Mommyn ku nice Daddyn ku ba?, ban ce kada wani ya sake baku abu ku karɓa kuci ba?, shine har yau zaku bishi kushiga motar sa, kunsan shine?,
to sai nayi muku duka yau sai na kaiku wa ɗawisu ta caccake ku bari ku gani."
namike tsaye tare da ruko hannun su ina cigaba da faɗin
"Ɗawisu kawai zan kai ku wasu sune zasu yin maganin ku."
kuka suka sake da karfi suna faɗin "Wayyo Mommy kai ki kai mu."
"Ai bazaku bari ba sai na kai ku gurin su su hana ku da kansu."
nayi maganar ina jansu.
ihu sosai suke suna faɗin
"Mommy mun bayi." komawa nayi na zauna kan kujera ganin sun tsorata sosai najasu jikina na rungume su, ina faɗin
"To kuyi shiru nafasa kai ku amma idan kuka kara sai na kaiku, zaku kara ko?".
kai suka girgiza da sauri nace "Kada ku sake zuwa gurin wan da baku sanshi ba bare har kushigs motar sa, kuma kada ku sake ce masa Daddy shi ba Daddyn ku bane nice nan Daddyn ku kunje jo?."
kai suka kuma gyaɗa wa suna jan shashsheka.
a hankali narika shafa kansu cikin tsananin tausayin su, wasu zazzafan kwalla ne suka ciko ido na, ban dakatar da su ba har sai da suka gangaro kan fuskata ta, nakai tafin hannuna na goge, yayin da nake daɗa mannna kan su a kirjina, ina jin tausayin su na daɗa shiga na.
maganar zuci nafara yi yayin da zazzafar hawaye mai cike da ɗin bin kuna ke cigaba da zuba a ido na.
"Kuyi hakuri bana so ku sanya wa ranku abun da babu shi a rayuwar ku, nafiso ku tashi da sanin cewa bakuda shi ni zan zame muku garkuwa uwa uba."
daɗa rungume su nayi ina jin kuna cikin raina lallai tabbas ba shakka anyi min tabo mai muni ni da ƴaƴana wan da bazan taɓa mancewa da shi a rayuwa ta ba.
kwallar idanuna na share tare da kokarin danne damuwa ta.
ɗago wa nayi jin sallamar Bappa na amsa ina mai cigaba da kokarin danne damuwar dake azalzala ta cikin zuciya, naɗan gyara zamata cikin dabara na share ragowar hawayen idona, ya karaso ya zauna. huf su Nasmah suka mike a jikina Naseem daya dubi Bappa yace "Bappa Daddy fa yana waje?." sai kuma ya juya da sauri yana faɗin
"Dan je guyin Daddy." ido na ware da mamaki kamar ba yanzu nagama masa barazana har da kukan sa ba amma gashi ya tashi yana faɗin zai je gurin mutumin.
Bappa yayi murmushi da faɗin
"Dawo nan mutumina, ai yatafi." yafaɗa yana ruko hannunsa kana ya cigaba da faɗin
"Yaro kenan shi kamar dabba yake duk mai kyautata masa to zakaga yana son kasan tuwa da

shi,
wlh nayi mamakin ganin Ahmad Tijjani Sabil, nakuma yi mamakin ganin sa tare da yaran nan, koda yake hakan ba abun mamaki bane."
da ɗan mamaki na dubi Bappa jin sunan mutumin a bakin sa, Bappa ko daɗa faɗaɗa murnushin dake bayyane kan fuskar sa yayi kana yaci gaba da faɗin
"Yaron kirki ne sosai kinga ma bai ganeni ba sai da nayi masa tuni,
ai wannan yaro Allah dai ya masa albarka yakawo babban gudunmawa cikin rayuwar mu a Ruga, ya inganta mana rayuwa yakawo haske cikin rayuwar mu kwarai da gaske, lokacin da ɓarayin shanu suka addabe mu babu dare babu rana, sukashe mana makiyaya su kaɗa mana shanukai, kwasam sai Allah yajefo mana shi, wata rana yazo rugar mu a matsayin bako watan sa guda tare da mu, ranar da yazo ɓarayin shanu suka shigo rugar mu, suka saci shanukai suka raunata mana makiyaya Allah yatakai ta kwanan su na gaba, sai dai mun rasa makiyayin mu guda ɗaya kuma mun san su suka sace shi, ya kwashe su yakai su asibiti cikin gari, ranar hankali yatashi muka ɗau aniyar ɗaukar mataki da kanmu.
ranar da ya cika sati uku, har lokacin ɓarayi basu kara kawo mana hari rugar muba sai dai rugar da muke makota da su,
da yammacin ranar an je kai masa abinci kamar yadda aka saba sai aka iske shi da wani makiyayin mu cikin ɗakin da aka bashi yake kwana ciki, makiyayin da muke tunanin ɓarayin shanun nan sun tafi da shi, ya ɗaɗɗaure shi, yanata gana masa azaba da wani irin na'ura.
wan da yakai abincin yakurma ihu nan da nan jama'a suka taru munyi mamakin ganin makiyayin mu tare da shi yana bashi azaba,nan ƴan gari suka rika cewa a kashe shi ashe shima ɓarawon shanu ne muke tare da shi.
cikin tsawa yace duk mudakata yace kunzo nan kuna ta wani har gowar ku mara amfani kuje ku tare ƴan ta addan da suka dunfaro rugar ku domin kona ku su kuma tafi da dukiyar ku. cikin rashin fahimtar abun da yake nufi muka shiga kallon junar mu, shiko ci gaba da baiwa makiyayin mu azaba yacigaba da yi, dai-dai lokacin kuwa muka soma jin karar bindiga daga can nesa, nan fa hankali yatashi jama'a suka fara kokarin watsewa domin ɗaukar makamin kare kansu.
wani irin gigitaccen kara makiyayin nan ya saka lokacin da ya datse masa yasar hannun sa guda,
cikin tsawa yace masa, Ta wani kusurwa zasu shigo,? su nawa ne kuma?, wasu irin bindigogi ne a hannunsu?!!.
cikin tsananin jin azaba yasoma magana cikin matukar wahala yashiga bashi amsar tambayar dayayi masa.
munyi matukar mamakin jin abun da makiyayin nan yafaɗa to me haka yake nufi?, a lokacin bamu sami damar jin amsar tambayar muba,
sai muryar AHMAD Tijjani Sabil mukajiyo da karfi yana faɗin.
Kowa ya koma gidan sa kada wani yafito waje,duk abun da zakuji kada ku fito. kamar yadda yafaɗa kuwa haka mukayi batare da musu koni man jin ba'a si ba kowa yayi gidan sa, sai dai bamu zauna haka ba kowa da makami a hannusa domin kare kai.
ranar tashin hankalin da muka shiga ba zai faɗu ba, dan muna shiga gida ƴan tadaddan nan suka karaso cikin rugar mu, wasu suna kunce dabbobi wasu kuma suna ta harbi.
shigowar su dakamar minti ashirin, muka jiyo jiniyar sojoji ta ko ta ina suka sanya rugar mu a

tsakiya.
nan suka shiga bata kashi ranar kamar rugar mu zata fashi dan harbin bindiga, an ɗauki tsawon mintina 30, kafin kikaji guri yayi tsit.
sai hayani ya da magana da turanci haɗe da hausa ake,
can aka fara magana da abun sauti irin wan da hukuma suke magana da shi domin sanar wa ko bada umurni wa al'umma,
aka ce kowa ya fito, nan muka fito cikin ɗar-ɗar duk da asanar wan nasu sun sanar mana da cewa hukuma ne ke magana,
amma a tsorace muke kuma bamu fito haka kawai ba sai da makaman mu, domin kare kai, duk da kuwa munsan su bindiga ne a hannusu mukuma akasin haka sai dai munsan Allah yana tare da mu.
koda muka fito ganin hukumar ne da gaske nan hankali yaɗan kwanta kaɗan, Allah yabasu nasarar cafke ƴan tadaddan nan wasu daga cikin su sojojin sun harbe su gasu kwance cikin jini, wasu kuma gasunan kwance a ɗaɗɗaure bindigogin su a zube a gefe.
Ahmad Tijjani Sabil yana tsakiyar hukuman nan yayin da wannan makiyayin namu ke kwance a gabansa shima a ɗaɗɗaure.
bayan jawabi da ban hakuri da hukumar nan sukayi mana, da alkawarin bamu kariya da tsaro, suka tattari ƴan ta'addan suka saka su cikin mota, Ahmad ya ɗaga wannan makiyayin namu yatura shi cikin mota,
nan wasu daga cikin sojojin suka tafi da ƴan ta'addan suka bar motan soja guda.
ranar acikin rugar mu suka kwana suna bamu tsaro kwanan su uku kafin suka tafi,
Ahmad kuwa bai bar rugar ba har sai da yagina mana makaranta da asibiti yazuba mana malaman asibiti  dana makaranta, makarantar ne ma Fatu take ciki, tun daga lokacin muke samin tsaro sosai, munyi matukar farin ciki da zuwan Ahmad cikin mu dan kuwa ya tallafawa rayuwar mu kwarai da gaske, har rana mai kamar ta yau ba'a kuma shiga rugar mu da sunan sata ba."

Numfashi na sauke cike da alhinin labarin da Bappa ke bani nace
"Ikon Allah to shi wannan makiyayin naku yaya iyayen sa sukayi dajin shima ɗan fashin ne, yanzu ku duk zaman ku da shi bakusan shi ma ɗan fashi bane?".
yace "Sam bamusan ɗan fashi bane, to ai shi asalinsa ma ba bafulatani bane, zuwa yayi rugarmu tun yana yaro yace zai rika yi mana kiwo muna biyan sa, shekaru 16 muna tare da shi, muka bashi duk wani yar da ashe macuci ne bamu sani ba, yana ha'intar mu, har sai da Allah ya turo mana Ahmad Tijjani Sabil."
kai na jinjina cike da mamaki ina faɗin
"Tab lallai to shi ya akayi yasan ɗan fashi ne shi da yazo bai jima ba, ku da kukayi shekara da shekaru da shi baku sani ba?."
Bappa yace "Wlh duk kanin mu kowa abun da yayi ta faɗa kenan bayan komai ya lafa, sai dai bamu sami amsar tambayar ba, dan ko shi Ahmad ɗin da muka tambaye shi bamu sami wani kwakkwaran amsa ba, sai muma muka bar shi bamu tsanan ta masa tambayar ba, munji daɗi da farin cikin da Allah ya nufa shi zai zame mana karshen matsalar mu."
Bappa yana maganar ne cikin nuna tsantsar farin ciki da jin daɗi...
na ce "Lallai kam to Allah ya tsare na gaba."

ya am sa da amin amin kana yamike yana faɗin "Bari na shiga ciki."
yana tafiya naruko hannun su muka haura sama...

Yauma kamar kullum narako su Naseem ina tsaye har sai da naga fitar su,
kana na koma ciki, wanka nayi ina gama kimsawa nayi breakfast, wan da nasa Zulai takawo min shi cikin ɗaki,
ina gama breakfast ɗin nahaye gado dan bacci ne a idanuna
ban farka ba, sai wajen karfe shabiyu saura ƴan mintina dabasu fi 20 ba, wayata na janyo na kira Number Yakubu, kasan cewar yau juma'a da wuri ake tashin su, bugu ɗaya ana biyu ya ɗaga, nace
"Kayi maza kaje ka ɗauko su Nasmah." yace "To Hajiya da ma nima yanzu ina kan goge motar kenan yanzu zan tafi."
"Kabar wani goge mota katafi kaje ka ɗauko su." nayi maganar tare da kashe wayar, mikewa nayi nashige bathroom nayi wanka tare da dauro al'wala, ina fita na sauya kaya.  ganin lokacin salla da saura sai na nufi kofa nafita kasa na sauka.
Talatu da Zulai duk suna parlour'n suna ganina sukayi min sannu da fitowa,na amsa ina yi musu yaya aiki, suka ce alhmdllh, an tsaftace gurin ko ina yayi tsaf sai kamshe ke tashi.
ina jin matukar daɗin zama da su sabo da suna baiwa aikin su kulawa sosai.
a ɗaya daga cikin kujerun parlour'n na zauna, tare da saka idanuna kan TV ganin shirin da ake.
zamata baifi da minti 10 ba najiyo muryar su Naseem daga kofa ta waje suna kwaɗa sallama, kallon kofar nayi da murmushi akan fuska ta, suka turo kofar da gudu suka shigo suna faɗin
"Mommy mun dawo Mommy mun dawo."
faɗaɗa murmushi na nayi tare da faɗin
"To sannun ku da dawowa."
in da nake suka taho da gudu na buɗe hannuna suka faɗo ciki na rungume su, ina dariya da faɗin
"An yi karatu sosai dai ko?."
kai Naseem ya gyaɗa. nace "To madallah." na dubi Nasmah nace "Likita na anyi karatu sosai ko?." itama kai ta gyaɗa tana washe baki, Naseem ko baki ya turo yace "Mommy ni baki ce min tojan ki ba."
cikin muryar dariya nace "Oh soja na."
shima dariyar yayi cike da jin daɗin sunan dana kira sa da shi.
Nasmah ko mikewa tayi a jikina tarike kugu tare da jujjuya idanun ta tace
"Ai nafi Naseem yin kayatu da yawa  yana ta wasa da wani yayo, ni nayi kayatu da yawa dan yika yima mutane ayyuya kuma."
ido na waro yan da take yi da ido ya bani dariya nace
"A.a.a Naseem ɗin wato wasa kaje ka zauna kake yi ba karatu ba ko?".
nayi maganar tare da rike haɓa ina kallon sa, yace
"Hum kaiya ne take yi, nayi kayatu da yawa kuma Daddy yace nayi kayatu da yawa idan nayi da yawa da yawa, yace dai jo ya auke mu a gida."
Nasmah tace "Um ai Daddy yace ni ne dai jo ya auke ni nafika kayatu da yawa, ai nayi mishi kayatu da yawa ma yau kuma."
Naseem yayi kamar zai ture ta yana faɗin

"Ai nima nayi ma Daddy kayatu da yawa."
ido na waro da mamakin kin sunan da suke ambata sunan da nayi ta musu barazana kan kuma faɗar sa, nace
"Kai kurafa min baki, wani Daddy'n."
nayi maganar cikin tsawa dan ni a tunani na ma wani ne daban ba wancan mutumin da na kwaɓe su da shi ba.
Yakubu da yashigo rike da school bag ɗin su yakaraso ciki Talatu ta amshi jakar tayi cikin bedroom ɗin su da shi, ya washe baki da faɗin
"Ai Hajiya Ahmad Tijjani Sabil suke nufi, ai ina isa na iske su tare da shi abakin get din makarantar su tare da shi, naji yana tambayar su karatu suna ta zuba masa karatun da aka musu, nace kai ashe fa yaran nan za'ayi masu ilimi ne anan wlh kuwa."
yayi maganar yana mai cigaba da washe baki.
fuska na tsuke sosai tare da mai da dubana kan yaran kana na mike tsaye na ruko hannun su na janyo su muka haura sama,
muna shiga ɗaki na sake su ina faɗin "Ni ƴasu yazan yi da yaran nan wato ku bakwa ji, duk abun da zanyi ta faɗa muku bazaku jiba shi wannan Ahmad yake ko wane wlh dole na ɗau mataki a kansa, idan bana ɗau mataki akan lamarin ba zai rushe min ginin danake ta gina shi, yana ta kokarin rushewa ya haka ne kam, ina ruwan shi da su meye haɗin shi da su da zai rika sanya musu wani ra'ayi a cikin zukatan su."

Duban yaran nayi nama rasa wani irin masifa zan musu, ko da na musu ma abanza gobe zasu kuma,
zubewa nayi bakin gado da tunanin yan da zanyi na ɓullo wa lamarin, yazama dole na ɗauki mataki kan lamarin idan ba hakaba, to kuwa tabbas ginin da nake ta kokarin gina shi domin yayi karko to kuwa zai iya rusa min shi, tabbas zan ɗauki mataki kansa, "Amma mene ne mafita?.
nayi wa kai na tambayar ina gyara zama ta,
"Mafitar kenan kawai ki canza musu makaranta."
zuciya ta ta bani amsa, kai na jinjina da gaskata abun da zuciya ta ta faɗa min, hakanne kawai mafita ta yadda zasuyi nesa da shi, idan kuma ba haka ba to kuwa abun da nake ta kokarin cire masu kwaɗai tar sa a zukatan su shine zai faru, dan kuwa in har hakan yaci gaba da faruwa zasu tashi da sanin wani mahaifi a ransu wan da bana son su san haka, nice nan uwa kuma uba a rayuwar su, sam bana son su tashi da jin cewa zasu sa mi uba ni zasu cigaba da jina uwa kuma uba a rayuwar su.
bana so su sanyawa ransu abun da baza su samu ba a rayuwar su, to mene ne amfanin sanya wa ransu hakan,
gara kawai su san cewa ba su  da uba, su ji a ransu ni ce uban nasu kuma ni ce uwan su.
wannan kaɗai shine mafita in sauya musu makaranta in nesan tar da su daga gare shi, in ma koyarwa yake a makarantar imma mene ne baya sake ganin su bare ya cigaba da cusa musu wani ra'ayin, ai dai sun rabu bashi basu, bazai sake ganin suba suma haka bare su sake kiran shi da wani Daddy,
"Ɗan rainin wayo har da cewa surika ce masa wani Daddy, sai kace wani uban su ko meye gamin sa da su oho."
naja dogon tsaki tare da yin kwafa kana na mike, nashiga tuɓe musu uniform ɗin su, ina faɗin

"Ku da shi ɗin duk zanyi maganin ku."
bathroom na jasu da kai na nayi musu wanka yau, muka fito na saka musu wasu daga cikin kayan su da yake bedroom ɗina, sai da na nagabatar da sallar azahar kana na janyo su muka sauka kasa.
dinning area muka zarce bayan munci abinci najasu muka tafi part ɗin su Inna wuro, nan muka tarar da Faty ita ma dawowar ta daga school kenan, nan muka yada zango mukata hira...
da yammacin ranar zaune nake a parlour'n sama na ɗago wayata na laluɓo number shugaban makarantar su Naseem.....!

Mommyn Twins ce

8

Nan nake shai da masa bukata ta nakan canza su Naseem makaranta.
shugaban makarantar nasu yace "To ba bubu da muwa amma dan Allah muna so musan dalilin da yasa ake son sauya musu makarantar ko kuma makarantar tamu babu koyo ne yan da ya kamata?".
nace "Ko kaɗan ba haka bane ba kawai dai ina so ne na canza musu makarantar ba wai kodun rashin koyo ba, ai ba za'a ce makarantar ku babu koyo ba, yara suna fahimta sosai, kawai dai yaɗan yi nisa ne."
yace "To in dai kuwa haka ne to dan Allah kada a ciresu a makarantar gaba ɗaya, akwai ɗaya makarantar mu dake wata unguwa mafi kusa da ku in dai kina so sai a maida su can ɗin, ranar Monday idan suka zo sai ayi transfer ɗin su can ɗin."
shiru na ɗan yi cike da nazarin maganar sa, sai kuma nace
"To shi kenan a mai dasu can ɗin."
har munyi sallama zan kashe wayar yayi saurin cewa
"Dan Allah Madam a daure a kawo su sai a kaisu wancan makarantar, idan akace an cire su gaba ɗaya kokon to zai shiga zukatan iyayen yara zasuyi zaton ko wani matsala ce mai girma aka samu cikin makarantar, tun da bawai barin garin zakuyi ba,

zamu iya samun dakilewar customer, adai duba lamarin da kyau Hajiya."
"Babu damuwa in sha Allah za'a kawo su sai a kai su wan can ɗin."
godiya yashiga yi min kana mukayi sallama na kashe wayar.

Ina sauke wayar number Ukhtee na kira yayi ta ringing ba'a ɗaga ba,nakuma mai da kiran shima har yakusa yanke wa kafin ta ɗaga, da sallama.
na amsa cikin harshen larabci nace
"Oh kai Ukhtee ina kika aje wayar haka ina ta kiranki baki ɗaga ba?, ko yanga kike min an ce miki ni saurayin kine."
dariya tayi tare da faɗin
"Saurayi kuma haba dai kedai wayar tana bedroom ne nikuma ina parlour, nama shigo ɗaukar abune cikin ɗakin naji wayar tana ring, ai da haka zaki ta kira ma ban sani ba, ya kuke ina yarana suke?."
"Lafiya lau duk muna lafiya, yaran ki suna can gurin Bappa sunki biyo ni suna can suna damin sa da surutu, ni nagaji da hirar ne nadawo side ɗina naɗan huta suna can."
larabcin nake ina ta haryaɗa shi.
dariya tayi jin yan da nake ta kwamusa larabcin, tace
"Oh kin dawo kasar ku yaren kasar ku yana so ya korar miki da yaren kasar muko?."
nima dariyar nayi tare da faɗin
"Ashe kin gane inata yi da kyar amma fa su Naseem sunanan da shi a bakin su domin makarantar isilamiyyar su larabci zalla ake, shi yasa yake nan zaune a bakin su."
tace "Kai naji daɗi wlh gara ai su zauna da larabcin a bakin su, ke kizauna da yaren kasar ku tun da shi kika zaɓa."
nace "To ya zanyi mahaifa ta dole naso yare na ke ma ba kina son yaren kiba?."
tace "Sosai ma."
"Oh to shine nima baki so naso nawa yaren."
mukayi dariya. hira kukayi tayi sosai da Ukhtee wani maganar idan nayi ita zata gyara min shi dan larabcin bai gama nuna baki na ba.
sai can da jinawa mukayi sallama.

Yau Monday kamar yan da nasa ba na rako su Nasmah gun mota, Yakubu dake goge motar yayi saurin buɗe motar nasaka su ciki,bayani na yiwa yakubu kamar yan da mukayi da shugaban makarantar su idan sun je za'a haɗa su da wani domin yayi musu jagora zuwa ɗaya makarantar.
ina tsaye ina ɗaga musu hannu har suka fita...

Kai tsaye Yakubu yaɗau hanyar makarantar, kamar koda yaushe hira yake da yaran yanata washewa da dariya kamar yan da suma suke ta washe baki.
suna isa bakin get ɗin makarantar yayi parking yafito, kana ya buɗe musu suka fito, suna fita suka shige cikin makarantar direct office suka nufa daga nan aka haɗa su da wani malami da zai kai su ɗaya makarantar, suka fito tare.
suna fita bakin get ɗin school ɗin,
wata lafiyayyi zazzafar mota tayi parking a gefe, tun kan motar ta kakarasa parking Naseem

yafara murna yana faɗin
"Laa ga Daddy yazo laa ga Daddy yazo."
Nasmah ma kuwa ihun murna ta sake tare da sa gudu sukayi gurin motar.
da sauri ya buɗe motar ya fito yaware hannayen sa ai ko da gudu suka shige jikin sa ya rungume su, duk suka saki dariya har dashi, kana ya mike yashiga ɗaga su yana cillasu sama sai kya-kya ta dariya suke.
sai da yayi wa kowannen su haka har sau uku kana yadire su kasa,
Yakubu ya karaso in da suke yana washe baki da faɗin
"Ranka shi daɗi barka da war haka."
amsa wa yayi fuska a sake sai dai gaba ɗaya hankalin sa na kan su Nasnah da suke ta zuba masa surutu.
shima wannan malamin da aka haɗo su da shi ya karaso yana faɗin
"Barka da zuwa yellaɓoi."
yace "Yau wa, yaya ji da ɗaliban?."
malamin yawashe baki tare da faɗin
"Muna kai kam."
yace "Masha Allah."
malamin ne ya dubi yakubu da kuma yaran yace
"To muje ko."
yayi maganar yana duban motar su.
sai a lokacin Ahmad ya ɗago da kallon sa kan yaran yadawo da shi kan su Yakubu kana yace
"Ina kuma za'a je ba makaranta za'a shiga ba?".
yayi maganar yana shafa kan su Naseem.
malamin yace "A'a zamu tafi da sune ɗaya makarantar mu."
duban sa Ahmad ya kuma  da alamun tabbayoyi ɗauke a fuskar sa,
kana yace "Wacce makarantar kuma?."
yace "Ɗaya daga cikin makarantar mu ne za'a mai da su."
da fuskantar mamaki Ahmad yace
"Har sun gama wannan makarantar ne da za'a tura su wata makarantar daban?."
kai malamin ya girgiza tare da faɗin
"A'a ai za'a sauya musu makarantar ne anyi musu transfer can ne."
ɗan shiru Ahmad yayi kana yace
"Malam ɗin yana ciki?."
kai malamin ya gyaɗa tare da faɗin
"Eh yana ciki." yace
"Okay to muna zuwa." yafaɗa tare da gyara rukon Naseem da Nasmah a kowani hannun sa guda, ya janyo su suka shige cikin makarantar.

Malamin ya dubi Yakubu dake ta washe baki yace
"Wai nikam da ma ƴaƴan Ahmad Tijjaji Sabil ne kake kawowa makaranta?."
Yakubu ya daɗa washe baki yace "A'a ƴaƴan me *HAM'NAS* Company ne fa."
"Au ƴaƴan mai *HAM'NAS* Company ne to shi Ahmad Sabil dangin su ne? lallai Allah mai yin yan da yaso yahaɗa family guda da tarin dukiya."

Yakubu yace "Eh ƴan uwa ne."
yafaɗi hakan ne kawai dan bashi da amsar bashi, dan shi kansa bai isa yace suna da dangan taka ko basu da shi ba, a matsayin sa na mai ai kin gidan ba lallai dole yasan dan gin gidan ba, san nan kuma baya so ya disga kan sa gaban malamin, ko ba komai shi ma za'a rika yi masa kallon wani...
suna nan tsaye
zuwa can Ahmad yafito shi kaɗai batare da yaran ba.
ido suka zuba masa ganin yafito shi kaɗai, yakaraso in da suke, duban malamin yayi tare da faɗin
"Ka koma kacigaba da koyar da ɗaliban ka, kai kuma ka koma gida ka dawo da wuri ka ɗau ke su."
yakara she maganar da duban Yakubu.
Yakubu yace
"Ranka shi daɗe hajiya tace na tsaya sai mun  kai su kafin na komo gida."

Yace "Kar ka damu kaje ka abin ka."
yace To. yashiga mota in da tuni malamin ma yakoma cikin makarantar.
shiko Ahmad a hankali ya isa jikin motar sa ya shige ciki...

Da misalin karfe 12
a hankali na mike na shige bayi wanka nayi haɗe da ɗauro al'wala nafito,nashirya cikin wani doguwar rigar atamfa pauda da man lip kawai na goga sai turare dana fesa a jikina,
a hankali na isa jikin window labulen window'n naɗan janye shi gefe tare da zuge glass.
ido na kurawa furannin da suke ta kaɗa wa gwanin ban shawa,
idanuna na sauke can bakin get jin karar buɗe get ɗin, da murmushi nake kallon kofar,
dan nasan su Naseem ne suka dawo, ɗan gimtse annurin fuska ta nayi ganin ba motar kai su makaranta bane wata motar ne daban ta shigo.
a sannu motar ta isa ta gyara parking a gefen farfajiyar gidan,
an ɗau tsawon minti 10 kafin aka buɗe motar,
ido na waro cikin tsananin mamaki da shiga shoc ganin wan da yafito daga cikin motar, cikin matukar kufula nake kallon sa yayin da yazaga ɗaya gefen ya buɗe, sai ganin Naseem da Nasmah nayi sun fito daga cikin motar suna ta washe ba ki.
"What! me nake gani haka, yaran da nasa a canza musu makaranta domin sa wai bin su yakuma yi?."
cikin matukar ɓacin rai nasaki labulen da sauri na juya nafita a ɗakin na nufi kasa,
da sauri na ke sauka har ina haɗa step cikin hanzari nakarasa sauka nayi waje da sauri.

Suna tsate jikin mota sai zuba masa surutu suke shiko sai binsu da murmushi mai haɗe da dariya yake,
tun kan na karaso in da suke nashiga faɗin
"Kai malam wai meye hakan ne, wai meye gamin ka da yaran nan ne kam?!."
dai-dai lokacin na iso in da suke, kugu na rike cikin masifa nacigaba da faɗin
"Meye da lilin ka na wani shishige musu da kake kana ta wani cusa musu

wani ra'ayi meye nufin ka da su?."
maganar nake a tsai-tsaiye kuma cikin ɗaga murya cikin masifa nakuma faɗin
"Bana bukatar wani ya raɓe su da manufa irin naka kagane ko malam?."
tun da na fara maganar ido kawai ya zuba min batare da yace komai ba, idanun sa kan lip ɗina,
a sannu yaɗan yi baya ya jin gina bayan sa jikin mota hannayen sa ya sarkafe a kirjin sa,
harshen sa yaɗan zuro waje yalashi pink lip ɗin sa,
har lokacin fuskar sa na ɗauke da murmushi wan da dimple suka daɗa kawata annurin fuskar sa.
cikin kuma ɗaga murya na dubi su Naseem nace
"Idan baku wuce kun shiga ciki ba na rantse sai na ɓaɓɓala yaro anan gurin ku wuce mutafi nace!."
nafaɗa ina nuna musu hanya.
Nasmah tace "Mommy ja mu jo."
ido na waro wato ma na jira su kenan sai sun gama abun da suke.
shiko wani murmuahi yakuma sakewa.
tsayuwar sa ya gyara tare da duban yaran kana ya mai da duban sa kai na sannan yafara magana
"Zaki ɓalla su?."
ya faɗa tare da kuma sakin wani murmushi kana ya ɗan sun kuya yarage tsawon sa dai-dai tsawon yaran ya dubi ko wannen su yace
"Kuje ciki ayi muku wanka kuci abinci ku kwanta ku huta kuyi bacci idan kun tashi kuyi karatu gobe zan tambaye ku karan tun da kukayi kun ji ko?."
kai suka gyaɗa masa suna faɗin
"Tom." yace "Yauwa to maza a je ciki."
Naseem yace "Daddy dakajo anjima?."
kai yagyaɗa yana mai cigaba da wannan murmishi wan da kamar da shi aka gina fuskar sa yace
"Sosai ma zan zo mana."

Cikin hatsala haɗe da ɓacin ran ganin yau ma kamar na ranar da na same su tare da shi a kofar makarantar su, ina nayi musu magana sukayi kamar basu san ni ba,
sai shi da suke ta biye masa suna bashi amsar duk abun da yace musu,
bugu da karin bacin raina kiransa da sunan dana hane su a gabana.
cikin tsawa nace
"Kai Naseem me nace maka waye Daddy'n ka wato bakaji ba ko, ban ce muku kada ku kuma cewa wani Daddy ba, wato duk maganar da nake muku aban za bakwa ji ko, idan naji kasake cewa wani Daddy sai na fasa maka baki,wuce mutafi nace!."
ko da nake masifar harlau idanunsa a kai na, sai ya saki wani murmushin gefen baki yayin da gefen kumatun sa na dama ya lotsa, har kuma lokacin yana rike da kafaɗar su.
a sannu yaɗan sun kuyo yadubi Naseem kana yakuma dubi Nasmah kana yakuma sakin wani murmushin sannan yace
"Naseem Nasmah mene ne ma suna na?."
suka haɗa baki wajen cewa "Daddy Daddy tunan ka."

yace "Kai yaran nan to Allah yayi muku albar ka, to maza ku tafi ciki ayi muku wanka kuci abinci maza kuje."
ya faɗa yana tura keyar su.
ai ko da gudu suka yi ciki suna dariya, ganin rainin wayon nasu da yawa yake wato umurnin sa ma zasubi ba nawa ba. nadube shi tare da rike kugu nace
"Kai malam kana ji ko, kada ka sake zuwa in da yara na suke kada ka sake kasake zuwa in da suke, kada ka sake cusa musu ra'ayin cewa wai kai Daddy'n su ne, kai ba Daddy'n su bane basuma san ka ba, ni ban gayyaci wani acikin lamarin ƴaƴana ba,karabu da harkar yara na idan kuma ba haka ba wlh zan ɗauki tsatstsauran mataki a kanka, kada ka kuskura ka sake zuwa in da yara na suke, kada ka sake yi musu karya kan abun da ba haka bane, bana kara kan haka dan ƴaƴana nice kaɗai uwan su kuma uban su,
dan Allah malam kada ka sake cusawa ƴaƴana wannan gurguwar ra'ayin, ka gane ko?!."
na karashe maganar da nuna masa yatsa haɗe da murguɗa masa baki, na juya a hatsale ganin duk maganar da nake madadin ya shiga taitayin sa sai ma daɗa sakin wannan murmushin nashi yake.
tafiya na soma cikin fushi dan nalashi takwabin yau sai na zane yaran nan tun da har ni zasu gwadan wani yafi ni muhimmanci agurin su har zasu ji maganar sa akan nawa.
sai jin maganar sa nayi daf dani
"Kece uwan su kuma uban su to ya akayi kenan hakan ta faru, ke kika ba kan ki cikin kenan,faɗa min da ma a she mace tana bawa kanta ciki da kanta, dama a she uwa tana bawa kanta ciki ita kaɗai batare da uba ba??."
wani irin juyi nayi jin sautin sa kusa dani batare da zato ko sammani ba, maganar yashige ni tamkar shigar shoc cikin jini na, wani irin mugun kallo na watsa masa tare da jan dogon tsaki, najuya na nufi kofar side ɗina da sauri...
shiko bayana yabi da wannan murmushin kana ya juya yashige motar sa yaja yabar gidan.

Koda na shiga banbi takan su Naseem ba dan nasan koda na yi musu hukuncin danayi niyyar ma bashi zai sa su dai na abun da na hanasun ba,
sai kawai nashige ɗaki nazube bakin gado, kamar an zabure ni kuma na mike na isa gaban mirror in da wayoyi na suke ajiye, number Yakubu na kira, nafara zazzage masa masifa
"Wato Yakubu dana ce kaje ka ɗauko su shine bakaje ba kabar wannan ɗan rainin wayon mutumin wai Ahmad yake ko wa yaje ya ɗau ko su ko?,
idan ka gaji ne kafaɗa sai a sallame ka."
da sauri yatari numfashi na da faɗin
"Dan Allah Hajiya kiyi hakuri wlh yanzu haka ina hanyar dadowa ne ina ma kokarin kiran ki kenan sanar miki sai ga kiran ki, naje makarantar aka ce min yazo ya ɗauke su, ai Hajiya baki sani bama ɗazu da zamu kai su sabon makarantar yazo ya mai da su cikin makarantar yace mutafi mu barsu anan."
ido na waro da ɗinbin mamaki mai haɗe da mugun ɓacin rai,
ban san san da na dakawa Yakubu tsawa ba nace
"Dalla malam ya isa ni da kai na nace ayi abu kan ƴaƴana sannan wani can daban yazo yace ba hakaba kai kuma ka yarda, umurnin sa kabi kenan? ok to ka wuce gidan sa daga nan kaje can yacigaba da baka umurnin!."

nakashe wayar rai ɓace,
"Lallai ma wato ashe ma ba'a kai su makarantar ba shike nan ya hana ko me?."

Afusace na danna number shugaban makarantar yana ɗagawa nace
"Malama ya zan ce ga abun da nake so sannan kuma wani yazo ya hana kuma ku amin ce, to gaskiya daga yau bazama su sake zuwa makarantar ba ma sun fita kenan."
da sauri yace
"Ranki shidaɗe mahaifin su ne yazo yace kada a canza musu makarantar bawai yin kan mu bane."
kashe wayar nayi jin raina yadaɗa ɓaci.
dogon tsaki naja tare da yin kwafa nama kasa cewa komai saboda sabar bakin ciki,sai dai naci alwashin daga yau baza su sake zuwa makarantar ba,
zan mai da su *HAM'NAS* International School Of Science And Technology.

After 1 week

Tsawon sati guda agida suka yishi ranar Lahadi nasa aka kawo musu uniform na *HAM'NAS* International School Of Science And Technology.
washegari Monday da misalin karfe 7 aka gama kimsa su tsaf,
muna tsaye a parking space, daga can na ɗagawa Faty hannu da fito war ta kenan daga side ɗin su, nayi mata alama da tayi sauri, ta Kara so da sauri, tace
"Ina kwana Adda HAMDAH." murmushi nayi tare da faɗin "Lafiya lau antashi lafiya."
"Lafiya lau." tafaɗa tare da
duban su Nasmah tace
"Yau yara sun koma School ɗin mu."
hannun ta Nasmah tarike taɗago kanta tana duban ta tace
"Aunty Faty School inku akwai lilo?."
Faty tace "Eh har da abun zame-zame da mota mai lilo da doki mai lilo."
tsalle Naseem ya tuma yana faɗin
"Yeee nine zan shiga moto in tuka ku."
dariya duk mukayi, na dubi Yakubu dake ta faman goge mota, nace
"Dan Allah kabar goge motar nan haka in ba halitta zaka sake masa ba, kutafi haka kada kasa su makara,kuma dai kaji abin da na faɗa maka wlh aka kuma samin wata matsalar duk wani hakuri da magiyar ka bazai maka amfani ba."
nayi maganar ne cikin jin haushin sa na rannan dan da kyar na hakura da hakurin da yayi ta bani.
da sauri ya bar goge motar yabuɗe marfin motar yana faɗin
"Zo ku shiga Naseem, wlh hajiya in sha Allahu baza a sake samin wata matsala ba, wancan rabar ma tsautsayi ne, dakuma ganin shi babban mutum ne a kasar nan shiyasa ban masa musu ba, dan gudun kada yasa a kwashe ni akai ni gidan maza,
dan musu da babban mutu awannan zamanin haɗari ne."
tsaki naja tare da faɗin

"Kabari zai kai ka karshen ɗauri kenan."
najuya naso ma tafiya ina ɗagawa su Nasmah hannu da cigaba da faɗin
"Kaɗai ji abun da na faɗa maka."
yace "Kwarai Hajiya, ai daga yau bazaki sake jin wata masala ba."
ban kuma bi ta kan sa ba nawuce part ɗin su Inna Wuro."

A parlour na tadda su Bappa suna breakfast na zauna nima bayan mun gaisa Inna Wuro tazubo min kayan breakfast ta turo min gabana, nan nashiga ci muna ɗan taɓa hira.
Bappa yace
"Mutanen sun tafi makaranta ko?."
nace "Eh sun tafi." Bappa yayi murmushi tare da faɗin "Yanzu kam an bar kuka idan za'a tafi."
"Dama ai rashin sabo ne yanzu kam an saba."
cewar Inna wuro. Bappa yace "Hakane kam wai me yasa ne aka sauya musu makarantar ko yayi musu nisa ne? ko da yake *HAM'NAS* International School yafi shi nisa, me ya sane?."
"Babu tsaro yan da yakama ta a makarantar shi yasa."
nafaɗa a takaice.
Inna wuro tace "Hakkum gaskiya sabo da Allah kam ya kamata su kara sa ido kan ɗaliban su, susan duk wani wan da zai kawo ɗalibai yakuma zo ɗaukar su, duk da dai ranar Malam yace min mutumin kirkin nan ne Ahmad Tijjani Sabil yaje ya ɗauko su ake tunanin ko masu garkuwa da mutane ne, amma dai ya dace sosai su sa ido kan ɗaliban su."
kai kawai na jinjina batare da nace komai ba,akasan raina kuwa faɗi nake
"To waya sani ma ko mai satar mutanen ne dole zan sa jami'an tsaro cikin gidan nan tun da har ya fara shiga cikin gidan nan yana leken asiri."
maganar Bappa dana ji shi ya kashe min zancen zucin danake
"HAMDAH har yanzu banji kin ce komai ba kan maganar mu ta rannan,
Yakamata yanzu kam kiyi aure ki fidda miji na gari kiyi aure, domin darajar ki yadaɗa ninkuwa, kwanakin can munyi maganar nan bakice komai ba,
daraja da kimar hace baya ɓata cika cif har sai tana tare da abokin rayuwa wato mijin aure."
tea ɗin da na kurɓa ne nahaɗiye shi da kyar, sam bana son jin wannan kalmar gaba ɗaya naji nakoshi da abincin a hankali na mai da cup ɗin na aje kana a hankali nasoma magana.
Bappa aure kuma, ai ni bazan yi aure ba rayuwa ta a haka tafi min."
yace "A kul ɗin ki kada na sake jin wannan maganar, a wannan shekarun naki zaki ce baza kiyi aure ba, nutsuwa bata taɓa cika sai da abokin rayuwa, kiyi na zari sosai ga abokan kasuwancin ki da suke zuwa gidan nan, ko wannan Alhj Muttari nan ai mutumin kirki ne ko ranar yaso yimin zan cen sai dai bai fito muraran yayi maganar ba,
in yaso sai ku dai-dai ta kiyi auren ki kamalar ki ta daɗa cika."
Inna Wuro tace
"In ban da HAMDAH ma ai mutane basu taru sun zama ɗaya ba, dan wani abu yafaru da rayuwar auren ki na fari bashi zai sa nan gaba yakuma faruwa ba,ai Allah baya taɓa jarabtar bawan sa da abun da bazai iya ba, duk kuma musulmi an sanshi da karɓar kaddara me kyau ko mara kyau,
ki gode masa ta hanyar kuma kara yin wa ni auren."
"Hmm." kawai nace dan bana jin kamar abun da suke faɗan zai kasan ce, har can kasan

kololuwar raina bana jin zan kuma aure, babu abun da natsana a yanzu kamar aure.
meye acikin auren ban da tashin hankali da musifa, in dai har aure nutsuwa ce kamar yan da suka faɗa to gara na tabbata ni bani da wannan nutsuwar.

Duk wani nasiha da jan hankalin da su Bappa suke jin su kawai nake,dan a yanzu babu abun da nafi tsana ma kamar aure!.
sai da na bari suka gama yi min nasihar kafin na mike nace dasu zanje na ɗan kwanta kafin su Naseem su dawo, abin cin da ban karasa ci ba kenan nafito.
ina fita daga side ɗin wata mota na shigo wa cikin gidan, a hankali na ke tafiya har na iso in da motar tayi parking kasan cewar dole sai nabi ta hanyar kafin na wuce side ɗina,
ina isa dai-dai in da motar take sai ji nayi an.......!

Mommyn Twins ce

9

An buɗe murfin motar,  baya na ɗan yi da sauri dan kaɗan ya rage marfin ya bige ni, kasan cewar nazo daf da motar sosai. da sauri na ɗago dan ganin wan da ke cikin motar, ido na waro da ɗinbin mamaki ganin mutumin da su Nasmah suke cewa Daddy ne, tsayuwa ta na gyara ganin yazuro kafar sa waje yafito daga cikin motar,baki na buɗe cikin masifa ganin yan da yayi kusan bige ni da murfin motar sa, "Malam ya haka baka ganine?."
nayi maganar ina yi masa kallon sama da kasa.
tsayuwar sa ya dai-dai tare da mai da murfin motar ya rufe, kana yashiga nuna min yatsa tare da kaɗa yatsar yasoma magana.
"A kan wani dalili zaki rika birkita wa yara ƙwaƙwalwar su, kinyi yunkurin sauya musu School abaya, ba'a baki dama ba shine kika ajiye su a gida tsawon sati guda, sannan kika sauya musu Makarantar, ilimi kike so su samu ko kuwa birkita musu ƙwaƙwalwa kike son yi, kada ki kuma yunkuri da tunanin sauya musu makaranta kan wani dalilin ki mara amfani, idan kuma ba haka ba."

sai yayi kwafa tare da kaɗa yatsar sa.
kamar daga sama nake jin maganar nasa mamakin sa da furucin sa suka sani gyara tsayuwa ta ina yi masa kallon kacika mai karfin hali.
"Dakata malam."
nafaɗa ina ɗaga masa hannu, kana nacigaba da faɗin.
"A kan dalilan su ƴaƴana ina da ikon yin komai da su, dalilina mai amfani, kada ka kuma cewa dalilina bashi da amfani tun da baka sanshi ba,
ƴaƴa nawa ne nike da ikon yin komai kansu, malam kafita daga rayuwar ƴaƴana kana ta yau darar su da danganta su da kai, da suna mai kama da uba, ƴaƴana basu da uba kuma basa bukatar uba domin bazai yi musu amfanin komai ba, rayuwar su a haka tafiye musu rayuwa da uba sau dubu dan bashi da wani amfani a gare su."
sassauta maganar da nake nayi tare da haɗe hannaye na biyu kana nacigaba da faɗin
"Dan Allah kafita daga rayuwar ƴaƴana kada ka yaudare su da wannan kalma ta uba, dan basu da uba kuma basa bukatar uban, kuma ba shegu bane ƴaƴane tsaftatattu mafiya daraja."

Afusace yashiga matso ni, ganin yan da yanayin sa ya sauya gaba ɗaya, sai na shiga ja da baya, shiko maso ni ya cigaba da yi tare da nuna ni da yatsa, yana huci kana yasoma magana cikin ɗaga murya
"Idan kika sake cewa basu da uba sai ranki yayi mummunar ɓaci, idan kika kuma sako kallamr yaudara sakani na dasu!..."
sai yayi kwafa tare da kaɗa yatsar sa alamun gargaɗi,
mamakin ganin karfin halinsa muraran nake, wai ni da ƴaƴana ake nuna min iyakata a kansu, bil hakki da gaskiya yake maganar dan kuwa fuskarsa ta nuna, niko
baya na kuma ja ganin yan da ya matso ni sosai yana maganar kamar zai kai min hannu, wani irin kallon shekeke nabisa da shi sannan na ce
"Idan ba yaudara bace mene ne, kana cusawa yara abun da babu shi, cikin rayuwar su, ina sanar maka da hakan ne sabo da matsaltawan ka kansu, na dai faɗa maka kafita daga tsafgar ƴaƴana idan kuma ba haka ba zan sa ayi maka gargaɗin da zaka fi fahimta."
ina kai wa nan najuya.

Shan gaba na yayi a fusace cikin muryar da yake nuni da tsantsar gargaɗi ya ce
"Yazamo na karshe fitar kalmar nan daga bakin ki, idan kika sake kika sake furta kalmar durkuso cikin rayuwar su, bazan sa ayi miki hukunci ba ni zan yi miki hukunci da kai na! ki sake nanata kalmar basu da uba kigani!."
yayi maganar cikin
fusataccen amon sauti, a zaburi namatsa gefe dan maganar nashi ta shige ni rabon da ayi min ihu da tsawa irin haka har na mance, shiyasa abun yazo min a sabo.
ba zato naji kafata ta ta dama ta wuce cikin abu kamar rami, da sauri na juyo sai kawai na tafi luuu gaba ɗaya, idanuna na rumse da karfi ina jiran najini a kasa, sai jina nayi zundum cikin ruwa,
kara na ƙwalla wan na hakan yayi sana diyyar wucewan ruwa cikin bakina,
fafutukan niman numfashi nashiga yi, da niman ceton kaina, duk buɗe bakin da zanyi sai ruwa ya wuce ciki, nayi-nayi na iya mike wa tsaye na kasa, duk da kuwa zurfin ruwan idan zan shiga

da kafata iya kirji na yake zuwa min.
Shiko Ahmad da sauri ya faɗa cikin swimming pool ɗin ganin yan da ta ke bubbuga hannu da yin sama da shi
da alamun niman ceto.
hannu na ya ruko da karfi ya ɗago ni yamikar da ni tsaye.
ruwan da ke kunshe cikin bakina dana ki haɗiye shi dan cikar da ciki na yayi, na furzar da shi tare da sauke tagwayen numfashi, ina damke cikina da ruwa yacika shi, a wahalce na na ɗago hannuna ɗaya na share fuskata tare da tattaro gashi na daya rufe min fuska, na mai da shi baya,
ida nuna na sauke kansa, dai-dai lokacin daya kai
hannu  ya share ruwan dake fuskar sa, sai a lokacin na lura ruwan dana furzar daga baki na a fuskar sa na fesa.
shima idanun sa a kai na tun daga gashin kaina yake bina da kallo har kasa, kasan cewar rana ya taso ya haske cikin ruwan ana iya kallon abun da ke kasan ruwan.
dogon tsaki na ja dan nakasa magana tsabar haushi, bugu da kari yan da cikina ya cike tam da ruwa.
a hankali na soma tafiya cikin ruwan har na isa bakin gaɓar gun matattakalar shiga da kuma fita daga cikin swimming pool ɗin,
a sannu na soma hawa maganar sa na jiyo,
"Ki tsaya a taimaka miki kirage ruwan da kika sha."
cigaba da haurawa ta nayi batare da
waige ko tsayu ba,
ina karasa fita da sauri nayi hanyar part ɗina jin zuciya ta na tashi, cikin sauri na shige cikin side ɗin direct sama na haura,
ina shiga bedroom ɗina da sauri nashige bathroom, ai tun kan na karasa bakin toilet nafara sheka amai tsakiyar bayin, zallar ruwa narika aman sa.
da kan sa aman ya tsaya kamar yadda yazo bazato ba sammani, numfashi narika sauke wa ina tallafe da cikina da yanzu nake jin sa wayam, sai dai ɗan murɗar da yake min.
a daddafe na tsaftace bayin na tuɓe kayan jikina da suka jike gaba  ɗaya na wurgasu cikin wishing machine, nafito doguwar riga mara nauyi na zura, kana na isa bakin gado na zauna ina mai cigaba da sauke numfashi,
tsaki narika ja  a-kai-a-kai tsabar haushin da nake jin kaina ciki, har lokacin kasa iya furta komai nayi.
idan na tuna ruwan da na hambuɗa a cikina sai naji kamar nayi ihu, sauki na ma ɗaya jiya-jiyan nan nasa aka fidda ruwan dake cikin swimming pool ɗin, aka wanke cikin sa a ka kuma zuba wani, ban kuma yi amfani da shi ba.
wani dogon tsakin naja yayin da na kai bayana na kwanta kan gado.
mamakin karfin hali da takaicin mutumin nan suka rika zuwar min,
wai ni yake yiwa gargaɗi kan ƴaƴana,
ya kuma yi sanadiyyar faɗuwa ta cikin ruwa, badun kwanana na gaba ba wata kila da yanzu ana kan shirin kai ni makwanci.
Dole nasa jami'an tsaro cikin lamarin dan ban amin ta da mutumin nan ba, awani dalili zai rika shiga min cikin gida kai tsaye har yarika yimin barazana kan ƴaƴana.

Mikewa zaune nayi tare da ɗaukar waya ta, number Mr Aliyu nakira wato P.A na, ko da ya ɗaga bayan mun gaisa na ɗaura da faɗin
"Mr Aliyu ina so a saka min jami'an tsaro a gidan nan."
da sauri ya ce "Madam meke faruwa akwai matsala ne?."
yayi maganar cikin nuna damuwa sosai kana yaci gaba da faɗin
"Ai Madam tun farko shiyasa nace azuba jami'an tsaro gida kamar wannan dole sai da manyan Security masu rike da bindiga, kikace abar mai gadi kaɗai ma ya isa, ina kuwa zai isar wa gida kamar wannan, yanzu kuwa zan fita in sha Allahu anjima zamu zo da su."
na ce "To Allah ya kaimu."
nakashe wayar, ina katse kiran kiran Bappa na shigowa, na daga da sallama daga cikin wayar Bappa ya ce
"HAMDAH ko kina bacci ne?." na ce
"A'a ba bacci nake ba Bappa." ya ce
"To kizo yanzu maza." da sauri na mike jin yana faɗin haka ya kashe wayar.
cikin hanzari na nufi side ɗin su Bappa da sauri na dan Bappa bai taɓa min irin wannan kiran ba nasan komai akayi akwai wata masalar, da ire-iren waɗan nan tunanin nashige cikin side ɗin.
turus naja na tsaya yayin da jikina ya kama ɓari ganin Yakubu durkushe yana kuma rungume da uniform ɗin su Nasmah,
cikin tsanani tashin hankali na karaso cikin parlour'n gaban Yakubu natsaya cikin rawar murya da kuka keson kwace min na ce
"Ina yara na?!."
nayi maganar cikin rawar murya sosai tuni hawaye yacike ido na.
Bappa da ke zaune kan kujera ya dube ni tare da faɗin
"Zo zauna nan HAMDAH." yanu na min kujerar da ke kusa da shi, ban iya bin umurnin Bappa ba dan kuwa hankali na yakai kololuwa wajen tashi, duba da yan da Yakubu yake ɓari yakuma rungume uniform ɗin gam-gam.
Inna Wuro ce ta mike tazo taruko faɗata ta jamyo ni ta zaunar da ni kan kujerar, tuni hawayen da suka cuko idona suka fara zuba. Bappa ya girgiza kai  yana faɗin
"Muma mun shiga irin yanayin nan da kika shiga a yan da yashigo mana kamar an rakoshi a guje,
tam bayar da na fara mishi shine ina yaran suke ganin uniform ɗin su a hannun shi, da kyar ya iya ba mu amsar suna nan kuma suna makaranta, yaji tsoron ya tinkare ki kai tsaye shiyasa yazo nan."
kai Yakubu yashiga gyaɗa wa yana ɗan rarrafowa da guiwar sa yana kuma faɗin
"Dan Allah dan Annabi Bappa Malam ka rokar min afuwar ta wlh duk yan da naso na hana faruwan haka bai yuwu ba, wlh fin karfi aka nuna min muraran."
Bappa ya katse shi ta hanyar ɗaga masa hannu ya ce
"Ya isa." kana Bappa ya juyo da kallon sa gare ni ya ce
"Lokacin da suka fita zai kai su makaranta a hanya suka haɗu da Ahmad Tijjani Sabil ya sai da su, yake tambayar su ina zasuje ganin ba hanyar makarantar su suka nufa ba, sannan kuma ga wata uniform ɗin daban a jikin su, to shine shi Yakubun ya shai da masa in da zasu, shikuma Ahmad yace kada ya kuskura ya kaisu wannan makarantar yawuce ya kaisu wan can

makarantar su, to dai a takaice tare suka tafi da shi wancan makarantar da aka cire su yasa aka basu wani uniform, yakuma tuɓe musu najikin su shine yabashi wan da yacire musun yace ya mai do shi gida,
to shine ya dawo hankali tashe yakuma ji tsoron yaje ya tinkare ki da batun shine ya zo nan, kafin na kira ki sai da na kira shi Ahmad ɗin sabo da ina da lambar sa dan ranar da yazo nan na karɓi lambar sa, ashe dai zatayi  amfani gaba akuma irin wannan ranar,shine na kira sa dan ji dalilin sa na yin hakan,
ya bani tabbacin dalilin sa na yin haka, kuma na gamsu, yace yawai ta canza musu makaranta a karancin shekarun zai iya birkita musu ƙwaƙwalwa gara abar su idan suka gama can ɗin kan lokacin sun daɗa wayo sai suyi gaba, kuma nima nayi nazari naga hakan yafi abarsu a can ɗin, nayi masa maganar dalilin ki na canza musu makarantar yace za'a kara tsaro sosai babu wata matsala."

Yakubu da tun da Bappa ya soma maganar yake ai kin gyaɗa kai da buga bayan hannun sa cikin ɗaya tafin hannun sa, yayi kalar tausayi, Bappa na gama maganar shima ya ɗaura da faɗin  "Wlh tallahi Hajiya na rantse miki da Allah, ba laifi na bane, na dage wajan ganin ba'a kuma samin wata matsala ba kamar yadda nayi miki alkawari, wlh Hajiya dana buɗe baki zanyi masa musu dawani yafito daga cikin motar sa, ya shake ni sai da naji kamshin kabari, shi ya hana mutumin da yanzu na sheka,
ki gafar ceni Hajiya ki tai maka kibar ni a bakin aiki na."

Numfashi na sauke jin akasin abun da nake tunani yafaru a kansu, dan Ni nagama tunanin hatsari sukayi sun mutu shine yakawo kayan su gida.
duban Bappa nayi ina shere hawayen fuska ta nace
"Yan zu Bappa ka amin ce da abun da yafaɗa kenan?, to shi ina ruwan shi da su me ya shafe shi da lamarin su da har zai rika shiga, har fa Daddy yake cewa surika ce mishi meye gamin sa da su."
murmushi Bappa yayi irin tasu na manya kana ya ce
"To in ban da abin ki HAMDAH ai wan da ya nuna yana son naka yagama yi maka komai a rayuwa, kuma da kike cewa yana shiga lamarin su basu kaɗai ba lamarin koma waye yana shiga, idan baki mance ba na taɓa baki labarin sa nazu wa rugar mu da yayi, muma ba lamarin mu yashiga ba yakuma jiɓanci lamuran mu, yayi silar magance mana wutar fitinar da take ta kunno mana,
ko jiyan nan da daddare munkalli labarai gidan TV wasu iyaye sun fito suna mika masa godiya kan gudumawar da ya bada kan ƴaƴan su, su iyayen ma basu ma sani ba ƴaƴan ne suka dawo gida suke faɗa musu alkhairin da yayi musu,
a makarantar gwamnati suke karatu ya cire su ya mai dasu na kuɗi,
sannan kin ce meye gamin sa da su,
ke da kike taimakon bayin Allah meye gamin ki da su?,
ai shi tai mako basai wan da kasani kake taimaka masa ba, duk wan da Allah ya sa da rabon sa yafaɗo ta kansa sai ka taimaka masa ladan ka na gurin Allah,
shiya sa Allah ya halittomu kala biyu mai kuɗi da kuma talaka hakan kuma jarabta ce, idan kai

me kuɗi ne kayi kokarin cin jarabawar da yayi maka, wato kajikan na kasa da kai, ka kuma tsare dokokin Allah, to da yardar Allah babu shakka zaka shiga aljanna ta sanadiyyar jaraftar ka da yayi da arziki,
idan kuma kai talaka ne, karike talaucin ka kabi dokoki Allah, kai ma zaka wuce aljanna da yar dar sa.
shi tai mako ba sai wan da kasani kake yi masa ba.
kiran sa da sunan uba kuma da suke yi, ai duk ɗa nagari shike daraja nagaba da shi yakira sa Yaya wan da ya haifesa kuma yakira sa da sunan uba, wan da yayi jika da shi yakirasa da Kaka, abun alfahari ne ɗanka yazamo daga cikin irin waɗan nan ƴaƴan, ba ai bu bane dan sun kirasa da suna Daddy tun da yakai ya haife su, zaki so ace ƴaƴan ki suna da rashin kunya ko basu da tarbiyya?."

Shiru nayi batare da nace komai ba.
murmushi Inna Wuro tayi,dan ta fahimci in da maganar tawa ta dosa, kana tace
"HAMDAH kenan ai laifin wani baya shafar wani."
kana ta kawar da zancen da faɗin
"Sai kiyi wa Yakubu hakuri ya dai na wannan tafa hannu da ɓarin jikin da yake."
da sauri Yakubu ya daɗa rarrafo wa gaban mu yace
"Whl Innar Gida kada kiga shakar da mutumin nan yamin, tsaro biyu ne suke girgiza ni a jikina, tsoron kada Hajiya ta kore ni daga ai ki na, da kuma tsoron wannan basamuden mutumin da suke tare da Ahmad Sabil daya makuren makogaro."
yayi maganar yana ɗaga wuyar sa da nuna mana in da ya shako san.
dariya duk sukayi ban da ni dana murmusa kawai.
na yar da da dukkanin maganar da Bappa yayi, sai dai inajin abune me wuya na iya jure wa dajin kalmar uba na fita daga bakin su Naseem.
Bappa yacewa Yakubu ya tashi ya tafi anjima yaje ya ɗauko su a makarantar.
ya mike yana zuba godiya yayi waje.

Haka su Bappa sukayi ta jana da hira bani na bar side ɗin ba sai wajen karfe 12, gani lokacin dawowar su Naseem yayi nayi musu sallama nakoma side ɗina.

komawa ta bada jimawa ba su Nasmah suka shigo a guje, kalmar da suka fara furta min shine Daddy'n su ya ce gobe zai zo ya ɗauke su a mota.
ban iya ce musu komai dan ko na faɗan ma abanza ne...

A ɓangaren Ahmad Tajjani Sabil, tun da yabar gidan tuki yake kamar mai koyon tukin, a haka ya iso bakin wani katafaren get me girma da tsaruwan gaske, yayi hon batare da ɓata lokaci ba a ka wangale masa katafaren get ɗin,
a sannu ya dannan hancin motar sa ciki, ya ilahi ya lillahi gida ne mai matukar girman gaske, alkalami na bazai iya zana girma da tsaruwan gidan ba, FAN'S na barku ku hasasho da kanku.
a hankali ya isa parking lot in da motoci da suka kai guda biyar ke jere agun ya yayi parking, a

sannu ya buɗe motar yafito,
daga can wasu matasa guda uku suka iso in da yake da sauri, suna faɗin
"Barka da dawowa master."
hannu kawai ya ɗaga musu tare da yi musu murmushi, batare da yace komai ba, yasoma tafiya a hankali ya iso ba kin wata kofa, jiki ba kwari ya tura kofar yashiga da sallama ɗauke kan laɓɓan sa.
wata kyakkyawar mace fara ƴan duma-duma ce ke zaune cikin katafaren kayataccen parlour'n, tana ganin sa ta ajiye wayar dake rike a hannun ta, ta mike da sauri,
ta nufo shi da ɗan sassarfa, tun kafin ta karaso ya buɗe hannayen sa ta shige cikin jikin sa ta rungume shi, hannayen sa ya haɗe yazagaye bayan ta tare da manna mata kyakkyawan sumba a goshi, ido ta lumshe tare da buɗe wa lokaci guda, kana ta ɗago kanta ta mannan masa kiss a kumatu.
yan da tayi shima haka yayi, ya lumshe idon tare da kuma buɗe wa, itako hannun ta tayi sama da shi ta sakalo wuyan sa taɗan langwaɓar da kai gefe kana ta soma magana cikin shagwaɓa
"Aboki ka mance da nine?." ido ya waro da alamun maganar tata tayi girma, baki ta cuno gaba tace
"To shine nayi ta kiran ka a waya baka ɗaga ba, kuma baka neme ni ba tun da ka fita, ni da na nime kan kaki amsa kiran."
maganar take cikin shagwaɓa kamar zata fashe masa da kuka.
kuma tun ta ya kama yaɗan ja kana ya ce
"Na isa naki ɗaga kiran ki kinga wayar da na fita da ita ɗaya wayar tana gida ai."
yayi maganar yana nuna mata wayar dake rike a hannun sa.
murmushi tayi tare da faɗin
"Ai har da nayi fushi."
hannun sa ta ruko tana faɗin "Toho muje kayi wanka."
ta janyo hannun sa sukashi ge cikin wani kayataccen bedroom, suna shiya da kanta ta tuɓe masa kayan jikin sa, boxes kaɗai ta bari takuma janyo hannun nasa sukayi cikin bathroom.
Ta taimaka masa yayi wanka suka fito ɗaure da towel a kugun sa.
lokacin an fara kiraye-kirayen sallar azaha jallabiya ya zura ya jasu sallah nan cikin ɗakin,
ko da suka idar, zaman sa ya gyara ya jingina da jikin bayan sa da jikin garu-bango yana lazumi, ido taɗan tsura masa kana sai kuma ta mike ta fita jim kaɗan ta dawo ɗauke da tray mai girma a hannun ta, a gaban sa ta dire, kana tashiga buɗe kulolin da suke kan tray'n har guda uku,
wani daddaɗan kamshi ne suka fara tashi daga cikin kulolin, nan da nan ɗakin ya kaure da kamshin lafiyayyun girkin.
tazuba cikin plt tare da saka cokula guda biyu, ta gyara zaman ta da kyau ta maso gaban sa, in da ta saka plt ɗin a tsakiyar su, suka rika cin abincin gwanin ban sha'awa
sunayi suna ɗan taɓa hira da zolayar junan su, a haka har suka kammala, takwashe kayakin ta mai da su kitchen,
ko da ta dawo ta taddashi ya koma gado, yana ɗan danne-danne a waya.
kimsa in da suka ɓatan tayi kana tazo bakin gadon ta zauna, dai-dai in da kansa yake, ta gyara zaman ta da kyau ta ɗago kansa ta ɗaura kan cinyar ta, yayin da ta cusa hannunta cikin sumar

kansa tana ɗan yamutsa shi cikin tsalon sa mutum yayi bacci.
aje wayar dake rike a hannun sa yayi, kana yayi sama da
hannun sa ya shafi gefen fuskar ta, a hankali cikin muryar jin baccin da yafara ziyar tar sa, ta sanadiyyar abun da take masa, ya ce
"Kawa nayi bacci kenan?."
kai ta gyaɗa tare da faɗin
"Eh nasan ka gaji."
numfashi ya sauke kana yayi kasa da hannun sa yadaɗa gyara kwanciyar sa da kyau a hankali yashiga sauke numfashi.
batare da ɓata lokaci ba bacci yayi gaba da shi da taimakon yan da take sarrafa gashin kansa da wasu sassa na jikin sa.
sai da ta tabbatar da baccin nasa yayi nisa, sannan ta ɗaga kansa a hankali ta janyo pillow ta saka masa kana ta mike tafita, domin sanya ido kan aikin da masu aiki suke
gudanar wa a gidan...

Da misalin karfe uku da rabi ya farka bathroom ya faɗa can yafito ruwa na ɗiga daga jikin sa da alama wanka yakuma,
gaban wardrobe ya tsaya yaciro kaya wani dakakken yadi ne wan da daganin sa ma kasan bana wasa bane sai dai manyan kam.
bayan ya saka ya isa gaban mirror
turo kofar a kayi daga cikin mirror yazubawa kofar ido, lallausan murmushi ya sake wan da sai da kumatun sa suka lotsa, lokacin da suka haɗa ido da ita tacikin mirror,
baki ta ɗan turo gaba kana ta tako zuwa in da yake,
ta ɗaura hannun ta kan hannun sa daya ɗaura kan turare yana kokarin ɗauka, ta amshi turaren sannan ta dube shi tare da faɗin
"Shine zaka yi wanka baka neme ni na taya ka bako?."
kai yaɗan langwaɓar sannan ya ce
"Nayafe miki ai nasan kin sha wuya wajen sani yin bacci."
turaren ta ɗago tafara fesa masa a jiki sannan tace
"Babu wani wuya gun ai kin lada ni dai wayo kayi min ka hanani samin wannan ladar."
"Kinfa tara ladan nan da yawa amma rabawa zamuyi ko?."
yayi maganar cikin tsigar zolaya yana kuma jan kuma tun ta.
kafaɗa ta make ta ce
"Naki wayon naka yafi nawa yawa ai."
dariya suka sakar wa junan su.
sai da ta fisa masa turaruka wajen kala uku kana ta gyara masa zaman hular kansa, ta ce
"Kafito sosai fa."
"Haba original mirror ai ba ma sai naga wannan jebun ba."
yafaɗa yana nuna mirror.
murmushi tayi kana taɗan tsura masa ido sai kuma ta ce
"Aboki me ke damun ka?." tayi masa tambayar cikin nuna tsantsar kulawa.
da sauri ya ce "Wani abun kika gani ne, to ni kuma me zai dame ni bayan ina da ke."

ya kai bakin sa kan goshin ta tare da mannan mata kiss.
numfashi ta sauke tare da ɗan yin shiru tana nazartar yanayin sa, kana ta ce "To shike nan muje na rakaka katafi masallacin gashi ana kan kiran sallah."

Hannun ta ya damke cikin nasa cikin son kawar mata da shakkon dake hangowa kan fuskar ta ya ce
"Babu komai fa." da sauri ta katse shi da faɗin
"Ban kuma cewa komai ba fa muje katafi masallaci......"!

Mommyn Twin ce

10

Tun da yatafi masallaci bai shigo gidan ba sai bayan sallar isha, dan tun san da aka idar da sallar zai koma ciki, yayi ba'i dan haka yasa akayi musu masauki a parlour'n ba'i,
basu kuma bar gidan ba sai daf magriba, dan haka masallaci ya zarce sai yanzu bayan sallar isha ya shigo.
ko da yashigo parlour'n babu kowa, sai sanyi me fidda daddaɗan kamshi ke tashi cikin parlour'n.
direct bedroom ɗin sa ya wuce, hular kansa ya cire ya ɗaura saman bedside, kana yatafi a hankali zuwa bakin gado ya zauna, a hankali yakai bayan sa ga katifa ya kwanta rigingine, yayi pillow da hannayen sa kafar sa na kasa yana ɗan lilo da shi.
shiru yayi yayin da ya kurawa pop'n ɗakin ido, kamar mai karantar wani abu a jiki.
a hankali ta turo kofar ta shigo da sallama, ido ta kura masa na ƴan dakikai kana a sannu ta taka zuwa bakin gadon,
sai ta faɗa jikin sa gaba ɗaya ta sake nauyin ta a kansa,
ido ya waro tare da faɗin
"Wash zata karya ni, Kawa kin kara nauyi fa."
cikin muryar dariya ta ce
"Allah Aboki babu wani nauyin dana ƙara in da nake da haka nake yanzu ma."

"Tap waya faɗa miki ke baki ganki kwana biyu sai daɗa zama duma-duma kike ba, niko sai tatse ni kike."
kwanciyar ta tadaɗa gyara wa a kansa cike da shauki tace
"Kai Aboki kai ma fa baka ganka bane kayi kiba kwana biyun nan."
dariya yayi yana dai-dai ta fuskar su a hankali ya manna mata kiss kan laɓɓanta.
yan da suke yiwa junan su idan ka gani zaka fagimci santsar kauna soyayya shakuwa yarda a saka nin su.
cike da shauki ya mirgino ta yadawo da ita kasa shi ya haye kanta,
nauyin sa shima ya sake mata, yana faɗin
"A hakan kike cewa nayi kiba jini fa babu ko nauyi kamar pepa kullum kina tsotse ni, kullum sai na tsame wani abu daga jikina na zuba shi jikin ki, taya bazaki daɗa kara zama wata duma-duma ba."
ƴar karamar kara ta sake tana faɗin
"Allah Aboki kayi nauyi wash Aboki na tuba ɗaga ni."
ƴar dariya yayi tare da shafa sumar kanta yana nan a kanta.
ƴan wasan ni suka cigaba da yi sakanin su me cike da zallar shauki da kauna,
zallar soyayya da ɗin bin kauna kake hangowa tsagwaran ta a tattare da su.

Cikin yanayin da suke ta dube shi tana faɗin
"Aboki ka rama ɗaga ni na tashi, idan ka kara yafi haka nima sai na rama."
tayi maganar tana ture shi.
ƴar dariya yayi mata tare da mirginawa ya koma gefe yakwanta rigingine tare da yin pillow da hannayen sa biyu, ta mirgina tayi pillow da damtsen hannun sa, sai kuma ta ɗago tasaka hannun ta a kumatun ta, yazamana da guiwar hannun nata najikin katafi, in da da kyau take iya kallon fuskar sa, duban sa tayi da kyau naƴan sakanni kana a hankali taso ma magana
"Meke da mun ka aboki?." tayi maganar idanunta cikin  nashi. idanun sa ya lumshe tare da buɗe wa yaɗan ja numfashi kana yace.
"Tambayar ɗazu kuma har lau, to me kika gani yanzu bacci nake ji."
murmushi tayi kana ta shafa gefen fuskar sa sannan ta ce
"Bacci kuma him Aboki kenan,
adalilin yin baccin ka na rana zaka kuma yin wani baccin ne da misalin karfe 12 na dare, yanzu karfe 8:30 saura akwa uku da rabi  lokacin baccin ka yayi, sam karya baya yi maka kyau sabo da rashin iya shi da bakayi ba shi yasa ko kayi ake saurin gane ka."
kokarin kawar da maganar yayi ta hanyar janyo ta jikin sa, kana ya shiga wasa da wasu sassan jikin ta,
 a hankali ya furta
"Kawa ke baki ga in da idona sukayi ba bacci ne a cikin su, da alama dai baccin da ɗazu kika sani bai ishe ni ba."
ta ce "Him    wai ni yau ake ɓoyin wani abun, Aboki yaushe ka fara ɓoye min damuwar ka, yaushe ka fara sanya hijabi sakanin sirri na da naka, duk faɗin da kake ni da kai abu guda ne ashe ba haka bane??, shin da ma ashe akwai wata ranar da zaka ɓoye min damuwar ka, ni ce fa wacce muke tauna matsalolin mu mu magance sa batare da wani ya sani ba, ashe dama faɗin mu tsirrin junan mu ne da kake abun ba haka yake ba, ban taɓa tunanin zuwan wannan

ranar ba."
ɗan sakai ta maganar nata tayi tare da mike wa zaune ta tankwashe kafafun ta takuma duban sa da kyau, nan take sai ga hawaye yacika idon ta, hannun sa ta ruko ta kankame shi cikin nata, ta ce
"Tabbas akwai abun da yake damun ka
da ma ai ni na sani akwai ranar da zatazo irin haka."
hannun sa ta daɗa kankamewa cikin nata, taci gaba da faɗin
"Kayi hakuri amma ka sani nafika jin damuwa fiye da kai, ni na riga da nasa ni, dama kana hana ni damuwar ne kai kana yi,
idan da a ce mutum shi yake ba kan sa abu da karfin dukiya WALLAHI dana sadaukar da dukiya, WALLAHI idan dana san in da zanje na sami maganin da zansha yazamo silar haihuwa dana tafi ko da bangon duniya ce,domin samin farin cikin ka, nagaza baka ɗa kayi hakuri kayi hakuri kayi hakuri!!."
takuma nanata kalmar hakuri yayin da tuni hawayen idon ta suka fara zuba.

Da sauri yamike zaune tare da janyo ta jikin sa yana faɗin
"Ke meya kawo wannan maganar?, banace kada nasake jin wannan maganar a bakin ki ba?,meye na yin ta meya kawo ta yanzu kuma?,
Okay so kike ki kawar da farin cikin da ke nan ko?,
hauhuwa dama ashe mutum shi yake bawa kansa haihuwa?, okay kin mance cewa Allah shi yake bai wa bayin sa haihuwa?, so kike kiyi tsaɓo to kiyi gaggawan tuba, maza yanzu."
yayi maganar yana share mata hawaye.
kana yaci gaba da faɗin "Dai na kunan kada na sake jin wannan maganar a bakin ki, kada na sake ji idan kuma so kike ki koyi yan da zaki rika ɓata min rai to ki kara yin ta,
na ce miki ina son haihuwa Allah bai nufa na samu bane, idan yaso sai ya bamu bare ma muna da su ƴaƴan da muke yi musu hidima kama daga gidan marayu makarantu da dai sauran su suɗin ba namu bane, suma ƴaƴan mu ne, mai da hawayen kinji Fara ƴar duma-duma ta." "
kai ta shiga girgiza wa tana faɗin
"Nayi shiru bazan sake ba ka yafe min."
kai ya jinjina kana ya koma yajin gina bayan sa da jikin gado, ita ko zaman ta tagyara suna fuskantar juna ya ce
"Ko ke fa fara ƴar duma-duma ta to na yafe."
dariya tayi kana taɗan langwaɓar da kanta cikin muryar shagwaɓa a hankali ta ce
"Na yar da ba abun da na faɗa yanzu ke damin ka ba amma na tabbata akwai wani abun, zuciya ta baza ta sami sukuni ba har idan ban za mo silar kawar da damuwar ka ba, amma babu damuwa tun da ka nuna baka so na sani, yau rana ta farko daka taɓa ɓoye min damuwar ka, ban taɓa tunanin akwai ranar da zata zo ka ɓoye min damuwar ka ba, damuwar ka tawa ce kamar yan da yake tawa takace,
ai ban san cewa haka yanzu ka ɗauke ni ba shike nan babu damuwa."
tayi maganar tana kokarin sauka a gadon.
dakatar da ita yayi ta hanyar rike hannun ta kana yaɗan ja numfashi sannan ya ce
"Abar shi kawai faɗar shi ma bashi da wani amfani."
ido ta kura masa sannan tace

"Haka kace abar shi yaci gaba da damun ka da cin ka a rai ko?, kada ka mance nafi kowa sanin ko kai waye tun sati biyu da suka wuce na fara  fahimtar akwai wani abun da ke damun ka, ban daɗa gaskata hakan ba sai yau da ka shigo gida, rungumar ka da nayi jikin ka da zuciyar ka suka tabbatar min da haka, dakuma tabbacin damuwar naka yakaru a yau,
tanbayar ka danayi ɗazu da zaka tafi masallaci yakuma bani amsar abun da nake zargi, babu halin da zaka shiga koda dai-dai na second 1 ne ban gane shiba."

Ganin yan da ta hakikan ce tanuna damuwar ta matuka a kanshi takuma nuna ɓacin ranta nakin faɗa mata da yayi wan da ada ba haka asakanin su.
sai ya janyo ta jikin sa ya rungume,
tabbas ita wata sashi ce a rayuwar sa da bazai iya ɓoye mata komai na rayuwar sa ba, kamar yan da tun fari suka gina rayuwar su ta hanyar faɗawa junan su sirrukan su,
bata ɓoye masa komai kamar yan da shima baya ɓoye mata, ko a yanzu dayake ta kokarin barin abun cikin zuciyarsa shi kaɗai yana ta shan fama da ɗawai niya da zuciyar sa dan bai saba ba sam.
numfashi ya ja kana a hankali yasoma magana
"Akwai wani abun da ke damu na amma sam banso na fitar ba naso nayi jarumtar iya barin sa a raina dan faɗar sa sam bashi da amfani."
wani numfashi yakuma saukewa kana a hankali ya cigaba da magana
"Kiyi hakuri da abun da naketa ɓoye shi a zuciya ta ni kaɗai, wan da nagaza iya dan neshi sabo da ban saba da irin saba, yabani wuya sosai a zuciya ta, kiyi hakuri yanzu da zakiji shi a kan laɓɓana, tabbas da gaske bazan iya ɓoye miki sirri na ba kokarin yin haka dana yi kuwa dan cigaba da ganin kwanciyar hankalin ki yabani wuya sosai a zuciya,
nayi ta kokarin danni shi cikin zuciya ta hakan ya garara gashi bugun farko kin gano da akwai abun da yake dami na."
hannun ta ya damke cikin nasa kana yaja numfashi ya sauke sannan yaci gaba da faɗin
"Wata ranar da Company na ya tura kayan bukata izuwa wata makarantar yara, kamar da yan da kika sani a ka saba,
lokacin da motar Company ya isa aka shai da min da isar sa, sai na tashi da kai na naje makarantar domin ganewa ido na kalar farin cikin da yara zasuyi kan kayan da aka kai musu wan da yawan ci kayakin wasa ne irin na yara,sai sabbin kujeru, dan nima naji daɗi, duk da kuwa makarantar bana Gwamnati bane, makaranta ne ma irin na ƴaƴan masu kuɗi,
lokacin da na shiga makarantar nayi arba da wasu yara guda biyu, sunata wasanni da kayakin wasan da aka kai musu, duk  da yara dayawa agurin amma nafi ganin farin cikin waɗan nan yara guda biyun sosai cikin matukar farin ciki da kuma jin daɗi suke ta wasa da kayan da motar Company na ta sauke,
naji daɗi matuka ganin farin ciki a fuska da zukatan ɗaliban, amma sai dai hankali na yafi karkata kan farin cikin da ke baiyana ga waɗan nan yara guda biyu,
kasan cewar lokacin tashi yayi nan ɗalibai suka fara watsewa, wasu diraibobin su suka zo suka kwashe su wasu kuma motar makaranta ta kaisu, haka yara sukayi ta watsewa.
ina nan a cikin makarantar muna magana da shugaban makarantar bayan mun gama maganar na fito, lokacin tuni students sun watse, a bakin get na tadda waɗan nan yara guda biyun, da lokacin da na shigo makarantar su na fara ganin su da ɗin bin farin ciki kan fuskokinsu, tare da

mai gadin makarantar suna zaune a bakin get.
ko da na iso gurin su kan su na shafa tare da duban mai ganin na ce,
yaya su ba'a zo ɗaukar su bane kokuma motar makaranta zasu bi kuma naga ɗalibai duk sun watse.
mai gadin ya ce
Ba motar makaranta zasubi ba direban su ne zai zo ya ɗauke su ko mai akayi dai yanzu yana hanya, yau an ɗan makara ne wajen zuwa ɗau kar su.
kan su na daɗa shafawa sai nayi waje cike da jin sha'awar yaran, ina fita kuwa sai suka biyo ni a baya, sai na tsaya naruko hannun su ina tanbayar su yaya sunan su,
kai yaya sunan ka nafara tambayar na mijin sai yace min sunan sa Naseem, ita kuma macen tace min sunan ta Nasmah,
nafahimci wayo sosai tattare da yaran duk da kuwa ƙarancin shekarun su, dan bazasu wuce shekaru uku zuwa uku da rabi ba,
bayan nayi musu tambayar sai suma suka mai da min tambayar.
to kai ma yaya sunan ka, wayon yaran ya burge ni sosai jin yan da suma suka iya mai da min tambayar,
Sai nace musu sunana Daddy, kin san wani irin yanayi nagani a tare da su lokacin da nace musu suna na Daddy?."

Dan sakai ta maganar yayi tare da daɗa matse hannun ta cikin nasa kana yaci gaba da faɗin
"Ihun murna suka sake haɗe da tsalle suka rungume ni suna faɗin laa kai Daddy ne irin Daddy'n su Aeeman,ɗin class ɗin mu, to kai Daddy'n su waye ne?, maganar yaran yasa Ni shiga wani yanayi, sai dai farin cikin danake hango wa tare da su da kuma fahimtar da nayi kalmar sunan Daddy dana furta musu yazo mu su a sabon abu ko makamancin haka,
Sai na ce musu Daddy'n ku.
kin san me yaran sukayi?."
nan ma hannun ta yakuma damke wa cikin nashi kana yaci gaba da faɗin.
"Da ɗa rungume ni sukayi suna ta tsallen murna da nanata kalmar sunan Daddy,
wani irin abu naji acikin jiki na da zuciya ta, a duk san da suka furta kalmar Daddy a gare ni, sai naji wani irin farin ciki da jin daɗi mara misaltuwa a gare ni, cikin kan kanin lokaci naji yaran sun shige cikin zuciya ta,
har nake ji tamkar ƴaƴan da na haifa ne a gaba na suke kira na da wannan suna,
abun da na daɗa lura da yaran a lokacin sosai na ke hango jin daɗi irin na samun sabon abu a tare da mutum, sai suka ce min
Daddy kai ma zaka bamu chocolate irin wan da Daddy'n Aeeman yake bashi. na ce musu kwarai kuwa, to lokacin akwai ragowar Chocolate a mota wan da nake baiwa yara a gidan marayu idan naje,
sai na ruko hannun su nace muje na basu chocolate yana mota ma kuwa.
lokacin da muka nufi gun mota, a dai-dai lokacin wata yarin ya ta iso gurin a cikin mota."

Sai kuma yayi shiru batare da yaci gaba da Maganar ba.
ita ko zaman ta tagyara sosai wannan karon ita ta mai da tafin hannun sa cikin nata tasar kafe yatsun su guri guda, kana ta sanya idanun ta cikin nashi, cikin daɗa karfafa shi da bashi kwarin

guiwar gama fidda damuwar da take ganin tamkar ta yaye masa, tagyaɗa masa kai cike da bashi kwarin guiwar yaci gaba da da fidda damuwar da take yi masa kallon cuta ce barin sa a ransa.
A hankali kuwa yaci gaba da maganar  yayin da ya daɗa sarkafe hannun nasu sosai,
ya ce "Kawa kin san me naji?, wani abun mamaki naji wan da ban san  mene ne shi ba,
bayan da yarin yar ta ɗauke su ta tafi da su,
sai na tsinci kai na cikin wani irin yanayi mai ka ma da da muwa,
mai kama da son in sake ganin su, amma nafi alakanta son in sake ganin yaran ne,
bayan kwana biyu sai naji tunanin nawa yanata rikiɗa, madadin tunanin yaran su biyu sai ya dawo uku, zuwa lokacin na gama fihimtar har da ita yarin yar nake son sake gani.
nayi mamakin kai na matuka,
wata rana dana fita muka kuma haɗuwa da su a kan hanya ta ta zuwa mittin,
a tunani na ganin da nayi musu wannan rana shike nan zuciya ta zata huta da tunanin abun da bai shafe ta ba, amma ina bayan rabuwar mu da su sai naji tamkar kara min ake.
Bayan wasu kwana biyun sai nasa ayi min  bincike a kan su wato ita da yaran dana ke yi musu kallon kannen ta ne,
nayi mamaki matuka lokacin da labarin su ya iso min, dajin waɗan nan yara nata ne ma ana ita ta haife su.
mamaki na shi ne ganin ta kara ma sosai, nasamu cikakken labarin su, da duk kanin bayanan tarihin rayuwar su..."
shiru yayi tare da jan numfashi ya sauke, sannan ya ce
"Labarin su mai cike da ban tausayi na girgiza da jin lamarin, sai dai a yanzu su ba abin tausayi bane, dan Ubangiji ya zartar da ikon sa gare su..."

A hankali yashiga bata labarin su kamar yan da aka kawo mishi cikakken tarihin su, bai ɓoye ko rage mata komai ba kamar yadda baiyi da farko ba, bayan gama shaida masa abin da aka sanar masa a kan su sai ya cigaba da faɗin
"Kin san wace ce wannan yarin yar?."
kai ta girgiza jiki a sanyaye yayin da idanun ta suka cika da ƙwalla tap suna shirin zubowa.
taji bala in tausayin su da jin labarin su jikin ta yayi matukar sanyi.
ya ce "I ta ce mai Company *HAM'NAS*."
ido ta waro ta ce "Mai Company *HAM'NAS* mai *HAM'NAS* Nigeria Limited?."
"Kwarai kuwa ita ce."
kai ta jinjina tare da faɗin
"Allah mai iko wan nan shine sakayyar da mafificin rahama yayi mata sakamakon cin jarabawar da ya ɗaura mata tabbas labarin rayuwar ta abun a tausaya  ne, a da yanzu kam Allah yayi mata sauyi da mafificin rahamar sa."
sai gata tana hawaye cikin matsanancin tausayin labarin rayuwar HAMDAH da taji, har da jan sheshshe ka.
ta kai hannun ta share hawayen ta tare da faɗin
"Allah kayi mana mai kyau kasa mu dace duniya da kiyama."
ya ce "Amin." sai ya saki hannun ta yakoma ya kwamta tare da lumshe idanun sa.
a sannu ta gyara ita ma sai ta kwanta gefen sa tare da yin pillow da damtsen hannun sa, a

hankali takai hannun ta kan fuskar sa, a sannu tashiga shafa gefen fuskar sa, in da kayataccen saje ke kwance a gurin lub-lub gwanin ban sha'awa.
duban sa tayi da kyau cikin kulawa a hankali ta ce
"Aboki." idanun sa da suke lumshe yaɗan buɗe su a kanta sannan ya amsa da
"Na'am." in da ya am sa can cikin kasan mako shin sa, laɓɓan sa ne suka motsa tanan ta fahinci ya amsa kiran nata.
idanun ta cikin nashi, sannan tace
"Aboki bayan sanin labarin ta kuma sai me baka karasa bani labarin ba."
idanun sa ya lumshi cikin son kawar da zancen ya ce
"Wani labarin kuma ai na gama baki labarin."
murmushi tayi tare da faɗin
"Baka kara sa ba da saura dan acikin duk kanin labarin da ka bani baka bani asalin gundarin labarin ba, kawai dai ka ce min kana
jin wani abu a kanta mene ne shi?."
"Ba ko mai fa." yafaɗa a takaice yana gyara kwanciyar sa, tare da juya wa ya fuskanci jikin garu, yana faɗin
"Zanyi bacci ki tai maka min kisa yayi daɗi."
hannun ta ta cusa karkashin gashin kansa ta bayan keyar sa, yana jin haka da sauri ya juyo dan yasan jan masa sumar zatayi da karfi bawai tayi masa yan da zaiyi baccin ba.
dariya tayi tana faɗin
"Ai da baka juyo ba Aboki yau aski zan maka."
ido yaɗan waro ya ce "Aski da hannu."
farr tayi da ido ta ce "Zan nimo abin yin askin ai taɓawa nake naji ta in da zan fara."
ya ce "Faɗi gaskiya dai ƴar guntun muguntar ce ta motsa."
dariya takuma in da shi kuma ya murmusa yana kokarin mai da idanun sa ya lumshi tayi saurin dakatar da shi ta hanyar faɗin
"Me zaka ɓoye min ne iye sai fa ka karasa bani labarin nan dan baka gama bani ba."
shiru yayi bai ce komai ba,
Murmushi tayi tare da faɗin
"To ni bazan karasa baka labarin, tun da yau ka aro hijabi ka sakata sakanin mu, zan yaye ta yanzu dan babu ita sakanin mu har gaba da abadan."
ɗan numfashi ta ja tare da cigaba da faɗin
"Tun da ka sanya ido kanta Ubangiji yayi ikon sa,ya datsa maka sonta, a lokacin da baka taɓa sammanin a kwai ranar da hakan zata kasan ce da kai ba, dan kai a tunanin ka ni kaɗai ce Ubangiji ya dasa maka sona cikin zuciyar ka, babu wata macen da zata kuma samin gurbi cikin zuciyar ka,
ka mance da cewa Allah shi ne sarkin mulki mai yin yadda yaso da bayin sa, nasan ka da son yara amma son da kake yiwa waɗan nan yaran na daban ne, kana yi musu irin son da uba yake yi wa ƴaƴan sa, haka ne ko?."
tayi magaran  tana duban sa da murmushi sosai kan fuskar ta.
numfashi ya sauke kana ya janyo ta jikin sa sannan ya ce
"Haka ne." ya faɗa dan babu ɓoye-ɓoye ko karya sakanin su, ko yan zu ma dayayi kokarin yin hakan sabo da wani dalilin yasha wuya sosai da fama da abun cikin zuciyar sa.

wani yelwataccen murmushi ne ya baiyana kan fuskar ta, kana ta ce
"Kana son ta?." kai ya gyaɗa alamar Eh sannan ya ce
"Amma abar maganar domin bana jin zan iya haɗa ki da wata."
gyemun sa taja, sai kuma ta ɓata fuska sannan tace "Haka Allah ya ce, bana son ka canza daga halin dana sanka baya yi maka kyau,
dama kan haka kake masaltawa zuciyar ka aje damuwar da bata saba ba, shine har kake son ka koyi karya ko?,
kana son ta, tun daga farkon labarin ta naji nima ina son ta ina son ƴaƴan ta, ita ta musamman ce yarin ya karama mai halin man ya ba kasafai ake samun irin su a duniya ba, ni ma ina son ta, zan ku ci gaba da son duk wani abun da kake so har idan bai saɓawa Shari'a ba har karshen rayuwa ta zan cigaba da son sa."
mike wa zaune yayi ya lankwashe kafafun sa kana ya dubi ta da ɗin bin farin ciki da jin daɗin kasan cewar ta cikin rayuwar sa ya ce
"Haki ka babu wan da yakai ni dace da samun mace ta gari, da ace kowani na miji irin ki ya samo a matsayin mata shi da damuwa ko tashin hankali bazai gansa ba har karshen rayuwa, Allah yayi miki albarka matar aljanna, faran tamin da kike Allah kema ya faran ta miki fara ƴar duma-duma ta."
"Ameen Ameen ameeeeeen."
tafaɗa tana jan ɗan  gyemun sa irin na gayun nan.
sai kuma da sauri ta saki gyemun ta ce
"Ka faɗa mata kana son ta kuwa?."
kai ya girgiza ya ce "Ban faɗa mata ba."
ta ce "To me ya sa?." ya ce "Sabo da baza ta amince ba."
"Kamar ya, zakace bazata amin ce ba, baka tin kare ta da batun ba ka bata laifi." tayi maganar tana rike haɓa.
kuma tun ta yaja kana ya ce
"Um to tana da masifa tsiwar tsiya ce da ita."
dariya tayi sosai tare da tafa hannu ta ce
"Masifa haɗe da tsiwa kuma, a'a kada kayi wa kanwa ta fin tsayi." shiko murmushi yayi yana faɗin
"Allah idan ta fara tsiwa sai kin sha mamaki."
dariyar ta kuma ta ce
"Zata amin ce kai dai je ka latsa ta kuma ka gani in sha Allahu zata amin ce, wata mace ce zataki tayin ka duk haɗuwar ta da dukiyar ta kuwa,
ai mijin nawa da farin jinin sa aka halitto sa, shiyasa ma har gida ake kawo masa hari, wannan bazawarar taka ma jiya ta zo."
dariya duk kanin su suka fashe da shi, zillo tayi gefe ganin yami ko hannu yana kokarin ruko ta, tasan sarai baya so tari yi masa maganar ire-iren waɗan nan matan da suke kawo masa hari.
 janyo ta yayi jikin sa ya rungume yana faɗin
"Zakiyi baya ni." dariyar take tana daɗa shige wa cikin jikin sa.
Kissing yashiga ai ka mata yana faɗin.
"Hakika nayi dace da mace ta gari ƴar uwa ta jini kawa kuma abokiyar shawara,
tabbas duk wan da yasa mi mata kamar ki yagama more yaruwar sa har gaba da abadan,

ke matar aljanna ce insha Allahu da yar dar Allah zamu shiga aljanna ni da ke da kafafun mu."
Baki ta turo gaba ta ce
"To HAMDAH fa?."
ya ce "To har da ita." mumushi tayi tare da daɗa rungume shi ta ce
"In sha Allahu kuwa Allah ya tabbatar mana."
ya am sa da amee. nan suka shiga nuna wa junan su tsantsar kauna da soyayya in da zancen ya sauya suka lula duniyar ma'aurata...

Wane ne AHMAD?......!

Mommyn Twins ce

11

Ahmad Tijjani Sabil shine cikakkoen sunan sa, mahaifinsa Alhaji Tijjani Sabil shahararren ɗan kasuwa ne wan da ya jone da siyasa,yayi suna ya shahara a kaf faɗin Nigeria har ma da kasashen ketare,
mutum ne adali mai gasjiya da rukon amana da son jama'a, yana da taimako matuka musamman ga nakasa dashi.
matan sa biyu Hajiya Karima da Hajiya Harira. Hajiya Karima itace uwar gida shekarun su biyar da ita Allah bai sabu haihuwa ba,
bayan shekaru biyar ɗin yakaro aure in da ya auro Hajiya Haririi, cikin yar da da buwayar Allah tana shiga Allah yabata ciki.
hankalin Hajiya Karima yayi masifar tashi, sai dai bata nuna wa a fili  ƴar kasa take yi dan ta iya makirci, a fili kam nunawa take tana son cikin sosai.
bayan wata tara Hajiya Harira ta haifo ɗan ta namiji yaci suka Ahmad.
Ahmad yatashi cikin gata da soyayya, tun daga kan sa Allah bai sake basu haihuwa ba.
Ahmad ɗa ɗaya tilo ga Alhaji Tijjani Sabil, yayi karatun sa na primary da secondary a nan kasa Nigeria in da daga nan Alhaji Tijjani Sabil yaɗaga sa daga nan ya millashi kasashen ketare acan ya kammala karatun sa in da ya dawo Nigeria da sakamako mai kyau.
dawowar Ahmad Nigeria da wata ɗaya aka ɗaura musu aure da ƴar uwar sa, wato yarin yar kanin mahaifinsa, Rasheedat,

wan da dama can suna soyayya tun kafin ya bar Nigeria, a gidan su ta tashi shakuwa ce mai karfi sakanin su wacce har takai ga haifar da sosayya, yabar ƙasa Nigeria da alkawarin aure sakanin su, dan haka yana dawowa batare da ɓata lokaci ba aka ɗaura musu aure tare da gaggaru min biki, irin namasu akwai.
Ahmad da amaryasa Rasheedat zama suke na amana da sansar kauna da soyayya da tarairayar junan su, basa kaunar abun da zasuyi ya ɓatawa ɗayan su rai, babu wan da yake ɓoyewa wanin sa sirrin sa,
yar da da amin ta da suke yi wa junan su, har ya kai ga suka lankayawa junan su suna, in da Ahmad yake kiran ta da kawa dan acewar sa bashi da kawa kuma aminiyar da ya wuce ita.
ita ce murfin rufe sirrin sa itace sirrin sa ma gaba ɗaya.
Ita kuma take kiran sa da aboki dan kuwa bata da wan da ya fishi, shine kawa kuma aminin ta.
yan da suke gudanar da
rayuwar su gwanin ban sha'awa.
bayan wasu shekaru da auren su mahaifinsa sa wato Alhaji Tijjani Sabil yayi hasarin mota a hanyar sa na zuwa airport in da zai tafi kasar waje domin gudanar da wasu kasuwancin sa, nan take Allah ya karɓi rayuwar sa.
Bayan rasuwar sa da shekaru biyu Hajiya Hariri wato mahaifiyar Ahmad ita ma ta rasu, sakamakon ciwon zuciyar da ya kamata bayan rasuwar mijin ta da yayi faraɗɗaya batare da ciwo ba.
Ahmad yashiga tashin hankali rashin uwa da uba daga karshe ya fawwalawa Allah komai.

Bayan rasuwar mahaifansa duk kanin ragamar dukiyar mahaifinsa da kaddarorin sa yadawo karkashin kulawar sa, shiyake kula da komai sakanin dukiyar sa da kuma dukiyar mahaifinsa.
Shekaran su 8 kenan da aure Allah bai basu haihuwa ba,
ko dai-dai da rana ɗaya Ahmad bai taɓa sawa kan sa damuwa kan rashin haihuwar su ba, ya san cewa Allah ne bai kawo lokaci ba,
shi yake rarrashin Rasheedat a duk san ta nuna damuwar ta kan rashin haihuwar nasu.
yakan yi mata tuni kan cewa Allah ne mai badawa kuma bai mance da su ba lokaci ne dai baiyi ba.
Ahmad mutum ne mai son yara duk da kasan cewar sa mutum mai son yara, bai taɓa tunanin kara aure wai ko dun zai sami ƴaƴa ba.
a duk in da yara suke zakaga ya na yawan ziyar tar gurin, kamar makarantun yara da gidan marayu, ko tafiya yake idan yaga yara sai ya tsaya ya nimi yayi musu wasa da kuma kyauta, shi yasa yawan cin taimakon sa tafi yawa kan yara da gajiyayyu, sai dai masu karfin ma bai barsu ba.
Ahmad yayi suna a duk faɗin Nigeria tai makon sa yazaga ko ina.

(Wannan kenan kaɗan daga cikin labarin Ahmad)★

A can cikin garin Bauchi

Ummi Aunty Rafee'at da Aunty Jaleela Nusaiba ne zaune cikin parlour'n Ummi, suna ta hira, kamar yadda suka saba a kowani makon karshen wata suna kawo wa iyayen su ziyara.
suna tare cikin parlour suna ta hira,
Fauzan ne yafito daga cikin bedroom ɗin Ummi hannun sa na bayan sa da alama wani abun yake ɓoye wa. Aunty Rafee'at ta dube shi tana faɗin
"Autar Ummi me kake yi ne cikin ɗakin ka ɓata shiru kamar baka nan?."
"La wayar ki Aunty Rafee'at ya ɗauka yaje ya ɓoye yake yin Game da shi." Nusaiba ta faɗa tana rike haɓa da yin sama da wuya tana leka abun da yake ɓoyewa bayan shi.
harara ya dalla mata tare da faɗin
"To haɗel ina ga wayar Aunty Rafee'at ɗin can kan hannun kuje ra."
huf Nusaiba ta mike dan son ganin abun da yake ɓoye wan, ta bayan sa tazo ta fizge abun da ke hannun san
tana faɗin
"Ai sai naga abun da kake ɓoye wan in ma abu na ne sai ka bani."
rikewa yayi da karfi bata sami damar kwace wa ba ya ce
"Dalla masa can idan kika yaga fa."
"La Fauzan mu gani a ina ka samu."
Nusaiba ta faɗa tana mika hannu ya bata abun da ke hannun sa,
kusa da Aunty Rafee'at ya zauna in da dama nan yake zaune ɗazu kafin ya tashi ya shige wani ɗakin dake gefe a nan cikin parlour'n.
gaba ki ɗayan su suka maida kallon su gare shi kana kamar haɗin baki Ummi Aunty Rafee'at Aunty Jaleela Suka ce
"A ina ka sami hotunan nan?."
da sauri Aunty Rafee'at ta karɓi wasu daga cikin hotunan in da Aunty Jaleela ita ma ta karɓi sauran,
nan take annurin fuskokin su ya ɗauke, damuwa hade da ɗin bin kewar wacce ke cikin hoton yadirar musu lokaci guda.
a ɓangaren Ummi kuwa kasa iya furta komai tayi gaba ɗaya jikin ta yayi sanyi, ɗan kuzarin da ke tattare da ita ya kauce.
Fauzan ya ce
"A ɗakin da aka zuba kayan Aunty HAMDAH na samu cikin akwatin ta."
"Allah sarki HAMDAH dube ta kamar a kirata ta amsa."
cewar Aunty Rafee'at tana nuno wa Aunty Jaleela ɗaya daga cikin hoton HAMDAH da suke hannun ta.
karɓar hoton tayi tana duba yayin da idanun ta suka kawo ƙwalla.
wani hoton ta Aunty Rafee'at ta zubawa ido nan take sai ga hawaye shar a idon ta, murmushi tayi yayin da ƙwalla ke cigaba da zuba a idon ta, kana ta ɗago hoton ta na faɗin
"Kaga ƴar gidan Inna an sha gayu, Jaleela kin tuna hoton nan?."
Amsar hoton tayi ta ce "Wannan hoton kamar shine wan da ranar da mukaje Dass muka samu taje takar ɓo shi nan ko?."
dariya
Aunty Rafee'at tayi yayin da ƙwalla ke cigaba da zuba a idon ta tace "Ƙwarai shi ne taci ƙwalliyar ta Inna'r ta ta bata kuɗi taje ta ɗauki hoto, ta kawo kikayi ta kushe wa har Inna ta ce

mu tattara mu koma in da muka fito, tun da tsiya zamu kawo mata gida, kin san Inna da HAMDAH, Allah sarki Inna Allah yayi miki rahama."
Aunty Jaleela tayi murmushi tare da share wasu zafafan hayen da suka zubo mata ta ce
"Ai ita ta fara taɓo ni wai naga hancin ta ashe dama haka yake ko Ya SALEEM ɗin da ake cewa hancin su iri ɗaya nata yafi nashi ƙyau,
in duba na gani ta fini ƙyau."
"Ke dai baki da hakuri HAMDAH kuma zolaya."
cewar Aunty Rafee'at tana murmushi.
ta ce "Allah babu waninnan Aunty Rafee'at kin san kakar ta ai bata ganin laifin ta yarin yar nan ta raina ni kamar ni wata sa'ar ta bacin na bata shekaru da yawa, ko Ummi?."
ta karasa maganar tana duban Ummi dake zaune shiru.
Ummi ko kai ta jinjina tare da mai da hawayen da suka ciko idon ta kana ta ce
"Ganin ta ma har tayi miki rashin kunyar ai abun daɗi ne."
kaf parlour'n yayi tsit yayin da zuciyoyin su ke kuna tunani da kewar HAMDAH yadawo musu sabo fil a zukatan su
hannu Ummi ta kai ta share wasu zafafan hawaye tana faɗin
"Ko wani hali take ciki ko a muce ko a raye Allah kaɗai ya barwa kan sa sani."

Sallama Abba da yanzu shigowar sa yayi, duk babu wan da ya amsa masa, har ya karaso cikin parlour'n ya zauna babu wan da ya lura da shigo war sa,
ya fahimci duk kanin su hankalin su baya tare da su,
yana zama kuwa dai-dai lokacin Ummi take faɗin, kalmar ta na karshe.
shiru yaɗan yi yayin da yanayin sa yasau ya.
gyaran murya Abba yayi, sai a lokacin duk kanin su suka juyo in da yake, nan suka shiga yi masa sannu da dawowa,kana ya mike jiki ba ƙwari yayi cikin bedroom ɗin sa...

A can cikin unguwar

G.R.A kuwa

Na'ima na hango da kawar ta Raliya zaune cikin bedroom ɗin Na'aima, daya daga cikin ma'aikatan gidan ne tayi sallama bakin kofar ɗakin,suka ce ta shigo.
ta shigo rike da yaro a hannun ta wan da akalla zai iya kai wa wata 11 zuwa shekara ɗaya, baki Raliya ta washe tana faɗin
"Kawo min shi nan kaga magajin gida ɗa ga Abdallah Idris Abdallah in kiya SALEEM, kaga Irfan ɗan gidan SALEEM sai girma yake."
mika mata shi ta yi ita kuma tayi waje.
dariya Na'ima tayi ta ce
"Kai aminiya wannan kirari haka har kinsa naji wani karin da ɗi."
zama Raliya ta gyara kana ta dubi aminiyar nata ta ce
"Sha kurumin ki kiji daɗin ki wata rana kece ke rike da ragamar dukiyar SALEEM."
tafawa sukayi tare da shekewa da dariya Na'ima tace

"Kamar yan zu kuwa, ko yanzu ma na fara jin kamshin su."
wani dariyar suka kuma shekewa da shi.
kana Raliya ta dubi ɗan tana faɗin
"Wai har yanzu bai fara tafiya bane duk uban kayan in ganta lafiyar da ake tafka mishin nan?."
"Sati biyu daya wuce yafara ɗan takawa, ai kam yana yana ci da shan abubuwan guna jiki dan duk fitan da SALEEM zai ya idan zai dawo sai ya shigo da wani abun."
Raliya ta ɗago yaron tana dudduba jikin sa tare da faɗin
"Ai kuwa dubi jikin sa kamar ɗan turawa luwai-luwai da shi sai sheki yake."
shiru sukayi da maganar nasu jin an turo kofar,
Ya SALEEM ne ya shigo da sallama ai kuwa yaron najin muryar sa ya fara tsalle yana mika hannu,
daga bakin kofar ya tsaya lai dar dake rike a hannunsa ya aje nan bakin kofar,
Raliya ta gaishe sa kai a kasa kamar mutumi yar kwarai, a takai ce ya amsa mata gaisuwar nata batare da ya dube ta ba,
Na'ima ta mike tare da karɓar Irfan tana faɗin
"Oh ji yaro daga ganin uban sa yaka ma murna wai fa gurin ka yake son zuwa."
tayi maganar tana nufo shi,
kafin ta iso in da yake yajuya yayi waje.
bin bayan sa tayi tana faɗin
"My SALEEM barka da dawowa."
"Yau wa." yafaɗa a takai ce tare da nufar side ɗin sa tabi bayan sa.
yana shiga bedroom ɗin sa, wayoyin sa ya zuba su kan beside kana yashiga tuɓe kayan jikin sa.
in da yake ta karaso cike da muryar kirsa ta ce
"My SALEEM tun ɗazu Irfan yake ta murnar ganin ka baka ganshi bane?."
bai yi magana ba sai da ya karasa tuɓe rigar jikin sa kana ya mika hannu ya karɓi yaron, shiko sai washe baki yake, murmushi yayi masa tare da lakace kumatun sa kana ya ce
"Hy ykk." baki yaron yakuma washewa.
sai ya mika mata shi kana ya cigaba da tuɓe kayan jikin sa, yarage daga shi sai boxes kana ya wuce bathroom.
baki ta taɓe ta gyara rukon yaron tayi waje,
tana shiga ɗakin ta Raliya ta dube ta ta ce
"Ya naga kin dawo da shi bazaki bar sa gun uban sa suzau na ba."
baki ta taɓe tana zama bakin gado,
ta ce "Ai wannan uban nasa murɗaɗɗen uba ne ke bakiga shigo war sa da nake masa magana juya wa yayi ya fita batare da yace ko mai ba, da ace agaban wasu yayi min ai da ya dizgani dan ma Allah ya taimaka a gaban ki ne."
"Wai kina so ki ce min baya karɓar sa ne ko me?."
"A'a yana karɓar sa har ma yayi masa wasa ko kwanakin can ma dayayi ciwo yake hanani bacci ɗaukar sa nake da daddare na kai masa shi su kwana, yana yi masa wasa amma yan da yake masan bai min ba,
baya nuna rawan jiki irin wan da uba yake nuna wa kan ɗan sa musamman idan yaro yana karami kamar shi ɗin nan,

wani lokaci har nayi tunanin na nime ki muje gurin boka sai kuma na shashantar da abun, dan nasan miskilanci a jinin sa yake, in baki mance ba boka ma haka yace mana, shi yasa ma kawai na dai na damuwa."
Numfashi Raliya ta sauke ta ce
"Har naji sanyi in dai wannan ne kawai ai bawata matsala bace, adai juri zuwa rafi, ina labarin kuɗin da Dr Mukhtar ya nima lokacin jinyar Irfan ɗi, kai Dr Mukhtar bashi da mutunci in dai a kan kuɗi ne to komai ma zai iya."
matso wa kusa da ita Na'ima tayi, kana ta waiga gefe da gefen ta sannan cikin kasa da murya ta ce
"Ai baki sani ba shekaran jiya ya tura masa da 500k kan wancan 500k ɗin nan yanzu jibi zamo koma asibitin na basa kason sa na am so nawa, daga nan kuma yakuma tsara yan da wani kuɗin zai kuma zuwa."
dariya Raliya tayi suka tafa tace
"Kai aminiya daga haifan yaron nan zuwa yanzu da ko shekara bai cika ba an tatse sa abun da ya fi 5 Miliyan."
fuska Na'ima ta yamusa tare da faɗin
"Um ai ma dai wani wahalar banza nake, kuɗin nan namune ni da magajin sa, da na karɓi wannan bazan kuma karɓar wani ba, zan karɓe su ne a dunkule da zaran lokaci yayi."
Raliya zatayi magana wayar ta ta fara ring, tsaki taja ganin mai kiran nata tare da tura wayan gife.
Na'ima ta dube ta ta ce "Ya dai aminiya ba tsohon kamu kenan."
ta ce "Rabu da jarabebbe sai azabar jarabar tsiya baya bada kuɗin arziki, ranar kusan kwana yayi a kaina yaɗau naira dubu 50k yabani, shine yau ma yake son muje mu kwana, ina zan iya wannan tsiyar sabon Alhajin dana yi yanzu haka mun shirya tafiya kwana da shi, account ɗi na yayi nauyi yaushe zan tsaya kula irin su kananun ƴan iska,
tsabar jarabar sa wai baya gane yin harka da roba wai zai cire nace wlh kana cire wa zan fita na tafi,
na isa ai na san waɗan da nake harka da su ba condom."
dariya Na'ima tayi tana faɗin
"Ai da kun je shima an gwada lafiyar sa sai kuce gaba da fafata wa."
"Allah ya sawake min ai bana harka da talaka irin sa dubu 50k fa, ka kwana a kai na kaɗau naira dubu 50k ka bani kamar na zama shegiya."
wani kiran da ya kuma shigo wa wayar ta ce ya katse musu hirar ɗaga wayar tayi rai ɓace dan a tunanin ta wannan wan da taki ɗaukar kiran sa shi yakuma kiran ta yanzu.
murmushi ta sake ganin ba shi bane wan da take sumayen jin kiran sa ne,
ta ɗaga kiran cikin kwarewa da iya bari ki ta kara wayar a kunne.
mike wa tayi tana faɗin
"Okay I'm coming."
sai ta sauke wayar a kunne, ta dubi Na'ima ta ɗauki jakar ta tana faɗin
"To alhaji na ya zo bari na tafi sai mun yi waya."
tayi mata sallama ta tafi.

Abuja★

Yau tun tashi na nake jin jikina ba daɗi da alama zazzaɓi ne ke son rufe ni, a daddafe nayi al'walan sallar a zahar nazo na gabatar da Sallah.
ina idar wa na haye gado naja bargo na rufe jikina, kasan cewar yau Lahadi babu school su Naseem suna gida,
so nake na samu na ɗan rumtsa kafin su shigo, ko zan samu baccin ya saukar min da zazzabin, dan bazan iya shan masa magani ba kwata-kwata bazan iya ba dan zan iya yin amai. kwanciya ta na gyara ina jan hanci na daya toshe, nasan zazzaɓin mura ne na ruwan sanyin dana yi ta shiga, kwana biyu ana sanyi ruwan cikin swimming pool yana yin sanyi sosai kuma haka nake shiga ciki.
idanuna na lumshe a hankali ina jin kaina na tsara min, so nake nayi bacci ko zan samu zazzaɓin yaɗan sauka, batare da nasha magani ba.
Nasmah ce ta turo kofa da gudu ta haye gadon ta faɗa jikina, ta yaye blanket ɗin dana rufe jiki na har zuwa kai na, ta leko fuska ta tana faɗin
"Mommy kina da lafiya ne?." murmushi nayi tare da gyaɗa mata kai, da jin kalar hausan nata, idan zata ce mutum bashi da lafiya sai tace wai yana da lafiya ne.
fuska ta ƙwaɓe tare da mara baki ta ce
"Nima ina da lafiya." tayi maganar tana shige wa cikin blanket ɗin.
kwanciyar ta na gyara nayi mata pillow da hannu na, na dube ta da murmushi ganin yan da take ta wani mammatse ido tana cuno ɗan karamin bakin ta gaba wai ita a dole bata da lafiya.
na ce "Me ke yi miki cewo?." kyakkyafta ido tayi takuma cuno ɗan karamin bakin nata gaba kana ta nuna kan ta da yatsar ta. na ce "Kan ki ke yi miki ciwon?."
ta ce "Eh cine yake min jafi."
shafa kan nata nayi tare da faɗin
"Sannu bari nasa Dr yazo ya baki magani ko zai bari." kai ta gyaɗa,
mumrmushi na kuma ganin ta mai da idanun ta ta lumshi nasan bacci take ji sai na ja blanket ɗin na gyara rufe mata jikin ta, ina mai cigaba da kallon fuskar ta da murmushi wato adole tun da nima bani da lafiya ita ma bata da shi, oh Nasmah kenan iyayen manyan ce.
a hankali nima na mai da idanuna na lumshe babu jimawa kuwa bacci yayi awon gaba da ni.

Da misalin karfe 4:30Pm na farka na ɗan ji daɗin jiki na sabo da baccin da nayi amma dai hanci na na nan a toshe ciwon kan ma haƙa.
ahankali nayi ƙoƙarin ɗaga kan Nasmah a hannun na na maida shi kan pillow sai ta farka, sai na ɗago ta nayi da ita bayi wanka nayi mata kana nafito da ita, ni ma na koma nayi.
bayan na idar da sallar la'asar na saka kaya itama na saka mata, kana na ruko hannun ta muka fito, kasa muka sauka muna shiga cikin parlour'n Naseem da Faty suka shigo, zama nayi ina faɗin
"Gara da bakuzo tun ɗazu ba sai da muka gama baccin mu."
dariya Faty tayi tare da faɗin
"Kai Adda HAMDAH ai har munfito ɗazu zamu zo, sai kuma muka wuce gun lilo, da mun hana ku bacci."

murmushi nayi na ce "Gara da kuka tsaya can gun lelon ai da yanzu kun hana mu yin bacci ku bakuyi ba mu ku hana mu yi."
Talatu data dire tray'n abinci saman kan table ɗin gaban mu, ta ce
"Barkan ku da hutawa, uban ɗaki na muje kayi wanka naga gimbiya kam da wankan ta ta sauko, kai ne ka tsaya gun lilo ko ka ɗebo rana."
tayi maganar tana ruko hannun Naseem.
sukayi cikin bedroom...

Washegari ya kasance ranar Monday bayan su Naseem sun tafi makaranta bacci na koma, cikin bacci naji wayata tana ring, idanuna a rufe na mika hannu na janyo wayar, na ɗago shi tare da buɗe idanu na kan shi, ganin sunan daya bayyana kan screen ɗin wayar.
yasani ware idanuna sosai, sunan shugaban makarantar su Naseem ne.
nayi saurin ɗaga kiran tare da kai wayar kunne, muryar sa na jiyo hankali tashe yana faɗin
"Madam gamu a asibiti Nasmah ta."
ɗip wayar ta yanke cikin tsananin firgici na mike zaune nan da nan na nimi baccin da nake ji ɗin na rasa,
hannunna na ɓari na dan na number sa na mai da masa kiran, yayin da nake jin kirji na na dukan uku-uku.
"Innalillahiwa'inna'ilaihirraji'un." na furta a fili, wayar tayi ta ring har ta kusa yanke wa kafin aka ɗaga da sauri cikin matukar firgici da tashin hankali na ce
"Ina Nasmah take me ya same ta?!." ya ce
"Gata nan kwance ta......!

Mommyn Twins ce

12

Da sauri cikin matukar tashin hankali tun kan ya karasa abun da zai faɗa na ce "Tamutu tamutu ko?!!."
nayi maganar hankali a mugun tashe dan nagama tsinkewa da yan da naji yake maganar.

ya ce "A'a Madam ba mutuwa tayi ba, dama bata da lafiya ne?,
tun zuwan su School ɗin Aunty'n su tace taga yanayin ta kamar batajin daɗi, shine ta tambaye ta sai tace mata wai kan ta keyi mata zafi, to tafita taje ta ɗauko magani a office kenan ta dawo ta samu tana rike da kanta tana kuka tana faɗin kanta zafi, kan tayi aune ma ta faɗi kasa a sume, tun ɗazu muna asibiti ban so kira na sanar ba sai ta farfaɗo amma har yanzu likitoci sun kasa shawo kan ta."
"Innalillahiwa'inna'ilaihirraji'un wlh lafiyar ta lau ta bar gida."
na furta da karfi yayin da jikina ke cirawa cikin azama na duro a gadon wayar na kare a kunnena ina tambayar sa wani asibiti ne, yana faɗa min nakashe wayar batare da na tsaya sauraran abun da yake cigaba da faɗa ba.
wardrobe na buɗe na janyo mayafi na takalmi mara tudu na saka da sauri nafita na nufi ƙasa, bibbiyu nake haɗa steps,ina sauka na nufi kofa har ina haɗawa da sassarfa.
su Talatu suna zaune cukin parlour'n da sauri suka mike ganin yanda na sauko a firgice, tambaya ta me ke faruwa suka shiga yi suna biyo ni a baya,
tuni nayi waje ban tsaya basu amsa ba, har parking lot suka bini, suna tambayar abun da ya faru. sai a lokacin na ce da su "Nasmah ce ke asibiti asume."
salati suka shiga yi suna tambayar garin yaya.
wan nan karon ban tsaya basu amsa ba dan ji nake tsayuwa basu amsa ma ɓata lokaci ne.
kan kace me sabbin Security ɗin da aka zuba cikin gidan sun iso in da muke, ganin yan da su Talatu suketa rafka salati, suma duk tambayar da suke ban tsaya basu amsa ba, su Talatu ne suka sanar musu abun da ke faruwa.

Yakubu nashiga kwaɗawa kira,
da sauri haɗe da gudu yafito daga cikin ɗakin su, da sauri na shige cikin mota, yana ganin haka ya koma ɗakin da sauri ya fito rike da makullin motar cikin hanzarin yashige motar.
cikin matukar da muwa da rawar murya nace
"Yakubu kayi sauri ko ka bani key ɗin motar ni naja."
key yayi wa motar tare da figar ta aguje, da gudu mai gadi ya buɗe get muka fita a gidan, sai da muka haura titi kafin yake tambaya ta in da zamu nafaɗa masa sunan asibitin.
duk gudun da Yakubu yake gani nake kamar bayayi asibitin tayi min nisa.
Number da aka kira ni da shi aka sanar min da tana asibitin na kuma kira wayar tayi ta ring ba'a ɗaga ba,
kuka ne naji ya zo min nayi saurin toshe baki na a raina nake faɗin
"Shike nan ta mutu."
kokarin mai da kiran nake dai-dai nan najiyo muryar Yakubu yana faɗin
"Hajiya mun iso."
da sauri na ɗago dan ban san har mun iso ba.
da sauri na buɗe motar na fito batare da na jira faɗin da yake bari ya zo ya buɗe min motar ba.
da sauri haɗe da sassarfa nayi cikin asibitin, a kofar shiga cikin parlour'n asibitin na haɗu da Aunty'n su Nasmah tana kokarin fitowa cikin sauri take tafiya da ka ganta gaba ɗaya hankalin ta a tashe yake.
tana gani na ta juya da sauri tana faɗin
"Madam ta farfaɗo amma tana ta kuka."

da sauri nabi bayan ta ina faɗin "Ina take."
tun da ga cikin parlour'n nake jiyo kukan ta, da gudu nanufi kofar room ɗin da nake jiyo kukan ta ciki,
wasu daga cikin ma'aikata asibitin sukayi yunkurin dakatar da ni, ban ko saurare su ba
na tura kofar na sa kai ciki.
ina ji Yakubu daya biyo ni yana sanar musu da ko ni waye.

Likitoci har guda uku a tsaye a kan ta suna rirrike da ita sai ihu take tana bige-bige, da gudu na isa in da take na kusa sakanin su na rungume ta,sai kawai nima na fashe da kuka ina faɗin "Nasmah me ya same ki, me ya same ki Nasmah?!!."
kuka sosai na ke ina rungume da ita, itama kukan take tana ta fisge-fisgen nan kamar wacce bata cikin gayyacin ta.

Turo kofar aka yi da karfi yana gaba wani na biye da shi.
in da muke suka karaso da sauri, wan da ke biye da shi ɗin ya dubi likitocin da ke cikin ɗakin yana faɗin
"Wai har yanzu bakuyi wani abu a kai ba?."
cike da girmamawa sukace "Sir muna kai kenan yanzu ta farfaɗo so taki tsayuwa Muna kan kokari ke nan mu shawo kan matsalar, ruwa za'a saka mata sai dai taki tsayuwa sau uku ana samun jijiya sai ta gauce ya ɓata, zamu nima ta kafan ta ko kai ne a saka mata, na hannayen ta kam duka mun rasa su."
cikin faɗa Dr da suka shigo tare da Ahmad da alama  shine babban su ya ce "Shirmen banza sai kace ba ai kin ku ba."
sai kuma ya dubi Ahmad ya ce
"Sorry Sir ko mai zai dai-dai ta insha Allah."
kai kawai Ahmad ya jinjina ya ɗan maso in da nake rungume da ita ya ce
"To meye amfanin kukan, kin rungume ta kina kuka ita tanayi, to da wanne zata ji da ciwon da ke damin ta ko da wannan kukan naki?."
hannu ya mika ya ɓamɓare ta a jikina, sake masa ita nayi dan na rasa abun yi guda ɗaya ganin yanayin nata yakuma jefani cikin kiɗi ma, da firgici da tashin hankali, ya ɗago ta ya saka ta a kafaɗar sa ya na faɗin
"Kun ɓula ta da yawa dubi yan da hannayen ta suka fara kumbura."
"Sorry Sir ta ki tsayuwa ne."
ɗaya daga cikin likitocin yafa ɗa. tsaki yaja kana ya ce
"Me yasa tun kan ta farfaɗo baku ni mi jijiyar ba, sai da ta farka zakuyi ta ɓula ta."
"Sorri Sir hakan bazai yiwu ba do le sai ta farfaɗo."
tsaki yakuma ya, yana jijjiga ta da bubbuga bayan ta, yana faɗin
"Shiiit ya isa sorry baby yi hakuri kin ji sorry sorry."
maganar yake daf kunnen ta yana ci gaba da jijjiga ta da bubbuga bayan ta.
baya nayi, najin gida na da jikin garu-bango, ina mai cigaba da kukan cikin yin kasa da sauti.
Dr da suka shigo da shi ya ya nufi kofa yana faɗin
"I'm coming Sir." sai yayi waje sauran likitocin suka bi bayan sa.
bai yi magana ba sai ci gaba da jijjiga ta da hura mata iskar bakin sa cikin kunne yake, a

hankali kukan nata yarika raguwa, sai ajiyar zuciyar da take sauke wa a kai a kai,  har tayi shiru tana mai cigaba da sauke ajiyar zuciya.
jim kaɗan likitan ya dawo wannan karon su biyu suka shigo, yana gaba ɗaya daga cikin waɗan da ɗazu suke kan ta na biye da shi rike da wasu kayakin amfani irin na ma'aikatan lafiya.
Dr ya dubi Ahmad da murmushi yana faɗin
"Ikon Allah abun da mu likitoci muka kasa yi gashi uba yayi wa ɗiyar sa, baby da ma so kike sai Daddy'n ki yazo kafin ki bamu damar yin ai kin mu ko."
yayi maganar yana leko fuskar Nasmah da ke lumshe da alama bacci ke son ɗaukar ta.
murmushi Ahmad yayi yana shafa kanta, kana ya ce
"Yan zu zaku iya yi mata abun da ya kamata."
Dr ya ce "Okay." ya mika hannu ya karɓe ta yana kokarin kwantar da ita kan gado.
ai ko ta buɗe ido tare da sakin kuka.
da sauri Ahmad ya ɗauke ta yashiga jijjiga yana faɗin
"Shiiit Nasmah ya isa yi shiru jinki."  ai ko tayi tsitt,har kuma lokacin ida nunta suna lumshe.
zama yayi bakin gadon kana a hankali ya kwantar da ita yana ɗan jijjiga ta da faɗin
"Sorry kwanta a saka miki magani kiji sauki ko,babu zafi yanzu a gama miki mu tafi hawa doki."
alama yayi wa Dr da ya soma ai kin sa, yakuma ce masa yabita a hankali, kana shi kuma yarika shafa kanta yana yi mata magana a hankali daf da kunnen ta.
 a hankali likitan ya soma gudanar da ai kin sa irin na kwararren likita.
bugun fari ya samo jijiya a hannun ta na dama,
 batare da ɓata lokaci ba ya ɗaura mata ruwa mai ɗauke magunguna masu karfi da inganci.
nan da nan cikin sakanni kalilan bacci yayi gaba da ita.
bayan likitan yagama duk abun da ya
kamata ya dubi Ahmad yana faɗin
"Allah ya sawaka in sha Allah ko mai zaiyi normal idan ta farka."
ya an sa da amin kana likitocin suka fita.

Numfashi na sauke mai sauti san da ido na ya sauka kan Nasmah da ke bacci tana sauke numfashi a hankali, idanuna na rumtse tare da jan sheshsheka cikin kukan da nake har lokacin, sai dai zuwa yanzu kukan nawa a hankali yake fita.
cikin zuciya ta nake yiwa Ubangiji godiya ganin ta sami bacci.
har lokacin yana sunkuye a kanta yana shafa kanta yayin da ɗaya hannun sa ke rike da hannun ta da akayi mata karin ruwa.
maganar sa najiyo yasani buɗe idona a kan sa.
"Ke kin ishe mu da wannan koke-koken na ki, kifita waje kije kiyi sa a can kin dame mu, ko so kike ki tashe ta da Wannan kukan naki mara amfani,
tun tuni yarin ya tana tare da ciwo kin barta da shi a jikin ta har sai da yayi (C), ke baki da wayon sanin yaro bashi da lafiya ne,
a hakan ne kike cewa ke zaki iyar musu yaushe kikayi wayon kula da kanki bare ki kula da su."
baki na murguɗa cikin zubda ƙwalla na buɗi baki zanyi magana, sai wayata ta fara ring, dago wayar nayi ina mai share hawaye ganin Bappa ke kiran, sai nayi picking call ɗin na kara wayar a kunne,
daga cikin wayar Bappa ke faɗin

"HAMDAH wani asibiti ne?."
ina faɗa masa sunan asibitin ya kashe wayar.

Zama nayi kan kujerar da ke gefe na jin kafata ta gaji sosai,
ina mai ai ka masa da harara ina ci gaba da murguɗa masa baki.
magana ya soma yi yayin da idanun sa ke kan Nasmah da take ta baccin.
"Wayon ki a iya nan kaɗai ya tsaya,
sabo da ke baki da wayon magan ce naki shine ita ma zaki barta da shi ko, dubi idon ki ke kan ki ma baki da lafiya amma baki da wayon da zaki iya magan ce ciwon naki."
a fusace cike da tsiwa nace
"Idan kai ke raba wayon bana so karike shi, har abada kada nayi wayo."
nayi maganar ne cike da jin haushi, ban san meye damuwar sa na jifana da kalmar rashin wayo a koda yaushe a duk san da muka haɗu da shi ba.
yabi ya ishe ni da wasu maganganu ya barni naji da damuwar ciwon ƴata.
fuskar Nasmah ya shafa tare da sakin murmushi har sai da dimple ɗin fuskar sa ya bayyana.
baki na taɓe tare da kawar da kaina gefe, dan zuwa yanzu hankali na yafara kwanciya, bai kuma magana ba sai zaman sa daya gyara ya daɗa gyara rukon hannun Nasmah da ke hannunsa sakama kon ɗan zaburan da tayi cikin bacci.
ni ma ido na na mai da kan waya ina ɗan lallatsawa.

Tun daga can waje nake jiyo muryar su Bappa ina kokarin mike wa suka turo kofar, Bappa na gaba Inna Wuro Faty Yakubu da Sule direban su Bappa, suka shigo.
hankali tashe Bappa yake faɗin
"Subhanalillahi garin yaya me ya same ta haka?."
dai-dai nan suka karaso bakin gadon da Nasmah take kwance.
Bappa ya leko fuskar ta yana cigaba da faɗin
"Amma ta farfaɗo ko."
Ahmad ya ce "Eh ta farfaɗo yan zu dai bacci take."
"Masha Allah, kaji ikon Allah ko yarin ya tabar gida lafiya sai kuma ga ciwo, kai sannu Nasmah."
Inna Wuro ta faɗa tana shafa kanta. Bappa ya dubi Ahmad yana faɗin
"Sannu Ahmad sannu fa da kokari Allah ya saka da alheri."
murmushi yayi kana suka
shiga gaisawa, bayan gaisuwa da jajen abun da yafaru Bappa ke faɗin
"Wai haka kawai ta suma kuma me likita ya ce ke da mun ta?."
Ahmad da idanun sa ke kan Nasmah dake ta baccin ta har yanzu kana ya ce
"Typhoid ne har yayi mata (C) da mamaki ace wai ciwo irin haka har yayi yawa a jikin yaro irin haka ba'a sani ba, har yakai matakin da zai iya sumar da ita wai duk ba'a sani ba."
Bappa ya ce "Ikon Allah amma kuwa abun da mamaki, wai da ma bata da lafiya ne HAMDAH? ko irin zazzaɓi a tsatstsayen nan ne take?."
ya karasa maganar yana duba na. da sauri ganin yan da wannan Ahmad ɗin yake taso ya mai da alhakin ciwon ta kaina.
na ce "Lafiyar ta lau bata kuma zazzaɓi a tsatstsaye."
"Kuma bata taɓa ce miki wani gurin ta na ciwo ba, yaro ke nan Allah sarki kuma kema baki taɓa

lura da yanayin ta ya sauya ba."
cewar Inna Wuro, tayi maganar cikin jimami da alhinin ciwon nata.
"Babu wani alamar da na taɓa gani na ciwo tattare da ita, kuma bata taɓa cemin wani gurin ta na ciwo ba, in ban da shekaran jiya da nake
kwance kai na na ciwo ita ma tazo ta ce min kanta na mata zafi, kuma nasan a lokacin ɗin dan nima na ce kai na nayi min ciwo ne shi yasa ita ma ta faɗa."
nakarasa maganar ina ɗaga hanci sama dan ganin yan da ɗan shishshigin nan keta wani girgiza kai. da sauri na mai da idanuna kan sa jin yana faɗin
"Ashe dai ta ma faɗa miki bata da lafiya amma bakiyi serious a kai ba, dan ta faɗi kan ta na zafi lokacin da naki yake ciwo sai ya zama nata karya ne?,
taya za'ayi ki fahimci hakan tun da baki da wayon sanin haka."
ido na waro baki buɗe jin yakuma jifata da kalmar rashin wayo,wai shin wannan mutumin me yake jin kansa ne,shi ji yake yafi kowa wayo kowa yi masa kallon rashin wayo yake?.
a kufule na buɗi baki zanyi magana, Bappa ya katse ni da faɗin
"Ai shi yaro idan ba lura kayi da yananin saba wani ɗan bashi da azancin faɗar abun da ke damin sa, ko da yana jin wani gurin sa na ciwo, sai dai in kai ka gane hakan daga yanayin sa na yau da kullum, kirika lura da yanayin su tanan zaki rika fahimtar ciwon su,
Allah sarki da gaske kan nata nayi mata ciwon ne sai tace yana yi mata zafi, Allah yabaki lafiya Nasmah."
Amin duk aka amsa da shi, baki na tura gaba muna gaɗa ido dashi na murguɗa masa baki, wani murmushi ya sake sai da dimple ɗin sa suka bayyana,ya mai da idanunsa kan Nasmah yayin da fuskarsa ke nan ɗauke da murmushin nan.
ido na ɗan kurawa fuskar sa wan da dimple ya daɗa kawata shi. baki na taɓe ina mai ɗauke idanuna a kansa...

Muna nan cikin ɗakin kiran sallar azahar ne yasa su Bappa fita dan zuwa masallaci, har da shi, yarage daga ni sai Inna Wuro da Faty.
Inna Wuro ta shiga toilet ɗin cikin ɗakin ta yi al'wala tafito tace da ni naje nima nayi muje masallacin cikin asibitin muyi sallah, tun da ga Faty in muka dawo sai itama taje tayi... muna isa masallacin ana idar da sallah, su mazan suka koma ciki mukuma muka shige cikin masallacin. ko da muka idar muka koma ciki, abakin gadon na kusa da Nasmah in da ɗazu yake nan yanzu ma yake zaune.
zaman mu baifi da minti 20 ba akayi knocking ɗin kofa, Yakubu dake tsaye ta kusa da kofar yabuɗe.
wasu maza guda biyu suka shigo niki-niki da kayan abinci duk kanin su sanye da rigonan irin na ma'aikatar hotel.
cikin girmamawa suka shiga gaida Ahmad kana suka gaida ƴan cikin ɗakin, suka dire manyan basket ɗin dasuka shigo dashi, nan suka shiga zuba abinci suna mikawa kowa, da mamaki nake kallon su dan nidai a sani na ban bada umurnin kawo abinci daga wani hotel ba.
maganar ɗaya daga cikin mutanen naji ya na faɗin
"Gashi hajiya." ɗago idanuna nayi daga kan wayar da nake natsawa na dube shi, plt ɗin abinci yake miko min, kai na girgiza tare da faɗin
"Nakoshi."

"A'a me kikaci HAMDAH nasan tun fitar ki ba abin da kika ci."
cewar Bappa yana duba na.
"Bana jin yunwa." nafaɗa ina mai da idanuna kan wayar. "Zama da yunwa bashi da amfani wan da gashi komai yazo da sauki kici abinci itama bakiga tana baccin ta ba, sauki ce ke samuwa cikin bacci insha Allah."
Inna Wuro ta ce "Insha Allahu kuwa lafiya nata kan samuwa."
ni dai ban kuma cewa komai ba,
plt ɗin abincin suka mikawa Faty dake kusa da ni.
wani ɗan ma dai-dai cin basket daga cikin waɗan da suka shigo da su, abincin cikin sa na musamman shi suka zuba masa suka mika masa hannu ya daga tare da faɗin
"Akarawa kowa yaci."
Bappa da yakai loman abinci yahaɗi ye ya ce "A'a Ahmad ai wannan ma ya ishe mu maza karɓi ka ci wannan ya ishe mu haka ga abibci nan idan bamu koshi ba duk zamu kara, Allah ya saka da alkhairi an gode sosai Allah yakara buɗi."

Jin yan da Bappa yake ta zuba masa godiya yasa nasan cewa shi yayi odar abincin, baki na taɓe a raina nake faɗin
"Sai kace ance masa bamu ci abinci bane ko yunwa ke damin mu."
wayar sa ce tayi kara yamike yafita batare da ya karɓi abincin ba,
Bayan sa nabi da kallo
"Gulma shi da yasa a kawo dan tsabar gulma shi ne yaki ci to da waya mai da mayunwata."
Faty dake daf da ni ta juyo tare da faɗin
"Adda HAMDAH me kika ce?."
"A'a bada ke nake ba da wancan ɗan gulmar nake."
"Wafa?." ta faɗa tana kallon waɗan da suke cikin ɗakin.
"Ba kowa." na faɗa ina mai da idanuna kan waya.
tun da ya fita bai dawo ba ganin ya jima sosai bai dawon ba yasa nayi tunanin ya tafi ne, gara ma ya tafin ɗan shishshigi.
har wajen la'asar muna nan zaune Nasmah bata farka ba zuwa lokacin kam bakin gadon na dawo na zauna. akai-akai likitoci ke zuwa duba ta, tun bayan fitar sa.
ana kiran sallar la'asar su Bappa suka fita bayi Inna Wuro ta shiga ta ɗauro al'wala tafito ta shinfiɗa sallayar da nasa Yakubu ya ɗauko a mota, ina nan zaune kusa da Nasmah da har lokacin take ta kan bacci, ido na tsura mata gaba ɗaya yanzu na kagu ta farka. na ɗau alwashin duk likitan da yakuma zuwa zai saka wani allura cikin drip ɗin dake shigan ta zan hana, dan na lura kamar shi ke da ɗa sata cigaba da baccin. ban tashi ba har sai da Faty ta idar da nata sallar, kana nashiga toilet ɗin room ɗin bayan nayi al'wala nazo na gabatar da salla.
ko da na idar ina nan zaune kan sallayar ina lazumi,da sauri na ɗago kaina jin  Inna Wuro tana faɗin
"Nasmah kin farka ne?."
da sauri na mike ganin tana ɗan motsa hannun ta, da sauri Inna Wuro dake gefen ta ta roko hannun nata da aka mata karin ruwa da shi take ta kokarin ɗaga shi,
cikin hanzarin na iso bakin gadon ina faɗin
"Nasmah Nasmah tashi kada ki sake komawa baccin nan."

a hankali ta buɗe idanun ta na bin cikin ɗakin da kallo.
sannu Inna Wuro da Faty suka shiga jera mata.
ɗaya hannun ta na roko da murmushi ganin idanun ta wasai naci gaba da faɗin
"Sannu Nasmah kan naki ya dai na yi miki zafin?."
fuska ta kwaɓe sai kuma ta fashe da kuka.
"Subhanallahi yi hakuri kinji Nasmah yi shiru kinji idan kikayi kuka kan zai ci gaba da yi miki zafin fa yi shiru abin ki."
Inna Wuro ta faɗa da alamun rarrashi.
kai na gyaɗa tare da faɗin
"Eh kin ji yi shiru abin ki Nasmah." sautin kukan nata takuma karawa tana ta kokarin fizge kannulan da ke hannun.
da sauri ya turo kofar ya shigo , cikin hanzari ya iso bakin gadon. ta gefen da nake ya tsaya tare da ruko hannun ta da hannuna ke kai, da sauri na ɗauke hannuna dan yan da ya sauke hannu nasa kan nata sai da ya taɓa nawa hannun.
ɗan matsawa nayi ganin yan da mukayi daf da juna.
"Shiiit ya isa haka bar kukan nan."
ya faɗa yana shafa kanta kana ya ɗago wayar sa ya daddanna ya kai kunnen sa "Na shigo." yayi maganar yana sauke wayar.
kan ta yaci gaba da shafawa yana kuma cigaba da faɗin
"Yi shiru bari azo a cire miki wannan abun ki huta."

Cikin mintinan da basufi 3 zuwa 5 ba Dr ya shigo ya cire mata ruwan dan dama saura kaɗan ne ya rage, a na cire mata Ahmad ya ɗago ta ya saka ta kafaɗar sa yashiga jijjiga ta har tayi shiru.
bakin gadon ya zauna kana ya ɗaura ta kan cinyar sa, ya dubi Faty ya ce
"Fatimah haɗa mata tea ta sha." yayi maganar yana kallon basket ɗin da ma'aikatan hotel ɗin nan suka zo da shi suka tafi suka barshi a nan cikin room ɗin.
Faty ta ce tom. ta haɗo tea ɗin da sauri ta mika masa, ya amsa, tare da gyara wa Nasmah zama kan kafarsa ya saka mata cup ɗin a baki yana faɗin
"Sha maza muje ki hau lilon doki daga gun kisha Chocolate ko."
ai ko tabuɗe baki ya kafa mata cup ɗin, sai da tasha fin rabi kafin ta ɗaga kanta.
Dr dake tsaye a gefen su yayi dariya tare da faɗin
"Nasmah Daddy ne kaɗai mai yin rarrashi a yarda ko?."
Inna Wuro ta ce
"Ai kam mu duk rarrashin da zamuyi sai dai ta sa mana ihu."
duk sukayi dariya ban da ni da kuma shi da ya murmusa.
"Ɗan shishshigi." nayi maganar a kasan raina tare da jan guntun tsaki a fili. duk suka juyo suka kalle ni.
Inna Wuro taciga da faɗin
"Har uwar tata ma taki yar da rarrashin nata."
mike wa yayi tare da sakata a kafaɗar sa yasoma tafiya tare da faɗin
"Tasan itama bata wuce rarrashin bane."
yana kaiwa nan yayi waje Dr ya rufa masa baya, ido na waro tare da yin kwafa wannan mutumin sainayi maganin sa.

Inna Wuro da Faty kuwa dariya sukayi.
Faty ta ɗauki sallayar da mukayi sallah muka nufi waje.
a can farfajiyar asibitin muka iske su suna tsaye suna magana da Bappa.
kafin mu karaso ya shige motar sa in da ya saka Nasmah a gefen sa yaja motar mai gadin asibitin ya buɗe masa get ya fita.
cikin takaici haɗe da mamakin karfin hali irin nasa nabi bayan motar da kallo.
bansan dalilin sa na son yimin shishshigi cikin rayuwa ta ba, akan wani dalilin zai tafi da ita, to ma ina zai kaita tun.
maganar Bappa naji yana faɗin
"HAMDAH muje ko." juyowa nayi sai gani nayi har kowa ya shige mota.
"Bappa akan wani dalili zai tafi da ita?."
ya ce "Gida zai kai ta dan taki yar da na karɓe ta kuma aciki ma yace min taki yarda da ku,idan ya barta zatayi ta kuka ne kuma likita ya ce ba'a so tarika kuka, sabo da ciwon kannan nata sai ya iya motsa mata, muje zamu same su a gida ma yan zu,
yaron arziki mai son taimakon al'umma."
da sauri na ce
"Waya ce masa bukatar taimako muke." nayi maganar ina waigin hanyar da suka fita tare da murguɗa baki kamar yana gani na.
murmushi Bappa yayi kana ya ce
"Babu wan da ya ce masa ana bukatar taimako halinsa ne hakan."
juyawa nayi na shige cikin mota ba tare da na kuma cewa komai.

Koda muka isa gida ganin babu motar sa yasa nayi tunanin ko har ya ajiye ta ya wuce ne, da sauri nashiga ciki.
Naseem da ke tare da su Zulai ya rungume ni yana yi min oyoyo.
su Talatu sunayi min sannu da dawowa ya mai jiki, ban iya basu amsa ba sai tambayar su nayi
"Ina Nasmah?."
"Hajiya ba tana asibiti ba."
cewar Zulai. kaina girgiza tare da faɗin
"An dawo da ita gida." Talatu tace "A'a Hajiya ba'a dawo da ita ba."
da sauri na juya nafita waje a sakar gida na tadda su Bappa suna kokarin wucewa part ɗin su na ce
"Bappa bai fa dawo da ita ba."
murmushi yayi tare da faɗin
"Zai dawo da ita je ki huta."
juyawa kawai nayi badun naso ba sai dun bana so nayi masa musu.
Nakai tsawon awa guda zaune cikin parlour zaman jiran dawowar ta,
ganin guri ya fara rufawa magriba ta kusa sai na mike na haura sama, sai da nayi wanka na gabatar da sallar magriba kafin na sauko.
nasa Zulai ta kawo min tea sai a lokacin na sa wani abu a ciki na.
zuwa yanzu kam ina ji bazan iya cigaba da hakuri da sa sammanin dawo da ita ba, yunkurin mike wa nayi dan zuwa gurin Bappa, ya faɗa min gidan sa naje na ɗauko ƴata.
da sauri na waigo kofa jin an turo kofar parlour'n........!

Mommyn Twins ce

HMD

WASA FARIN GIRKI

13

An turo kofar Nasmah ce ta shigo da gudu ta karaso in da nake tafaɗa jikina tana faɗin
"Mommy na dawo."
da murmushi kan fuskata  cike da jin daɗin ganin ta wasai, kamar ba ita bace ɗazu kwance kan gadon asibiti ba'in da take. na
rungume ta sai kuma na ɗan ɓata fuska tare da faɗin
"Sai yanzu kika san da ni? ina ɗazu yi kikai kamar baki sanni ba."
"Taya zatayi kamar ta sanki,da kika barta da ciwo ai ma tayi kirki da yanzu ta nuna ta sankin."
da sauri cikin razana na ɗago kaina jin maganar a sama babu zato ko sammanin jin sa.
cike da ɗinbin mmk nake kallon sa, da tunanin ta yadda akayi ya shigo batare da sanin shigowar nasa ba, da kuma ganin kokarin sa na shigo min parlour kai tsaye.
huf Naseem dake gife na ya mike da gudu yaje ya rungume shi, yana faɗin
"Oyoyo Daddy." sama ya ɗaga shi ya cilla shi sau biyu kana ya dire shi a kasa, yana shafa kansa fuska ɗauke da murmushi, ya ruko hannun sa ya karaso cikin parlour'n.
a saman kujerar da ke fuskatata ya zauna tare da ajiye laidar da ke rike a hannun sa saman table ɗin gaban sa.
Nasmah ta mike a jikina tadawo in da yake suka saka sa a sakiya sunanta zuba masa surutu shiko nata biye musu.
laidar da ya shigo da ita ya buɗe ya ciro wata ƴar ma dai-dai ciyar laida a ciki mai ɗauke da

magungunan Nasmah ya ajiye a gefe kana yaciro sauran abubuwan ciki, ai ko yaran suka fara murna ganin kayan makulashe da cime-cime. wannan yace wannan yake so wannan yace wancan yake so, shiko sai binsu da murmushin nan nasa yake yana biye musu, duk wan da ya ce yana son wannan sai ya mika masa.
haɗa rai nayi tamau nayi kamar ban san da wani halitta cikin parlour'n ba.
Zulai da ta fito daga cikin kitchen sai taja ta tsaya, ganin wan da ke zaune cikin parlour'n sai kuma ta karaso da sauri ta zube gaban sa tashiga gai dashi cikin girmamawa,
ya amsa yayin da hankalin sa gaba ɗaya ke kan yaran.
da sauri ta mike ta koma kitchen jim kaɗan tafito ɗauke da tray da drink haɗe da cup a kai, gaba ɗaya bakin ta ya kasa rufuwa sai washe shi take, ta karasa ta dire tray ɗin bisa table ɗin gaban sa,
ta tsiyaya drink cikin cup ɗin kana taɗan tura shi gaban sa tare da faɗin
"Bismillah ranka shi daɗe."
ta juya da sauri ta shige tana ci gaba da washe baki.
Bayan ta nabi da kallo sai kuma naja gajeren tsaki ganin yan da take ta wani rawar jiki.
maganar sa naji a sama
"Ko ruwa ke baki iya bada wa bane idan bako yazo bare ayi masa sannu da zuwa?, sai ai kin tsaki da murguɗa baki kika iya?."
ɗago kai na nayi karaf muka haɗa ido baki na murguɗa masa tare da mikewa saye na nufi step.
na haura sama na barshi nan zaune shi da su Naseem.
shiga na ɗaki bada jimawa ba su Nasmah suka shiko suna ce min wai yatafi, nace yafi ruwa tafiya ɗan shishshigi.
lai da nagani rike a hannun ta na amsa na buɗe, magungunan ta ne ciki, na bubbuɗe na bata kamar yadda nagani a rubuce...

Ko da Ahmad ya bar gidan direct gidan sa ya nufa,
a parlour ya tadda Rasheedat saman dinning ita da masu ai kin gidan, sunata shirya abinci kan dinning.
duban ma'aikatan tayi tace duk su tafi sashin su. ka idan ta ne ita har idan ya dawo ko yana gida  to bata barin masu ai'ki cikin sashin su.
su na fita ta karaso in da yake wan da tuni har ya zauna saman ɗaya daga cikin kujerun parlour'n.
a gefen sa ta zauna tare da ruko hannunsa ta ɗaura kan cinyar ta, a sannu tashiga kunce agogon dake ɗaure a hannun sa.
"Barka da dawowa Aboki."
tafaɗa idanun ta a kan fuskar sa ɗauke da murmushi.
gefen fuskar ta ya shafa tare da faɗin
"Da fatan na same ki lafiya ya zaman gida?."
murmushi ta kuma tana ruko ɗaya hannun sa da ke kan fuskar ta, ta kawo shi saitin bakin ta, ta sumbaci hannun nasa kana ta ɗan ciza hannun.
da sauri ya ɗago hannun yana ɗan yarfe shi da faɗin
"Kawa zan rama yanzu."
yayi maganar tare da kanne mata ido ɗaya.

mike wa tayi tana faɗin
"Yau fa bacci nake ji dawuri zanyi bacci."
murmushi yayi tare da bin bayan ta da kallo yana shafa sajen fuskarsa har ta haura saman dinning.
ta sauko ɗauke da tray ta karaso ta dire shi kasa gefen kafafun sa.
ta dube shi tana faɗin
"Sauko na baka abinci kaci kayi wan ka muje muyi bacci."
sauko wa yayi daga saman kujerar ya zauna kasa ya jingina bayan sa da jikin kujerar, hannun ta ya ruko ya matse cikin nashi kana ya ce
"Bacci ki rubuta ki ajiye sai nan da karfe 2 na dare."
ido ta waro tare da faɗin
"2 na dare? kai ina yayi maka yawa."
"Baya yawa ai,kin sani kema." yafaɗa yana daɗa kanne mata ido...

Ta zuba musu abinci suna ci suna ɗan taɓa hira da zolayar junan su.
cokalin data kai loman abinci bakin ta ta ajiye, kana ta gyara zaman ta da kyau ta dube shi sannan tace
"Amma fa kayi min sauri wai har ka mai da Nasmah gida?."
kai ya gyaɗa ya na taunar a binci.
"Ya akayi ka faɗa mata kana sonta kuwa?."
kai ya girgiza tare da faɗin
"A'a ban faɗa mata ba."
fuska ta ɗan ɓata ta ce "Me ya sa?."
"Ba komai." ya faɗa a takaice.
"Har sai yaushe zaka faɗa mata so kake wani ya riga ka?."
numfashi ya ɗan sauke kana ya ce
"Ina ganin kamar bazata amin ce bane shiyasa."
ido ta ɗan waro tare da dafe kumatun ta da hannayen ta biyu sannan ta ce
"Waya faɗa maka? kaifa na dabanne cikin maza babu macen da zaka tinkara tace bata so, nasan waye mijina jarumi ne cikin jaruman maza, babu macen da zaka mika mata tayin so taki karɓa, ko ka mance har gida ake kawo maka hari,
tabbas jikina na bani HAMDAH taka ce zaka same ta, gobe kayi kyakkyawar shiri kaje ka faɗa mata, zata amin ce dan mijin nawa bana wasa bane."
ta karashe maganar da kashe masa ido.
plt ɗin abincin dake gaban su ya ture gefe tare da janyo ta jikin sa, cak ya ɗago ta yayi cikin bedroom da ita.

Washegari da misalin karfe 8 na dare
Ahmad ne tsaye jikin mirror yana fesa turare a jikin sa,
Rasheedat na tsaye gefen sa tana gyara masa zaman kayan jikin sa.
murmushi ta bisa da shi a kararo na ba adadi kana ta kuresa da ido sannan tace
"Aboki kafito fa shar da kai, da ɓarin jiki kanwata HAMDAH zata tarbe ka."
ta karashe maganar da kashe masa ido ɗaya, janyo ta jikin sa yayi tare da sumbatar goshin ta

yace
"Zugi ko?."
"Bazugi bane gaskiyar kenan muje kayi sauri dan da farar safiya ake kama fara."
ta yanyo hannun sa sukayi waje, har parking lot ta rakashi tana yi masa fatan nasara sai da taga fitar sa kafin ta koma ciki...

Zaune muke a parlour ni da su Nasmah yau da wuri sukayi bacci. sakamakon maganin Nasmah dana bata, ganin tayi bacci yasa Naseem shima kwanciyar yace shima zaiyi baccin ba jimawa kuwa baccin ya ɗauke sa.
Talatu na kurmawa kira nace tazo ta kwashe su ta kaisu ɗaki.
koda ta taho ta kwashe su, zamata na gyara, na mai da idanuna kan TV tare da mai da hankali na sosai kan shirin da ake.
Turo kofa a kayi tare da yin sallama.
batare da na ɗago ko duban maiyin sallamar ba na amsa, yayin da idanuna ke kan TV.
sai kuma na ɗago da sauri kamar an zabure ni, jin amon sautin Muryar nayi min yawo a ƙwaƙwalwa,
karaf idanun mu ya sarkafu da juna yana daf da isowa tsakiyar parlour'n.
da ɗan mamaki nake kallon sa "To me kuma ya kawo sa?."
nayi maganar a kasan raina.
fuska na ɓata tare da kawar da kaina na mai da idanuna kan TV. a sannu ya iso ya zauna gefe kan doguwar kujerar da nake zaune.
"Barka da warhaka, ni bari na gaishe ki tun da ke baki iya ba." ta wutsiyar ido na kalle sa batare da na juyo in da yake ba na taɓe baki a hatsale nace
"Doka ce ita gaisuwar kokuma wajibi ce."
Murmushin nan nasa yayi wan da sai da kumatun sa gefe da gefe suka lotsa, kana yagyara zaman sa da kyau ya fuskanci ni sannan ya ce.
 "Idan naso basai hakan ta kasan ce ba."
da sauri na juyo in da yake idanun sa a kaina, baki na murguɗa tare da kawar da kaina, ɗan gajeren tsaki naja tare da faɗin
"Ko zaka mai da shi yazamo wajibin ne?."
yakuma sakin wani murmushi tare da shafa gefen fuskarsa zuwa ɗan kayataccen gyamun sa irin na gawu, kana a hankali ya soma magana yayin da fuskar sa ke ɗauke da murmushin nan, wan da kamar da shi a ka halicci fuskar nasa.
"Kin taɓa ganin in da akayi wa abin da ake so dole?."
da ɗan mamaki na dube sa. gira ya ɗaga min tare da faɗin
"Yes ke da kanki zaki mai da shi yazamo wajibi lokacin da muka zamo abu guda,sakon soyayya ta nazo isar miki da fatan kema zaki tarbe shi hannu bibbiyu, ƙawa ta bani kwarin guiwa da addu'ar ta a kaina da baya faɗuwa kasa."

Wani irin shekeke nake duban sa kamar daga sama nake jin batun nasa.
"Soyayya." na furta kalmar batare da sanin fitar sa ba.
zaman sa ya gyara sosai ya daɗa fuskanta ta kana ya ce
"Aysha inkiya HAMDAH, tun ranar da kikayi min sharrin satar yara tun a ranar Allah ya bani ke,

ashe kece ma ɓarauniyar gaggaruma kuwa tun da har kika iya nasarar sace zuciyar Ahmad Sabil,  ina son ki Ƙawa ta bani tabbacin kema zaki soni, aure na taho da shi ba wasa ba..."
zumbur na mike batare da jin karashin zancen nasa ba, wani irin kallo nake binsa da shi, sai nake ji da ganin abun kamar a mafarki.
baya nashiga ja tare da girgiza kaina. wai dama ashe akwai wani mara kunyar na mijin da zai zo ya furta min kalmar so?, maza mayaudara maciya amana masu mai da alkhairi izuwa sharri.
kai na cigaba da girgizawa tare da faɗin
"Karya kake wlh karya ne,bazaka taɓa iya yaudara ta ko ka cutar da ni ba, wlh Allah bazai taɓa baka nasara ba, kuma kayi gaggawar tashi ka fice min a gida tun bansa anzo an fitar min da kai ba."
gaba kiɗaya jikina ya ɗauki rawa tsigar jiki na ya tashi, jin kalmar daya zomin da ita mafi muni da tsana a rayuwa ta.
sai kuma na juya da sauri na nufi step na haura da sauri.
 cikin ɗaga murya nake faɗin
"Kayi gaggawar fita a gidan nan tun kafin a zo a fidda ka."

Bayan ta Ahmad yabi da kallo har ta ɓacewa ganin sa, kana ya sauke numfashi da ɗan karfi, a hankali ya mike har lokacin idanun sa nakan step ɗin kamar wacce take gurin har lokacin.
sai kuma ya juya yanufi kofa ya fita.
yana dai-dai ta parking a kayataccen parking lot ɗin gidan sa ya fito, ya nufi ciki direct bedroom ɗin sa ya nufa dan gaba ɗaya jin sa yake wani iri.
ji yayi an rungume sa ta baya, numfashi ya sauke tare da sako hannu ya juyo ta suna fuskantar juna.
fuska ta ɗan kwaɓe ta ce "Shine kayi kamar baka ganni ba zaka wuce abin ka ko?."
ido ya ɗan waro ya ce "Na isa sam ban ganki ba."
cikin tsigar zolaya taɗan cuno baki gaba tare da faɗin
"Ai na ɗauka tun yau za'a fara nuna min halin anyi sabuwa za'a faka tsohuwa a gefe."
ido ya kuma waro wa tare da sakin murmushi yadaɗa janyo ta jikin sa, lafiyayyen kiss ya sauke mata a goshi kana ya ce
"Wace ce tsohuwar dama ashe kin tsufa ban sani ba?."
yayi maganar yayin da idanun su ke sarkafe da juna.
baki ta turo gaba ta ce "Kai ka faɗa ai."
"Yaushe kenan?."    "Yanzu da ka shigo mana."
"Ni dai Ƙawa bata tsufa ba, kuma bazata taɓa tsufa a gabana ba, sai dai idan ke kika yi mata sharri."
murmushi tayi tareda daɗa shige wa jikin sa sosai, sai kuma ta ɗago tace
"Ayafe min bazan kara mata sharri ba."
murmushi ya sake tare da faɗin
"An ya fe miki."
baki takuma washewa ta ce "To faɗa min nasarar da mukayi na sace zuciyar HAMDAH."
kai yaɗan rausayar gefe kana ya ce
"Ta ce bata so na." ido ta waro da sauri tace "What! wai da gaske dan Allah?."
ya ce "Eh da gaske to taki saurara ta me hakan yake nufi tana nufin bata sona kenan ba."

numfashi ta sauke daɗan karfi kana ta zare jikin ta daga nasa, ta ruko hannun sa ta janyo sa suka yi cikin bedroom ɗin sa, tana faɗin
"Wlh har ka sa jikina yayi sanyi naɗau ka ita ta faɗa maka da bakin ta."
"Kusan haka ɗin ne ai." kai ta girgiza dai dai lokacin da suke zama saman doguwar kujerar da ke cikin katafaren ɗakin, har lokacin hannun ta na rike da sa, fuska ta marairaice ta ce
"Aboki baka dai  bi ta hanyar da zata amince ba dai, gaskiya zaka sake shiri gobe ka tinkare ta."
a hankali yayi baya ya manba bayan sa da jikin kujera idanun sa ya lumshe tare da kuma buɗe su, sai ya saki murmushi batare da yace komai ba.
ido tazuba masa tana karantar mijin nata, tabbas tana hango so da kaunar HAMDAH muraran a tare da shi,duk da kokarin sa na ɓoye mata a matsayin ta na matarsa wacce dole zata ji ba daɗi ace mikin ta na bayyana damuwa da son da yake yiwa wata mace bayan ita.
sai dai a gefen ta ita sam abun ba haka yake ba takan jingina matsayin ta na mata a gare sa, ta kusanto da kusancin su na ƴan'uwantaka, wacce take jin zata iya taimaka masa a kan duk abun da yake so.
kuma ko ba haka bama ita daban ce cikin mata, so da kyakkyawar fahimtar dake sakanin ta da mijin ta na daban ne shiyasa take jin son duk abinda yake so.
A hankali takai kanta izuwa kafaɗar sa ta kwantar da kan nata yayin da ta sakalo hannun ta guda ta bayan sa ɗaya hannun kuma a gefen wuyan sa, iskar bakin ta taɗan hura masa cikin kunne, a sannu ya lumshi idanun sa. kana a hankali cikin taushi da tsigar iya kwantar wa miji hankali ta ce
"Aboki gobe idan Allah ya kaimu sabon shiri zamu yi, ka dage wajen shawo kanta,  nafa sanka da kokari wajen iya sarrafa zuciyar mace, bada baki ba da iya ido kawai da kyakkyawar halittar surar jiki da Ubangiji yayi maka, shiyasa suke biyoka har gida, mace ɗaya bazata gagare mu ba."

Haka Rasheedat tayi ta zuba masa kalamai masu kwantar da hankali da karfafa guiwa...)

Acan cikin garin Bauchi kuwa
Rayuwa tayiwa Na'ima daɗi abin da take nima ta samu, SALEEM yazamo nata ita da ɗan ta. sai dai har yanzu halinnan nasa na miskilanci yana nan yanzu ya daina damin ta tun da bokan ta ya daɗa jaddada mata cewa halittar sa ce babu yan da za'ayi a canzashi.
kuɗi kuwa tatsar sa take ya zame mata banki musamman takuma buɗe account na tara kuɗaɗen dake fita a gurin sa ba adadi.
a ɓangaren Ummi kuwa yanzu tagama yarda ɗiyar ta tana nan a raye, dan jikin ta yana bata da addu'o'in da take mata ba dare ba rana, da wan da ta saka arika yi mata. takan kwanta bacci tayi mafarkin taga ɗiyar ta a raye kuma shicin koshin lafiya.
kullum addu'ar ta Allah ya baiyana mata ita cikin gaggawa.
zuwa wannan lokacin fuskar Abba yakan bayyana damuwa da tunanin ɗiyar sa wacce a yanzu ya ɗaura alhakin komai daya faru a kansa, duk da baya iya furta hakan a kan laɓɓan sa. amma da ka gansa zaka fahimci damuwa sosai a tare da shi.

A ɓangaren su Mamie da Abbu ma kuwa har yanzu haka abun yake sai dai damuwa a iya zuciya badai su furta ba... Wannan kenan...

Yau asabar duk kanmu muna sashin su Bappa, dan yau tun safe su Uncle Mahmoud da matar sa da ƴaƴan su suka zo, sai hira muke sha cike da jin daɗi, sau tari idan na ɗago kaina sai na tsinci idon Uncle Mahmoud a kaina, wayar sa ce tafara bada sautin kara a lamun shigowar kira,ya mike yayi waje.
naji daɗin tashin nasa dan kallon sa ya fara dami na, jin karar wayat tasa kuma ya tuno min da tawa wayar dana baro ta cikin bedroom ɗina.
na dubi Faty dake ta faman wasa da su Naseem nace
"Je ki ɗauko min waya ta a ɗaki."
ta amsa da To ta mike har ta kai bakin kofa na ce "Oh zo Faty baza ma kigani ba na ɓoye ta cikin wardrobe sabo da su Nasmah da suke kokarin fasa min ita ɗazu, bari naje na ɗauko kawai."
nakarasa maganar da mikewa tsaye na nufi kofa na fita.
maganar Uncle Mahmoud najiyo daga ta ɗan can bayan side ɗin har na sa kai zan wuce,sai naji yana ambatan suna na.
cak naja natsaya jin yana cigaba da faɗin
"Bazaka gane bane itafa yarin yar yanzu tafi karfi na, babu ta yan da za'ayi na tinkare ta da wani batun ina sonta, amma wlh kullum da ita nake kwana nake tashi, nabarwa Allah zabi inata addu'a idan Allah ya ƙaddara zata zamo tawa babu ja ko kankari, amma wlh ina son HAMDAH har cikin raina.."
ido na ware tare da kai hannu na na toshe baki na da sauri nawuce na bar gurin, zuciya ta cike fal da mamaki.
Uncle Mahmoud anya kuwa ba karya kunnuwa na suke jiye min ba kuwa,
wai wace kaddara ce take ta kokarin afkomin a ƴan kwanakin nan.
a fili na furta
"Ya Allah ya Ubangiji kada ka kuma jarabtata da abinda bazan iya ba, kabarni nacigaba da rayuwa ta a haka,kasan tuwata da wani na miji tamkar kuma rugujewar rayuwa ta ce."

Hon ɗin da naji a gabana yasani dawowa cikin hayyaci na. ido na zuba masa dai-dai lokacin da ya buɗe marfin motar ya fito.
gefe na kauce ina kokarin wuce shi sai ya sha gabana.
naɗago na dube shi tare da dalla masa harara ina faɗin
"Wai meye hakan kake yi ne?, bani hanya na wuce malam tun ban sa an karta maka rashin mutun ci ba." wani irin
murmushi ya sake mai bayya na ai nihin kyan fuskar sa, mai narka zuciyar duk mai kallon sa tare da shafa gefen fuskar sa zuwa ɗan gyamun sa kana ya ce "Zaki iya kuwa kyakkyawa ta?, ba ma wannan ba nazo ne naji in da batun mu ya kwana,
kin san kuwa ranar ɗin nan da kyar na iya bacci duk tunanin ki ke ta addaba ta, sai da Kawa tayi da gaske kafin na samu na iya bacci."
wani irin shekeke na kalle sa nace

"Batun ku da wa?, kana ji ko ka dai na wan nan zakewar da kake dan bazata yi maka kyau ba."
na raɓa gefen sa zan wuce, yayi saurin kuma shan gaba na
"Baki murguɗa min kyakkyawar bakin nan ba yau haka kawai zaki barni."
yayi maganar idanun sa cikin nawa, da sauri na janye idanuna jin wani irin shock ya ziyar ceni.
nawuce shi da sauri, muryar sa najiyo yana faɗin
"Kwana biyu na baki kije kiyi tunani bayan kwanaki biyun kuma kishirya zan kawo sadakin ki."
tsaki naja dai-dai lokacin da nake shigewa cikin side ɗina.
"Wannan mutumin fa ɗan rainin wayo ne nakarshe, wai har yana faɗa min wai wani wai da kyar Kawar sa tasa shi yayi bacci dan ya nuna min tantirancin sa a fili har Kawa yake da shi mttss.""
naja dogon tsaki a fili.
yana na miji ba aboki yake da shiba Ƙawa yake da.
koda na ɗau waya ta najima cikin ɗakin kafin na fita,
bakin get na nufa in da security suke, suna gani na suka shi ga gaida ni cike da girmamawa,
na amsa kana na ɗaura da faɗin
"Kada ku sake barin mutumin can da yazo ɗazu yakuma shigowa, kada ku sake barin sa ya shigo."
Suka amsa da "To Hajiya."
na juya na koma part ɗin su Inna Wuro, muka cigaba da hirar mu, sai dai wannan karon ban bawa Uncle Mahmoud daman cigaba da satar kallo naba a kujerar dake bayan sa na zauna.
sai dare su Uncle Mahmoud suka bar gidan...

Bayan sati biyu tun wancan lokacin Ahmad bai kuma zuwa ba naji daɗin hakan, dan ba shakka nasan yazo ne aka hanashi shiga kamar yadda na bada umurni.

a bangaren Ahmad kuwa a ranar da yazo gidan HAMDAH tafiya ya kama sa yabar kasar, duk waɗan nan kwanakin bai yi su a Nigeria ba.
satin sa biyu cif-cif yadawo Nigeria a ranar da yadawo da daddare yanufo gidan, Rasheedat bata barsa ya fito ba sai da ta shirya sa da kan ta, har parking lot ta raka shi,kamar kullum tana yi masa fatan nasara da samun duk abin da yasa a gaba na alkhairi...

Muna zaune a parlour ni da su Naseem ya turo kofa da sallama.
da gudu su Nasmah sukayi in da yake, tun kan su karaso ya ware hannayen sa, suka faɗa ciki ya rungume su duka tare da bin ko wannen su da sumba a goshi da kumatu.
sannan ya mike tsaye yarika ɗagasu yana cillasu sama, sai washe baki suke suna faɗin
"Daddy a kaya mana."
shiko yarika biye musu daga bisani yaruko hannayen su suka karaso cikin patlour'n.
ya zauna suka ɗale jikin sa, wani ɗan madaidaiciya kyakkyawan bag dake hannun sa ya mika musu yana faɗin
"Tsarabar ku ce ciki maza ku sauka kuci."
ai ko da sauri suka duro a jikin sa a tsakiyar parlour'n suka zazzage bag ɗin, kayan lashe-lashe da tanɗe-tanɗe da ciye-ciye ne ciki, suka dukufa mishi.
murmushi ya bisu da shi kana ya mai da duban sa gare ni ya ce
"Madam yauma sai na roki gaisuwar ne?."

yi nayi kamar ban san da wani halitta a gurin ba.
taso wa yayi daga in da yake zaune ya dawo kan kujerar dake kusa da Ni,
a sannu naji saukar hannun sa kan hannu na dake saman hannun kujera, ba zato naji ya sarkafe ya tsuna da nashi.
wani irin bugawa kirjina yayi da mugun karfi nan take jikina yaɗau wani irin shock, a sannu yashiga murza tafin hannun sa mai laushi tamkar auduga cikin nawa yayin da ya soma magana a hankali.
"Nayi tafiya sati na biyu bana kasar ni da na bada kwana biyu ayi tunani, zuwa yanzu kam nasan ba mafita ba in akwai abin da yafi mafita ma kin samar mana, HAMDAH."
yakira suna na cikin wani irin yanayi kana yaci gaba da faɗin
"Kin shirya karɓata a matsayin abokin rayuwar ki na gaba, ki tai maka kada kisa zuciya ta ta sami matsala, ina SON KI HAMDAH! ke ma kuma nasan zaki so ni, ki mance da baya mugina sabuwar rayuwa na musamman."
da karfi na rumtse idanuna na so nake na janye hannuna dake sarkafe da nasa amma na kasa, yayin da bugun zuciya ta ya tsananta, da kyar na iya fizgo numfashi na janye hannuna da kyar, a wahalce na buɗe idanuna a kansa sai ya mannan idanun sa cikin nawa tamkar haɗuwar kurar karfe, gabaki ɗaya jikina sai yayi min mugun nauyi hatta laɓɓa na kasa iya motsa su nayi,kana nakuma gaza iya janye idanu na cikin nasa,
wasu abubuwa nake hangowa cikin idanun sa masu mugun kashe jiki da saukar da kasala.
numfashi nakuma fizga da kyar na iya tattaro jarumtata najanye idanuna na mike tsaye.
da sauri shima ya mike yana kokarin mai da idanun sa cikin nawa nayi saurin sunkuyar da kaina tare da faɗin
"Dan Allah ka tafi karabu dani kafita acikin rayuwa ta, kabar ni nayi rayuwa ta cikin salama, bana son ka bakuma zan taɓa son wani na miji ba a rayuwa ta, ban so bama aka iya cutar dani bare kuma na so, dan Allah dan Annabi naroke ka na haɗaka da su ka kyale ni kafita a cikin rayuwa ta."
jin kuka na kokarin kwace min sai na juya da sauri na nufi step, ina jin su Nasmah suna tambayar sa "Daddy da ka tafi ne?."
ya ce musu "Eh amma gobe zan dawo da safe in sha Allah zan zo na ɗauke ku muje yawo."

A kan gado na zube sai kawai na fashe da kuka, narasa yazan yi da rayuwa shin ba za'a iya barina nayi rayuwa ta ni kaɗai bane, meyasa ake son matsaltawa rayuwa ta. shin su maza cuta kawai suka iya ne babu tautsayi a lamarin su, zuciya ta ta bani amsa da faɗin
"Tun da har ɗan uwan ki na jini ya iya cutar da ke to wa kike ganin bazai iya yi miki kwankwacin irin haka ba."
kuka sosai na fashe da shi cikin. muryar kuka nake faɗin
"Ya SALEEM bazan yafe maka ba kai da matar ka, tabon da kuka yi min
shi yake janyo wasu mazan su so raɓa ta dan suyi min kalar tasu tabon..."

Washegari kamar yadda Ahmad yayi alƙawarin zuwa gidan da safe kuwa sai ga shi.
ina daga cikin ɗaki nake jiyo ihun yaran suna faɗin
"Oyoyo Daddy Oyoyo Daddy."
koda na leka ta window dan tanan nake jiyo muryar su, can na hango su kasa tsakar gidan, ido

na waro cikin ɓacin ran ganin security'n da nace kada su barshi ya shigo sune suka mika masa gaisuwa cike da girmama wa.
sake labulen window'n nayi, na koma bakin gado har na kwan ta sai kuma na mike da sauri tuno maganar sa na jiya da yake faɗin yau zai zo ya tafi da su yawo.
da sauri na nufi kofa ina zuwa tsakiyar step's yana turo kofar,sai na ja natsaya.
shima daga bakin kofar ya tsaya idanun sa a kaina, baki na murguɗa tare da duban su Naseem dake gefen sa nace
"Kuzo nan."
kafaɗa suka make Naseem ya ce "Mommy da mubi Daddy muje yawo muhau lilon doki."
"Zaka wuce ne ko sai na zo gurin na fasa maka baki ina magana kana mayar min da amsa."
"Gaskiya ya faɗa miki ai, ko so kike yayi miki karya? dama na shigo ne na ganki ina fata kina lafiya."
baki na murguɗa masa najuya na koma sama...

Tun da yafita da su bai dawo da su ba sai yamma lis, ina jin shigar sa na mike ina kokarin haurawa sama, yayi saurin iso ni cikin kasa da murya yace
"Nazo ne ki yanka min sadaki fa yakama ta ki tsaya muyi magana."
"Baka da kuɗin da zaka iya biyan sada ki na."
nayi maganar cikin gatse na juya na haura sama abina...
bayan ta yabi da murmushi laidar tsarabar da suka dawo da shi ya mikawa Zulai da ta karaso ciki parlour'n tana mika masa gaisu, kana yace takai yaran ayi musu wanka. sannan yayi waje...

After 2 days

Kwance nake a kan gado da misalin karfe 12 na rana, a kayi knocking ɗin kofa, murya na ɗaga da faɗin "Wane ne? daga bakin kofar Talatu tace
"Nice Hajiya, kinyi bakuwa ce."
"Bakuwa kuma?". ta ce "Eh." shiru na ɗanyi kana
na ce "Wace ce." ta ce "Wata ce sai dai ban gane ta ba." "Okay ina zuwa.." jin kaɗan na mike na fito, a parlour'n kasa na hango ta. tun kan na karasa muka haɗa ido sai ta sai tayi min murmushi. nima murmushin na bita da shi kana na karaso na zauna saman kujerar da ke fuskantar ta.
nan muka shiga gaisawa ɗan shiru ne ya biyo baya kana daga bisani ta ɗago tana tambaya ta ina su Nasmah.
naɗan yi mamakin jin sunan yaran a bakin ta sai kuma na batsar da faɗin sun tafi School.
ta ce "Masha Allah Allah ya dawo mana da su lafiya."
Amin na amsa da shi. zaman ta ta gyara kana ta kuma dubana da kyau sannan tace
"Kin gane ni kuwa?." kai na girgiza a lamun a'a. murmushi taku kana tace
"Kiyi hakuri nasa an taso ki dole ce tasa hakan, tai mako nazo nima a gurin ki dan Allah ki taimaka min, kamar Yadda Allah ya taimaka miki."
"Tai mako?." nafaɗa ina duban ta, sam batayi kama da masu niman taimako ba, kama daga kalar ta kalar fatar jikin ta har izuwa kayan dake dankare a jikin ta, sarka da ƴan kunnen da ke

dankare a wuyan ta shi kan sa na gold ne, taya za'ayi ace niman taimako tazo..
kai ta gyaɗa min alamar Eh kana taci gaba da faɗin
"Kwarai kuwa tai mako nazo nima gurin ki, sunana Rasheedat Ahmad Sabil, mata ƴar'uwa kuma Ƙawa a gurin Ahmad Sabil, bashi da abokin da ya wuce ni."
numfashi ta ɗan sauke kana ta zamo bakin kujerar ta miko hannu ta ruko hannuna tarike gam sannan taci gaba da faɗin........!

Mommy Twins ce

HMD

WASA FARIN GIRKI

14

"HAMDAH dan Allah ki taimaka min mijina yana cikin wani hali duk a ta sana diyyar ki,
tun da nake da shi ban taɓa ganin shi cikin damuwa haka kawai ya keɓe shi kaɗai yana tuna ni ba, sai da ya haɗu da ke, dan Allah ki taima kiso mijina ganin sa cikin damuwa tamkar rugujewar farin ciki na ne, baya bacci mai tsawo acikin guntun baccin da zaiyi kuwa kalmar sunan ki kaɗai yake furta wa,
ki taimaka mana kodon ɗaurewar farin cikin daya ginu tun shekarun baya, kada tawaya ta shigo cikin sa dan Allah kijefa gudummawar ki cikin wannan rayuwa mai ɗinbin farin ciki da fahimtar juna kikuma haskaka mana shi,
dan Allah dan Allah HAMDAH kiso mijina ki taimaka mana na roke ki, Ahmad bashida wata illa wlh na rantse miki ni bai taɓa rage ni da komai ba ban taɓa ganin wata illar sa ba Ahmad mutum ne na gari mai tsoron Allah,
na tabbata zai kula dake fiye da yadda kike sammani bazai taɓa cutar dake ba kamar yadda

kike sammani, Ahmad mutum ne nagari."
ɗan sakai ta maganar nata tayi kana takuma damke hannu na sannan taci gaba da faɗin
"Dan Allah na roke ki HAMDAH kiso mijina ki aure shi Please and please HAMDAH yana cikin damuwa sosai, bazan taɓa samin nutsuwa ba har sai na ga samun kwanciyar hankalin sa, dan Allah kiso mijina HAMDAH!."
takarashe maganar da sakin hannuna ta haɗe hannayen ta biyu tare da faɗin
"Dan Allah dan Allah!."

Tun da ta fara maganar idanuna a kan ta cike da ɗinbin mamaki mamakin ta da maganar ta suka jefani cikin dogon nazari mai cike da ɗin bin mamaki,
"Wai shin da gaske ita matar sa ce?." tambayar da nayiwa zuciya ta kenan. Allah mai iko yau gani cikin wata rayuwa,nan da nan tunanin rayuwa ta ta baya yarika zuwar min,
a kan na auri mijin ta har wuka ta ɗauka zata kashe ni, akan na auri mijin ta ta mai dani ƴar sharan ta, ta mai dani mai girka mata ruwan wanka bayan tagama biyan bukata da mijin ta.
akan na auri mijin ta ta yimin mummunar ƙazafi mai cike da tarin kazanta, ta tarwasa farin cikin family ta raba uwa da ɗiyar ta, sai gani a wata rayuwar da yau wata mace ce tataho nimawa mijin ta aure. sukuma wannan duniyar salon tasu kalar yaudarar kenan.
Su zasu taho su jaka da kansu domin idda mummunar kudirun su akan ka.
da sauri nace
"Dan Allah kiyi hakuri ki dai na haɗani da Allah, bazan iya yi miki wannan taimakon ba, kuma dan Allah na roke ki kada ki sake zuwa, me nayi muku kuke son ganin sai kun gallazawa rayuwa ta."
da sauri na mike tsaye ina cigaba da faɗin
"Rayuwa ta ni kaɗai ya fiye min rayuwa da wani, sabo da babu komai cikin rayuwa da wasu sai tashin hankali, ki tafi dan Allah."
na haɗe hannaye na biyu ina girgiza mata su, kana na juya da sauri.
da sauri ta mike tana faɗin
"Dan Allah ki saurare ni HAMDAH."
ban ko juyo ba nayi sama da sauri...

Jiki ba kwari tafita taja motar ta, office ɗin Ahmad tawuce, tana isa kasan cewar ansan matar sa ce, batare da an dakatar da ita ko bincike ba ta wuce direct cikin office ɗin,
batare da niman izinin shiga ba ta murɗa handle ta kusa kan ta ciki,
yana zaune cikin rantsatsen ofishin nasa mai kyau da tsaruwa sai tashi da daddaɗan sanyi mai fitar da sansanyan kamshi yake.
yana ganin ta ya ture F ɗin da ke gaban sa, ta karaso ta
zube kan kujerar dake fuskantar sa jiki ba kwari,
cikin kula ya dube ta yana faɗin
"Ya dai Kawa wani abun ne?."
fuska ta marairaice ta ce
"HAMDAH ce taki ta saurare ni."
numfashi ya sauke kana ya miko hannun sa ya ɗan kwanto saman teburin gaban sa ya ruko hannayen ta duka biyu yana ɗan matse su,

sai ya ɗan saki murmushi da faɗin
"Kinje gidan ta ne?."
kai ta gyaɗa masa alamar Eh.
kai ya jinjina sannan ya ce
"Ai da ma da wuya ta saurare ki dan gani take jiya kamar yau ne, taso muje gida dan dama bacci nake ji."
motar ta suka hau in da suka bar motar sa a nan office ɗin...

Washegari da safe ina zaune a parlour ina breakfast bayan tafiyan su Naseem School,sai ganin mutum nayi ya shigo ɗauke da katuwar jaka a gabana ya taho ya dire jakar.
kana ya zauna saman kujerar dake fuskanta ta. kallo ɗaya nayi masa na kau da kai, a kasan raina na ce
"Mutum kamar maye sai shegen uban naci."
gajeren tsaki naja a fili, tare da ajiye cup ɗin tea ɗin danake sha saman table.
kamar kullum fuskar nan tasa na bayyane da murmushi.
"Barka da safiya kyakkyawa ta wacce bata iya gaisuwa ba." ya faɗa idon sa a kan fuska ta, ban yar da na haɗa ido da shi sai kawar da kaina gefe nayi tare da murguɗa masa baki.
"Yauwa gaisuwar ki kenan ɗaya da kika iya murguɗa baki, amma fa yana miki kyau sosai fa."
yayi maganar tare da bayyana murmushi mai sauti, yana shafa gefen fuskar sa kana yaci gaba da faɗin
"Me ma kika ce bani da kuɗin da zan iya biyan sadakin ki?, shine na kawo miki wannan kicire adadin sadakin naki in kuma sunyi miki kaɗan akwai ire-iren su ko guda nawa kike bukata."
duban katuwar jakar da yake kokarin zuge zip ɗin sa nayi, ido na gwalalo cikin jakar, ɗaurin ƴan 1k-1k ne tam ciki sababbi katakar da alama daga banki ne yanzu aka fito da su.
kallon sa nayi tare da ɗauke kai nakuma duban kuɗin sai na yamusa fuska tare da faɗin
"Da zakayi gaggawar ɗauke wannan abin da zai fi maka, ko irin su sau dubu zaka jera a nan bazasu taɓa kai adadin sadaki na ba."
na mike na wuce na barsa nan zaune.

Kan sa ya dafe da dukka hannayen sa biyu, duk wani abin da take masa tamkar daɗa kara rura wutan son ta ake a zuciyarsa, ya lashi takwabin ko ta halin yaya sai ya same ta insha Allah, duk da yasan kuɗin sa bazasu taɓa yi masa maganin komai ba, dan ba irin su HAMDAH ake siya da kuɗi ba.
a hankali ya mike ya janyo jakar part ɗin su Bappa ya nufa, yayi sallama daga kofa aka bashi izinin shiga, da sallama yashiga cikin parlour'n.
Bappa da Inna Wuro suna zaune cikin parlour'n, Bappa na ganin sa ya mike da sauri tare da faɗaɗa fuskarsa da murmushi yana faɗin
"Lale barka da zuwa Ahmadu kai ne tafe da safen nan, sannu dai bismillah ga guri zauna."
zama yayi suka shiga gaisawa cikin girmamawa da mutunta juna.
Inna Wuro ta mike da faɗin bari ta kawo mishi abun kari, ya ce A'a tabari shikam alhmdllh.
ɗan shiru ne ya biyo baya kana a hankali Ahmad yasoma magana cikin sunkuyar da kai.
"Bappa Malam dama gurin ka nazo da niman wata alfarma."
Bappa ya mai da hankalin sa sosai kan Ahmad dajin wai alfarma yake nima a gurin sa, mutum

kamar Ahmad shi a iya tunanin sa babu wani abun da zai je ya nima a  gurin wani.
ya ce
"Ikon Allah Ahmad har akwai wani alfarman da zaka nima a gurin mu, to ina sauraron ka faɗi koma mene ne."
har lau kansa a kasa ya soma magana
"Auren HAMDAH nazo nima,kuma tafe nake da sadaki na, ranar munyi magana da ita sai take cewa bani da kuɗin da zan iya biyan sadakin ta, shine yau na taho da kuɗi amma sai ta ke cemin basuyi mata ba, kuma  taki tsayuwa mu fahimci juna bare nasan iya adadin kuɗin da take so, shine na zo gurin ka, ga kuɗin nan ko za'a bata sai nasan nawa take da bukatar kari."

Wani irin farin ciki ne mara misaltuwa ya lullube zuciyoyin su Bappa da jin abin da ke tafe da Ahmad Tijjani Sabil, na batun niman auren HAMDAH. sai kuma
 Bappa ya saki salati yana faɗin
"Inji HAMDAH ɗin, shine kai ma kabiye wa shirmen ta ka ɗauko kuɗi cikin jaka kafito da shi kan titi a wannan zamanin da muke ciki."
murmushi yayi tare da tura jakar gaban Bappa ya ce
"Bappa Malam a bata sai ta faɗi nawa take da bukatar karin."
Bappa ya zuge zip ɗin jakar da Ahmad ya tura masa gaban sa, ya waro ido cikin jakar dake cike tam da kuɗi ya ce
"Ahmad wai shin wannan kuɗin duka shine kuɗin sadakin mutum har kuma ake faɗin idan baiyi ba a karo?."
sai kuma ya girgiza kai tare da yin murmushi irin nasu na manya ya ce
"To ka ɗauki kuɗin nan maza katafi da shi ka mai dashi banki."
ya mika hannu ya ɗauki ɗaurin kuɗin ɗaya kana ya shiga kirga shi, yana kai hamsin sai ya zare naira dubu hamsin ɗin kana ya mai da sauran cikin jakar ya zuge zip ɗin jakar ya rufe sannan ya dubi Ahmad ya ce
"Mafi kankancin sadaki shine albarkar aure, maza ka ɗauki kuɗin nan ka mai da su ma'ajiyar su, wannan shine sadakin ta Allah ya sanya musu albarka kaje nabaka auren HAMDAH."

Farin cikin da Ahmad yashiga a lokacin bazai misaltu ba, yashiga zubawa Bappa godiya kamar zai zuba guiwowin sa kasa, Bappa ya mikar da shi yana faɗin
"Ɗauki jakar maza ka tafi kada ka tsaya wani guri yanzu kiwon mutum ake kaje duk ran da ka shirya kazo a saka muku ranar aure."
Ahmad ji yayi kamar ya yi ta tuma tsalle dan farinciki yafita zuciyarsa wasai kamar anyi masa albashir da gidan aljanna...
bayan fitar sa Inna Wuro da Bappa suma farincikin nasu suka rika bayyana shi a fili Bappa ya ce
"Ikon Allah Allah mai kyauta da kari wai yau Ahmad Tijjani Sabil ne yazo niman auren HAMDAH,kin ga yan da Allah yake lamarin sa ko, mutum kamar Ahmad Sabil Allah mai girma da ɗaukaka."
Inna Wuro ta ce
"Wlh Malam abun ba'a cewa komai sai godiyan Allah, wani hanin ga Allah bai wa ce, Allah yanata sauya mata abubuwa mafiya alkhairi a rayuwar ta."

"Kwarai kuwa ya jarabceta yakuma bata ikon cin jarabawar sannan kuma yarika haɗata da alkhairin sa,
a kwanakin nan ina yawaita ganin shi Ahmad ɗin a gidan nan ashe dai nima ne ke kawo sa, kai masha Allah wlh naji daɗin lamarin nan sosai ba kaɗan ba."
haka su Bappa suka rika yabawa da sambarka...

Ina daga kwance a kan gado ina Game a wayata, naji karar mota koda na mike nazo jikin window na leka, shi nagani yana fita daga gidan, nayi mamakin ganin sai yanzu zai tafi dan ni a tunani na tun barina parlour shima ya tafi.
da sauri na fita na nufi bakin get dan na fiskanci security nan ƴan rainin wayo ne, dana ce kada su kuma barin sa ya shigo shine kullum sai sun buɗe masa get ya shigo.
tun kafin na karaso in da suke na soma magana
"Nace kada ku sake barin wannan mutumin ya shigo gidan nan amma kullum sai kun buɗe masa get ya shigo, akan wani dalili?."
Duk kanin su shiru sukayi sai kallon kallo suke wa junan su.
magana na cigaba dayi
"To daga yau kada ku sake barin sa ya shigo nafaɗi na karshe kun dai ji abin da na faɗa ko?."
nan ma kallon junan su sukayi kana ɗaya daga cikin su ya ce
"Kiyi hakuri Hajiya hakan ne bazai yiwu ba mun so gwada hakan amma ba mai yiwuwa bane."
"What!." nafaɗa da karfi zan kuma magana sai wayata ta bafara bada sautin kara alamun shigowar kira, ko da na duba mai kiran ganin Bappa ne yasani saurin ɗaga wayar, da sallama.
ya ce "HAMDAH bacci kike ne?."
na ce "A'a Bappa."
ya ce "Kizo yanzu maza ina niman ki." na ce To. da sauri na juya jin abun da Bappa yace bai taɓa yimin irin wannan kira haka a gaggauce ba, cikin hanzari na nufi side ɗin su.
da sallama na shiga suna zaune na karaso na zauna ina faɗin.
"Gani Bappa."
ya ce "Har kin iso kodai dama kina hanyan zuwa ne?."
murmushi nayi ina faɗin
"Da ma dai ina bakin get ne ka kira, ina kwana Bappa, Inna Wuro ina kwana."
duk suka amsa da "Lafiya lau an tashi lafiya ya kwanan yaran."
na ce "Lafiya lau alhmdllh."
Bappa ya ce "To madalla, da ma na kiraki ne akan wata muhimmiyar magana amma kafin nan, HAMDAH me kika ɗauke mu wani matsayi muke  a gare ki?."
da sauri na dubi Bappa sai naji maganar tasa tazo min a bazata na ce
"Bappa kallon mahaifa ban taɓa yi muku kallon da ya gaza haka ba, amma Bappa me yakawo wannan maganar?."
kai ya jinjina tare da faɗin
"Masha Allah naji dadin fitar wannan kalmar daga gare ki, HAMDAH na yanke hukunci a kan ki batare da sanar da ke ko niman shawarar ki ba, dan na tabbata hukuncin dana yanke shine abu mafi a'ala a rayuwar da kike yin sa yanzu batare da abokin rayuwa ba,
HAMDAH yau na karɓi sadakin auren ki duk da cewa kece yanzu ke da alhakin hakan,sai dai yaro baya taɓa girma gaban iyayen sa musamman ke da haryanzu kuruciya ke tattare da ke,

zaman ki a haka babu miji wani nakasu ne daga girman ki  da ake gani a idon duniya, aure shine cikon kima da martabar mutum,
sam ba a son musulmi Mumini yazamo
mai ruko a rayuwa, shin ashe ba zaki godewa Allah da irin ɗin bin ni'i'momi da tarin alkhairan da ya miki yake kuma kan yi miki ba?,
idan kika gode masa ta hanyar mancewa da duk wani abun da yafaru a baya sai ya daɗa saka miki da alkhairan sa mafiya fifici."

Wani irin sarawa naji kaina keyi min da mugun karfi,
Gaba ɗaya Bappa ya gama kashe min jiki da kalaman sa yayin da ƙwaƙwalwa ta ya tsaya cak ya daina aiki na ƴan sakanni, da ido kawai nake bin Bappa, bansan meyasa suke son sai nayi aure ba, saboda basu san wahala da tashin hankalin da ke cikin sa bane ko me.
sai dai me bazan iya yiwa Bappa musu ba, dan har cikin raina a matsayin mahaifi na ɗauke sa, amma wlh a yanzu babu abin da nafi tsana kamar aure, aure bai bani farin ciki da nutsuwan da ake faɗa ba, sai zallan fitina da tashin hankali.
a hankali na furta
"Babu damuwa Bappa duk abin da ka yanke a kai na me kyau ne."
Fuskokin su ne ya cika da annuri dukkanin su suka shiga sanya min albarka Bappa ya ce
"Allah yayi miki albarka HAMDAH ya tsare gaban ki da bayan ki,
ina da tabbaci da yakinin Ahmad Tijjani Sabil bazai yi miki rukon wasa ba dan mutumin kirki ne Ni, Allah ya sanya alkhairi cikin rayuwar
auren ku."
Inna Wuro ta amsa da "Amen ameen ameeeeeen ya rabbil izzati."

A gigice na ɗago ina duban Bappa jin sunan wan da ya ambata na ce
"Wa Ahmad!?.......!

Mommyn Twins ce

HMD

WASA FARIN GIRKI

NA

RASHEEDAT S DIRECTOR

15

Ganin yan da nayi maganar da alaman shiga firgici dajin cewa Ahmad ne wan da Bappa ya karɓi sadakin sa, sai yayi saurin tarar numfashi na da faɗin
"Eh Ahmad in ban da abin ki HAMDAH ace mutum kamar Ahmad yataho niman auren ki ai abun alfahari."
"Bappa ni wannan mutumin fa.."
sai kuma nayi shiru batare da na karasa faɗan abin da zan faɗan ba.
murmushi Bappa yayi tare da girgiza kai ya ce
"Shi mutumin me yayi, kada kice komai kiyi addu'a zakiga alkhairin sa da yar dar ubangiji."
shiru nayi ban kuma cewa komai ba amma a kasan raina sam banji daɗin lamarin ba,
a tunani na ma wani ne daban yakawo sadakin ashe wannan ɗan anacen ne me shegen naciyar tsiya, wato dana ce yatafi da kuɗin sa shine yazo gurin Bappa ko.
kwafa nayi ina ciza laɓɓana na kasa.
haka Bappa yayi ta min nasiha, ina dai zaune ina jinsa sai da ya gama kafin na mike nafita...

Bayan kwana Uku Ahmad ya dawo gurin Bappa da tambayan sa rana, Bappa ya bashi wata ɗaya yace ya dawo bayan wata ɗaya a ɗaura auren.
Ina zaune a parlour ya shigo da salla, su Nasmah suna ganin sa sukayi gurin sa a guje, kamar kullum haka yayi ta biyewa shiriritan su.
daga bisani ya juyo in da nake, in da nayi kamar bansan yana gurin ba.
ganin irin kallon da yake min yasa ni jan guntun tsaki, idanun sa ya lumshe tare da sake buɗe su a kaina kana ya ɗan saki murmushi yace
"Kyakkyawa ta albishirin ki."
ban ko juyo in da yake ba bare ya sa ran cewa zan tanka masa.
murmushi mai bayyana zallan nishaɗi da jin daɗi ya sake sannan yace
"Wata ɗaya Bappa Malam ya yanke min na bani ke, duk da yayi min nisa amma ina cikin farin ciki sosai,
ke ya kama ta ki yanke min kwanakin amma sam kin ki saurara ta da lokacin bazai kai har haka ba,
shi kuma ina jin nauyin sa, kin ga abin da kika jamin ko."
ɗan sakai ta maganar nasa yayi kana ya mike tsaye, zato na tafiya zaiyi  sai gani nayi yadawo kujerar da nake ya zauna,tare da leko fuska ta.
kawar da fuskata nayi gefe, yasaki murmushi mai sauti tare da faɗin
"Yakamata kibani aron lokacin nan naki mai tsada aro nace ba kyauta ba Please, zan maida miki kayan ki da zaran mun gama tattaunawa kan batun hidimar auren mu,
wace Kasa kike so muje a gudanar da shagalin bikin mu, dan Kawa tace bai kamata ayi bikin a Nigeria ba, wani kasa kike so aje a yi acan."

fuska na haɗe na ce "To ni me yada meni ina ruwana in yaso ayi a sama ba'a doron kasa ba."
Ido ya ɗan waro yace
"A sama kuma? wane mu ai bamu kai nan ba."
baki na murguɗa nace "Kada ka kaini da nisa dama yaushe kazo bare ka isa, ai sai isassu, saka saki nake nufi ba'a sama ba a kasa."
"Uhm igiya zaki ɗaura mana muna lilo koko a jirgin sama."
baki na kuma murguɗa wa namike ina kokarin barin gurin.
da sauri yace "Baza a bani aron lokacin ba kenan kyakkyawa ta?."
ban ko kulashi ba nayi gaba abina.....

Tun daga ranar kullum sai yazo bakuma zan kulashi ko na saurarare ba, hakan kuma bashi zai hanashi hobe ya fasa zuwa ba.
ana saura sati biyu bikin
Hajiya Rahama matar ministar Bukar tazo,
bayan mun gaisa nasa aka cike ta da kayan abinci da sha, tana ci muna ɗan taɓa hira cikin hirar take cewa
"Hajiya HAMDAH kin kimu ko nima a waya bare zuwa gida, sai kawai kwasam nasami labarin wai zakiyi aure abun farin ciki wai Ahmad Tijjani Sabil zaki aura, wlh kar kiga yan da nayi farin ciki amma nayi fushi wai sai a bakin wasu zan ji ai ko a waya zaki tura min da sako."

Muemushin yake nayi nace "Ayi min afuwa wlh abubuwa ne zukayi yawa sai a hankali yanzu."
tace "Haka ne kam shirye shiryen biki ga harkokin kasuwan ci abun kam sai a hankali,shiyasa nayi miki uzuri na taso na taho da kafata, Allah ya sa ayi da mu."
zaman ta taɗan gyara sannan ta kalli gefe da gefen cikin parlour'n kana cikin kasa da murya tace
"Amma ya banga karin wasu ma'aikata cikin gidan nan ba, ko zuwa suke su zo."
cikin rashin fahimtar abib da take nufi nace
"Wasu ma'aikatan kuma ai Talatu da Zulai sun wadaci ai kin cikin gidan nan."
tace "Ba waɗannan ma'aikatan nake nufi ba masu gyaran jiki na amare."
baki na taɓe nace
"Masu gyaran jiki kuma, babu wasu masu gyaran jikin da a kayyato."
ido ta waro tare da faɗin
"Wai kina nufin  aure saura sati biyu baki fara gyara ba?, kin san wa zaki aura kuwa?, mutumin da akace matarsa ta mallake sa sai yanda tayi da shi, to wlh yakama ta ki farka tun da wuri kisan abun da kike ciki."
"Uhm nifa babu wani gyaran jikin da zanyi a barshi kawai."
tace "Mene kan kishiya zaki shiga kice bazakiyi gyara ba, matar da ake faɗan ta kowa sai yabada labarin ta, to ko ba komai bace ita ace mutum kamar Ahmad Tijjani Sabil ai dole ayi gyara sufa irin waɗan nan manyan mutanen tanan ne kaɗai zakabi ka mallake su, tun da kai ba hanyar shirka zakabi ba, idan ita da ake labarin nata tana yi sai taje can taci gaba da yi,
kai ma dai baza'a barka a baya ba,
akwai tawa shahararrir mata wacce ake kiran ta da Dr mata Hajiya Lubabatu tana da ma'aikata

da dama tana tura su gari ya gari, ta kware wajen iya gara Yakamata a gaiyatota  ba ma'aikatan taba ita da kanta tazo, hausawa suka ce idan kana da kyau kakara da wanka,
Yakamata kiyi huɓɓasa kifarka da wuri, bari yanzu ma na nime ta."
tana kaiwa nan taɗaga waya ta daddanna ta kara a kunne, jim kaɗan ta soma magana nidai ina jin amma sam ni ban so takira wata ba danni ban sa auren a ka ba.
bayan sun gama wayan ta dube ni tace
"Mun gama magana da ita zatazo gobe, dan ma yau tana gurin wani aikin ne amma tace zata aje ƴar aikin ta acan ita zata zo nan, dan na faɗa mata ko wace ce ke sai ki zauna da shiri gobe zamuzo da ita, zanbi gidan ta na ɗauko ta gobe idan Allah ya kaimu."
"Allah yakai mu." nafaɗa a takaice..

Washegari da safe kamar yanda Hajiya Rahama ta faɗa sai gata da Hajiya Lubabatu,
Hajiya Lubabatu ta bukaci dana ware mana ɗaki guda domin gudanar da aikin ta, ɗaya daga cikin ɗakunan sama nan muka yada zangon mu,batare da ɓata lokaci ba ta fara gudanar da aikin ta.
ranar sai da nayi kuka tuno da Aunty Rafee'at da Hajiya Lubabatu ta haɗa magunguna cikin cup ta ce nasha, sai na tuna ranar data kawo min magunguna a gidan Ya SALEEM tace daga hannun shahararriyan nan aminiyar ta Asma'u Jos ya fito,
ranan nayi kuka sosai tuno da ahlina, Hajiya Lubabati tayi ta rarrashi na da tambayar abin da ya sameni sai dai ban bata amsa ba da kyar ta shawo kaina nayi shiru, sannan taci gaba da aikin ta.
kwanan mu goma da Hajiya Lubabatu, duk wan da ya ganni sai sambarka, ni kai na nasan na sauya sosai, nakara kyau na kara cika ko ina na ya cika tup-tup, kullum muna tare da Hajiya Rahama da wasu kawayen ta, dan acewar ta itace babbar kawa ni dai ina biye mata a haka dan Hajiya Rahama ba sa'ata bace ta girme min nesa ba kusa ba.

Bana fita kullum ina ɗaki in nafita kuwa to iyakata parlour'n sama, kamar yanda Hajiya Lubabatu tace bazan fita ko nan da can ba har sai ta gama aikin ta.
shiyasa ma na sami sa'ida daga gun wannan ɗan anacen dan ko yazo iyakar sa parlour'n kasa yakaraci zaman sa yatafi dan bana sauka.
ana saura kwana uku bikin ranar tun da safe Hajiya Rahama da kawayen ta suka zo, Aunty Nusaiba matar Uncle Mahmoud itama da wasu kawayen ta sukazo, su Inna Wuro da Faty duk muna tare da su a side ɗina,
abin ka da taro ko babu yawane sai kaji hayaniyar nan ai ko parlour'n sama da kasa duk ya dauki hayaniyar jama'a.
wasuyan motoci guda biyar suka shigo gidan masu ɗauke da tambarin sunan Company'n Ahmad Sabil.
duk kanin su shake suke tam-tam da kaya.
shigar su ke da wuya kira ta shigo wayata, koda na duba mai kiran ganin bakuwar lamba ce, kamar bazan daga ba sai da kiran takusa yanke wa kafin na ɗaga da sallama, daga cikin wayar numfashi naji an sauke kana daga bisani a ka soma magana
"Kyakkyawa ta barka da safiya ina fata kina cikin koshin lafiya ke da yarana gaba ɗaya."
Shiru nayi batare da na amsa shiba sai murguɗa bakin da nayi kamar yana kallo na. yacigaba

da faɗin
"Ga ba'i a waje suna niman izinin shiga."
kashe wayar nayi ina kunkuni kasa-kasa "To ina ruwa da an hana ba'in shiga ne ko kuma wani sabon sai da hali ne."
Aunty Nusaiba dake kusa da ni tafube ni tana faɗin
"Wasu ba'i kuma?." baki na turo gaba nace "Wai wannan Ahmad ɗin ne wai wani wai ga ba'i a waje ko da an hana su shiga ne da zai wani kira yana faɗa wa mitane."
tace "A'a kodai motocin da yanzu naji shigar sun nan ne naga mutane tsaye a jikin motar wata kila sune ba'in to ace su shigo mana."
Faty tashiga kwallawa kira Faty dake ɗakin su Naseem tafito parlour da sauri tace
"Yi sauri kije kicewa mutanen da suke wajen nan su shigo sai ki sauke su a parlour'n kasa."
tace To,
jim kaɗan ta dawo tace sun shigo suna parlour, Aunty Nusaiba ta sauka taje ta same su.
bajimawa ta dawo tace min
"Masu ai ki ne wai Ahmad Sabil ne ya turo su wai zasu fita da kayan cikin side ɗin nan su shigo da wasu."
kafin nace wani abu Hajiya Rahama tace
"To bismilla su fara mana, sai su fara daga kasan idan suka gama sai a koma kasan a basu guri su gyara nan ɗin."
tace "To haka ko za'ayi." ta juya ta koma domin sanar musu.
a raina nake faɗin
"Kamar wani an sashi ni shishshigi ne bana so."

Batare da ɓata lokaci ba ma'aikatan da suka kai wajen rai goma dukan su maza ne suka fara gudanar da ai kin su,
kan kace me sun gama kwashe kayan cikin parlour'n kasa, kama daga kujerun cikin parlour'n, bed and bedside drow dressing mirror wardrobe dake cikin bedrooms ɗin parlour'n, zuwa kayan kitchen and dinning.
kaf sukayi waje dasu suka jibge su cikin ɗaya side ɗin cikin gidan da bakowa ciki.
nan suka rinka shiga da kayan da suka zo dasu a mota suna shirya komai yan da ya kamata.
zuwa karfe 1 sun kammala komai sun shirya komai a inda ya kamata.
nan suka bukaci haurawa sama domin cigaba da aikinsu, muka dawo kasan muka basu guri.
lokacin dana sauko kasa sai nazamo ƴar kallo tamkar ba parlour na dana sani ba abun ba'a cewa komai tsaruwar sa ya wuci misali, kowa sai tabawa da sam barka yake....

Sai wajen yamma suka gama kammala komai sukayi mana sallama suka tafi.
abin kamar karya nake ganin shi sai daɗa zamowa gaske yake,ana gobe ɗaura aure Ahmad yaki rani lokacin ana yimin lalle, naki ɗagawa  sai da yayi min missed call biyar kafin na ɗaga, yace
"Madam gani na shigo fito muje asibiti a bincika miki lafiya ta."
"Meye damuwa ta da lafiyar ka."

nafaɗa tare da kashe wayar.
ina kallon wani kiran nasa na kuma shiga haka naki ɗagawa, ga haushin lallen da aka bi aka dame ni da shi nifa in da anbi tanawa da duk waɗan nan fidda ficen da an barsu.
tsaki naja jin wani kiran ya kuma shigowa a fusace na ɗago wayar niyyata na gaya masa magana idan bai dai na dami na ba,
sai naga number Bappa ne ya bayyana kan Screen ɗin wayar, da sauri naɗaga wayar tare da yin sallama Bappa yace
"HAMDAH fito kuje asibiti ga Ahmad na jiran ki, kinsan yanzu ba ayin aure sai da gwajin lafiya kuje ku gwada lafiyar ku sabo da sai da shi
yanzu ake yin aure, kafin a ɗaura aure gobe dole sai an bukaci takardar shaidar ingancin lafiyar ku wan da yafito daga hannun likita."
nace "Bappa lalle ake min kuma yanzu akayi bai bushe ba."
yace "To bari ace yatafi in yaso anjima sai ya dawo."
To na amsa da shi a takaice...

Sai bayan sallar la'asar kafin lallen yabushe aka wanke, duk nabi na gaji, a gabiye na faɗa cikin bedroom ɗina, nashige cikin bayi domin yin wanka nakuma gyara jiki na, dan naji alamar zuwan al'ada ta. shi yasa nace wa Hajiya Lubabatu zanje ɗaki na na ɗan watsa ruwa acan na huta dan nagaji da yawa,
ina gama kimsa jikina nafito, gaban mirror na zauna nasoma shafa haɗin mayuka masu daɗin kamshi data haɗa min.
waya ta ce tashiga ruri ganin mai kiran yasa nayi banza, yayi ta kira yafi a kirga ban ɗaga ba. knocking akayi tare da yin
sallama daga bakin kofa, jin muryar Faty ce yasa nace tashigo.
tace "Adda HAMDAH wai kizo inji Yaya Ahmad."
fuska na ɓata nace "Kice bazan zo ba."
har takai bakin kofa nace "Bappa na gida ne?." tace "Eh." nace "Kice masa ina zuwa."
ta amsa da to tayi waje.
tsaki naja a fili nace
"Wlh badun kada Bappa yace naraina sa ba Allah da ba abin da zaisa naje."
sai da nagama iya yanga ta kafin nasaka kaya nafito ina gyara mayafin kaina, su Nasmah na ganina suka biyo ni da gudu suna faɗin "Mommy damu biki." Aunty Nasiba dake parlour'n kasa tana tare da masu aiki suna ta shirya abinci, nace mata zamuje asibiti tace "A dawo lafiya Allah ya tsare."
nace "Amin." nayi waje su Naseem suka biyo ni suna cigaba da faɗin zasu bini..

Yana zaune a mota yana ganin mu tun kan mukaro ya fito acikin motar.
ihun murna yaran suka sake sukayi gurin sa a guje suna faɗin
"Laa Daddy yazo oyoyo Daddy." ya buɗe hannun sa suka faɗo jikin sa ya rungume su yana dariya tare da bin ko wannen su da sumbata.
na karaso gurin fuska ta ɗaure tamau, yasake yaran yana faɗin
"Kuzo mu buɗe wa Madam mota kada ta gaji da tsayu." yazaga ɗaya barin ya buɗe yadube ni

dakyau sannan yace
"Kyakkyawa ta bismilla taho ki shiga." yayi maganar tare da nuna min hanya da hannu yayin da ɗaya hannun sa ke rike da marfin motar.
fuska na yamutsa namatso jikin marfin motar, ganin yana tsaye daf da in da zanbi nashiga cikin motar, sai na ja natsaya tare da naɗe hannaye na a kirji.
murmushi ya yi kana yaɗan ja da baya kaɗan tare da faɗin "Bismillah Madam." baki na taɓe nashige cikin motar da bismilla. yamai da marfin ya rufe.
tuni su Naseem sun shige gidan baya sai tsalle-tsalle suke. yazaga gefen direba ya shiga ya ja motar a hankali yayi hon mai gadi ya buɗe get yasa kai yafita a hankali.

A hankali yake tukin kamar mai tautsayin kasa, yayin da su Nasmah keta zuba masa surutu yana biye musu, lokaci zuwa lokaci sai ya juyo ya kalle ni, niko na ɓata rai nayi kamar bana cikin motar.
sai da naji ya gyara parking kafin na ɗago, *HAM'NAS* International Hospital na ganmu ciki. maganar sa najiyo yana faɗin
"Mushiga kyakkyawa ta ko na sauko na buɗe miki ne?."
tun kan yarufe baki nayi saurin ɓalle marfin motar nafita ina jan karamar tsaki........!

Mommyn Twins ce

16

Ina fita daga cikin motar na shige cikin asibiti, batare da na jira fitar sa ba,
yabuɗe wa su Nasmah yaruko hannun su suka biyo baya na, a kusan tare muka shiga  cikin parlour'n asibitin.
cike da girmamawa ma'aikatan asibitin suka shiga yi mana maraba da zuwa,
direct office ɗin Dr ya nufa bayan yace nazo mu shiga.
kamar bazan bisa ba har sai da yakai bakin kofar office ɗin kafin na biyo shi,
Dr na ganin mu ya mike da sauri yana amsa sallamar da Ahmad yayi.
Dr yace "Barkan ku da zuwa bismilla."
yanuna mana kujeru biyu da suke fuskantar juna wan da suke gaban table ɗin sa, sai da muka zauna kafin shima ya koma mazaunin sa,
bayan gaisuwar da ya mika mana cikin girmamawa kana ya shiga yiwa su Naseem da suke like

jikin Ahmad wasa.
Dr ya dubi Ahmad yace "Rankashidaɗe  an shirya za'a iya gudanar da aikin yanzu?."
yace "Eh." batare da ɓata lokaci ba Dr ya kirawo wasu Nurse's biyu mace da na jiki, in da macen taja jini na namijin kuma yaja nasa.
muna nan zaune can da ɗan jimawa suka dawo da Result ɗin test ɗin,
suna mikawa Dr suka fita, Dr yashiga buɗe takardun, shiru yayi tare da duban mu dukkan mu kana ya kuma mai da idanunsa kan takardan,
da sauri Ahmad da gaba ɗaya yanayin sa ya sauya a ƴan sakanni yace
"Yaya dai Dr me ke faru!?." yayi tambayar da yanayin shiga damuwa,  jim kaɗan Dr ya ɗago da murmushi yadube mu yana faɗin
"Komai dai-dai babu wata matsala."
Ahmad ya sauke wani dogon numfashi  kana ya mike tsaye fuskantar sa ɗauke da murmushi mai bayyana zallan farin ciki, Dr ya mika masa hannu yana faɗin
"Allah ya sanya alkhairi yabada zaman lafiya."
da sauri yace "Amen amee ameeeeeen ya rabbil izzati."
ya mikawa kowa result ɗin sa.
har gurin mota Dr ya rako mu sai da muka shige mota sannan ya koma ciki.
yaja motar muka fice daga harabar asibitin.
har lokacin fuskarsa sa na bayyane da zallar jin daɗi da farin ciki,sai zuba murmushi yake. niko lokaci zuwa lokaci sai na ja karamar tsaki dan acike nake tam.
ya juyo gefen da nake ya dube ni da murmushi kana ya mai da idanun sa kan titi yace
"Kyakkyawa ta kin ji albishir mai daɗi ko, ina cikin farinciki sosai da kika sami kyakkyawar sakamako a kaina, ina da tabbacin zaki daɗa samin nutsuwa dajin inganci lafiya ta,
baki ji yan da naji ba ɗazu da Dr nan yayi shiru bai faɗi result ɗin ba yana kuma kallon mu, tunani na ɗaya ace nine keda wata matsalar shike nan nasan baza a bani ke ba, niko ban damu ace kina da wata matsala ba ahaka nake so kuma zanyi rayuwa da ke."
annurin fuskarsa yakuma faɗaɗawa sannan ya kuma dubana yana faɗin
"Kyakkyawa ta bazakiyi farin ciki da jin result mai daɗi ba dajin ingancin lafiya ta."
baki na murguɗa nace "To ni inaruwana da wani ingancin lafiyar ka, mutum da lafiyar sa an sa yaje an wani ɓula masa jiki akarin banza,  ."
nayi kwafa ina kawar da kaina gefe.
da sauri yace "Yihakuri Madam  na tabbatar kina da lafiya dan kisan lafiya ta yasa mukaje asibitin ayi min afuwa a gafarce ni, juyo ki kalle ni ki tabbatar da gaskiya ta kinji kyakkyawa ta."
daɗa kawar da fuskata nayi ina cuno baki gaba haɗe da murguɗa masa bakin,
murmushi mai sauti yayi yana leko fuskata... awani katon ShopRite ya tsaya yajuyo gefen da nake yace
"Kyakkyawa ta sauko mu shiga."
ko kallo bai ishe ni ba bare yasa ran amsawa ta.
tare da su Naseem suka shiga can suka fito niki-niki da kayan ciye-ciye...
Muna isa gida tun kan ya karasa dai-dai ta parking nakai hannu jikin matfin motar zan buɗe najita gam, sai da ya dai-dai ta parking ɗin batare dana dube sa ba nace
"Buɗe min." nafaɗa a takaice,
jin yayi shiru baiyi magana ba ya sani juyowa gefen da yake a kufule, karaf muka haɗa ido da

sauri na janye ido na, shiko numfashi ya sauke tare da faɗin
"kin ki faɗa min in da kike so ayi shagalin bikin mu."
"Da zai fi maka karike tambayar ka kadai na dami na da ita, danni babu abin da zai kai ni gurin wani biki."
ya ce "Shike nan an daina damin ki duk yan da kike so haka za'ayi,
wai duk wannan lallen wani akayi kai gaskiya naji daɗi na, amma yayi kyau sosai fa, shine ba'a faɗa min nabada kuɗin lallen ba bayan an san hakki nane, kawo na kara gani dole ma na biya kuɗin sa."
yakai hannu ya kamo nawa yana cigaba da faɗin
"Kice zan sha kallo gobe amma bari na fara tun yau."
da sauri nayi yunkurin fisge hannu na jin wani irin shock lokaci goda ya sarga min, sai dai yan da ya rike hannunan ban sami damar iya fizge wa ba.
"Sake min hannu Malam kabuɗe min kofa nafita." nafaɗa ina ta kiciniyar kwatar hannun nawa.
yace "To naji amma muga wayar ki."
"Adalilin me zan baka waya ta?."
"Aro zaki bani yanzu zan duba abu na baki."
gyara rukon wayar nayi a ɗaya hannu na na ɓata fuska nace "Ka sakar min hannun kakuma buɗe min kofa."
numfashi ya fesa yajuya baya ya dubi su Naseem gaba ɗaya hankali su na kan kallon katun ɗin da ya saka musu a wayar sa tun fitar su daga ShopRite ɗin nan.
kana ya dawo da kallon sa gare ni a hankali yaɗan rankwafo in da nake har ina jiyo kamshin sa sosai, idanu ya lumshe  tare da kuma buɗe wa a kaina, da sauri na rumtsa idanuna ganin yana ta kokarin saka nasa cikin nawa, ga yan da yamatso ni sai nake jin jikina yayi min nauyi wani abu mai kamada kasala nata kokarin ziyartata,
"Ka sake min hannu ka buɗe min kofa." nayi maganar cikin ɗan ɗaga sauti yayin da idanuna ke rumtse.
yace "Zan sake ki zan kuma bude miki bayan kin bani aron wayar ki."
da sauri na mika masa wayar dan yana yin yanata daɗa shiga ta.
ya amshi wayar tare da sakar min hannu, a tare muka saki numfashi mai sauti, nayi saurin gyara zamata na matsa tajikin kofa sosai.
shima zaman nasa ya gyara kana yashiga latsa wayata daga bisani yaɗau ɗayan wayar sa shima ya daddanna sannan ya mika min wayata yana faɗin
"Na biya kuɗin lallen da aka tsara min ɗin nan."
yana rufe baki kuwa saiga shigowar alat na 1 million.
fuska na yamutsa, shiko murmushi yayi tare da buɗe min kofar, nafita da sauri ina tafiya ina kunkuni,
bayan na yabi da murmushi har na ɓacewa ganin sa, yafito ya buɗewa su Nasmah yace musu su shiga ciki shi bari ya tsaya yayi salla dan lokacin ana kiran sallar magriba...

Ina shiga na tadda su Aunty Nasiba natakan ai ki sukayi min barka da dawowa na amsa inayi musu sannun su da aiki.
koda na haura sama kayan jikina na narage sannan na fita na shiga ɗakin da su Hajiya

Lubabatu suke, tana ganina tace "Yanzu nake kan maganar ki yauce rana ta karshe ga sauran kayan ki da yawa ga su dai na haɗa karɓi kisha yanzu cikin dare kya karasa sauran."
tamika min cup mai haɗin magunguna ciki, na karba ina yamusa fuska na sha nan ta sani na kwaɓe kayana tashiga mulke ni da wasu sinadaran,
har wajen karfe biyu na dare idanun mu biyu dan a daren akayi min gyaran gashi,
bamu muka kammala komai ba sai wajen karfe huɗu na asuba bayan ta wanke ni da ruwan turare nan na wuce ɗaki na,
nafaɗa gado dan gaba ɗaya idona rufewa yake sabo da tsabar bacci,
na gyara kwanciya ta ina kunkuni kasan raina
"Haka kawai a hana mutum bacci akan karin banza."
batare da ɓata lokaci ba bacci yayi awon gaba da ni....

Can cikin bacci najiyo muryar Faty tana bubbugani da kiran suna na,
mika nayi tare dayin salati na bude idanuna.
fuska na ɓata nace "Faty meye haka mutum yana baccin sa zaki kama tada ni."
kai ta langwaɓar gefe tace
"Ayya Adda HAMDAH kiyi hakuri Bappa ne yace nazo na tada ki yayi ta kiran wayar ki baki ɗauka ba."
a hankali na mike zaune tare da kuma yin mika haɗe da salati,
na dubi agogon dake like da mirror karfi 12:30, ido na waro nayi mamakin ganin yan da lokaci yatafi haka.
janyo wayata dake karkashin pillow nayi ido na waro kan wayar ganin missed call ɗin Bappa yacika wayar.
da sauri na sauko a gadon na ɗau katuwar jijabin sallah ta na zura nayi waje Faty ta biyo naya na,
wani irin daddaɗan kamshi ne yaziyar ci hanci na san da na kusa kai na cikin parlour, an gyara ko ina sai kamshi ke tashe, babu kowa cikin parlour'n sai kamshi da sanyin da ke tashi ciki.
step na nufa da ɗan sauri, na sauka kasa
mutane ne tam cikin parlour'n ka da wan da na sansu da wan da ban sansu ba, a sakiyar parlour'n kuwa wasu zuka zukan akwatuna ne da suka kai set 6 kaloli daban-daban, Inna Wuro na zaune gaban akwatunan tana gani na tayi min murmushi, nima na mayar mata tace
"An tashi ne HAMDAH?." nace "Eh Inna inasu Nasmah ne?."
tace "Ai yau su Nasmah ba  zama anayi musu wanka suka  fita wai Daddy'n su na jiran su a waje." kai kawai na jinjina.
can na hangi su Hajiya Rahama da Hajiya Lubabatu suna ta nuna wa wasu mata kusurwa-kusurwan cikin parlour'n in da zasu kunna turare.
nayi musu sannu na wuce su in da wasu suka bini da guɗa suna faɗin
"Kaga amarya ta fito hasken ta ya bayyana."
banbi ta kansu ba nayi waje.
ina shiga side ɗin su Bappa na taddashi tsaye yana gyara zaman babban rigar jikin sa yana gani na yace
"HAMDAH ina kika saka wayar ki nayi ta kiran ki baki ɗagawa?."
nace "Bappa bacci nake."

yace "Ina takardar sakamakon da likita ya baki jiya a asibiti? ga mutane can an fara hallara ana idar da sallar juma'a za'a ɗaura gashi lokaci ya tafi ɗaya saura yanzu yi maza ki kawo min."
wani irin rass naji gaban kirji na ya yanke jiki a sanyaye nace
"Yana ɗaki."
yace "Yi maza ki kaso min." nan da nan naji jikina yayi mugun sanyi, na dubi Faty nace "Faty je ki ɗaki zakiga takarda kan mirror ki ɗauko."
tace to ta juya da sauri ta fita.
niko
a hankali nayi baya nazauna saman kujera dan gaba ɗaya jikina yagama sanyi har nake jin jikina nason yayi wa kafafu na nauyi, a bun da nake ganin sa kamar wasa dai gashi nata kokarin zamowa gaskiya.
lura da yanayin da na shiga yasa Bappa yashiga yimin nasiha, ina dai jin sa amma gaba ɗaya hankali na baya gunsa.
batare da ɓata lokaci ba Faty ta dawo rike da takardan, ta mika min nikuma na mikawa Bappa ya amsa da sauri ya fita.
nakai tsawon minti goma zaune a gun daga bisani na mike a hankali na fita na koma side ɗina.
koda na shiga bedroom ɗina akwatunan dana gansu a parlour'n nan su nagani jere cikin ɗakin, kan gado nabi da kallo, wani dankararren leshi ne haɗe da gyare da jaka da takalmi,da sarka da ƴan kunne da abun hannu mai sheki da ɗaukar ido,
turo kofa akayi da sallama Hajiya Rahama ne ta shigo ta dube ni tana faɗin
"Ƴan uwan Ahmad suka kawo akwatunan nan kina bacci yasa ba'a ɗagaki ba, amma anyi musu sallama da tukuici na musamman, na sending musu 500k ta account ɗin su, an haɗa su da drinks katon ashirin haɗe da cincin da diblan da akayi jiya na ba'i sai dai babu yawa tun da ba'a san da zuwan su ba, boket shida ne kawai, yanzu nasa a karayin wani saboda wan da za'a baiwa ba'i, hakan yayi dai ko?."
nace "Yayi sosai ma bani account number ki na samiki kuɗin."
tace "A'a nima gudumawa ta kenan kibarshi, ga kaya nan an cire miki sai kiyi wanka ki saka."
nace to tare da yi mata godiya, tajuya ta fita,
na tuɓe hijabi na na shige bayi, wanka sosai nayi na kimsa jiki na da kyau sannan na fito, gaban mirror na zauna nashiga mulke jikina da mayuka masu daɗin kamshi haɗin hajiya Lubabatu,
simple make-up nayi amma nayi kyau sosai dan nasha gyara sosai ga kyan halitta ta da ubangiji yayi min.
a hankali na mike na isa in da kayan yake na ɗago su na soma sakawa, ɗin kin leshin riga da zani ne tsarin ɗin kin yayi, bayan na saka kayan na ɗau sarka da ƴan kunnen nazo gaban mirror na saka,sannan na murza ɗaurin ɗankwali, a hankali nabi jikina da turare natsaya ina kare wa kaina kallo tacikin mirror.

Kamar daga sama najiyo sautin babban masallacin unguwar mu ana faɗin "Fatihaaaa Allah yayi aure ya ɗauru Allah ya bada zaman lafiya da zuriya ɗayyiba."
kirji na ne yayi wani irin bugawa da har sai da na kai hannuna na dafe kirjina, wani irin jiri ne ya ɗibe ni na kwalla kara tare da zubewa kasa na rushe da kuka mai matukar tsuma zuciya tamkar zan shiɗe.

Faty ce ta shigo ta sha wankan ta rike da ɗankwali a hannu Aunty Nasiba ta dube ta cike da zulaya tace
"Duk a cikin gayen ne haka rike ɗan kwali a hannu."
dariya tayi tana faɗin
"Gun Adda HAMDAH zani ta ɗaura min."
ta haura sama ta tura kofar da sallama da sauri ta karaso cikin ɗakin ganin yan da na haɗe kai da guiwa nake ta faman rusar kuka,
tashiga girgizani tana faɗin
"Adda HAMDAH me ya same ki?."
ban iya bata amsa ba sai sautin kuka na daya karu,
a kiɗime ta sake ni tayi waje, tun daga saman step tashiga kwaɗawa Inna Wuro kira, sabo da hayaniyar jama'a yasa Inna Wuro bata jiyo kiran ba, da sauri Faty ta karasa sauka tazo in da Su Inna Wuro ke zaune ta ruko hannun ta tana yi mata nuni da sama da faɗin
"Adda HAMDAH."
"Me ya sami HAMDAH!?." Inna Wuro tayi tambayar hankali tashe ganin yan da Faty'n ta ruɗe tana nuna hanyar sama ta mike tsaye da sauri ta haye sama Faty na biye da ita.

Ina durkushe a gurin har lokacin kukan nake kamar raina zai fita. hankali tashe Inna Wuro tashiga faɗin
"Subhanalillahi HAMDAH lafiya me yasame ki?."
ta ɗago kaina dana haɗe da guiwa, sai kawai na zube a jikin tare da kuma fashewa dawani sabon kuwa, cikin muryar kuka sosai nake faɗin
"Inna Wuro wai da gaske an ɗaura auren Inna Wuro ina jin tsoro suma zasu cutar dani."
bayana tashiga bubbugawa jiki a sanyaye ta gyara zaman ta a kasan tadaɗa kwanto da kaina bisa kafar ta tashiga rarrashi na da kalamai masu kwantar da hankali haɗe da natsiha mai shiga jiki da karfafa guiwa. har sai da taga nayi shiru hankali na yado jikina kafin ta fita a ɗakin ta barni ni da Faty da itama tagama shan kukan ta...

Har yamma ina daki ban fito sai wajen sallar magriba bayan nayi wanka na sauko kasa, nan na tadda mutane sunanta watsewa, Hajiya Rahama da Aunty Nasiba nata sallamar mutane da kayan tsaraba.
nan na shiga tayasu har jama'a suka watse, yarage Hajiya Rahama da Aunty Nasiba da Hajiya Lubabatu,
bayan sallar isha Hajiya Rahama da Hajiya Lubabatu sukace zasu tafi, har gurin mota muka raka su ni da Aunty Nasiba, nayi ta musu godiya sosai bayan na sallami Hajiya Lubabatu da kuɗi mai tsoka.
sai da mukaga tashin su kafin muka juya, a tsakiyar gidan muka rabu da Aunty Nasiba tace min zata wuce sashin su Inna Wuro acan zata kwana, nayi-nayi mukoma side ɗina mukwana a can taki.
koda na koma ciki na tadda su Zulai sunata daɗa gyara cikin side ɗin suna gamawa suka tafi ɗaya side ɗin dan tun ranar da aka zuba sabbin kaya suka kwashe kayan su suka koma can.
tuni Naseem da Nasmah suka yi bacci saboda gajiya dan tun da safe da suka bi Ahmad ban

sake sasu a idona ba sai yamma.
ɗakin su na shiga na gyara musu kwanci tare da yimusu addu'a sannan naja musu kofa na fita na koma ɗakina....

A ɓangaren Ahmad kuwa, cikin gidan sa cike tam yake da jama'a shigowar sa kenan cikin parlour'n sa bayan ya sallami wasu ba'in sa, jama'a sai zolayar sa suke dayi masa kirari, ɗaya daga cikin ɗakunan da suke cikin parlour'n ya shiga,
wasu manyan mata ne zaune cikin ɗakin yakaraso ya zauna tare da gaida su, suka amsa sunayi masa ya gajiyar hidima.
ɗaya daga cikin matan ya mai da hankalin sa gare ta yace
"Hajiya naga kiran ki ɗazu ina tare da jama'a ne."
tace "Eh dama na kira ne naji wata shirin ake kanyi na ɗauko amaryar naga dare nadaɗa yi ne, ga jama'a sun fara watse wa."
murmushi yayi tare da faɗin
"Ai Hajiya wannan amaryar baza ta ɗauku ba abar masu tafiya sutafi abin su kawai."
tace "Kamar ya ba zata ɗauku ba?."
zaman sa ya gyara sannan yace.......!

Mommyn Twins ce

*HMDH*

*WASA FARIN GIRKI*

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR

Yace "Hajiya za'a ɗauko ta amma ba yauba sai bayan ɗan wani lokaci."
Hajiyar takarkata baki tana faɗin
"Aure jibge kayi ne? yo in ba haka ba ace duk girman gidan nan ba rashin ɗaki ba ba komai ba, kayi aure kabar matar ka wani waje bazaka haɗa kan iyalen ka guri guda ba, ko gimbiyar taka ta hanaka kawota gidan ne?."
yace "Hajiya ita kuma meye nata a ciki, ai in da wan da yake son auren nan ma to bayan ta ne, wani ɗan karamin dalili ne kawai yasa yau baza a ɗauko ta ba."
tace "Eh ai dama ita bata laifi badai ta yi sake an yi auren ba ai wayon ta ya kare."
Murmushi Rasheedat data sako kanta cikin ɗakin ta sake dan duk abin da suke a kan kunnen ta,ba farau bane hakan gun Hajiya da dangin ta, a koda yaushe gani suke ta mallake shi sai abin da tace zaiyi, ko wannan auren ma dasuka jishi lokaci guda sunyi matukar murna acewar su yanzu ne zai auri mata ita kam itace mijin shine matar,duk da dai bahaka suka so ba sai dai babu in da suka iya haushi da sanar Rasheedat shi yasa su yin murnar auren nasa. gani suke ta gama mallake sa sai abin da ta ce tahana wasu shigowa suci arziki, ita ba haihuwa ba, Hajiya Karima itace Uwar gidan Alhaji Tijjani Sabil wato mahaifin Ahmad, wacce yanzu yake kallon ta a matsayin uwa,
tun kafin ya auri Rasheedat Hajiya Karima taso haɗa shi da ɗiyar kanin ta wacce take hannun ta suna tare duka da Rasheedat ɗin a gidan mai suna Sakeenat, yaki amin cewa yace sai ƴar uwar sa ta jini,
duk yan da Hajiya Karima takai ga shiga da fitan ta haka Ahmad yaki sam yake kuma Allah bai bata ikon juya shi ba.
karshe dai haka ta hakura badun taso ba, a ɓangaren Sakeenat ma kuwa tana son Ahmad kamar tayi yaya har kuma gobe tana son sa, sabo da shi taki zaman auren da aka mata ko yanzu da take zawarci tana fata da burin mallakar Ahmad, sai dai abune mai wuya dan ko gaisuwar ta baya amsawa...
Rasheedat
ta karaso cikin ɗakin ta dire babban tray da aka shirya musu abincin su ciki, kana tayi musu barka da warhaka, a yatsine hajiya Karima ta amsa bai dame ta ba tana dago wa suka haɗa ido da Ahmad suka sakarwa junan su murmushi.
kana tayi waje.
wayar sa ce tayi kara ya ɗaga kiran sannan ya mike yafita.

Da sauri ya bi bayan Rasheedat dake kokarin shiga corridor dazai sadata da side ɗin ta, ya ruko hannun ta ya janyo ta sukayi gefen sa suka shige cikin bedroom ɗin sa, suna shiga ɗakin ya janyo ta jikin sa ya rungume tare da marairaice murya ya ce
"Wash Kawa nagaji." gemun sa ta ja tace "To yau dai bazan ce ma sannu ba dan yau rana ce ta musamman gajiya dole."
fuska ya marairaice yace "Haka zakice?." tace "Haka na faɗa, muje na tayaka wanka kanwata nazaman jiran ka, dan kasan dai kai zakaje ba dai ita tazo ba."
murmushi yayi tare da shafo gefen fuskanta yace

"Hukuncin da aka yanke min kenan?."
tace "Har ya zartu ma kuwa."
a tare suka saki dariya, nan tashiga taimaka masa yarage kayan jikin sa kana suka faɗa bayi, ta taimaka masa yayi wanka kana suka fito, nan ma ta tayashi sa kaya sannan ta bisa da turaruka masu daɗin kamshi.
gaban wardrobe ta isa ta buɗe ta ciro jaka mai ɗan girma sannan ta rufe ta buɗe ɗaya gefen tashiga ciro kaya tana zubawa cikin jakar,
ido ya zuba mata ganin yan da take aikin zuba kaya cikin jakar yace
"Kawa ina za'a kai kayan kuma?."
bata bashi amsa ba har sai da ta cika jakar tam da kaya kafin ta juyo ta dube shi tace
"Ina zuwa." ta fita jim kaɗan ta dawo da mayafi a kanta
ta ruko hannun sa tare da faɗin
"Taso muje na raka ka duba kagani har karfe 11 saura."
yace "Kawa ina kuma?." tace "Ina kuwa in ba gidan HAMDAH ba ko kasan cewa lokacin ta kake shiga, yanzu haka tana can tana zaman jiran ka."
ido yaɗan waro yace "Shine da wannan katuwar jakar kamar wan da ake kori na."
tace "Eh ayau kam kusan haka din ne."

Ta janyo hannun sa tare da ɗaukar jakar sukabi ta kofar baya,ɗaya daga cikin motacin sa suka shiga ya jasu a hankali suka fita.
a hanya ta sashi ya tsaya ya siya gasassun kaji kafin suka wuce.
suna isa bakin get din gidan yayi hon masu gadi suka buɗe masa, yakusa hancin motar ciki yana dai-dai ta parking  suka fito a tare, tana rike da jakarsa inda shi ke rike da laidar gasassun kajin da suka tsiya, suka nufi side ɗin.
Sauko wata kenan daga sama yunwa ta dame ni dan wunin ranar yau bansa komai a ciki na ba, na shige kitchen nashiga bude buɗe ko zan ga abin da zan sawa cikina,
wani kula na buɗe mai ɗauke da tuwon farar shinkafa mai ɗume, na ɗau plt na saka laida ɗaya, kana na buɗe ɗaya kular dana gani a kusa dashi, miyar agushi ne daya ji busashshen kifi da hanta na zuba akai kana nafito parlour na zauna nasoma ciki.
knocking ɗin kofa akayi har sau uku akai-akai, ido naɗa zubawa kofar da tunanin mai buka kofar da daddaren nan, nai tunanin ko su Talatu ne, na mike a sannu na isa jikin kofar na murza key ɗin tare da buɗo kofar.
da ɗan mamaki na kalli waɗan da ke bakin kofar, Rasheedat ta saki murmushi da faɗin
"Kada ace bacci kike muka taso ki?."
murmushin yake namayar mata ganin yanda take ta yimin magana cikin fara'a.
shiko na tsaye bai yi magana ba amma idanunsa a kaina, ganin yan da ya kafe ni da mayatattun idanun nan nasa sai na saki kofar najuya na koma ciki.
suka biyo bayana, zama sukayi kan kujera in da nikuma na zauna kan hannun kujerar da ke can karshe ina zaman jiran jin abin da ya kawo su da daddaren nan.
Rasheedat ta dube ni fuska ɗauke da annuri tace
"Narako sa ne da kaina na baki hakurin rashin zuwan sa da wuri wlh ba'i ne sukayi yawa sai a hankali, gashi nan na kawo miki shi da fatan za'a kula da shi yanda ya kamata,

to ni bari naje dare yana daɗe yi sai da safen ku Allah ya tashe mu lafiya."
ta mike tare da duban Ahmad tace
"Aboki bani makullin motar na koma."
ido ya waro yace "A daren nan zaki fita ke kaɗai? bazai yuwu ba bari nasa a maida ki."
murmushi tayi tana karɓar key ɗin a hannun sa tace "Babu abin da zai faru da yardar Allah Allah zai tsare, ka mai da ni karamar yarin yace nifa yanzu na girma."
ta kashe masa ido tana kokarin juyawa ta tafi.
nayi saurin mikewa tare da dakatar da ita ta hanyar faɗin
"Da kin tsaya kin koma da shi da zai fi muku."
ina kaiwa nan na juya na haye sama...

Rasheedat tayi murmushi tare da dafa kafaɗan sa tace "Aboki katashi ka bita ka shawo kanta, kasan amarya sai da lallami."
kai ya jinjina yaruko hannayen ta duka biyu yayi kiss ɗin su, kana ya lumshe idanun sa tare da buɗe su a lokaci guda,
ya mike tsaye yace
"Muje a maida ki gida hankali na zaifi kwanciya."
koda suka fita ɗaya daga cikin security gidan ya umurce sa daya mai da ita gida, yana tsaye saida yaga fitar su kafin ya koma ciki.
yana shiga ya rufe kofar side ɗin kana ya haura sama. yana kusa kansa cikin parlour'n sama, idanunsa ya lumshe tare da jan numfashi ya shaki daddaɗan kamshi mai sanyi da rasa zuciya, a hankali ya buɗe idon nasa cikin kayataccen parlour'n a fili ya furta "Masha Allah."
a sannu yafara taka kafafun sa cikin parlour'n yayin da yake rarraba idanunsa ga kofofin bedroom's ɗin da ke cikin parlour'n,
a sannu ya nufi wasu kofafin bedroom's
guda biyu wan da suke a jere, yasaka hannun sa jikin ɗaya kofar ya murɗa a hankali ya tura kofar, ya kusa kansa ciki.
can ya hangi su Naseem kan gado suna baccin su cikin kwanciyar hankali,
murmushi ya sake a hankali ya karasa shiga cikin ɗakin a bakin gado ya zauna yashafi gefen fuskar ko wannen su yana binsu da murmushi kamar waɗan da idanun su biya, kana ya mike ya daɗa jan bargo ya rufe musu jiki, yafita ya ja musu kofar.
numfashi ya sauke lokacin da yamaso jikin ɗaya kofar da ke kusa da bedroom ɗin su ya tura kofar ya leko kansa ciki,
babu kowa cikin ɗakin sai dai a gyare yake tsaf-tsaf gadon cikin ɗakin yasha shinfi ɗakin sai kamshi yake tashi, shakar kamshin yayi yana mai jin dadin kalar kamshin da side ɗin gaba ɗaya yakeyi, kuma ko wani bedroom da kalar kamshin da yake tashi.
mai da kofar yayi ya rufe ya juyo ya zuba wa ɗaya kofar dake can gefe ita kaɗai ido.
a sannu ya taka izuwa jikin kofar, sai kuma ya ja ya tsaya na ƴan dakiku kana a hankali ya kai hannun sa jikin handle ɗin kofar a hankali ya murɗa ya tura kofar a sannu ya kusa kansa ciki.
wani irin dogon numfashi yaja yana mai shakar daddaɗan kamshin daya bigi hancin sa...
firgit na mike zaune jin an turo kofa, cike da mamaki nake kallon sa yana tsaye idanun sa a lumshe a sannu yaware idanun nasa a kaina.

A hankali ya soma takowa cikin ɗakin, ina ganin haka na yi saurin zamowa bakin gadon ina binsa da kallon tuhuma, gani ya dumfaroni gadan-gadan yasani mikewa da sauri nace
"Meya kawo ka cikin ɗaki na?, ka ketare tun daga kasa ka hauro sama kashigo min har cikin ɗaki?."
sai da ya matso daf dani kafin yasoma magana
"Hurimi iko mallaki, duk na haɗa yau, babu wani shamaki sakani na da ke meye nayi min wannan tambayar kyakkyawa ta."
yayi maganar yana kokarin ruko hannuna, nayi baya da sauri cikin ɗan ɗaga murya nace
"Kafita min a ɗaki Malam."
ido ya zuba min babu ko kakkauta wa yana bin jikina dawani irin kallo, da sauri na kalli jikina, riga da wando na bacci ne a jikina rigar mai tsiririn hannu irin mai gidan bra ɗin nan, mai tsamtsi ne sosai ya bi jikina ya lafe.
kan na an kara har ya matso daf dani har jikin mu na gogan juna, baya nayi da sauri na matsa baya kasan cewar ina tsaye daf da bakin godo ne sai ji na nayi na zube kan gadon.
da sauri na mike zumbur na saka hannaye na bibbiyu na ture kirjin sa na bi gafen sa nasa kai zan wuce,
sai ji nayi ya cafko hannuna ya janyo ni jikin sa har sai da na garu da jikin sa,
"Ka sake ni idan ba haka ba wlh sai nayi maka abin da baka taɓa tunani ba."
ɗan rankwafowa yayi saitin fuskata a hankali ya furta
"Za ki sa a zo a fitar dani ko? wani sam bazai iya ba kin taɓa ganin in da aka fidda miki ɗakin matar sa."
sai kuma ya saki murmushi mai sauti a sannu ya sauke yatsar sa kan baki na yana ɗan zagaye lip ɗina, sai ya lumshe idanun sa a lokaci guda ya buɗe yace
"Suna da kyau sosai gwanin ban sha'awa."
yayi maganar tare da ɗan matsa laɓɓana,
da sauri na bige hannun sa, ina wasa masa harara.
na fizge jikina da sauri na nufi kofa na buɗe nafita,
ɗakin su Nasmah na shige na maida kofar na rufe tare da murza key, nahaye tsakiyar su nayi kwanciya ta.

A ɓangaren Ahmad kuwa bayan ta yabi da kallo har ta fita, kana ya sauke numfashi a sannu ya masa bakin gadon ya zauna yakai tsawon minti 20 kafin ya mike yafita a ɗakin, kasa ya sauka ya ɗau jakar kayan sa ya dawo dakin,
yabuɗe jakar ya ciro jallabiya mara nauyi ya tuɓe kayan kijin sa ya saka sannan ya haye gadon ya kwanta tare da janyo pillow ya rungume a jikin sa yana mai shakar daddaɗan kamshin dake tashi daga jikin pillow'n zuwa gadon gaba ɗaya
a fili ya furta
"Yarin yar akwai son kamshi."
sai kuma yasaki murmushi yana daɗa rungumar pillow'n, ya ɓata tsawon lokuta masu tsawo kafin bacci yasami nasarar ɗaukar sa.

Washegari kiran sallar asuba a kunnen sa ya mike yashiga bayi yayi al'wala yafito da ɗan sauri ya fita dan lokacin ana kokarin tada ikama, har zai wuce yadawo kofar su Naseem ya bubbuga,

kamar a mafarkk najiyo buga kofar da ake na mirgina cikin magagin bacci na ɗan ɗaga murya nace
"Waye?."
yace "Kitashi kiyi sallah lokacin salla yayi."
tsaki naja jin muryar sa dan ni nagama mance wa ma da wani cikin gidan, najuya na gyara kwanciyata na mai da kaina na cigaba da bacci na, dan ina fashin sallah...
Bayan an idar da salla Ahmad ya iso gurin Bappa dake zaune sakiyar masallacin yana koyawa masu aiki da security karatu, shima yaɗau Kur'ani akaci gaba da yi da shi, sai da guri yayi haske sosai kafin Bappa ya tashe su, kowa yafita zuwa gurin aikin sa.
Ahmad ya gyara zaman sa yashiga gai da Bappa ya amsa kicin kula da sakin fuska sannan ya ɗaura da faɗin
"Ashe dai anan ka kwana." kai Ahmad ya sunkuyar yace "Eh." Bappa yace "Masha Allah to ya cikin gidan?."
yace "Lafiya lau alhmdllh."
ɗan shiru Ahmad yayi kansa a kasa, Bappa ko farin ciki ne fal cikin zuciyarsa da yau HAMDAH ta kasance matar aure yana da tabbacin daɗa samin nutsuwa cikin rayuwar ta, kuma yana hasashe da sa ran mijin datake aure bazai hofantar da ita ba.
Ahmad yaɗan muskuta har lau kansa a kasa yace
"Da jiya naso mutafi can gida na da ita amma sai nayi tunanin hakan ba mai yiwuwa bane."
Bappa yace
"Gaskiya kam yiwuwar hakan abune mai wuya dan nasan HAMDAH bazata yarda ba, sai dai kawai karika zuwa nan ɗin, a hankali idan ka shawo kanta sai ku koma can ɗin."
kai ya jinjina shi kansa yasan hakan shiya sa ma bai fara tinkatar ta da wannan batun ba.
ganin yayi shiru bai kuma cewa komai ba sai duba agogo yake, yasa Bappa cemasa ya tashi yaje dan ya fuskanci nauyin sa yake ji.
Bappa ya daɗa jinjina girman soyayya da aure, duba da babban mutum kamar Ahmad Tijja Sabil dayafi karfin komai sai gashi yana rusunar da kai da kuma girman sa akan mace.

A hankali nayi mika tare da yin salati na mike zaune ina mussuke ido,
kallon gefe da gefe na nayi, su Naseem sai sharar baccin su suke.
a hankali na zamo bakin gadon na mike nashiga bayi, wanka nayi sosai kana na janyo towel daga cikin towel ɗin wankan su, buɗe towel ɗin nayi ina binsa da kallo, bashida wani girma sosai kuma a hakan duk shine babba cikin sauran towel ɗin da suke jere a ma ajin su cikin bayin.
a haka na ɗaura bai karasa kai min guiwa ba rabin cinyata a buɗe yake,
nafito najima tsaye cikin ɗakin na rasa ta yanda zanyi na fita a haka, gashi ina jin alaman jini na kokarin sauko min,
da sauri na nufi kofa ina jan tsaki dan bani da yadda zanyi pat ɗina na bedroom ɗina.
a bakin kofa na tsaya ina, shiru banji alamun motsi ba, a hankali na tura kofar sai da na leka kaina ciki babu kowa cikin ɗakin,
a hankali nasa kai nashiga gaban wardrobe na isa na buɗe, pant da pat na fara cirowa ina kokarin kwance towel ɗin, naji karar buɗe kofar bayi da sauri na mai da toewl ɗin na ɗaura,

da ɗan sauri na shiga ciro kaya na na juya zan wuce sai ganin sa nayi daf da ni,
kaucewa nayi kokarin yi yataro ni da sauri ya janyo ni na fado jikin sa.
"Meye haka!?." nafaɗa da karfi ina ture sa.
a hankali yacusa fuskarsa a gefen wuya na tare da shinshinar fatar wuya na yaja
numfashi, da sauri na shiga ture kansa tare da faɗin "Wai meye haka ne kam dalla ka kyale ni."
yaciro fuskar sa sai ya sakalo hannayen sa a kuguna yace
"Tun ɗazu nake cikin bathroom nakasa yin wanka ban iya yi ni kaɗan ba sai an taya ni, muje ki tayani kinjin kyakkyawa ta."
ɓata fuska nayi nace
"Nice zan taya ka wanka? capɗi lallai bazaka yi ba, zaifi maka kayi gaggawar zuwa in da aka saba taya kan, sake ni malam."
nakarasa Maganar da buge hannunsa na juya da sauri sai ji nayi ya.......!

Mommyn Twins ce

*HMDH*

*WASA FARIN GIRKI*

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

18

Ya cafko hannu na ya janyo ni nadawo kijin sa yasa idanun sa cikin nawa yana yimin wani irin

kallo,
idanuna na rumtse da kar fi,
nayi saurin kawar da fuskata gefe,
a hankali naji hannunsa kan kafaɗa ta yana murzawa a hankali cikin kasa da murya yace
"Ban iya bafa da gaske ki taima muje ki taya ni."
idanuna na ware da sauri jin yan da yake ta faman murza kafaɗa ta yana kuma yin kasa da hannunsa, batare dana kalli in da fuskarsa yake ba na fizge hannu na da sauri na nufi kofa na buɗe nafita.
ina shiga ɗakin su Naseem na tadda sun farka nace su sauka suje Talatu tayi musu wanka, suka ce to suka sauko sukayi waje, niko bayi na wuce na
 kimsa jikina kafin na fito na saka kaya, ina yi ina jan tsaki. ko da nagama saka kayan zama nayi bakin gado sai da karfi 11 ta cika kafin na mike nafito,
ina fita daga bakin kofar parlour najiyo muryar Zulai tana sallama, na amsa nace tashigo, ta shigo ɗauke da babban tray ta gaishe ni kana ta wuce dinning ta dire tray ɗin sannan tafita.
su Naseem ne suka hauro da gudu tun daga bakin kofa suke faɗin
"Mommy wai yau ba School?."
nace "Eh babu mana da akwai da ai yanzu kuna makarantar." tsalle suka shiga yi suna faɗin
"Yee yau babu School."
baki na rike ina zama kan kujera nace "Wai murna kuke." zubewa sukayi a jikina suna dariya.
karar buɗe kofa da naji yasa ni ɗagowa, karaf muka haɗa ido san ye yake cikin kananan kaya kan nan nasa yasha gyara daga suman kansa zuwa ɗan tsiririn sajen sa sai walkiya yake, murmushi ya sakar min da sauri na kawar da kai na ina taɓe baki, a raina nace
"Ɗan rainin hankali wayace kayi wankan."
da sauri su Nasmah suka mike a jikina sukayi gunsa a guje suna daɗin
"Laa Daddy yazo." rungumo su yayi yana dariya ya karaso cikin parlour'n  kujerar da ke fuskanta ta suka zauna, suka shiga zuba masa surutun nan nasu shiko kamar kullum ya cigaba da biye musu, yayin da rabin hankalin sa ke kai na.
cikin yaran ya shafa yace "Kunyi breakfast kuwa?."
kai suka girgiza alamar a'a. duba na yayi tare da shafa nasa cikin sannan yace
"Madam a bamu abinci yunwa muke ji."
baki na murguɗa nakawar da kai na gefe.
Naseem yasalo hannun sa a wuyan sa yace
"Daddy waye zai bamu abincin?."
yace "Mommy ce." zamewa yayi a jikin sa ya dawo jikina yace "Mommy wai kibamu abinci da Daddy muna jin yunwa."
fuska na ɓata nace "Akan baka san wacce take baku abinci bane? wuce kuje gun Talatu ta baku abinci."
"Wata ce can zata basu abinci meye aikin ki da sai wani ne zai rika kula da cikin su, taho nan Naseem babu wacce zata sake baku abinci sai ita."
ya karashe maganar da mikowa Naseem hannu, sannan yaɗaura da faɗin
"Ai naɗau ka kin yi wayon sanin haka ashe dai da saura."
da sauri na dube shi a hatsale nace
"Idan ka kuma ce min bani da wayo na rantse sai na gwada maka ai kin marasa wayo."

murmushi mai sauti yayi kana yace wa yaran "Kowa yaje ya wanko hannun sa muci abincin." ai ko a guje sukayi cikin ɗakin su.
mikewa yy daga inda yake zaune ya dawo in da nake, ya zauna daf dani sosai, kokarin matsawa nayi sai jin bakinsa nayi kan kumatu na ya manna min kyakkyawar sumbata,
da sauri na kai tafin hannu na na share inda yayi min kiss ɗin ina wasa masa harara.
murmushi mai sauti ya kuma, kana yasaka tafin hannunsa ya juyo da fuskata muna fuskantar juna, ɗaya hannunsa ya saka yaja hancina yace
"Amma dai ba yanzu ba sai anjima zaki nuna min ɗin ko?, yanzu dai ki taimaka ki bamu abinci muci ba kyau horo da yunwa, kuma ban iya ci ni kaɗai ba sai an bani ko a taya ni."
fuska ta nakwace daga hannunsa na mike ina murguɗa masa baki na sauka parlour'n kasa, nace Zulai ta haɗo min breakfast, anan parlour'n kasa na karya.
a sama kuwa yaja yaran suka haura dinning sukayi breakfast ɗin.
wayar sa ce ta fara kara alamun shigowar kira koda ya duba wayar ganin mai kiran yasa shi ɗagawa da sauri fuska ɗauke da murmushi ya kai wayar kunnen sa yace
"Kawa an tashi lafiya ya kaɗaici?."
a ɓangaren Rasheedat murmushi mai sauti tayi tace "Lafiya lau Aboki ya kwanan angonci?."
dariya duk suka sakewa junan su tace
"Dama gaisuwa ce naji kwanan lafiyar ka dana kanwa ta."
yace "Mungode amma yanzu zan zo nayi miki gaisuwar kema." da sauri tace
"A'a nayafe kayi zaman ka kawai kataɓa ganin inda ango yafito a rana irin ta yau?, kada kazo ba yauba kaji Aboki?."
"To anjima?." yayi maganar kamar karamin yaro dariya tayi tace "Ba yauba."
hira sosai suka yi tayi cike da shauki sai da ta kashe wayar da kanta tace kada a shiga hakkin amarya....
Ina zaune ya sauko shi da yaran ina ganin sa na ɓata rai namike na haye sama ɗakin su Naseem na shiga na murza key nayi kwanciya ta..
ban fito ba sai wajen karfe 3 bayan nayi wanka anan bayin cikin ɗakin, ko da nafito babu kowa cikin har na wuce bedroom ɗi na, ma baya ciki nasauya kaya na sauko kasa,
ɓuruntun su Zulai da hayaniyar su najiyo a cikin kitchen, kitchen ɗin na shiga na tadda su suna ta shigar da buhuhuna da katon-katon ɗin kayan abinci dana sha.
daɗan mamaki  nakalle lodin kayan dan nidai a sanina ban sa a kawo kayan abinci ba, na dubesu sannan nace "Wanan fa waya ce a kawo su?."
Talatu tace "Wasu ne suka kawo shine Alhaji yace mu shirya shi a stor."
baki na taɓe nace "Abinci fa? yunwa nake ji."
Zulai tace "An haura muku da shi sama."
juyawa nayi nafita batare da nakuma cewa komai ba,na koma sama,
dinning na isa na zauna, nashiga buɗe kulolin abincin da a ka shirya kan dinning ɗin kana na ɗau plt na zuba abin da naga yayi min, nasoma ci a hankali ina ci ina daddanna waya ta.
tun daga step najiyo muryar sa shi da su Naseem suna haurowa, har suka karaso ban ɗago ba dan nasan tare da shi suke,
ina kallon sa ta wutsiyar ido yaja kujerar dake kusa dani ya sauna in da yaran suka zauna a sauran kujerun,
saukar hannun sa naji kan cinya ta, da sauri na ɗago sai ya kashe min ido, fuska na ɓata na kai

hannuna kan hasa ina kokarin janye shi.
sai ya juya hannun nasa yarike nawa yana ɗan murzashi nace "Sake min hannu."
fuska yaɗan marairai ce yace "Kyakkyawa ta abamu abinci muci."
da sauri cikin jin yan da yake murza hannuna cikin tafin hannun na fizge nawa na mike cikin hanzari,na wuce ɗakin su Nasmah..

Tun da na wuce ɗakin ban kuma fitowa ba sai dare shima ɗin bayan nayi wanka ne, jin shiru babu motsin shi naje na sauya kaya, daga nan na ɗibi wasu kayana na kawo su ɗaya ɗakin dake kusa dana su Nasmah.
yau kwana uku kenan bana taɓa yadda muzauna guri guda da shi, idan yana parlour'n sama to ni ina na kasa idan kuma yana kasa to ina sama, idan kuma nagaji da zaman na koma ɗaki ina shiga kuma zan murza key.
a ɓangaren Ahmad kuwa duk da hakan yana damin sa amma sai ya daure, dan ya sawa ransa zai iya juran koma mene ne daga gare ta,burin sa kawai ta soshi koda dai-dai da ɗigon irin son da yake mata ne..

Da misalin karfe 6 na yamma su Naseem suka dawo daga islamiyya, ina zaune a parlour'n sama suka shigo, da murna na rungume su ina faɗin "Har an taso?." sukace Eh. nace
"To maza kuje Talatu ta muku wanka tana kasa idan kuma sun koma side ɗin su sai ku dawo nayi muku."
suna sauka na mike ina kokarin shiga ɗaki ya shigo, da sauri na sa kai cikin ɗaki zan maida kofar yayi saurin rike kofar, yi nayi kamar ban ganshi ba na juya zan shige ciki, sai ji nayi ya rungume ni ta baya.
a sannu yajuyo ni ta gaba ya gyara rukon da yayi min da kyau.
fizge-fizge nashiga yi ina faɗin
"Ni fa bana son haka ka sake ni ina ruwan ka dani ne kam Malam."
duk fizge-fizgen da na ke yana rike da ni gam bai kuma yi magana ba sai idon na ya kura min har sai da na gaji dan kai na natsaya ina maida numfashi.
a hankali ya maso da fuskar sa daf da nawa ba zato naji bakin sa kan nawa, ido na waro ina mai mamakin hakan sai kawai jin harshen sa nayi yana yawo da shi cikin bakina.
na daddage iya karfi na ina ta kokarin kwatar kaina, amma na kasa.
da karfi na rumtsa idanuna yayin da bugun kirjina ya tsanan ta jikina ya kama ɓari, tsotsar bakina ya ke babu ko kakkautawa kamar zai cinye min baki,
zuwa can ya zare bakin sa yana mai da numfashi,yayin da ya kafe fuskata da ido, jin ya zare bakin sa yasani buɗe idanuna da sauri ina mai da numfashi, ganin irin mayataccen kallon da yake min yasani mai da idanuna narufe da karfi.
a hankali yasoma magana
"Kyakkyawa ta yau kwanana uku a gidan nan ko sau ɗaya baki taɓa bani dama na zauna inuwa ɗaya da ke ba, gashi yau zan tafi kamar yan da addini ya tsara nayi miki kwana uku, dan Allah kibani dama a gaba na nuna miki yanda nake ji a kanki, ki sani ina son ki bazai iya misalta miki yan da nake jinki a raina ba, na roke ki kibani dama a gaba."
zare jikina nayi daga nashi, bai yi yunkurin dakatar da ni ba ya sake ni, sai hannu na da ya

kama yarike gam.
yace "Akwai abin da kike bukata?."
yayi maganar cikin tausasa murya sosai.
sintar kaina nayi da girgiza masa kai, na janye hannuna da sauri dan gaba ɗaya kallon da yake min jin sa nake har cikin jiki na.
bakin gado na isa na zauna, yatako in da nake nam ma hannuna ya kuma rike wa tare da zubamin mayatattun idanuwan  nan nasa sannan ya ce
"Babu rakiya ne?." na janye hannuna nakawar da kaina ina taɓe baki batare da nace dashi komai ba.
murmushi yayi tare da faɗin
"Na barki lafiya." ya juya yafita a ɗakin.
bayan sa nabi da harara ina mai gyara kwanciya ta
"Idan katafi ka tabbata a inda zakaje dama babu wan da yayi gaiyarka a nan."
na ɗau wayata nashi latsawa...

Motar Ahmad ne ya dai-dai parking cikin parking lot ɗin gidan sa.
yafito a hankali ya nufi cikin gidan, yayin da ma'aikata keta maso shi da sauri suna mika masa gaisuwa, yarika amsasu cikin sakin fuska.
da sallama yashi ga cikin parlour'n  babu kowa ciki, direct ya wuce bedroom ɗin Rasheedat.
tana zaune gaban mirror tana shafa mai, da sauri ta juyo hangosa ta cikin mirror da tayi, ta mike da mamaki tarike baki. shiko fuskarsa ya faɗaɗa da annuri ya karaso in da take ya rungume ta.
dariya ta sake tana mai cigaba da rike haɓa tace
"Aboki me ya dawo da kai kuma?." kiss ɗin goshin ta yayi sannan yace
"Kawa tambaya kuma?."
tace "Eh kai da mukayi bazaka dawo yanzu ba."
"Yau kwanana uku fa ko kin mance ne?."
"Ban mance ba." tayi maganar tana kai hannun ta kan maɓallin rigar sa tashiga ɓalle boturar rigar nashi sannan taci gaba da faɗin
"Shine zaka dawo yau ai yayi wuri, muje dai kayi wanka tukun duk da dai nasan daga gida ka fito, amma muje ka kara kaɗe bo kurar hanya."
ta janyo hannun sa sukayi cikin bayi, sosai ta taimaka masa yayi wanka, koda suka fito ɗakin sa suka koma, in da yasauya kaya, ta fita taje ta haɗo masa abinci ta dawo tadire shi a sakiyar ɗakin, suna ci suna hira da zolayar junan su kamar yanda suka saba har suka kamala cin abincin su.
lokacin aka kira sallar magriba nan yanufi masallacin dake cikin gidan sa, bai dawo ba sai bayan sallar isha sakamakon jama'ar da suka tsaida shi. a parlour ya tadda Rasheedat ya isa ya zauna kusa da ita da sauri ta ruko hannun sa tace
"Aboki ya ka zauna kuma kai da zaka wuce kada dare yayi sosai."
yace "Ina kuma?." fuska taɗan ɓata tace
"Gidan kanwata mana, ka tashi kaje mata wata guda na baku kaje na yafe mata kwanaki 30 cur."
janyo ta jikin sa yayi yace "Naji amma ba yau ba sai gobe, yanzu kam

zo kiji wata magana."
ya janyo ta sukayi cikin bedroom ɗin sa.
yan da taga yake mata kamar zai cinye ta da baki, da nuna a hannu yake muraran sai ta sinci kanta da tunanin fa daga gurin wata matar yafito, sai kuma tayi gaggawar kawar da tunanin hakan a ranta dan bata son hakan yayi tasiri a ranta,
dan bilhakki da gaske har cikin ranta take jin duk abu guda suke da HAMDAH......!

Mommyn Twins ce

*HMDH*

*WASA FARIN GIRKI*

*NA*

*RASHEEDAT S DIRECTOR

19

Washegari da safe bayan sun karya tace masa ya tafi, yace ba yanzu ba duk yan da taso yatafi da safen yaki sai da dare yayi bayan sallar isha kafin ya tafi.
Ina zaune a parlour sai ganin sa nayi, fuska na haɗe dan sam banso ya kuma zuwa ba,da baya gidan naji sakat na kwana ɗayan nan yazo ya takura min ya hana ni sakat nida gida na.
fuskarsa ɗauke da murmushi kamar kullum ya karaso,
daf dani ya zauna har muna gogan juna, ɗan rankwafowa yayi jikina har ina iya jiyo sautin fitar

numfashin sa, ya ruko hannaye na duka biyu a sannu yashiga murza su cikin tafin hannun sa, ido yalumshi tare da buɗe wa sannan yace
"Kyakkyawa ta babu ko ɗan barka da zuwa."
gajeren tsaki na ja  ina yunkurin mike wa, sai yayi saurin sake hannuna yasaka hannayen sa duka ya zagaye ni ta baya, ya janyo ni ya daɗa mannani da jikin sa sosai, a sannu ya kawo fuskar sa daf da nawa ya haɗe goshina da nasa, yayin da numfashin mu ke garwaya dana juna, ɗina a hankali ya manna bakin sa kan lip ɗi na yayi kissing nashi,
kokarin tura harshen sa yake cikin bakina da sauri nakawar da kaina gefe.
numfashi mai karfi ya sauke tare da rumtse idanunsa da karfi yakuma buɗe wa, daɗa rungumoni sosai yayi a jikin sa kana cikin kasa da murya da tausasa shi yace
"Please HAMDAH ko sau ɗaya kibani dama kin san yan da nake ji a kan ki kuwa?, ki taimake ni son ki na shirin illatar da ni."
"Ka sake ni ni ka sake ni nace."
nafaɗa cikin ɗan gaɗa murya ina kokarin kwatar kaina.
bai sake ni ba sai idon daya kafe ni da shi kamar zai cinye ni, niko narika mutsu-mutsu da tutture shi ina cigaba da faɗin
"Ka rabu da ni dalla Malam ka sake ni bana so."
bai ce kamai ba sai idon daya cigaba da bina da shi zuwa can a hankali yasoma magana
"HAMDAH me yasa bazaki saurareni ba, baki yarda da gaske ina son ki bane ban shigo rayuwar ki dan na cutar da ke ba, son da nake miki shi yakawo ni cikin rayuwar ki, meyasa bakya sona mene ne aibu na?."
Da karfi na daddage narika ture shi ina faɗin
"Ka rabu da ni ka kyale ni bana son ka kaima zai fi maka ka daina so na."
daga saman step muryar su Naseem ke tashi yayin da suke saukowa da gudu suna faɗin
"Mommy kijo ki canja mana kallon ansa me dodo ne."
da sauri ya sake ni ganin yaran suna daf da sauko wa, suka karaso da gudu suka zube a jikinsa, da sauri na mike ina wasa masa harara haɗe da murguɗa masa baki,
murmushin nan nasa ya bini da shi sannan cikin ɗan ɗaga sauti kaɗan yace
"Kyakkyawa ta ina son ki son ki a nan ɗina yake yakuma haifu a sassan jikina, in da duk gilmawar da jinan jikina zai yi dake yake numfasawa."
ya nuna dai-dai sai saitin zuciyarsa sannan ya cigaba da faɗin
 "Bazai fita ba baku ma zan taɓa dai na sonki ba, kema kuma zaki soni."
muryar Naseem na sinkayo yana faɗin
"Daddy muma kana son mu?."
dariya yayi yana rungume su a jikin sa yace
"Kwarai ma kuwa ina son ku, kuma son ku anan ɗina yake da ilahirin jikina gaba ɗaya."
yanuna ka san zuciyarsa kasa da inda yace anan nake.
murna suka shiga yi suna faɗin
"Yee muma Daddy yana son mu."
tsaki naja najuya na nufi sama,na barsu nan zaune suna ta tikar dariya har da shi.
dogon tsaki naja ina haurawa step's
"Mutum kamar mara zuciya duk abin da zaka masa bazai taɓa jin haushi ba, kullum fuska ɗauke da murmushi kamar gonar auduga."

nakuma jan gajeren tsaki ina shigewa parlour'n sama...

Da daddare bayan sallar isha nafito daga bedroom ɗina bayan na sarkake jikina nayi wanka tare da ɗauro al'wala dan yau nagama
period, sallaya na shinfiɗa na gabatar da sallar isha ina idanrwa na mike naje na saka kaya, ina kokarin fita a ɗakin ya shigo ganin yana kokarin matsoni,na ɓata fuska tare da kaucewa nayi waje abina.
ɗakin da tun ranar da yazo na dawo kwana ciki, nashige nayi kwanciya ta ci ki.
sai da nagama danne-dannen wayata nakai wajen karfe 11 kafin bacci ya ɗauke ni...
can cikin bacci narikajin ana tattaɓa ni firget na mike zaune, ina ware idanuna, ni dana kwanta da haske sai na tsince ni cikin duhu yanzu,
hannun mutum naji yakuma mai dawa jikina yana daɗa laluma ni ai da sauri nashiga lalumo wayata, ina ɗauka nayi saurin danna shi ya bada haske, ai da sauri na duro a gadon nayi saurin kunna wutan cikin ɗakin.
yana zaune a sakiyar gadon yayin da yake ta jan numfashi da kyar cike da alamun zurfafa cikin matukar bukatuwa, zamowa yayi bakin gadon ya mike yana yunkurin maso ni da sauri na ɗaga masa hannu nashiga ja da baya ina faɗin "Me ya kuma kawo ka nan? kafita nace ka fita!."
Na karasa maganar cikin ɗan ɗaga sauti ina kuma yi masa nuni da kofa kan ya fita.
numfashi ya ja a wahalalce yace
"Kar kiyi min haka HAMDAH kar ki mance nifa mijinki ne ina da hakki a kanki, HAMDAH son ki da bukatar ki zasu iya yi min illa ki taimaka ko sau ɗaya ne ki bani dama."
da sauri na katse shi da faɗin
"Ban san wannan ba kafita kawai kar kasake ka matso ni."
"HAMDAH ki saurare ni."
"Babu abin da zanji daga gare ka fita kawai."

Kan sa ya dafe da hannaye sa duka biyu yana mai rumtse idanunsa da karfi, a hankali ya juya cikin jan kafa yafita a ɗakin.
numfashi na sauke da sauri na isa jikin kofa narufe kofar tare da murza key,
na dawo na kwanta, nakai tsawon lokaci kafin bacci yakuma ɗauka ta.
washegari bayan tafiyarsu Nasmah School ina yin breakfast na tafi sashin su Inna Wuro dan sam bana so na kasance inuwa ɗaya da shi.
a parlour na tadda su Inna Wuro da Bappa na zauna muka ta hira, daga baya Bappa ya juya hirar izuwa
nasiha, ya mai da hankalin sa sosai a kaina tare da kiran sunana ya cigaba da faɗin
"HAMDAH cikin gidan naku lafiya dai ko?."
kai na gyaɗa da faɗin
"Lafiya lau Bappa." yace "Masha Allah Allah ya daɗa dauwamar mana lafiya da kwanciyar hankali, to HAMDAH yanzu Allah ya kawo ki wani lokaci na musamman sai kin jajirce wajen gudanar da lamarin ki, Allah ya ɗaura miki wani nauyin da dole sai kin bada kulawa sosai wajen isarwa da kuma sauke wa,
kiyi kokarin sauke duk wani nauyi da hakkin daya rataya a wuyan ki,
ta nan ne kaɗai zaki da ɗa ganin falala da ci gaban rayuwa,

HAMDAH mijin ki yana da hakki mai girma a kan ki, kiyi kokari ki jajirce wajen sauke duk wani nauyin daya rataya a kanki,
ki guji duk abin da zai kaiki da halaka,
miji yana da hakki mai girma a kan matar sa kamar yadda itama take da hakki a kansa,
amma ki sani aljannar mace yana karkashin kafar mijin ta ne,
idan tayi masa biyayya ta sauke dukkan hakkokin sa, to babu makawa da yardar Allah zata shiga aljanna cikin sauki.
idan kuma ta bijire masa to tana cikin asara,
kiji tsoron Allah aduk inda kike kizamo mace ta gari in da zakiji dađi ranar gobe kiyama,
aure ba abin wasa bane darajar sa yawuci duk in da ake tunani, idan kayi wasa da shi ko ka nimi ka wulakanta shi ko ka đauke shi abin banza, hakika zaka ga rashin daidai a rayuwar ka tun anan duniya,
yan da idan kayi biyayya ka tsare dokokin sa zai kaika ga aljanna, haka zalika idan ka hofantar da shi zai jaka izuwa wuta, Allah ya tsare mu da yin abin da zai kaimu ga shiga wuta."
Inna Wuro ta amsa da
"Amen ameen ameeeeeen ya rabbil izzati."
Bappa yaci gaba da yi min nasiha mai matukar shiga jiki da tsoratar wa, ba shakka jikina yayi sanyi zuciya ta ta kariya,
lallai duk kan musulmi mai imani babu wanda zai so ganin sa cikin azabar Ubangiji.
muna nan zaune Bappa bai gushe wajen cigaba da yimin nasiha ba.
har Ahmad ya shigo shima ya zauna Bappa yaci gaba da yi mana nasihar tare, babu wariya ko nuna banbanci...
Bappa ya đau tsawon lokaci yana yi mana nasiha daga bisani ya rufe taron da addu'a.
Ahmad yayi ta masa godiya kana ya tashi ya fita.
fitar sa bada jimawa ba,
Inna Wuro ta dube ni tace natashi naje ko zai bukaci wani abu ni ina nan,
na mike jiki asanyaye tare da yiwa Bappa godiya natafi..

A parlour'n sama na tadda shi yana zaune yana waya, na wuce shi na shiga bedroom đin dana koma kwana ciki, na kwanta bakin dago jiki ba kwari dan gaba đaya jikina yagama mutuwa da wa'azin Bappa,
shiga ta bada jimawa ba ya shigo, har ya karso in da nake ban đago ba,
ya tsaya ta gurin kafafu na
"Bacci zakiyi ne?." yayi maganar idanunsa a kaina,
tsintar kaina nayi da gyađa masa kai.
kai ya jinjina yace "Kiyi bacci mai dađi ni zan fita akwai wađan da suke jira na zamu yi zama, sai na dawo."
nan ma kai na gyađa ma sa, ya juya yafita da murmushi.
ina dai kwance badan bacci ya đauke ni ba har su Nasmah suka dawo daga school..
shiko tun da yafita bai dawo ba sai daf magriba, yana shiga kuma ya ja Naseem sukayi masallaci.
sai bayan sallar isha suka dawo..

Tun daga rana mai kamar ta jiya Ahmad bai sake tinkara ta da bukatar sa ba, yakuma dai na yunkurin taɓa jiki na, zai dai zauna a inda nake yayi ta jana da hira haɗe da wasa, tun ina yin banza da shi har yakai ga nakanyi murmushi da jin wani zancen nasa.
Yau kimananin satinsa biyu kenan a gidan,duk bayan kwana biyu yakan cemin zaije ya duba Kawa, idan kuma ya dawo zai zo min da sakon cewa tana gaishe ni.

Zaune na ke a ɗaki ina jiyo muryar su a parlour shi da su Naseem kasan cewar yau weekend ne, shima babu in da ya je har yanzu wajen karfe 12 da rabi, a hankali na mike jin an fara kiraye-kirayen sallar azahar,
nashiga bayi nayi al'wala na fito,
Nasmah ce ta shigo tace
"Mommy Daddy sun tafi masallaci yace nayi salla na a gida zan sami lada da yawa da yawa kamar haka."
ta kwatanta da faɗin hannayen ta biyu,
murmushi nayi nace "To je kiyi al'walar kizo muyi sallah."
tawuce da sauri tayo al'walar tafito mukayi sallar tare.
muna idar wa tayi waje dagudu wai zataje ta duba ko su Daddy sun dawo..
na mike na ninke sallayar na kaisa ma'ajin sa, kana na koma na kwanta...
turo kofa yayi da salla na amsa batare da na ɗago ba, ya karso cikin ɗakin abakin gadon kusa da kafafu na ya zauna, a sannu ya ɗago kafafuna duka biyu ya ɗaura kan cinyar sa, a hankali yashiga matse su yana ɗan jajjan yatsun tare da ɗan tankwashe su yana cigaba da matse su a hankali.
Idanuna na lumshe tare da buɗe su batare da na yi yunkurin hanasa abin da yake yin ba.
ɗan tsuramin ido yayi a hankali yace
"Tun jiya Hajiyar mu take ta tambaya ta ke wai bazan kawo ki ki gaishe ta bane, ko yanzu tafiya ta masallaci ma sai da ta kuma kira na, ya kama muje ki gaishe ta, ko bacci kike ji abari sai kin tashi?."
kamar nace Eh amma jin ya ambaci Hajiyar mu nasan cewa mamansa ke nan yake nufi, uwa kuwa ta wuci wasa dan kullum da nawa uwar nake kwana nake tashi, kai na girgiza masa alamun ba baccin nakeji ko zanyi ba.
yace "Okay to ki shirya muje a gaishe ta."
nan ne dai ban amsa sa ba ya ɗaga kafafu na a hankali ya aje su kan katifa kana ya mike yafita.
a sannu na mike na sauko a gadon bayi na shiga nayi wanka batare da ɓata lokaci ba na fito,
na zauna gaban mirror mai da pauda da man lip kaɗai na goga, na mike na isa gaban wardrobe ɗin ɗakin naciro doguwar riga daga cikin kayana dana kawo su ɗakin,
haɗe da bra da pant da sket ƴar ciki.
ina gama sa kayan nazo gaban mirror nayi rolling ɗin gyalen doguwar rigan a kaina, na fesa turare mara karfin kamshi sosai na ɗau wayata haɗe da hand bag, nasa takalmi mai ɗan tsini ba can sosai ba nafito, jin babu motsin kowa a parlour sai na nufi kasa,
tun daga saman step's ya kafe ni da ido, a hankali nake ɗaga kafata sabo da takalmin dake kafata gudun tsamtsin step ɗin.
a hankali na sauko, nan na tadda su Nasmah cikin sabuwar shiga da alama wanka a ka sake

musu.
kai na na kawar gefe ganin yan da yake bina da kallo babu ko kifta ido, lallausar murmushi ya sake yace
"Kyakkyawa ta kinyi kyau sosai."
baki na taɓe ina mai cigaba da kawar da fuskata.
yamike ya ruko hannun su Naseem yana faɗin
"Ku taso muje ko, kada Madam ta gaji da tsayuwa."
suka nufi kofa nabiyo bayan su,
muna isa gurin motar da ɗan sauri yadawo gefen mai zaman banza ya buɗe ya dube ni sannan yace
"Madam bismilla." ba tare dana kalle sa ba na shige cikin motar, yana kokarin rufe kofar nayi hanzarin kai hannuna naja kofar da kaina na rufe.
murmushi yayi kana ya zaga ya buɗe wa su Nasmah suka shiga, sannan ya dawo gefen direba ya shiga yaja motar a hankali, mai gadi ya buɗe get yasa kai yafita a hankali...

A hankali muka haura titi in da yake tukin kamar bazai yi ba,
a bakin wani katafaren ShopRite muka tsaya, ya dube ni sannan yace
"Ko zakiyi wa Hajiya tsaraba?."
shiru nayi ban amsa shi ba sai kuma na buɗe marfin motar na fita,
shima ya fito kana ya fito da yaran ya ruko hannun su muka shiga ciki,
tarba na musamman aka yi mana cike da girmamawa a cikin gurin,
turaruka da sabulai masu kamshi da tsada na ɗiba cikin basket ɗin da na ɗauka, su Naseem kuwa suka rika jidar kayan zaki, shima yana taya su.
nazo gurin biyan kuɗi sai suka karɓi basket ɗin da sauri suka zuba kayan cikin laida, ATM nayi kokarin cirowa acikin jakata, ɗaya daga cikin masu amsar kuɗi yace
"Hajiya kibar shi." naɗago jin abin da ya faɗa lokacin su Ahmad duka karaso gurin da sauri suka karɓi basket ɗin hannun yaran suka juye kayan cikin laida, ɗaya daga cikin ma'aikatan gurin ya karɓi laidodin da sauri yayi waje nan muka bi bayan sa,ban kuma ga lokacin da ya biyasu kuɗin su ba.
acikin mota mutumin ya aje laidodin kana ya gaɗa hannu yana yi mana sallama,
ina dai-dai ta zamata cikin motar kamar ance na ɗago idanuna ya sauka can saman katafaren ShopRite ɗin,
sunan sa ne manne da manyan harufa.
baki na taɓe a raina nace
"A she dai nasa ne shiya basu amshi kuɗin ba."

a bakin get ɗin wani katafaren gida yayi hon, batare da ɓata lokaci ba a ka wangale get ɗin muka kusa cikin gidan, gida ne katon gaske wan da girman sa yakai ya kawo.
a tsakiyar gidan ya paka motar in da mutane sukayi ta zuwa suna mika masa gaisuwa ba shi kaɗai ba har da ni.
har muka fita a cikin motar muka nufi ciki mutane nata tururruwan zuwa suna kwasar gaisuwa.
wani katafaren parlour muka bayyana cikin sa, da salla na saka kafata ciki.
wasu mata ne da ƴammata ke zaune cikin parlour'n, kamar bazasu amsa sallamar ba yayin da

dukkan su hankalin su ke kan abin da suke, sai da ɗaya daga cikin su ne ta ɗago sai kuma tace
"La Ya Ahmad." sai dukan su suka ɗago suna mai amsa sallamar da faɗin
"Sannu da zuwa." wata daga cikin su ta dubi Ahmad tana wani karairaya tace
"Sannu sa zuwa Ya Ahmad."
bai amsa ta ba sai sauran da suke ta faman mika masa gaisuwa ya amsa kana yace
"Hajiya fa." da sauri wacce yaki amsa gaisuwar nata tace
"Tana ciki bari nayi mata magana."
da sauri ta wuce jim kaɗan ta fito tana girgiza kugu tace "Wai ka shigo."
hannunsa naji cikin nawa da sauri na wai ga in da yake murmushi ya sakar min yace
"Muje."
a hankali muka nufi cikin wani dogon corridor kana muka isa baki wani kofa, yayi sallama bakin kofar daga cikin ɗakin aka amsa yayi min alama da mushiga, na zame hannuna cikin nasa yafara shiga mukabi bayan sa.......!

Mommyn Twins ce

*HMDH*

*WASA FARIN GIRKI*

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

20

Nayi sallama ina kusa kaina cikin ɗakin, wata ƴar dattiju war mata ce ke hakimce a kan kujera, ta amsa sallamar tana mai faɗaɗa fuskarta da murmushi,
tace "A'a manyan ba'ki ne agidan namu? barkan ku dai sannu ku da zuwa,zo zauna nan ɗiya ta zo maza ki zauna a kusa da ni."
ta nuna min gefen kujerar da take kai na alfarma.
a hankali na karaso ina kokarin zama a kasa gefen kafafun ta tace
"A'a tashi ki zauna a sama."
kai na sunkuyar cike da jin kunyar cewa na zauna a sama in da take zaune sai na gyara zamata a kasa gefen kafafun ta ina mai cigaba da tsunkuyar da kai.
a sakiyar ɗakin ya zauna kan lafiyayyen carpet mai laushi da ɗaukar ido, in da su Naseem suka zauna a gefen sa.
a hankali cikin sunkuyar da kai nace
"Inayini Hajiya mun same ku lafiya."
fuskata ta leko tana faɗin
"Lafiya lau amarya kunzo lafiya?,
wato Ahmad sai yau yakawo min ke ko, ai ko Allah yayi albarka ace rayuwa tana yin dai-dai."
kai na daɗa sunkuyar wa ina wasa da ƴan yatsu na ina murmushi.
shima ya gaishe ta ta amsa tana mikawa su Nasmah hannu tace
"Waɗan nan kyawawan yaran sune jiko kin nawa kuzo kusa da ni, kai ma Allah ya nuna min ranar da zanga naka haka tafe da kafar su."
murmushi yayi yana amsawa da amin
Naseem ne kaɗai yaje gurin ta Nasmah kam kin zuwa tayi sai daɗa lafewa jikin sa tayi...
nan da nan ta saka aka cike mu da kayan ci da sha,
ta dube ni cikin kula tace
"Ban ga kinci wani abin kirki ba, ko da wani abin da kike bukata ne daban akaso miki?."
kai na girgiza nace "A'a waɗan nan ma sun isa nakoshi ne."
baki ta washe tace
"To madalla ai koshi shi mukafi so, ka shigo gida kamar wannan kafita bada koshi ba ai shigar batayi amfani ba."
murmushi nayi ina cigaba da wasa da yatsun hannuna.
murmushi yayi yana yimin kallon kasa-kasa.
hira sosai Hajiya tayi ta jana da shi har na ɗan fara sake wa can ya mike yana duba agogon dake ɗaure a hannunsa yace
"To Hajiya zamu koma." da sauri tace
"A'a tun yanzu? na ɗauka sai dare ai ku koma."
yace "Yaran suna da islamiyya ne ga lokacin zuwan su yayi sai ranar da babu makaranta zasu zo su wuni miki."
tace "Amma kam banji daɗi ba ace yanzu kuzo yanzu ku koma, to in za'a sake kawo min su a kawo su da wuri su wuni min."
yace "To insha Allah."
tace "Allah ya tsare min kai gaban ka da bayan ka yarabaka da sharrin makiya ya bada Sa'a."
"Amin amin." ya amsa da shi fuska ɗauke da murmushi yana kuma yi mata godiya,
Ummi na ne ta faɗo min "Hakika lallai uwa akwai daɗi Ummi na kiyi ta bina da addu'ar ki nasan

a koda yaushe shi ke sani nutsuwa." kayan tsarabar da nayi mata na ajiye mata tayi ta godiya nan ta karɓi number ta mukayi sallama, har kofan parlour ta rako mu tana ɗaga mana hannu.
muna isa gida kiran Hajiya na shigo wayata tayi min sannu da hanya nayi mata godiya.
Talatu tayi wa su Naseem shirin islamiyya suka tada daru su sam Daddy'n su ne zai kaisu ba direba ba, haka ya ɗibe su a mota ya kaisu makarantar,
ko da lokacin tashi yayi ma shi yaje ya ɗauko su....
da daddare ina kwance har bacci yafara ɗauka ta naji karar wayata, na ɗau wayar ganin mai kiran nawa sai na ɗaga da ɗan sauri nakai wayar kunne tare da yin sallama.
daga cikin wayar Hajiya tace
"HAMDAH kuna lafiya kada ace dai na tashe ki a bacci?."
murmushi nayi nace "A'a babu komai wlh lafiyar mu kalau."
tace "To madalla a gaida yaran."
nace "To mun gode sai da safe."
ina sauke wayar sai ganin mutum nayi tsaye a kaina, yaɗan tsura min ido sai kuma ya tsunkuyo kaina ya shafo gefen fuska ta, da sauri na ruko hannun sa nace "Kabar taɓa ni."
ido yakuma tsura min kana ya saki murmushi a hankali kamar maiyin raɗa yace
"Nataya ki bacci?." da sauri nace "A'a." sumbatar kumatu na yayi yami ke yana faɗin
"Kiyi bacci mai daɗi sai mun haɗu a mafarki."
baki na murguɗa lalkausan murmushi
ya sakar min ya juya yafita tare da jamin kofa...

Bayan kwana biyu yau ta kasan ce ranar asabar,
da safe ina zaune a ɗaki ya shigo cukin ɗakin cikin shiga ta alfarma yayi kyau sosai ga annurin fuskar sa da ke abaytane mai karawa fuskarsa kyau,
ya karaso ya zauna a gefe na,
plt ɗin da ke gabana mai ɗauke da kayan fruit mai sanyi ya kai hannu ya ɗau fork ɗin da nake ci da shi ya ɗiba ya kai bakin sa, ido ya numshe yana taunar sa sai kuma ya buɗe idon a kaina yace
"Kice kayan daɗi kike ci shine kika ɓoye a ɗaki kika barmu can parlour Babu ko ɗan tayin nan ma."
fuska na yamutsa a kasan raina nace
fruit ɗin ne shine kayan daɗin."
"Kayan daɗi ne mana baga shi kin ɓoye saboda kar muci ba."
ido naɗan waro dan banyi zaton maganar tawa ta fito ba sai kuma na taɓe baki.
ya ɗibo fruit ɗin ya kawo shi saitin baki na yace "Buɗe baki na sami kyakkyawa ta."
fuska na kawar ina tura baki gaba, murmushi mai sauti yayi yace
"To ni saka min gashi na buɗe baki na."
ya buɗe bakin wanda jerarrun fararen hakora sukayiwa kawanya ciki, harshe mai taushi yakara daɗa  masa kyau gwanin burge wa.
fuska na ɓata na kai hannu batare da na ɗau fork ɗin da ya ci da shi ba naɗau yankakken ayaba na kai bakina, zaman sa ya gyara da kyau ya janyo ni jikin sa, hannayen sa duka biyu ya saka ya tallafo kaina da kyau in da bazan iya kwatar kaina ba,
da sauri na rufe idanuna ganin yana kokarin jefa fitanannun idanun sa cikin nawa,

saukar lips ɗin sa naji kan nawa kafin nayi wani yunkuri sai jin ɗumin harshen sa nayi cikin bakina,
a hankali cikin wani irin salo yake juya harshen sa cikin bakina, a sannu yashiga tsotsar ayabar haɗa da harshe na, wani irin fitinannen numfashi yake fiddawa da sauri da sauri ya ɓata tsawon mintu goma a haka, sai da ya tsotsi ayabar nan ta narke duka ya shanye ta. kana
a hankali yazare bakin sa a tare muka saki numfashi dukan mu,
baya nayi na jigina  da jikin gado tare da hararan sa dan naka sa magana,
shiko murmushi yayi tare da kashe min ido yana mai jan numfashi da kyar yana mammatse fitinannun idanun sa da suka sauya kala, baki na turo gaba na kawar da kaina gefe.
 a hankali ya shafo gefen fuskata yace "Kin wa hajiya alkawarin zaki je ranar weekend sai kirana take tun sassafe."
shiru nayi ban ce komai ba, dan jiya nima ta kira ni nace mata zamuzo ranar asabar ko lahadi.
yace "Sai ki tashi ki shirya ki cika alkawarin da kika yi mata muna jiran ki a kasa."
ya mike tare da sumbatar goshina ya juya yayi waje.
numfashi na sauke a hankali na mike na faɗa bathroom.
cikin minti 25 nagama shiri nafito na same su a kasa, ban ko kalle sa ba duk da tulin kallon da yake ta aika min da murmushin sa mai bayyanar da ainahin kyan fuskarsa, nayi waje suka biyo ni yana faɗin
"Ba jira ne Madam?."
nam ma ban tanka shi ba.
har muka shige mota yanata zolaya ta da jana da wasa wani bin,
idan yayi abib dariya sai na sinci kaina da yin murmushi amma aɓoye bana bari ya gani.
a haka muka isa gidan.

Yana dai-dai ta parking ya dube ni tare da ruko hannuna ya matse cikin nashi, yaɗan rankwafo ya sauke min kiss kan kumatu sannan ya ɗago,
fuska na ɓata na turo baki gaba
murmushi yayi yaɗan ja lip ɗin na kaɗan cikin kasa da murya yace
"Idan kika turo shi gaba kyau kike karawa, kamar nayi ta tsosa."
hannun sa na bige ina murguɗa bakin
ƴar karamar dariya yayi yace
"To ai hakan ma duk kyan yake kara mi."
hannu na yarfe nace "Ni ka kyale ni."
dariya ya kuma har yana tafa hannu.
sannan yace "Ni zan juya daga nan zanje wani guri idan kun shiga kice wa Hajiya zan dawo zuwa anjima."
ban amsa shi ba nayi sauri na buɗe motar nafita, su Naseem suka biyo ni.

Da sallama nashi cikin parlour'n kamar rannan mutane ne tam ciki,
yau kam ina yin sallama suka amsa har da yi min sannu da zuwa,
wasu ƴammata guda biyu suka dube ni da murmushi suna faɗin
"Sannu da zuwa Aunty HAMDAH matar Yaya Ahmad."
da sauri sauran ƴan cikin parlour'n suka waigo, wasu na faɗin

"La itace HAMDAH mai *HAM'NAS* Co Petroleum Nigeria Limited."
wasu daga cikin su suka basu amsa da faɗin "Eh fa itace."
nan suka shiga yimin sabuwar gaisuwa.
murmushi nayi ina faɗin "Sannun ku."
wata dake gefen su tana ai kin danna waya taɗago taja dogon tsaki tamike tabar cikin parlour'n, da mamaki nabi bayan ta da kallo, inata son tuna in da na taɓa ganin ta,
cikin kankanin lokaci na tuna anan gidan na santa ranar da na fara zuwa, itace wacce ta yi mana iso gurin Hajiya.
maganar ɗaya daga cikin ƴammatan nan naji tana faɗin
"Bari nayi miki magana da Hajiya."
nace to. ta shiga jim kaɗan ta fito tace "Kishiga tana ciki."
naja hannun su Naseem..
nayi sallama bakin kofar daga ciki ta amsa a hankali na shiga ina mai kara yin wani sallamar.
tana hakimce kan wani tattausan dadduma ta kishin giɗa da wasu filulluka na alfarma.
fuska ta faɗaɗa da murmushi tace
"A'a manyan baki ne haka, sannun ku da zuwa ku karaso nan ga gurin zama."
ta nuna min gefe da ita.
na karaso na zauna tare da gaishe ta ta amsa tana washe baki da shafa kan su Nasmah.
tace "Ina shi Ahmad ɗin?."
nace "Yace nace miki zai dawo anjima yatafi wani guri ne."
kai ta jinjina ta mike zaune.
hira tari jana dashi, niko sai binta da murmushi nake wani bin kuma na amsa mata, ina mai jin nauyin ta.
har aka kira sallar azahar muna zaune tana ta jana da hira, na ɗan muskuta nace mata zanyi sallah.
tace nashi ga bayin nan cikin ɗakin,
bayan nayi al'wala na fito na tarar bata ɗakin har da su Naseem, nagabar da salla, ina zaune ina tasbihi ta shigo wata na biye da ita da tray mai dauke da kayan abinci, ta dire a gefe na sannan ta fita.
Hajiya ta zauna tana faɗin
"Yaran nan sun sami ƴan uwan su yara suna can suna ta kan wasa."
murmushi nayi nace
"Ai su Naseem akwai son wasa."
tace "Yaran kenan ai kai babba wace wasa zaka tsaya yi, ai sai dai in akwai wasan nera to kaɗai zaka tsaya kayi shi."
"Uhm." kawai nace badun da fahimci karin maganar nata na karshe ba.
tray'n abin cin ta tura min gabana tace naci.
ɗan sakurar abincin nayi dan bana jin yunwa, na tura tray'n gefe ina faɗin
"Nagode."
tace "Nayi zaton zakici da yawa dan gidan nan babu kaɗan komai mai yawa ne."
"Nakoshi ne."
nafaɗa a takaice tare da yin murmushi..

Zaman ta ta gyara da kyau kana taɗan sunkuyo in da nake a hankali ta soma magana
"Ai ita kogi bata ki yayyafi ba komi akwai ɗin ka zaka so kari, ko ba haka ba?."
kai na gyaɗa ina cigaba da murmushi bawai kodun sanin inda batun nata ya dosa ba.
baki ta kuma washewa tana mai jinjina kai kana ta daɗa gyara zaman ta
kana a hankali tace
"HAMDAH."
takira sunaan, na amsa tare da duban ta jin yanda ta kira sunan nawa a sama, tace "Kuna lafiya dai babu komai ko."
kai na gyaɗa ina mai kuma amsa sabuwar gaisuwar nata.
ta mike ta fita jim kaɗan ta dawo, ɗauke da plt ta dire a gabana,
ta ce "Ki ci wannan wata kila zai fi miki sauran." kallon plt ɗin nayi tare da yin murmushi dambun naman kaza ce a ciki sai tashi da kamshi yake,
nace "Nagode."
ɗan shiru tayi taɗan waiga gefe da gefe kamar mai duban wani abu sai kuma ta kuma mai da hankali ta kaina cikin yin kasa da murya tace
"Akwai maganar da nake so muyi yanzu mai mahimmanci ne zaɓi kuma a gare ki, moriya da amfanuwa duka."
kai na jinjina ina mai sauraren ta.
tace "Shi arziki kogini idan ka yi tsayuwan daka wajen niman sa samun sa bazai taɓa baka wuya ba,
kina da kuɗi kin san daɗin su na tabbata ayanzu irin su dubu idan zaki samu ba zaki ki son su ba."
shiru nayi ina sauraran ta cikin rashin fahimtar in da batun nata ya dosa.

a hankali ta mike ta isa can gaban gado ta ɗau Laptop saman bedside ta dawo in da nake ta zauna agefe na akasa in da nake zaune, kana ta kunnan Laptop ɗin ta daddannan sannan ta aje a gabana.
hotuna da bidiyoyin kaddarori ne suka rika bayyana ciki, manya manyan gine gine gidaje masana'antu daga nan gida Nigeria har kasashen ketare,
ido na ware ina kallon tulin tarin dukiyar, da bansan ma'anar nuna min shi da take ba.
zuwa can ta saki dariya tare da rufe Laptop ɗin tace
"Wannan kaɗan ne daga cikin dukiyar Alhaji Tijjani Sabil wan da ayan zu yazamo mallakin Ahmad Tijjani Sabil, bayan tulin dukiyar da shi kansa Ahmad ɗin ke da shi, HAMDAH."
takuma kiran suna na tana mai dubana da kyau sannan tace
"A rayuwar nan na yanzu baka da burin daya wuce kazamo abin kwatance aduk in da kake duk in da ka shiga arika nuna ka, kayi fintinkau cikin kawayen ka, misali kamar ke a yanzu da kika zamo abin faɗa,
na tabbata kina so kida ɗa fin haka,
idan kuma kinso a yanzu zaki fi hakan cikin sauki zaki daɗa mallakar dukiya mai tarin yawa, ki ɗaukaku a duniya, cikin sauki idan kina da bukata a yanzu zaki iya zamowa haka."
shiru nayi ina sauraran ta da ɗinbin mamaki cikin raina, taya za'ayi nasami wannan dukiyar datake ta misalta min shi ɗinnan? ai ko lokacin da nasami dukiya ban samu ta sauki ba sai da rayuwa ta dana ƴaƴana takusa salwanta, amma kuma take cewa zan sami ninkin ba ninki kuma

cikin sauki, to ni wace ɗaukaka kuma ɗaukakar da Allah yayi min yanzu ma na gode masa..
katse min tunani tayi da faɗin
"Kin shiga tunanin ta ya hakan zai kasance ko?."
sai ta saki wani dariya tare da cigaba da faɗin
"Cikin ruwan sanyi ma kuwa, idan kika haɗa kai dani zakiji daɗi idan kuma kika bijire zaki faɗa cikin halaka, ina nufin rayuwar ki zata salwanta."
ido na waro da sauri na ɗago na dube ta,
wani irin hatsabibin murmushi ta sake kana ta girgiza kai tace
"Kwarai kuwa,
kin auri Ahmad bawai dun kina son sa ba sai dun son da shi yake miki, nasami labari sosai kan cewa bakya son shi kuma ina da tabbacin cewa har yau ba son na shi kike ba,
me zai hana muhaɗa karfi da karfe kibi ta wannan hanyar kici moriyar dukiya mai tarin yawa, ki kara kan naki, ki daɗa zamowa abin kwatance a duk faɗin kasar nan da ketare baki ɗaya."

Zuwa yanzu maganar nata yafara jefari cikin firgici da tsoro dan na rasa me take nufi dahar zata yi min barazana da salwanta rayuwa ta.
ɓari jikina ya soma a raina nake faɗin
"Innalillahi'wa'inna'ilaihirraju'un,abin da nayi gudu shiyake kuma tunkaro ni."
maganar ta najiyo tana faɗin
"Zaɓi yarage naki idan kin so a yau zaki iya aiwatar da komai."
ta mike tsaye taje taja drower har ta dawo ta zauna in da ta tashi kaina na sunkuye, yayin da firgici mai tsanani ya shige ni, sai nanata kalmar
Innalillahi'wa'inna'ilaihirraji'un nake.
"Ungo karɓi rike wannan." da sauri na ɗago ina duban abin da take mika min ɗin
wani kullin magani ne cikin laida, hannu na na ɓari na karɓa tare da kura masa ido.
tace "Wannan maganin shine hanya mafi sauki da zakibi ki mallaki dukiya mai yawa ki kara kan naki,
ki zuba wa Ahmad a cikin abinci ko sha, idan yaci zai kwanta jinya kada kiji tsoro dan ko likitoci bazasu taɓa gane wani abu yaci ba, kuma baza'a taɓa gane ciwon me yake damin sa ba a haka zai tafi daga nan kuma zance ya kare, zamu raba dukiyar biyu ki ɗauki rabi na ɗau rabi, tun rabar dana sami labarin auren ku na kasance cikin farin ciki dan na tabbatar zaki iya aiwatar wa tun da ba son shi kike ba."
wani irin ɓari hannuna da ilahirin jikina suka ɗauka cikin tsananin mamaki tashin hankali na ɗago na dube ta murya na rawa nace
"Kashe shi za'ayi." wani irin kafurin dariya tayi tace
"Kwarai kuwa nasan aiwatar da hakan bazai baki wuya ba tun da bason shi kike ba, ko da ace kina son shin ma so ɗin banza kuɗi ai yafi miki shi, yana mutuwa kuma zaki sami wanda yafi shi."
gaba ɗaya ƙwaƙwalwa ta ya tsaya cak ya daina ai ki firgici da tashin hankali su suka dabaibaye ni,
ta ko ina ɓari yake a jiki na.
kisa nice zan kashe mutum da hannuna wai uwa ce ke son gusar da ɗan ta anya ba mafarki nake ba?, da sauri na mussuke idanuna ina mai ware su a kanta maganar ta na natsinkayo a

sama
"Kada ki ɓata min shiri yin hakan babban kuskure ne, na tabbatar miki rayuwar ki dana ƴaƴan ki zasu salwanta,
kiyi tunani ki dubi tulin tarin dukiyar nan ace sudaɗa zamowa mallakin ki ki zamo abin nuni da faɗa a duniya, ba pillow zaki danne kansa da shi ba ba kuma wuka zaki daɓa masa aciki ba, wannan kaɗai zaki zuba masa cikin abinci daga nan shike nan arziki ya dawo naki."
hannuna mai maganin ta rike ta kalle ni tana dunkule min maganin cikin hannuna, cike da karfafa guiwa ta cigaba da faɗin
"Kada kiji tsoron komai ko ki tsaya tunani ki rika tuna tulin tarin dukiyar nan ki ai watar kada kiji komai babu wan da zai zarge ki dan babu ta in da za'ayi a gane, kuɗi yafi komai a rayuwa."
maganin ta karɓa a hannuna taɗau jakata ta jefa shi ciki tarufe tana faɗin
"Ki kula kada a sami matsala faruwan hakan babban matsala ce ga rayuwar ki."
kai na girgiza da sauri, murmushi tayi zata kuma magana akayi sallama daga bakin kofa, zaman ta ta gyara da sauri taɗan matsa gefe,

Ahmad ne rike da su Naseem a hannun sa suka karaso suka zauna,
fuska ta faɗaɗa da murmushi tadubi Ahmad tana faɗin
"Sannu Ahmadu numfashin Sabil an dawo."
yace "Eh Hajiya bar ka da gida."
tace "Yauwa Ahmad Allah yayi albarka ya tsare gaban ka da bayan ka."
"Amn amin." ya amsa yana mai murmushi. ya mike ya dube ni sannan yace
"Muje ko yau kinyi wa Hajiya wuni."
da sauri tace "A'a kam sai dai rabin wuni dai, tamayi kokari a hakan dan tafi wancan Rasheedat ɗin mai isa da kafafa."
murmushi kawai yayi, yayi waje tare da ɗaga kiran da ya shigo wayar sa yanzu.
jiki a sanyaye na mike, itama ta mike tare da ɗaukar jakata ta mika min sannan ta dube ni da kyau tace
"Ki kula ki ai watar da komai ya tafi dai-dai kada a sami wata matsala, ni zan kula da komai daga baya, ki kawar da abin da bakya so ki kuma sami karin dukiya mai yawa, ki ɗaukaka a duniya, kada kiji komai zan tsaya miki."
ta dafa kafaɗa ta tana mai kuma jaddada min.
yau ma har kofar parlour ta yi min rakiya tana,
ina dai-dai zama ta cikin motar na sauke numfashi da karfi har sai da ya juyo ya kalle ni.
a hankali na maida baya na na jingina da jikin kujerar motar, gaba ɗaya jiki na ya gama sanyi.
gefen da nake ya waigo ya dube ni kana ya mai da duban sa kan titi yace
"Madam ya dai?."
idanuna na lumshe batare da na amsa shi ba..
har muka isa gida idanuna a lumshe yake yana gyara parking najiyo Muryar sa daf da ni yana faɗin
"Ko na ɗauke ki nashi da ke ne?, naga kamar kin gaji."
a hankali na buɗe idanuna na jiki a sanyaye kai hannu na buɗe marfin motar nafita..

Ina shiga bedroom na wuce bathroom da sauri na shiga tube kayan jiki na dan gaba ɗaya wani irin a zabebben  zafi nake ji, tun daga ta ciki na har waje.
na daɗe cikin ruwan sanyi kafin na fito, duguwar riga mara nauyi na zura a jiki na batare da pant ko bra ba,
na zauna bakin gado yayin da maganar Hajiya ke tayi min yawo cikin kwakwalwa.
jakata na ɗago na buɗe na ciro maganin ina juyashi a hannuna yayin da bugun zuciya ta ta karo.
"Innalillihi'wa'inna'ilaihirraju'un, me yamata haka take son kashe shi? sabo da kuɗi?, kuɗin da zaka mutu ka barshi meye haka da tsanani ɗanka ka kashe shi da kanka sabo da son abin duniyar da zaka mutu ka barshi,
ba zan iya kashe mutum ba ba zan taɓa zamo sanadin wata raiba, da ma nasan babu komai cikin rayuwar aure face kunci da bakin ciki,
gani na kuma faɗa wa cikin wani ahalin da suke son ganin bayan junan su, meye nawa da zasu so jefani ciki dama ni na sani a haka rayuwa ta zata kare."
wani irin kuka ne mai matukar tsuma rai ya kwace min, sai na toshe baki na nashiga rusar kukan.
 a hankali aka turo kofa, da sauri na dunkule hannuna mai rike da  maganin nayi baya da shi da sauri na ɓoye shi a bayana,
ɗaya hannuna dana toshe baki na nashare hawaye na da sauri na haɗiye kukan.
a sannu yakaraso cikin ɗakin, ban yadda mun haɗa ido da shiba kaina a kasa, na ɓata fuska.
a gefe na ya zauna muna fuskantar juna.
ya ɗan tsunkuyo tare da leko fuskata yace
"Kyakkyawa ta bacci kike azaune ne?."
baki na turo gaba, yayi murmushi tare da faɗin
"Ashe dai idanun ki biyu."
hawayen da nake ta makewa ne suka gangaro, ido ya tsura min na ɗan wani lokaci batare da yayi magana ba, yayin da hawayen suka ci gaba da gudu babu ko kakkautawa.
da karfi yaja numfashi tare da furzar da iska mai zafi daga bakin sa, hankali tashe yashiga girgiza ni da faɗin
"HAMDAH me ya faru me ya same ki!?."
cikin muryar kuka nashiga faɗin
"Nace bazanyi aure ba arabu da ni a ka matsa min dole sai da nayi shi, bayan na riga da na sani babu komai cikin sa sai zallar kunci da tashin hankali,
me yasa kuke da son kan kune? me yasa kuke son ganin bayan rayuwa ta?,me nayi muku? ni banyi muku komai ba hatta ƴaƴan da suke ciki basu san komai ba basu ɗau alhakin kowa ba sai da aka zalunci su, har sun fito duniyar ma baza a barsu su huta ba?, me muka yi muku me muka tsare muku!?."
kuka ne sosai ya kwace min nashiga rera shi.
ido ya tsura min yayin da kamannin sa ya sauya gaba ɗaya fuskarsa ya rikiɗe daga nashi na kullum mai fidda annuri da fara'a, ya koma izu fuskar fusatattaun maza.
ya janyo ni jikin sa ya rungume ni da kafi kamar zai ɓalla ni,
da karfi-karfi yake sauke numfashi yayin da kirjinsa yake bugawa da karfi har ina iya jiyo sautin sa, kasan cewar kai na yana cikin kirjin nasa. zuwa ƴan wasu mintuna,

sai yashiga sassauta rukon da yayi min ɗin, yayin numfashin sa ya dai-dai ta, a hankali yashi ga shafa kaina yana ɗan bubbuga baya na. a hankali yasoma magana sai dai sautin maganar nasa yana fita da amon sauti mai ɗan kara,
"Idan har ina numfashi nayi miki alkawarin babu mai kuma saki kuka,bare har su taɓa bayin Allahn da basu taɓa aikata zunubi ba,
zan zame muku garkuwa da yardar Allah."
shiru ya ɗan yi sai kuma ya saki murmushi mai sauti, ya leko fuskata dake cikin kirjin sa sannan yace
"Ke da aka baki kwangila madadin ki ai watar sai ki zauna yin kuka."
wani irin rasss gaban kirji na ya yanke, me yake nufi kada ace dai ya gane abin da Hajiya ta bani na aiwatar a kansa..
maganar sa ce ta katse min tunani
"Tana mance wa da cewa Allah shike da ikon rayawa da kuma kashe wa, waɗan da tayi sanadiyyar kashe su ma Allah ne ya nufa kuma lokacin su ne yayi, bata da ikon kashewa a hannun ta Allah shi kaɗai yake da iko."
zuwa yanzu kam numfashi na ne ya so ɗauke wa, da sauri na ciro kai na a kirjin sa tare da zuba masa ido.
hannun sa ya mika ta baya na ya ruko hannuna dake rike da maganin dana ɓoye shi ta baya na,
ya buɗe tafin hannuna yaciro magani, ya dago shi yana jujjuyawa a hannunsa sai kuma ya saki murmushi mai sauti idanun sa cikin nawa yace
"Yaushe ne zaki saka min shi cikin abincin?, amma dai yau da hannun ki zaki girka min mai daɗi ko?."
ya karasa maganar da ɗaga min gira.
Idanuna na rumtse da kafi nakuma buɗe wa a kansa
kai ya langwaɓar gefe yace
"Kin gani ko kiyayyar da kike yi min har ta bata kofar son cimma burin wasu,
Hajiya Karima
ta yi sanadiyyar mutuwar Baba na, sabo da son abin duniya,tasa aka kwance masa tayar mota ta sanadiyyar haka yayi hatsari a take yarasa rayuwar, bayan rasuwar sa da kwana uku, mahaifiya ta tajisu suna maganar da waɗan da ta sasu suka ai watar da haka, ta sanadiyyar haka mahaifiyata ta kamu da ciwon zuciya sabo da bata da hujjar da zata kawo damin a kama Hajiya Karima da waɗan da tasa sukayi mata aiki, tayi ta fama da ciwon bada jimawa ba itama ta rasu da bakin cikin abin da Hajiya Karima ta ai kata,
tun daga lokacin ta fara sarkafar rayuwa ta dan a cewar ta sai ta gusar da ni kafin ta samu mallakar dukiyar mahaifina duka har ma da nawa,
tun bayan rasuwar mahaiyata ta mallake gidan mu ita da ƴan uwan ta, duk waɗan nan mutanen da kika gani cikin gidan mu ƴan uwan ta ne,
tabi ta hanyoyi da dama bata sami cimma burin ta a kaina ba, sai ta turo ɗiyar ɗan uwan ta wacce dama tun mahaifana na da rai taso haɗa ni da ita, idan baki mance ba yarin yar da ta gaishe ni ban amsa gaisuwar ta ba, ranar da muka fara zuwa gidan da ke, sai naki amin ta, da gaske Sakeenat tana sona, bata kuma yarda da muradin Hajiya na bayan munyi aure ta gusar da ni ba, da kanta ta faɗa min takuma bani tabbacin bazata iya kashe ni ba dan tana

sona,
na kore ta na mata kaca-kaca nace kuma kada ta sake kawo min kwatankwacin irin wannan maganar tayi wa Hajiya sharri ne,
nasan komai nakuma ki nuna mata cewa na sani tun ranar da mahaifina ya rasu nasan dukkanin shirin ta, har kuma rana mai kamar ta yau a tafin hannuna take komai."

Ɗan sakaita maganar yayi tare da jan numfashi sannan ya cigaba da faɗin
"Sai gashi yau tabiyo ta hannun ki da tabbacin ke zaki iya sabo da labarin data samu na bakya so na."
ido na zuba masa ciki matukar tausaya wa hakika labarin ya jijjiga ni yakuma bani matukar tausayi, duk da sanin shirin nata amma yake tare da ita yake yi mata kallon uwa da har nayi tunanin ita mahaiyar sa ce,
me yasa ya barta take rayuwa bai ɗauki mataki a kanta ba, bawai kuma dan bazai iya ba, duk tulin tarin hujjujin da ya ke da su ɗin na.......!

Mommyn Twins ce

*HMDH*

*WASA FARIN GIRKI*

*NA*
*RASHEEDAT S DIRECTOR*

Kallon sa nake cikin matukar tausaya wa, tabbas rayuwar sa abin a tauya ne, yana ji yana gani ake niman hallaka rayuwar sa, kuma a haka yake rayuwar sa tamkar bayi da wasa matsala, kullum fuskarsa ɗauke da farin ciki kullum acikin dariya da fara'a yake, ikon Allah to shi wannan wani irin mutum ne haka?.
hawaye ni naji sun zube min jikina yayi sanyi na mugun tausaya wa rayuwar sa da yake cikin hatsari.
magana ya cigaba da yi
"Ta nimi Rasheedat da kusan irin haka sai dai ita bata kaiga bata magani ba, kasan cewar Rasheedat a gidan mu ta tashi tasan dukkan halin ta, tun da ta fara faɗa mata wasu maganganun da basu ɗauke ta ba, sai ta yi saurin bijire mata, shike nan tun daga ranar ta ɗau ki tsana ta kuma ɗaura mata, dan dama sam bata son auren mu da ita tun da naki amin cewa da auren ɗiyar kanin ta, ako da yaushe cewa take wai tayi mata rashin kunya."

Numfashi na sauke nakai hannu nashare ɗan guntun kwallar da ya zubo min a hankali nace
"Shine kake cin abincin ta baka jin tsoron ta zuba maka maganin ciki?."
murmushi yayi tare da jan kumatu na yace
"Kina ji min tsoro ne kyakkyawa ta?."
ido na lumshe tare da kuma buɗe wa.
numfashi yaɗan sauke sannan yace
"Bazata taɓa gangancin yunkurin yin hakan ba, dan ita a karamin tunanin ta idan ta yi haka za'a iya zargin ta, shiyasa bata taɓa yunkurin kwatanta hakan ba, sai dai tasa ayi,
kada kiji tsoron ta idan ta gane kinji tsoron barazanar da ta miki, zata kuma samin da mar cigaba da yi miki barazana, idan ta kuma tarar ki da maganar kice ta sallawantar da rayuwar naku in zata iya,
zata kuma yi miki barazanar da zai firgita ki kada kiji tsoro dan  babu abin da zata iya."
kai na girgiza jiki a sanyaye, janyo ni jikin sa yayi tare da sakin ƴar karamar dariya yaleko fuskata sai ya kuma sakin murmushi mai sauti cikin yanayin sa na zolaya yace
"Har yanzu wayo da saura tukun ayi maka tayin dukiya mai yawa kaki karɓa."
baki na turo gaba tare da janye jikina daga nashi ina ai ka masa da harara, nayi yunkurin mike wa.
ya mai dani jikin sa yana dariya kasa-kasa.. yana yin sa yana bani mamaki shi da yakamata yayi zaman kunci amma ko da yaushe yana cikin walwala...

After 2 week

Hakan yayi dai-dai da watan Ahmad guda a gidan nan, a daren jiya ya koma gidan sa, tare da

su Naseem ya tafi kasan cewar daren weekend ne jiya. zuwa yanzu nakan ɗan sake masa har idan ya na yimin hira nakan ɗan rika amsa masa, duk sona dana rika share sa amma sai yasan hanyar da yabi yasa na kula shi, Ahmad mutun ne mai saukin kai, yana da faram-faram da son yawan fara'a da zolaya bashi da ɗaure wan kai ko kaɗan.👌🏻

Zaune nake a ɗaki kiran Bappa yashigo waya ta, ko da na ɗaga yace idan ba abin da nake nazo nace to.
a hankali nafita, shiru parlour babu motsin kowa, daga jiya zuwa yau side ɗin yadawo wani shiru haka  babu hayaniyar su.
na wuce sashin su Bappa bayan mun gaisa Bappa ya ɗaura da faɗin
"Jiya nasami kira daga jagororin da a ka ɗaura kan kula da ma'aikatan mulmula karfe daga Lagos, abun farin ciki suke shaida min an kammala ginin yau kuma da yardar Allah jirgi zata iso da kayan aiki."
baki na washe cike da farin ciki nace
"Masha Allah Allah abin godiya."
 Bappa yace "Kwarai kuwa, yanzu in da a ce so shine samu ya ace jibi muna can a sauke kayan a gaban mu,
yanzu sai ki nimi izinin zuwa a gurin mijin ki idan ya barki jibin sai mu je, gobe sai aje a biya kuɗin jirgi idan Allah yakai mu jibi da safe sai mu ɗaga."
"Izinin miji sabon salo lallai ma."
nayi maganar a kasan raina
maganar sa na jiyo yana faɗin
"Idan bai barki ba kada ki matsanta ni zan tafi, duk randa Allah yasa ya bari kije sai kije daga baya."
da sauri nace
"Bappa sai ya bari ai dai yasan irin harkoki na kuma dan shi ai baza a fasa zuwa ba."
"Akul ɗin ki kada na sake jin wannan maganar yafito daga bakin ki, idan yasan harkokin ki ai da da yanzu ba ɗaya bane, kuma ba'ayi yarjejeniya dashi kan zaki iya tafi gurin harkokin ki a duk sanda bukatar hakan ta taso ba,
kin san girman aure kuwa? to kada ki kuskura kiyi wasa da shi, ko nan da kofar gida kika leka har idan bada izinin sa ba sai mala'ikan Allah sun tsine miki, aure ba abun wasa bane HAMDAH yazama dole ki nimi izinin sa a duk sanda fita ya kamaki, bijere wa  hakan saɓawa dokar Allah ne, ki tambaye sa idan ya barki sai kije, kada ki kuskura ki tafi bada izinin sa ba, kinji ko?."
kai na gyaɗa, yace
"Yauwa Allah yayi albarka ki tashi kije idan ya barki sai mu tafi jibin."
nace to na mike na fita, ina tafiya ina magana
"Wai shi miji in za'a fita wai sai an tambaye shi."
na kaɗa harshe tare da yin kwafa..
ina shiga side ɗina na tadda su Talatu sun shigo yin aikin su na zauna nan parlour'n kasa suna aikin muna ɗan taɓa hira....

Washegari da yamma lis su Ahmad suka dawo, su Naseem suka yi ta cike ni da surutu da labaran abunuwan da sukayi aka kuma yi musu,
cike da kewar su narika biye musu ina dariya, suka rika bani labarin wai ɗayan Mamyn su tayi musu kaza wai ɗaya Mamyn su na ɗaya gidan Daddyn su har goyon su take.
ni dai sai binsu da dariya neke...
da daddare bayan sallar isha ina zaune bakin gado Ahmad ya shigo da sallama,
na ɗago na amsa masa sallamar tare da mai da kai na kan wayar dake rike a hannuna.
ya karaso cikin ɗakin a gefe na ya zauna, ya leko fuska ta yace
"Kyakkyawa babu ko ɗan barka da zuwan nan ne?."
baki na cuno gaba, murmushi yayi yace
"Yaushe ne zaki fara yin murna da gani na?."
baki na murguɗa ina kokarin kawar da fuska ta yiyi saurin juyo fuskar tawa ya sauke min kyakkyawar sumba kan lip, ya ɗan lumshe ido tare da buɗe su a kaina a hankali yace
"Suna da kyau da daɗin tsotsa."
yayi maganar da ɗaura hannu kan lips ɗi na,
hannun sa na bige ina cuno bakin gaba.
murmushi yayi mai sauti.
mike wa yayi zai fita har yakai bakin kofa naɗan kalle sa nace
"Bappa yace na faɗa maka zamuje Lagos jibi."
nayi maganar a takaice ina janje idona daga gare shi.
a hankali ya juyo daga in da yake tsaye yace
"Ayya Bappa Malam Allah ya tsare masa hanya."
a hatsale nace "Har da ni zamu tafi."
ido yaɗan waro yace "Wa har da ke ina ban amince ba bazaki jeba."
a hatsale na dube sa nace
"Bazan je ba? ka faɗi son ranka kasan dai da harkokina ka same ni tafiya kuma ba bashi."
murmushi yayi tare da faɗin
"Bazaki je ba haka na ce, shi harkokin naki sai na datse su a yau, duk ranar da kikayi wayon sanin iya tambaya ta da kanki ba basai an sa ki, ki tambaye ni ba wata kila na barki kije."
yana kaiwa nan ya juya yayi waje.

Wani shekeke nabi bayan sa da kallo abin ya ban haushi, wai nice yau zanje wani guri nake tambayar wani har yake ikirarin cewa bazani ba.
a fili nace "Idan nazo tafiya ka janyo ni na fito cikin jirgin dan kasamu ma na tambaye kan idan badun Bappa ba babu abin da zaisa na tambaye ka."
naja gajeren tsaki tare dayin kwafa.
washegari da safe Bappa ya kirani yace za'a je yin bukin na jirgi shin na tambaya an barni.
jin nayi shiru yasa Bappa faɗin
"Idan kin san ba'a barki ba kada ki yi gigin tafiya gashin kanki, ki hakura kawai."
a hankali nace "Bappa zai bari ma."
na kasha wayar da sauri na mike na fita na nufi kofar bedroom ɗina, har na ɗaura hannu kan handle sai kuma na tsaya, wai wannan mutumin me yake ɗaukar kansa ne na rantse sai na

zana masa iyakar sa idan ba haka ba shi har wani ji yake wai shi miji ne.
da karfi na murɗa handle ɗin natura kofar da karfi,
yana kwance a kan gado, yana kwance babu riga a jikin sa ya rufe jikin sa da blanket daga kafafun sa zuwa cikin sa idanunsa a lumshe da alama bacci yake,
na karaso bakin gadon na tsaya tare da rike kugu.
nasoma magana a hatsale cikin ɗan ɗaga sauti
"Wai na ce zan tafi kana gwada min bazani ba a wani dalili?, kada kaga ina tambayar ka,  karika son gwada min wani bushashen iko, narantse badun Bappa ya matsa min da sai na tambaye ka ba da ba abin da zai sa na tambaye ka, kuma yan zu ma tafiya ta zanyi ko ka bari ko baka bari."
duk maganar da nake idanunsa a rufe  hannu na mike da zummar bubbuga shi ya tashi  yaji matsaya ta, sai ji nayi ya fisgoni nafa faɗo jikin sa,
blanket ɗin jikin sa ya zare, babu komai jikin sa sai boxes, kokarin yunkurawa nake sai ya janyo ni ya haɗe ni da jikin sa, wani irin shack naji lokacin da na jini cikin fatar jikin sa, yayin da ɗumin jikin sa ya ziyar ci ilahirin jiki na.
ya saka hannayen sa gaba ɗaya ya zagaye ni da shi babu ta in da zanyi na kwace kaina.
a hankali ya buɗe idanun sa ya zuba su cikin nawa, numfashi ya sauke a hankali ya soma magana
"Yau she ne tafiyar naku?."
da sauri nace "Gobe."  yace
"Allah ya kai mu kicewa Bappa na amince kuma nima zan faɗa masa dan kar yayi zaton kin faɗa ne kawai, hakan yayi miki?."
a hankali cikin sanyin jiki da jin yan da ya amsa min duk da yan da nayi ta masa maganar a tsaye, sai na gyaɗa masa sai.
murmushi ya sakar min yace
"To Allah ya kaimu goben." a kasan raina na amsa da amin, idanunsa ya lumshe a hankali ya buɗe su, a sannu ya sauke bakin sa kan goshi na ya manna mishi kiss,
a hankali ya shiga yawo da hannunsa a bayana, jin abun nasa yana kokarin zarce iyaka, sai nayi huff zan mike na kasa sai na shiga ture sa ina faɗin
"Sake ni ka dai na bana so."
yace "Ina bacci na kika zo kika tada ni, alhalin ke ba tayani baccin zakiyi ba, da kyar na samu wannan baccin ya ɗau keni shine zaki ɓata min shi, to ai biya na zakiyi ɗumi zaki bani zan iya komawa baccin wata kila, idan kuma ban koma ba to sai kin bani asalin ɗimin, dan bazaki ɓata min bacci kitafi ba."
yana karasa maganar ya zuge zip ɗin riga ta har kasa ya raba shi da mahaɗin sa, ido na waro jin yana kokarin rabani da rigar, kafin nayi auni ya zare ta a jikina, wani irin nannauyan numfashi ya sauke,
ido ya kurawa fararen nonuwa na da suke cikin bra, numfashi ya fizga da kyar,
da sauri ya haɗe kirji na da nashi tsam ya rungume ni.
niko turesa na cigaba da yi ina fadin ya sake ni, bai kula ni sai da muka kai tsawon minti 20 a haka,
kafin yashiga sassauta min rukon da yayi min, yayin da gudun  numfashin sa yakaru.
da sauri na janje jikina na duro a gadon ban ko tsaya ɗaukar rigata ba nayi waje, sai da na koma ɗaya ɗakin kafin na sauya kaya....

Washegari da misalin karfe 9 muka fito parking lot, Inna Wuro da ma'aikatan gidan suna ta yi mana Allah ya tsare,
Ahmad da Bappa tuni sun shige cikin mota dan shi zai kaimu airport na isa jikin motar na buɗe gefen mai zaman banza na shiga, yaja motar suna ɗaga mana hannu muka fita,
dashi da Bappa sunata hira yayin da yake ta bina da kallon kasan ido, baki na murgaɗa masa na kawar da kaina.
har muka isa airport bai fasa bina da kallon ba.
yana dai-dai parking Bappa ya fita ina kokarin buɗe motar naji hannun sa kan cinya ta, yashiga murza shi da sauri na juyo muka haɗa ido, a hankali yace
"Zanyi missing ɗin ki." kai kawai na kawar na buɗe motar na fita.
bai bar airport ɗin ba sai da jirgin mu ya tashi..
ko da ya koma gida jiran lokacin tashin su Nasmah yayi daga school lokaci nayi yaje ya ɗauko su yawuce da su can gidan sa...

Ranar da muka isa Lagos washegari aka shiga da kayan aiki cikin katafaren Company, aka shirya komai a ma'ajin sa, aka rufe Company sai an ɗibi ma'aikata kafin ayi bikin buɗe Company.
Kwanan mu uku a Lagos muka juya Abuja.
ko da muka iso nayi mamakin ganin sa a airport ya kwashe mu yayi da mu gida.
muna isa gida baccin gajiya na kwanta dan tun da muka tafi ban sami nayi baccin kirki ba.
sai yamma lis na farka,
na faɗa bayi nayi wanka nafito naci abincin da naga an shirya saman dinning, nayi ta zuba idon gani su Naseem sun shigo shiru,
na mike na sauka kasa  Talatu na tarar a kitchen tana gani na ta kara yimin gaisuwar yaya gajiya,
na amsa nace
"Su Naseem fa basu dawo bane?."
tace "Eh gaskiya ban gansu ba naga Alhaji ya shigo amma ban da su ina ga bai dawo da su bane."
ban kuma cewa komai ba na juya na koma sama, zuwa yanzu kam ina so na gansu duk da kullum sai munyi waya da su ta wayar Ahmad a rana fin sau biyar.
bayan sallar isha ina idar da sallar na shiga bayi wanka na kuma  nafito ɗaure da towel,
turus na ja natsaya ganinsa zaune a bakin gado, fuska na ɓata na karaso cikin ɗakin ina ɗan jajjan towel ɗin kasa dan rabin cinya ta ya tsaya.
ido ya zuba min babu ko kiftawa.
tsayuwa nayi a tsakiyar ɗakin na ɗan dube sa nace
"Ka fita zan sa kaya."
ido yakanne yace "Ɓoye min halal ɗi na za'ayi, to shike nan bari na rufa idanuna kisa kayan ki."
ya kai hannunsa duka biyu ya rufe fuskarsa yana faɗin
"Narufe kisaka." ɗan guntun tsaki naja na isa in da hijabin salla na yake na ɗauka ina kokarin

saka sai ji naya an fizge,
da sauri na waigo nace "Meye haka? ka bani hijabi nasa."
cilla hijabin gefe yayi yadaɗa matsowa daf dani sosai har muna gogan juna, a hankali ya sauke hannunsa kan kafaɗa ta yashiga murza shi a hankali, yace
"Me yasa zaki cigaba da sanya masa hijabi a sakanin mu, kyakkyawa ta bakya tausayi na ne? a koda yaushe zaman jiran ranar da zaki juyo gare ni nake, sam bana so nayi miki dole, har yaushe zamucigaba da irin wannan zamar, kin san daya nake iya bacci da ciwon sonki da bukatar ki,
shin kin mance ina da hakki a kanki ne, bakya tsoron Allah ya tambaye ki kan hakki na?."
da sauri na kai hannuna kan nashi jin yana gangaro da hannun izuwa saman kirji na, na janye hannun shi ina faɗin
"Wani hakkin ban san shi ba."
murmushi ya sake yace "Dagaske to bari na nuna miki."
cak ya ɗago ni yadire ni kan gado shima ya hau ido na rumtse da karfi jin ya sauke hannunsa kan kirji na yana kokarin kwance towel ɗin da ke jiki na.
da karfi na rirrike hannunsa nace
"Kada ka kunce na rantse idan ka kunce..."
cak na haɗiya ragowar maganar tawa jin ya..........!

Mommyn Twins ce

22

Ya fizge towel ɗin gaba ɗaya yayi cilli da shi gefe, ido na rumtss da karfi tare da dukunkunewa guri guda na saki kuka ina faɗin
"Na rantse kayi gaggawar mai damin towel ɗin nan jikina, wlh idan ba haka ba sai na yi maka abin da baka sammani."

ido ya kafe ni da shi babu ko kiftawa yayin da ilahirin jikin sa ya ɗauki ɓari, wani irin muguwar sha'awa bukata so kauna begen kasantuwa su suka dirar masa suka cushe masa cikin kwanya. numfashi ya ja da kyar hannunsa na rawa yakai jiki na yashiga shafa ni, daɗa dukun kunewa nayi cikin muryar kuka nace
"Ka daina taɓa ni."
a hankali yaɗan rankwafo zuwa fuskata murya cike da ɗin bin fitina da wutar jarabar dake azalzalar sa yace
"Kyakkyawa ta kiyi hakuri, bazan kusan ceki ba harsai da amincewar ki, idan kin amin ta da ni kin shirya karɓar bakwanci na,na gabatar da kaina a gare ki,
amma ki sani nakai matakin da zan iya samin mummunar illa."
numfashi yakuma ja da kyar yaci gaba da faɗin
"Ina da hakki a kanki kada ki mance girman sa, bakuma zan matsa miki dole a kan sa ba son da nake miki bazai barni nayi miki dole a kan abu ba, ina son ki kuma da sonki zan mutu, har idan baki amince min na kusance ki ba , zan cigaba da jiran ki har ranar da zaki amince min da da kanki ko da ace ranar itace karshen numfashi na a duniya."
a hankali ya mike a kaina ya mika hannu da kyar ya janyo towel ɗin yarufe min jiki na da shi, wani kuka na sake mai cike da kunar abin da ya min.
baya na yaɗan shiga bubbuga wa da kyar ya iya furta kalmar "Kiyi hakuri."
shima ɗin da kyar. ya zamo bakin gadon ya mike da sauri yaɗan durkusa ya rike marar sa da karfi, yakai tsawon 10mn a durkushe a gun kana ya mike da kyar yana jan kafa ya fita a ɗakin.

Kuka nayi ta rerawa da bakin cikin tuɓe ni da yayi,
a hankali na mike ina jan hanci da faɗin
"Wani iskan ci yakama ya tuɓe ni in dai shi bashi da kunya an faɗa masa kowa mara kunya ne."
na sauka naje na saka kaya na dawo na kwanta..

A ɓangaren Ahmad kuwa a kan gado ya zube yayi ta murkusoso, yayin da yake jin marar sa kamar zata fashe dan ciwo, yayi ta mamaki da tambayar kan sa ashe haka yake ne wai abin ya bashi mamaki dan shi bai taɓa sintar kansa cikin irin wannan halin ba, lallai ya daɗa yarda HAMDAH ta daban ce.
a ranar kuwa bai iya rumtsawa ba haka ya kwana da mugun ciwon mara,
washegari bai iya tafiya masallaci ba a gida yayi salla, har wajen karfe 11 yana kwance da kyar ya lallaɓa yatashi ya shiga bathroom yayi wanka a daddafe ya fito, ya saka kaya ya ɗau makullin motar sa ya fita. wani
pharmacy ya je dan bashi da zabin da ya wuce ya samawa kan sa tablet dan yasan koda yaje ga Rasheedat ba lallai bane ta amince masa zatace hakkin HAMDAH ne ya koma gare ta....

Tun da yafita bai dawo gidan ba har yamma, gaba ɗaya kewan yara na ya dame ni, ya wani ɗauke su ya tafi da su basai ya dawo dasu ba tun da na dawo, kuma ai a gida nake barin su in zanyi tafita ta, waya na ɗaga da niyyar in kira shi nace ya dawo min da su, sai kuma na aje wayar na mike ina jan tsaki...
da yamma

ina zaune a parlour'n kasa yashigo,
fuska na ɓata ganin yana ta bina da murmushi har ya iso in da nake ya zauna gefe na, da sauri na matsa can gefe, murmushi mai sauti ya sake ya mika hannu ya ruko hannuna yace
"Kyakkyawa ta barka da gida."
baki na turo gaba tare da kawar da kaina gefe, mikewa yayi yana cigaba da murmushi ya zo ta gabana ya ɗan rankwafo a hankali yace
"Zo muje ki tayani wanka mana."
da sauri na ɓoye hannuna ta baya da yake kokarin ruko shi, saukar kiss naji a goshi na,
da sauri na ɗago idanun mu ya haɗe guri guda,
a hankali ya furta
"Kyakkyawa ta yaushe ne zaki fara so na da jin abin da nake ji a kanki?."
da sauri na janye idanuna daga nashi ina taɓe baki.
annurin fuskarsa ya yelwata mai matukar karawa fuskarsa haske da kyau yace
"Zaki soni a duk san da muka jone muka zamo abu guda, ranar da zaki karɓi bakwanci na."
wani kallon shekeke na bisa da shi, shiko murmushi ya kuma kana ya juya yana faɗin
"To bari na lallaɓa naje nayi wankan tun da bazaki tayani ba."
har ya ɗaura kafar sa ɗaya kan step nace
"Su Naseem fa suna ina ne?."
waigo wa yayi ya dube ni yace "Dama kina son su ne sai yau zaki tambayi in da suke."
a hatsale nace "Dama akwai uwan da bata son ƴaƴan ta ne?."
"Naɗau ka kina daga cikin su ai, zasu dawo amma ba yau ba."
yayi maganar yana cigaba da tafiya.
kwafa nayi ina bin bayan sa da harara..
ina nan zaune har aka kira sallar magriba, ya sauko cikin shigar tafiya masallaci, tun kan ya karaso na mike da sauri dan nasan sai ya zo in da nake, nashige kitchen, sai da naji fitar sa kafin na fito,
na haura sama, ina idar da salla na fito, a hankali na nufi saman dinning in da fridge yake na nufa dan kishin ruwa nake ji, na buɗe na ciro garar ruwa mai sanyi haɗe da cup dasuke a jere gefen fridge ɗin, na tsiyaye ruwan na sha.
kana na mai da ragowar ruwan, har zan rufe fridge ɗin sai idanuna ya sauka kan wani yoghurt dake baki-bakin fridge ɗin ya ɗau tsayi har bayan gorar yana zufa, na ɗau gorar haɗe da cup na rufe fridge ɗin na koma ɗaki.
a bakin gado mazauna na bude gorar na tsiyaya yoghurt ɗin cikin cup, a hankali nakai cup ɗin baki na ɗan kurɓa, a hankali na lumshe idanuna jin daɗin yoghurt ɗin da sanyin sa ya baibaye min baki.
narika kurɓar sa ina sha cike da jin daɗin sa, har sai da na shanye wanda nazuba cikin cup ɗin nakuma karawa, sai da naji cikina ya cika tam kafin namike nashiga bayi na kuskure bakina na fito na haye kan sallaya jin an tada sallar isha,
wata doguwar hamma na sake cikin sallata a raka'ar karshe, yayin da naji ilahirin jiki na yana yimin wani iri, a haka na idar da sallar, yayin da nake tajin yanayin na daɗa karuwa,
idanuna na mutstsuke da duka hannaye na biyu na mike tsaye tare da yin mika dana ji ya taho min babu zato ko sammani.
a hankali na ninke sallayar na kai ma'ajiyar sa haɗe da hijibin.

na dawo bakin gado na zauna, na ɗau wayata ina ɗan daddana shi.
mika na kuma yi, cikin jin yanayin dake daɗa shiga ta, nakasa tantance yanayin.
aje wayar nayi na gyara na kwanta tare da lumshe idanuna,
shiru nayi a hankali nake daɗa jin abin da nake jin na karuwa, a hankali na mirgina tare da yin mika na kankame jikina tare da buɗe idanuna da suka gama sauyawa kamar me maye,
hannuna na cusa sakankanin cinyoyi na na matse da karfi.
jin karar buɗe kofa yasa ni buɗe idanuna a hankali na zubawa kofar,
daga bakin kofar ya tsaya yazuba min ido, kana ya mai da duban sa kan gorar yoghurt ɗin da ke aje tsakiyar ɗakin.
a sannu ya tako ya iso bakin gadon ya rankwafo kaina yace
"Kyakkyawa ta."
shiru nayi na mai da idanuna na lumshe.
sosai ya kura min ido ina jin yan da idanunsa yake yawo a jikina, hannu ya sauke gefen fuskata ya shafo a hankali yace
"Ya dai kyakkyawa ta wani abun ne?."
a hankali na buɗe idanuna dasuka gama sauya wa nazuba masa sai kuma na mai da idon na rufe.
takun tafiyar sa naji na buɗe ido na zubawa bayan sa har ya fita.
juyi nayi nakuma sakin dogon mika.
ido na waro cikin matukar mamakin gano yanayin da nake ciki, da sauri na mike ina tangaɗi kamar ƴar kwaya na shige bathroom, kayan jikina natuɓe da sauri na cika ruwan zafi nashige ciki, ina mammatse ido,
shiru nayi ina jin ɗumin ruwan na ratsa ni. madadin saukin yanayin sai ji nayi kamar daɗa karuwa yake,
nasha mamakin kaina da abun da nake jin.
da sauri na fita na zo gaban wardrobe naciro rigar bacci na zura ban ko tsaya tantance wata iri ce ba bare na kaiga sa pant, dan nakai kololuwa wajen jin filling. sai da na saka naga bata karasa kai guiwa ta ba, mai tsiririn hannu ce da gidan bra..
baya nayi na zube kan gado tare da cusa hannaye na sakankanin cinyoyi na, nashiga juya kai cikin mawuyacin hali.
wace irin sabuwar al'amari ce ke faruwa da ni yau?.
hawaye yashiga zubo min nazube kan gado nayi ta juyi ina matse cinyo yi na, wai ko dun zanji saukin abin da nake ji,
amma ina babu sauki cikin lamarin, a hankali na mike zauna jin wuya na ya bushe kantakarau sai haɗiye miyau nake da kyar,
ragowar yoghurt ɗin da nasha ɗazu nasha na rage na ɗauka na kafa kaina sai da nashanye duka na ajiye gorar,
na koma na kwanta. nan ma juyin na cigaba da yi gaba ɗaya nagama jikewa, tamkar daɗa ruramin wutar abin da nake jin ake.

Zumbur na mike tsaye ina jan kafa na fita,
can na hango shi zaune cikin parlour yana kallo, jin karar buɗe kofa yasa shi juyowa ya zuba min ido dai-dai lokacin da nasaki wata doguwar mika.

idanuna na matse da karfi kana na buɗe, a sannu nashiga ɗaga kafafu na nazo na wuce ta gaban sa,
dinning na haura nabuɗe fridge naciro garar ruwa na kafa kaina nasha sosai.
ruwan na shiga cikina tamkar daɗa angizo min da wata muguwar filling yayi, sake gorar nayi yafaɗi kasa sai ga hawaye sharr, baya nayi na zube kan kujerar dinning nahaɗe cinyoyi na na batse, na kifa kai na saman dinning ina cigaba da ba
matse cinyoyi na da yuya kai.
kuka na fashe da shi da karfi, nashiga bubbuga kan dinning ɗin da hannaye na biyu...
da sauri ya mike yazo in da nake yana faɗin
"HAMDAH mene ne me ya same ki?."
ban ce komai ba sai kukan dana cigaba da yi,
da sauri ya kamo kafaɗa ta ya ɗago ni yana cigaba da tambayar abin da ya same ni.
jikina nashiga janye wa daga nashi jin kamshin sa ya baibaye ni yana daɗa kara min abin da nake ji.
yaruko hannuna da kyau ya janyo ni muka dawo cikin parlour,
ido ya kuramin yana kallon yan da hawaye ke sauka a idona na sai ya girgiza kai a hankali yace
"Kyakkyawa ta me ya same ki?."
kai na sunkuyar ina ci gaba da matsar kwalla.
a hankali ya janyo ni ya rungume jikin sa ya manna kai na a kirjin sa, wani nannauyar numfashi muka sauke a tare,
a hankali yashiga shafa kaina kana yace
"Kiyi hakuri HAMDAH amma ki sani wlh shine Allah ina son ki."
lamo nayi a jikin sa ina ɗan jujjuya kaina cikin kirjin sa cikin mawuyacin hali.
sai kuma nayi yunkurin janje jiki na daga nashi jin yanda zuciya ta take ta fizga na izuwa gare shi dan samawa kai na saukin abin da nake ji.
da sauri yayi hanzarin mai dani jikin sa, sai kawai nasaki kuka.
da sauri ya manna bakin sa kan nawa yashi tsotsa, ɓari jikina ya kama jin yana daɗa angiza min wutar fitinar da ke azalzala ta.
cak ya ɗago ni yayi da ni cikin bedroom ɗina wan da yake kwana ciki,
a kan gado ya dire ni, sai ya zauna gefe na tare da tsura min ido,
kana a sannu yaɗan rankwafo kaina yace
"Kin shirya karɓar bakonci na yau?."
ido na rumtse da karfi tare gantsare wa jin yan da jiki na yake wani tsuma tam kar allura ake min.
a hankali yakai hannunsa jiki na yashiga shafani, da sumbata ta,
a sannu yakai hannunsa izuwa kafaɗa ta yashiga murza hannun riga ta yana yin kasa da shi, a hankali yayi kasa da shi har zuwa saman kirji na,ɗan sakai tawa yayi a sannu yadawo da hannun nasa kan kirji na dai-dai saman, ababen kirji na ya daɗa rankwafofa kai na sosai ya saka yatsar sa guda ya janye rigar tayi kasa nonuwa na suka baina a fili.
kai na najuya gefe da sauri,
ido ya kafe ababen kirjina dasu yayin da fitar numfashin sa ya karuwa, maganar sa najiyo a sama
"Wai da gaske kin shayar da yara biyu a lokaci guda kodai gidan raino kika  kaisu?."

hannu na yarfe ina murza kafafu na kan katifa, gaba ki ɗaya idanuna sun gama rufewa da wutar fitinar da bansan da zuwan sa ba.
hannunsa ya sauke su kan nonuwa na.
idanuna na rumtse da karfi jin ɗumin tafin hannunsa kan ababen kirji na, a hankali yashiga shafa su da matse su,
mimmikewa na shiga yi gaba ki ɗaya jikina yadaɗa amsa wa, babu abun da nafi bukata a yanzu kamar naji sa cikin jikina.
da sauri na rirrike hannunsa jin ya shagalta wajen mammatse ababen kirji na, ya ɗago ya zuba min idanunsa da suka gaba canza kala a hankali murya can kasa yace
"Ya dai kyakkyawa ta kina marhaban da ni?."
ido na rumtse sai ga hawaye shar. kai ya girgiza min da sauri yace
"Kiyi hakuri." yafaɗa yana
zame hannunsa da ga rukon dana yi masa.
a sannu naji ɗumin bakin sa kan brest ɗina, wani irin bankaro kirjin nayi.
billahil azim in da yasan kalar abin da nake ji da bazai zauna yimin waɗan nan abubuwan ba, haushin kaina da tsanar yanayin da bansan yan da akayi ya zo min ba ya tabaibaye ni.
a sannu yayi kasa da rigar yaraba shi da jikina, yayin da yaci gaba da shafa sassan jikina, zuwa can ya ɗago a galabaice ya zubamin fitinannun idanuwan sa murya a sarke yace
"HAMDAH ki na maraba da ni kin shirya karɓar bakwanci na?."
wasu hawaye ne masu ɗumi suka zubo min ganin bani da mafitar da ya wuce abin da yake nufi, har idan ina son kai na da lafiya.
sai na rumtse idanuna tare da gyaɗa masa kai hawaye na cigaba da tsiyaya ta gefen ido na.
wani murmushi ya sake ya mike jikinsa na ɓari yazare gajerin wando da singlet ɗin jikin sa ya haye kaina yayi min rufma.
sumbatar fuskata ya shiga yi yayin da hannunsa ke kan ababen kirjina yana ta aikin matse su, kai na shiga yuyawa cikin matsanan ciyar filling, cikin rufewar ido da cushewar ƙwaƙwalwa naɗago hannaye na na sauke su a bayansa, ido na matse da karfi.
najayo sa izuwa jikina.
da sauri yashiga karanto addu'a cikin hanzari ya isa da marar sa izuwa nawa, har jikin sa na ɓari,
ido na rumtse da karfi jin yanda ya ziyarce ni.
wani irin dogon numfashi ya sauke tare da faɗin
"Washhhhhhhhhhh ahhhhhhhh kyakkyawa ta ashe haka kike shine kika ringa nisanta kan ki gare ni? me yasa kika son haram tamin wannan ni'imar, kyakkyawa ta washiiiiiii aaayyyhhh Allah dai ya saka miki tabbas Allah ya miki baiwa washiiiii Allah wahhhhyyy."
wasu irin sambatu yarika yi, yayin da yake nutso cikin gona ta.
numfashi nashiga  sauke wa a hankali a hankali, duk da ina cikin yanayin nan amma sai da naji zafi dan ya dage kwarai da gaske yana ta sukuwa kaina, sai dai zafin ma banbanci ne ina jin sa ina kuma jin wutar fitinar da take azalzala ta.
sosai ya dage yake kai koma a kaina yayin da yaci gaba da sambatu
"Wai da gaske kin taɓa aure amma dai bai taɓa lumewa in da na shiga yanzu ba, washiii ahhhhyy HAMDAH ina son ki ina son ki I love You I love You,
HAMDAH dan Allah ki soni ko rabin yan da nake son kine, na tambata zakici gaba da shayar da

ni wannan daɗin, wayyooo HAMDAH tai maka ki rike min nan."
ya nuna kugun sa da yake sama da kasa kamar zai ɓale.

Ya shari tsawon a wa huɗu a kaina zuwa lokacin a hankali narika jin abin da nake ji yana raguwa, yayin da wani zafi da mugun raɗaɗi suka biyo baya, kai nashi ga juyawa ina shure kafafu na,
lokaci guda na nimi filling ɗin da nake jin na rasa, kamar a mafarki nake ji da ganin abun,
ido na zuba masa ya haɗa gumi yayi sharkaf duk da sanyin AC da ke tashi cikin ɗakin,
yayin da gefen idanunsa ke tsiyayar da kwalla.
firgigit nayi kamar wacce ta farka daga bacci.
sai na saki kuka ina ture kirjin sa da shishure kafafu kan katifa, cikin Muryar kuka nake faɗin
"Ka kyale ni ka rabu da ni katashi min a kai wayyo Allah na wayyo zafi, nidai ka rabu da ni."
zuwa lokacin bai iya furta komai sai dai idanunsa da ke tsiyayar da kwalla, ta gafe idananun kuma suna rufe.
kuka sosai nayi ta yi ina faɗin ya kyale ni, amma tamkar baya jina hasali ma idanunsa a rufe suke,
sai kuma ɓarin da jikin sa ya ke.
da karfi ya fizgo wani numfashi sai kuma yashiga sauke numfashin da karfi-karfi yayin da gudun sa ya karu na wasu ƴan mintoti, zuwa can ya kankame ni kamar zai ɓalla ne tare da sakin kara wan da idan mutum yana daga cikin parlour zai i ya jiyo sautin sa..
lamo yayi a kaina yarika sumbatar fuskata, yana mai sauke numfashi a kai a kai...
da karfi na shiga ture shi ina faɗin
"Katashi min a kai nikam ka tashi min a kai."
a sannu yazare jikin sa ya kwanta gefe, yana mai cigaba da sauke numfashi.
niko cikin takaici da bakin cikin tuno abin da ya faru tun da fari sai nakuma sakin kuka, ina bubbuga kafafu na kan katifa..
a hankali ya mike yaɗau gajeren wandon sa ya saka ya mika hannu ya ɗago ni ya rungume jikin sa tare da bubbuga baya na cikin yanayin rarrashi,
fizge jikina nayi nakoma nakifa fuskata da jikin katifa, na cigaba da rera kuka na.
da sauri yakuma ɗago ni yana faɗin
"Dan Allah kiyi hakuri ki dai na kukan nan haka, toma wai kukan me kike yi ne iye kyakkyawa ta?
kin samar min da farin cikin da ban taɓa samin irin sa ba hakika ke ɗin ta musamman ce,
ban san da wani irin baki zan yi miki godiya ba, amma ki sani kin sanya ni cikin farin cikin da bansan taya zan iya misalta shi ba,
Allah ya saka miki da mafificin rahamar sa, yan da kika sani cikin farin ciki da kwanciyar hankali,
ya dauwamar dake cikin farin ciki da kwanciyar hankali har abada,
dan Allah kyakkyawa ta ki dai na wannan kukan har cikin kasan zuciya ta nake jinsa."
fuska ta ya leko tare da sakin wani lallausan murmushi yace
"Wai kukan me kike yi ne kam ko bai ishe ki bane na kara."
sautin kukan na kara ina tutture shi cikin muryar kuka nashiga faɗin
"Wlh Allah ban yafe ba ni ka rabu da ni."
ƴar karamar dariya yayi yace

"Baki yafe ba da aka yi me?."
"Taɓa ni da kayi." na faɗa a hatsale cikin sautin kuka.
dariya sosai yayi yana daɗa kankame ni a jikin sa yace
"Ai ni ban taɓa ki ba sai da amincewar ki ba ke kika ce nayi ba."
dukan kirjinsa na shiga yi ina faɗin
"Ni ban faɗa ba."
"Kin mance tun a parlour kike ta jana nazo na baki har a kan gadon nan ma jana kike, dan yanzu kin gama biyan buƙatar ki shine zaki ce haka ko."
yayi maganar cikin muryar dariya sosai haɗe da zallar zolaya yana leko fuskata.
kai na tsunkuyar cike da tsananin jin kunya, tuno da abin da ya faru ɗazu, tabbas ni kaina nasha mamakin kaina irin yan da nake ji ɗazu, tabbas nayi mamakin kai na ba ɗan kaɗan ba,
"Yau wa kin tuna ko to kada ki sake ganin laifi na, ai dama na fada miki sai da amincewar ki zan kusan ceki,
ina son ki kyakkyawa ta."
baki turo gaba da sauri nace
"Ni ka tashi kaje ka kawo min abinci Allah kasa na faɗi bazan yarda ba."
da sauri ya janyo pillow ya gyara min kwanciya ta kan pillow'n. ya mike da sauti yana faɗin
"Me kike so kici?." ban amsa shi ba sai yayi waje da sauri.

A hankali na mike zaune na ɗau riga ta na saka, a sannu na zamo baki. gadon dan fisari ce ta matsani, sai dai ina tsoron na mike kada na faɗi,
a hankali naɗan rika mikewa ga mamaki na sai naga na mike garau, nayi taku ɗaya zuwa uku babu alamar jiri ko ɓarin jiki tattare da ni.
nayi matukar mamakin bana jin ko ɗaya daga cikin biyu.
kai na jinjina da mamakin karfin jini irin na Ya SALEEM, ban isa ya kusance ni na iya mike wa tsaye da kaina ba har sai na sanya wa cikina wani abu, haka jikina kuma zai yi ta ɓari har sai jinin sa ya gama garwaye jikina...
da sauri ya shigo rike da tray yazo ya dire saman table, ya zo in da nake da sauri ya ruko hannuna yace
"Zo ga abincin kici kinji."
yana kokarin janyo ni, hannu na yarfe nace
"Ni fisari zanyi."
kafin na karasa faɗa ya kinkime ni yayi dani cikin toilet,
yana tsaye yace nayi fitsarin kafaɗa na make na ɓata fuska nace ya fita.
bayan sa ya juya yace "To bani ganin ki kiyi."
babu yadda na iya dan na matsu sosai. sai da nayi amfani da ruwan zafi wajen yin sarki dan ba karya HQ ɗi na yana yimin zafi sosai.
ina gamawa yataho in da nake yace
"To muyi wanka ko."
baki na turo nace "Ka fita."
kai ya girgiza kamar karamin yaro yace
"Tare zamuyi daga yau har kullum ma."
ido na waro kafin na ankara ya ɗago rigata ta kasa ya zare ta a jikina, ya tuɓe gajeren wandon

sa.
duk wani kina da tirjewa ta haka yasa mukayi wankan nan tare.
yaso ya ɗauko ni ya fito da ni naki fir nace da kafata zan tafi.
gaban wardrobe na isa na ciro doguwar rigar bacci har kasa na zura, na ɗau pant zan saka yayi saurin matsowa in da nake yarike shi tare da girgiza min kai yace
"Kar ki saka."
fizge abina nayi ina faɗin
"Akan wani dalili?."
murmushi yayi yana shafa gefen fuskarsa yace
"Kika sani ko anjima ki kuma bukata ta."
kunya ce ta lulluɓe ni ina mai takaicin yanayi na na ɗazu.
baki na murguɗa masa nace
"Allah ya sawa ke." dariya yayi tare da rungumo ni cikin yanayin sa na zolaya yace
"Allah shi kara dai, zo muje kici abincin kada yayi sanyi."
"Ni na koshi."
nayi maganar ina ture kirjin sa.
yace "Ko ɗan tea bazaki taɓa ba."
nace "Bazan sha ba nace."
"To shike nan muje mu kwanta."
ido na waro nace "A ina? ni ka rabu dani naje na kwanta."
"Yau kam dai ai zaki tayani kwana tun da kin hanani yin bacci da wuri yau, dole fa sai kin sani nayi bacci dan bazan iya yin bacci da kaina ba, tun ɗazu nake jin baccin nan kika hana ni yi."
ya dago ni cak ya dire ni kan gado, haka yayi ta zolaya ta da jana da wasa, har bacci ya ɗauke ni...
a ranar kam Ahmad bai iya rumtsa wa ba....👌🏻

Washegari bayan ya ɗaga ni nayi salla nakuma koma wa bacci, ban farka ba sai wajen farke 11, baya cikin ɗakin, a hankali na sauka a gadon na shi ge bayi nayi wanka na fito.
sai da na saka kaya kafin na isa gaban mirror na zauna,
na ɗau mai nashiga shafawa a hankali, idanuna ne ya sauka kan wani tablet a kan mirror, a hankali na kai hannu na na ɗauki tablet ɗin ina bin sa da kallo, da ɗinbin mamaki nake bin kwayan da kallo,
tabbas komai akayi wannan wayar tana da nasaba da yana yin dana shiga jiya, to me ya kawo shi nan taya akayi kuma na sha.
cikin kankanin lokaci nashiga tunano abin da ya faru da ni jiya kafin na shiga yanayin dana shiga daga baya.
nagama duk kanin iya tunani na, can tunani na ya tsaya kan yoghurt ɗin dana sha tabbas shine abu na karshe dana ci a daren jiya, daga kansa kuma nafara jin yanayin,
a hankali nashiga tunanin yan da aka yi na sami yoghurt ɗin, a bakin bakin fridge na gani kuma tabbas ba ni na buɗe shi ba, a buɗe nagani sai dai murfin yana jikin sa.
jin karar buɗe kofa ya sani juyo wa ya mai da kofar ya rufe, mai da kallo na nayi kan ƙwayar kana na kuma duban sa,

ido yaɗan waro sai kuma ya saki  murmushi, ya tako in da nake ya mika hannu zai karɓi tablet ɗin, da sauri nayi baya da hannnuna ina bin sa da kallon tuhuma nace
"Meye wannan?."
nayi maganar ina haɗe rai. kai ya lankwasar gefe ya janyo ni jikin sa ya rungume a hankali yace
"Kada ki zarge ni son ki ne sila."
ture kirjin sa nayi nace
"So da cuta, kayi amfani da shi wajen birkita min tunani..."
da sauri ya rufe baki na da tafin hannunsa ya girgiza min kai a hankali yace
"Ko da na saka miki ban yi ba fa sai da amincewar ki, ke kika ce nayi fa...........!

23

Nace "Wlh Allah ban yarda ba, shine zaka yi amfani wajen gusar min da tunani na." dariya sosai yayi yace "To hakuri zakiyi kuma ai kema kin rama, ba nima kin gusar min da tunanin nawa ba jiya, kuma ai ke kika sa na aikata hakan son ki na shirin kashe ni da sauran kwana na,
bukatar ki na shirin illata ni kin san da ya na kwana shekaran jiya,
shi yasa kawai na ai watar da  haka ba gashi na samar wa kaina mafita ba,
zo kiji yan da akayi."
ya ciro ni daga jikin sa ya zau kan kujerar gaban mirror kana ya zaunar da ni kan cinyar sa,
ya zuro hannunsa ya zagaye ni ta gaba tare da ruko hannaye na da kowa ni hannunsa yana ɗan murza su kana ya soma magana
"Ban san sha'awa yana sanya ciwo ba sai da na zo gare ki shekaran jiya,
marana kamar zai fashe, na kwana cikin mawuyacin hali, da safe na shirya natafi pharmacy domin sama wa kaina magani,
to mai pharmacy mutumi na ne bayan nayi masa bayanin abin da yake dami na sai ya bani magani, har na fita na shiga mota sai ya biyo ni har cikin motar,
ya bani maganin nan yace na zubawa Madam a cikin abin sha tasha magani magani na yana gurin ta, dan maganin da ya bani zai iya lafawa ne yanzu anjima ko gobe zai iya tashi min, amma idan nayi amfani da wannan zan sami ingantaccen magani a gurin ta zan warke,
na karɓa nayi masa godiya, ina dawowa gida kuwa shine naje na ɗau yoghurt a fridge na zuba a ciki, na ajiye akan idan na dawo daga masallaci nazo na baki kisha, duk da nasan da kyar ki amince ki sha,
sai gashi cikin sauki Allah ya taimake ni yaji tausayin bawansa da so ke kokarin  ajalin sa,

da kanki kikaje kika ɗauka kika sha, kuma banyi ba sai da amincewar ki.
niko nayi ta zunduma cikin rijiyar ina kwasar ruwa, kai kinji yan da kika rika bani shi kuwa nace wayyo Allah ashe haka yarinyar nan takware wajen iya mika abin, kai kinfa birkita min lissafi ba kaɗan ba. muɗan je ki ɗan kara min ne  ko ɗan kaɗan ne."
gaba ɗaya kunya yagama lulluɓe ni,
kai wannan mutumin bashi da kunya shi gaba ɗaya baya iya ɓoye maitar sa, da sauri na yunkura a jikin sa zan mike cike da jin kunya. yayi saurin maidani yana dariya.
yakawo bakin sa saitin kunne na a hankali yace
"Baza ki bani na safiyar ba."
kafaɗa na make yace "A taimaka dai."
baki na turo gaba nace "Allah idan ka sake samin maganin nan bazan yarda ba."
yace "Bazan kara ba idan na kara kema ki rama, muje muyi breakfast jiran ki nake dama ki tashi muyi."

Ya mikar dani tsaye ya ruko hannuna muka fito parlour.
kin cin abinci nayi na zuba nazuba masa ido, yace
"Kici mana kyakkyawa ta buɗe baki na saka miki."
kafaɗa na make nace "Ni bazan ci."
murmushi yayi yace "Ai nayi alkari bazan sake sa miki ba Allah babu komai a ciki muci kinji."
da kyar yayi ta lallaɓa ni har na yarda naci. amma hankali na yaki kwanciya har saida naga na kai wani lokaci ban ji wani sauyi tattare da ni ba.

A ranar Ahmad yaki bari na ko yamatsa in da nake yana nan like da ni, zolaya kuwa na shasa a gunsa tun idan yayi ina jin haushi har yadawo bani dariya, da kyar na samu na zame jikina nashiga bathroom, nacika ruwan ɗumi cikin bathtub nashige ciki,
dan har yanzu HQ ɗina yana yi min zafi,
da sauri na ɗago jin ya turo kofar, fuska na ɓata ina kare jikina da hannaye na.
ya karaso ciki ya tsaya a kaina yana kare min kallo, nace
"Meye haka kafita mana."
kayan jikin sa yashi tuɓe wa yana faɗin
"Idan nagama wankan kenan ko."
da sauri na mike na janyo towel ganin ya zare wandon jikin sa, ina kokarin ɗaura towel ɗin ya fisge ya mai da shi ma'ajiyar sa, kana ya shige cikin bathtub ɗin, ya ruko kafaɗa ta ya mai da ni zaune shima ya zauna.
ya mikar da kafafun sa, ya ware nawa da su ya danne nawa, kana ya janyo ni sosai yayin da joystick ɗin sa ke gogar HQ ɗina.
kallon cikin ruwan yayi in da joystick ɗin sa keta harbawa yana gogar HQ ɗina, kana ya dube ni a marairaice yace
"Kin ga in da yake son shiga."
idanuna na rutse da karfi, cikin matsananciyar jin kunya, nayi yun kurin mikewa amma na kasa.
batare dana buɗe idona ba nace
"Ni karabu da ni bana so."

murmushi mai sauti yayi a hankali naji saukar hannunsa kan ababen kirji na, sai ya rika ɗiban ruwan yana zubawa a kansu yana kuma matse su, da sauri na buɗe ido jin yana kokarin tura joystick ɗin sa cikin HQ ɗina.
da karfi na daddage nashiga ture kirjin sa ina faɗin
"A'a ni dai ka kyale ni."
idanunsa da suka fara sauyawa ya zuba min murya a cushe yace
"Ko kaɗan ki taimakawa bawan Allah da son ki ke shirin zautar da shi."
hararar sa nayi ta gefen ido,
murmushi yayi yana manna min kiss a goshi.
da kyar na daddage na samu na janje jikina nayi baya, dan naga da gaske yake ta son zurma abar tasa.
kan ya ankara na fita cikin bathtub ɗin na jonyo towel na ɗaura nafita
a bayin da sauri....

( *Bauchi state* )
G.R.A

Wani irin razani da birkita SALEEN yayi a lokaci guda ya mike zaune har jikin sa na cirawa, tare da dafe kirjin sa da karfi.
Na'ima da shigowar ta ɗakin kenan da sauri ta karaso in da yake, ta dafa kafaɗarsa tana faɗin
"Lafiya My SALEEM wai me ke damun ka ne, sakanin jiya da yau kake ta firgita cikin bacci?."
idanunsa ya rumtse da karfi, ya cusa hannayensa cikin sumar kansa ya yamutsa tare da furzar da huci mai zafi,
da sauri ya duro a gadon ya shiga bathroom yasakarwa kansa ruwa mai sanyi sosai,
yayin da yake sauke wasu irin tawayen numfarfashi mai haɗe da huci kamar wan da yayi tsere.
ido Na'ima ta zubawa kofar bayin,
ita fa abin nan yafara damin ta tun jiya da daddare suna kwance yayi wani irin zabura kamar mai tashin aljannu, gaba ɗaya yafita hayyacin sa, still gashi yanzu ya sake maimaita irin haka.
kai ta girgiza tana faɗin
"Nasan ko zan yi yaya da bakin sa bazai faɗa min ba dole naje gurin boka naji me yake faruwa."

Tana nan tsaye har ya fito ya wuce ta yaje ya sauya kaya, ta tako in da yake ta rungume sa ta baya a hankali cikin muryar kirsa da makirci tace
"Haba My SALEEM idan baka faɗa min damuwar ka ba mawa zaka faɗa mawa, wlh karkaga yan da hankali na ya tashi, anya ba magauta ke bibiyar ka ba?."
zame jikin sa yayi yaɗan juyo ya kalle ta sai kuma ya juya yanufi in da makullin motar sa yake ya ɗauka yayi waje...
A hankali yake tuki kamar mai tausayin titi, gaba ɗaya yanayin sa ya sauya jikin sa yayi sanyi kamar wanda ruwan sama yabige shi.
a haka ya isa family H ɗin su,

yana dai-dai ta parking ya fito a hankali ya nufi side ɗin Mamie.
a parlour ya yasame ta tana zaune tana kallon labarai, ya isa ya zauna sannan yashiga gaishe ta.
sama-sama ta amsa masa dan har yau bata sake masa,
tun da ta amsa gaisuwar kuwa ta mai da idanunta kan TV, ya karaci zaman sa ya mime yayi mata sallama can kasa ta amsa shi ya fita.

Side ɗin Ummi ya zarce yayi sallama ya shiga, babu kowa cikin parlour'n ya karasa ya zauna kan ɗaya daga cikin kujerun parlour'n.
Ummi dake cikin bedroom tana zaune kan sallaya tana jan jarbi tajiyo sallam,
ta mike ta fito can ta hango shi zaune yayi jigum.
ta karaso in da yake da murmushi ɗauke a kan fuskar ta
"Ah SALEEM kai ne? sannu da zuwa ya gidan da mutanen gidan, ina ango shine ba'a zo min da shi ba?."
gajeren murmushi yayi, yana gaishe ta, ta amsa cikin sakin fuska, kana ta mike taje kitchen ta taho masa da abinci da ruwa kamar yanda ta saba, a koda yaushe idan yazo gaishe.
zaman sa ya gyara a kasan carpet yashiga cin abincin da ta zuba masa cikin plt, yaci da ɗan dama kana ya kara da ruwa.
Ummi tayi ta jansa da hira hm da um
shine kawai amsar sa.
ya ɗan jima zaune kana ya mike yayi mata sallama,
Ummi tazuba wa bayan sa ido dan yana yin sa yafi kama da wan da yake cikin damu sosai.
daga gidan offece ya wuce haka ya wuni bai taɓuka komai ba...

*Abuja*

Bayan sallar la'asar ina tsaye cikin bedroom Ahmad ya shiyo dawowar
sa daga masallaci kenan, hannunsa rike da makullim mota, ya taho in da nake, rungume ni yayi tare da sumbatar goshina yace "Kyakkyawa ta, kin hana ni kari ki gani har dare ya fara yi, haka zan tafi baza ki ɗan kara min?."
kafaɗa na make, murmushi yayi yana daɗa janyo ni jikin sa yace
"To bari naje na ɗauko su Nasmah, kada a barki ke kaɗai ko zamu tafi can ɗin ne jibi sai mu dawo?."
harara na dalla masa ina zame jikina.
da sauri ya taro ni yana dariya yace
"Afwan kada ayi min hukuncin daban iya ɗauka ba."
bakin sa ya manna kan nawa yayi kissing ɗin sa sosai kana ya sake ni yana bina da murmushi har ya fita.
numfashi na sauke tare da zama bakin gado...
daf magriba motar sa tashigo gidan,
ina zaune a parlour'n kasa ya turo kofa da sallama, su Naseem dake bayan sa suka shigo da

gudu, Rasheedat na biye da su,
a jikina suka zube suna faɗin
"Oyoyo Mommy, Mommy kin dawo ne?."
murmushi nayi tare da shafa kan su nace "Eh nada wo." Naseem yace
"To Mommy ina tsara bar mu?."
Nasmah tace "Kin kawo mana tsaraba?."
kai na gyaɗa nace "Nakawo muku yana ɗaki."
ihun murna sukayi suna daɗa ɗalewa jikina.
Rasheedat dake ta binmu da murmushi tace
"Iye-iye amma dai zaku sanmin tsarabar taku ko?."
sauka sukayi daga jikina suka koma jikin ta suna faɗin
"Eh Mamy damu baki da yawa da yawa."
ido ta waro tace "Kai amma naji daɗi na duka ni kaɗai."
murmushi nayi ganin yan da take ta yi da yaran kamar zata goya su dan so,
tabbas duk wan da yaso naka yagama maka so a duniya.
ta juyo in da nake tana faɗin
"Wato shine zaki kwace min su yau ko?."
murmushi nayi nace "Ina yini Aunty Rasheedat."
fuska ɗauke da annuri tace
"Lafiya lau kin dawo lafiya ya gajiyar hanya?." nace
"Alhmdllh."
ina dago wa muka haɗa ido dashi, baki na murguɗa masa, shiko wani murmushi ya sake tare da jingina bayan sa da jikin kujera yana bina da kallon kasan ido.
kiran sallar da aka fara yi ne yasashi mike wa yafita zuwa masallaci,
na dube ta ganin yan da ta shagalta da biyewa yaran.
ta mike tana faɗin "Mujen ku muyi salla ko."
nace mata mu haura sama, tace a'a zata yi a kasa kawai. nan bayin kasa tayi al'wala da yaran a nan parlour sukayi salla. ni ma anan ɗin nayi al'walar nayi sallan.
koda muka idar hira sosai Rasheedat tayi ta min har aka kira isha, sai da aka idar kafin Ahmad ya shigo.
ya zauna aka cigaba da hiran da shi, duk da ni bawani amsa su nake ba, iya kace idan sukayi abin dariya na ɗan murmusa, haka suka yi ta jana da hiran.
a ɗan zaman mu da su yanzu na fahimci suna da kyakkyawar fahimta sakanin su dosai.
sai wajen karfe goma sukayi min sallama lokacin tuni har su Naseem sunyi bacci. tana gaba ya na biye da ita, tana fita ya dawo da baya da sauri ya rungumo ni yace
"Zanyi missing ɗin ki."
bakin mu ya haɗe ya tsotsi bakina da kyau kana ya ɗago yana bina da wani irin kallo, a hankali ya sake ni ya juya ya fita.
bayan sa nabi da kallo ina mai sauke numfashi, a hankali na taka bakin kofar na rufe kana na juyo.
na kwashi su Nasmah na kai su ɗakin su, na wuce bathroom ɗin ɗakin nayi wanka na fito, natafi bedroom ɗina na saka kaya, sannan na dawo ɗakin nasu na haye gado nabi ko wannansu da addua, kana na kwanta tsakiyar su ina mai shafa addu'ar da nayi a jikina.

a hankali bacci ya dau ke ni can cikin bacci naji wayata na ruri,
idanuna a rufe na laluɓo wayar tare da ɗaga kiran na kai wayar kunne batare da na buɗe idanuna ba,
muryar sa na jiyo yana faɗin
"Kyakkyawa ta kinyi bacci ne?."
"Um." nace cikin magagin bacci yace
"To ki tabbata mun haɗu cikin baccin nan kiji, kyakkyawa ta kina jina?."
juyi nayi a hankali nadaɗa manna wayar a kunne na nace
"Eh." yace "Kiyi mafarki na kinji? kiyi mafarkin muna tare kina shayar da ni daɗi."
idananuna na bude a hankali, jin yan da amon sautin sa mai sanyi ya doki kunne na, a hankali na mai da idanun na lumshe ina jin yana faɗin
"I love You I love you too, please kiyi tunani na koda na seconds ne kinji? kiyi magana kyakkyawa ta zakiyi?."
sinyar kaina nayi da faɗin "Um."
wani nannauyar ajiyar zuciya ya sauke yace "Ina son ki kiyi baccin ki mai daɗi."
zare wayar nayi na aje a hankali na gyara kwanciya ta,
bawai ko dun na koma baccin ba maganganun sa ne sukayi tayi min yawo cikin ƙwaƙwalwa da zuciya ta, yayin da amon sautin sa mai sanyi ke yawo cikin kunnuwa ta.
a hankali na sauke numfashi..........!

Bani da Cj idan na matsa sainayi page mai tsawo to fa wayar zata iya ɗauke wa bakuma zaku samu koda kaɗin ɗin ne ba kunsan matsalar nepa da ake fama da shi yanzu so sai a hankali

Washegari da asuba kiran wayar sa  ce ya ɗaga ni a bacci, ko da na ɗaga kiran sassanyan muryar sa haɗe da yanayin muryar wan da ya tashi a bacci yace
"Kyakkyawa ta tashi kiyi salla kinji."
kai na gyaɗa kamar yana gani na a hankali yakuma faɗin
"Kin tashi?." cikin muryar bacci nace
"Eh." yace "Yauwa to je kiyi salla kiyi mana addu'a sosai kinji."
shiru ban amsa ba ina dai sauraran sa in da yaci gaba da faɗin
"Zakiyi mana ko?." a hankali nace "Eh."
"Aha to tashi muje bathroom ɗin muyi al'walar tare."
yunkurin sa naji na alamun mike wa, a sannu nima na mike na sauko a gadon, maganar sa na juyo yana faɗin
"Kada ki kashe wayar shiga bayin kiyi al'walar ina ji."
baki na turo gaba nace "Ta ya zanyi al'walar da waya a hannuna ka kashe wayar ka ai na tashi."
yace "A'a Please Mai kyau ki saka wayar a handsfree ki aje tare nake so muyi al'walar."
a hankali na tura kofar bayin na shiga yayin da wayar ke makale a kunne na, na saka wayar a handsfree na ajeta gefen bathtub, na haura saman toilet domin nayi sarki maganar sa na jiyo yana faɗin
"Wacce irin ruwa zaki zubawa korama ta mai sanyi ko mai ɗumi?, sa wayar kusa da shi na ji ɗumin sa nayi missing ɗin sa sosai."
shiru nayi ban amsa shi ba nayi sarki na na mike. a kasan raina nace
"Da sanyin nan ne zaka tambaye ni da wani irin ruwa zan yi sarki to ko zafi ake ai bazanyi sarki da ruwan sanyi ba."
baki na turo kamar yana gani na na mike tsaye ina kokarin fara al'wala yace
"Nace ki saka wayar kusa da shi naji ɗumin sa kinji kyakkyawa ta?."
"Ni al'wala zanyi." nayi maganar ina kashe wayar, nayi al'walar na fita.
kasan cewar babu hijabin da zanyi salla da shi cikin ɗakin sai na fita na koma bedroom ɗina, bayan na idar da sallar zamata na gyara na jingina da jikin garu ina azkar.
kamar daga sama naji an turo kofa, da sauri na ɗago sai ganin sa nayi ya mai da kofar ya rufe.
fuska na ɓata dan  naji tsoron yan da aka turo kofar babu ko Knocking.
tun daga bakin kofar ya kafe ni da ido,  yayin da yake ta ai kamin da wani sihirtaccen murmushi, a sannua ya tako in da nake ya ɗan rankwafo kaina sai da ya sumbaci goshi na kana ya ɗago yana yi min kallon cikin ido cikin muryar sa mai sanyi yace
"Kyakkyawa ta, ina fata kin tashi lafiya, nayi kewar ki sosai, ki ka hana ni jin ɗumin kaya na ta waya ko shiya sa nazo na jisa a zahiri."
ido na waro jin abin da ya faɗa, yaɗago ni cak yadire ni kan gado,
ya zare hijabin jikina.
a hankali yashiga sumbata ta yarika bin sassan jikina da kiss yana yi yana shafani da shinshinar jikina,
a hankali ya kawo bakin sa saitin kunne na a hankali yaɗan ja numfashi ya manna bakin sa jikin fatar kunne na ya sumbace shi tare da faɗin
"I love You."
babu shiri na lumshe idanuna dan har cikin jikina nayi amon sautin sa, sassanyan muryar sa

tarika yawo cikin jikina.
kokarin ture hannunsa da ya sauke kan ababen kirji na nayi, da sauri ya ruko hannun nawa, murya a cushe yace
"A'a kyakkyawa ta ki barni naji ɗumin kayana  idan kika hana ni kuma sai na shiga in da bakya so ɗin."
 shiru nayi ina jin yan da yake ai kin matse su, a hankali ya manna bakin sa kan nawa, yajima yana sosar bakina yayin da jikina yasoma karɓar sakon sa, a hankali ya zare bakin sa,a tare muka sauke nunfashi.
ci gaba da shafani yayi zuwa yanzun kam gaba ɗaya jikina ya sake.
shiru nayi ina jin yan da yake ai ka min sakwannin sa, nakuma kasa dakatar da shi.
nayi mamakin kai na na rashin kara junkurin hanashi abin da yake ta yi a jikina,
a hankali yarika janye rigata sama har ya haura da shi saman ciki na,
idananu na buɗe da sauri jin ya sauke hannunsa kan pant ɗina yana shafa shi haɗe da murza shi kasa.
cikin hanzarin na rike hannunsa,
sai na shiga ture kirjin sa ina faɗin
"A'a nidai ka bari."
hannayena ya rike duka biyu yazuba min ido a hankali cikin fizgar numfashi yace
"Ina so naji ya yakwana mu gaisa da shi, nakuma ji ɗumin sa bayan shi babu abun da zanyi, idan kuma kika hana ni to tabbas zan shiga na tantance da kyau."
ya karashe maganar da kashe min ido.
baki na turo gaba nace "Ni dai a'a."
hannayena ya matse cikin nasa yayin da ya sanya idanunsa cikin nawa  a hankali yace
"Please da gaske babu abin da zanyi ɗumin sa kaɗai zanji."
da sauri na mai da idanuna na lumshe sabo da irin kallon da yake yimin, a hankali ya saki hannaye na.
a sannu naji saukar hannunsa kan pant ɗina sai ya rika ɗan murza shi kasa, da sauri na yunkura na rike hannunsa, cikin hanzari ya juya hannuna ya rike da ɗaya hannunsa yayin da ɗaya hannunsa kuma ya janye pant ɗin yayi kasa da shi.
idanuna na rumtse da karfi,
da karfi na mirgina na juya gefe na ja riga ta kasa.

Matsowa in da nake yayi ya kwanto jikina, sai ya zura hannunsa ta kasan rigar a hankali ya cusa hannunsa cikin HQ ɗina, idanuna na rumtse jin yan da yake tura yatsar sa da yawo da shi ciki.
wani irin gantsarewa nayi  da sauri nakuma mirgina wa gefe.
"Washiiii Allah kyakkyawa ta bamu gama gaisawar bafa yana kokarin karɓar gaisuwa ta shine zaki raba sakani."
da sauri na mike zaune ina daɗa jan rigata kasa hararar sa nayi tare da murguɗa masa baki.
ƴar karamar dariya ya sake ya rungumo ni, yana cigaba da dariyar
bakin sa ya kawo saitin  kunne na yace
"Kai kinji yan da rijiyar nan ta kawo ruwa kuwa ko za'a ɗan sammin ne in ɗibi ruwan."
da sauri cikin matsananciyar jin kunya na kife kai na jikin kafaɗar sa ina cusa fuska ta cikin

gefen kirjin sa.
dariya sosai yayi ya ɗago kaina yana ci gaba da dariyar,
narufe idananuna gam-gam naki buɗe wa.
cikin muryar dariyar yace "Buɗe idon ki kiji wani magana."
kafaɗa na make ina mai da kaina cikin kirjinsa.
shafa kaina yayi a hankali ya furta
"Ina son ki kyakkyawa ta, a kullum kamar daɗa kara min sonki ake yi."
luf nayi a cikin kirjin sa ina juyo sautin bugun kirjin sa a hankali a hankali.
wayar sa ce tayi kara a sannu ya mika hannnu ya ɗauka, batare da ya ɗaga kiran ba,
ya leko fuska ta sai ya manna min kiss a goshi. ya ɗago kaina ya tallafe da hannayen sa idananunsa a kan fuska ta yace
"Madam zan tafi ki zauna da shirin tarba ta gobe,
kiyi tunani ko na seconds ne  kinji?."
sai ya mike ya sauka a gadon yaɗan zuba min ido tare da sakar min sassanyar murmushin sa sai ya juya ya fita.
a hankali na yi baya na kwanta jikin pillow tare da zubawa kofa ido, a sannu na maida idanuna na lumshe,
amon sautin sa mai sanyi murmushin sa mai taushi laffuzan sa masu taɓa zuciya da shiga jiki.
su suka yi tayi min yawo cikin ido kwakwalwa da zuciya.
a hankali na sauke numfashi tare da mirgina wa gefe na kifu da ciki, tare da yin pillow da hannaye na.
daɗa lumshe idanuna nayi ina mai daɗa lafewa jikin katifa, a sannu wani bacci mai daɗi ya ɗauke ni.....

Da yammacin ranar Ahmad yakuma zuwa sai dai ban bashi dama yayi abin da yake so ba wato taɓa jikina, naki barin su Nasmah su matsa ko nan da can, sassanyan murmushin sa da wasu sihirtaccen kallo su yayi ta ai ka min da su,
bayan magriba da zai tafi yaruko hannuna yace nazo na raka sa. har munzo bakin kofar parlour yace da su Naseem suyi gudu su riga mu zuwa gurin mota.
ai ko a guje sukayi waje,
nan ya samu ya rungume ne yayi ta sotsar bakina, sai da ya saukar min da kasalar jiki da ta zuciya kafin ya sake ni yana faɗin
"I love You!."
baya na yi na koma cikin parlour na zube kan kuje ra.
shiko a hankali ya juya yana mai sakin murmushin nan nasa yayi waje....
washegari ya kama ranar da zai dawo gidan nan, tun bayan la'asar ya shigo gidan,
ina ta ɗan zirga zirga na daga kitchen zuwa parlour da kuma sama,
kasan cewar yau weekend ne kuma hakan yayi dai-dai da makon karshen wata, duk rana irin ta yau su Zulai suna zuwa duba ƴaƴan su, ganin har yamma tayi basu dawo ba ga shi kuma abinci ya kare su Naseem kuma sai damina suke da suna jin yunwa, shine na shiga kitchen dan girka mana ɗan wani abu.
duk in da na gilma idanunsa a kai na, daga karshe sai ya biyo ni kitchen ɗin wai zai tayani ai

kin, na ɗauka wasa ne sai naga ya zage muka ci gaba da yi, sai dai idan yaɗan yi wani abun sai ya sake ya rungume ni ya kuma yi kissing ɗi na a haka a ka gama aikin....

Bayan sallar isha Ahmad da su Naseem ne zaune a parlour'n sama,
ina daga cikin bathroom najiyo karar wayata har sau uku ya katse a kuma kira, sai da nagama wanka ta kafin na fito.
na isa bakin gado in da wayar ke ajiye na zauna tare da ɗaukar wayar,
wani kiran ne yakuma shigo wa, da murmushi na gaɗa kiran ganin sunan Ukhtee ne ya bayyana kan screen ɗin wayar,
aje wayar nayi a kan cinyata tare da saka shi a handsfree, nayi sallama.
daga cikin wayar Ukhtee ta amsa tare da faɗin
"Ina yara na?." dariya nayi da faɗin
"Baki fara tambaya ta ya nake ina lafiya ba shine zaki tambayi yaran ki?, to suna parlour kijira suzo ki tambaye su lafiyar tasu ni bazan faɗa ba tun da ni ba a tambaye ni tawa lafiyar ba."
tace "Ai bazan tambaye ki ba tun da nima kin mance da ni, ƴaƴana kuwa na tabbata su basu mance da ni ba,
tukun na ma ɗazu ne Maama ki faɗa min wani batu wai Bappa yake faɗa mata wai kinyi aure da gaske ne, so nake ki faɗan da bakin ki dan nasan Bappa dai ba zaiyi karya ba."
baki na na rufe da hannuna ina dariya kasa-kasa nace
"La Ukhtee wai da ma bakuyi maganar da ke ba."
tace "Ni tambayar ki kawai nayi da gaske kinyi aure?, so nake naji daga bakin ki."
"Yi hakuri Ukhtee afwan nayi zaton munyi maganar nan ai..."
da sauri na waigo batare da na karasa faɗin abin da zan faɗan ba jin an zauna a gefe na,
fuska na ɓata dan sam ban san da shigowar sa ba, daɗa masowa jikina yayi sosai ya saka hannunsa ya zagaye ni da shi ta baya.
maganar Ukhtee na jiyo tana faɗin
"Ai dama nasan baki damu da ni ba nice kaɗai na damu da ke, ace har kiyi aure ban sani ba in da kin faɗa min wlh da zan zo Nigeria, ko kina so kice min bakiyi auren bane kike ta kame-kame."
"Wane ita ai aure ba karya bane, nine nan shaidar ki, au bata faɗa miki zata yi aure ko tayi bane Ukhtee?."
Ukhtee da ta ɗan yi dim jin muryar sa sai kuma tayi murmushi mai sauti tace "A'a bata faɗa min ba ai bata da kirki, barka da warhaka."
yace "Yauwa barka dai, to ayi mata afwa bata laifi ni na amshi dukkan laifin zamu gaiyace ki watarana."
tace "To Allah ya nuna mana."
yace "Amin amin to mun gode sai da safe."
dariya tayi tace
"Ya kamar ana kori na?." yace
"A'a wai bacci take ji." ya kalleni tare da ɗaga min gira da kashe min ido.
da sauri nace "Ni ban faɗa ba."
ai da sauri ya kashe wayar ya sumbaci kumatu na yace
"To ni ina ji azo a sani nayi."

Da mamaki ɗaya zuwa biyu nake lallon sa, kokarin sa na karɓar zancen, da kuma yan da naji ya juya harshen sa izuwa harshen larabci,  yana zuba larabci babu ko gargada
tamkar Balaraben asali.
kumatu na ya ja yace
"Kin ki ayi biki kinga gashi an fara cin tarar ki, wace ce ita?."
"Jika ce ga masarautar Saudi."
na faɗa ina kokarin mike wa, yaki bani damar yin hakan  ta hanyar daɗa rungumo ni jikin sa,
yace "Zamu gaiyace ta nan gaba dan ya zama dole ayi biki nan gaba dole waɗan da suka halarci taron su sami farin ciki, zan shayar dasu farin ciki kamar yan da kika shayar da ni."
a hankali yashiga zame towel ɗin jikina kasa, nonuwa na suka bayyana,
a sannu ya sauke hannunsa kan ɗaya ya matse yaɗan sunkuyo da kansa yana kare musu kallo,
mike wa tsaye yayi nima da sauri na mike ina kokarin barin gurin naje na sa kaya, sai ya ruko hannuna yazuba min narkakkun idanuwan sa a hankali yace
"Ina zakije kuma?."
"Kaya zan sa." nafaɗa a takai ce ina kokarin zame hannuna yace
"To zo kiji wani magana kafin kisa kayan."
cak ya ɗago ni ya dire ni kan gado kana yaɗan kwanto jikina.
nace "Nifa kaya zan sa ka kyale ni naje na saka kaya."
a hankali yaɗan numfasa kana yaɗan ɗago jikin sa ya saka hannu ya zame towel ɗin cikin ɗan fizgar numfashi yace
"Ni na yafe miki kizau na a haka kawai."
ya kife tafin hannunsa kan ababen kirji na a hankali Yashiga shafasu da matse su, ido ya lumshe tare da buɗe su a kaina wan da tuni suka jima da sauya wa,
cikin sixy voice yace
"An ya kin baiwa yaran nan nono kuwa? ka da dai ace kin ɗau ki hakkin su ki hukuntasu kan laifin da basa da masaniya a kan sa."
baki na turo gaba nace
"Sai kuma ka gansu haka da lafiyar su, ban yaye su ba sai da suka kai na yaye."
murmushi yayi yayin da hannunsa yake kan ababen kirji na yana ta faman matse su a hankali yaɗan mike ya rankwafo kaina ya kawo bakin sa saitin nono na yazuro harshen sa, ya lashe kan Breast ɗin,
wani irin shock ne ya shige ni har sai da na ɗan mike tare da gantsare wa, shiko ɗan ɗago kansa yayi ya kalle ni tare da ɗaga min gira sannan yace
"Naga basu yi kama da waɗan da aka sha bane."
baki na kuma turo, tare da matse idanuna jin yan da sakon sa ya shige ni, a kasan raina nace
"Sai aka ce kuma komai sai ka sani ne."
"Idan a kan ki ne ba."
ido na ɗan waro da mamakin fitar maganar tawa.
saukar bakin sa kan ababen kirji na
naji, yarika tsaotsar su da shafani tun ina ɗan tutture shi har na dawo bana ko iya ɗaga hannuna sai da ya kashe min jiki gaba ɗaya kafin ya ɗan ɗago ya zame towel ɗin gaba ɗaya.
ya haye kai na jikin sa na ɓari yashige ni,

ban iya yun kurin dakatar da shi ba dan gaba ɗaya ya saukar min da muguwar kasala,
yayi ta sarrafa ni yana sakin sambatu, yajima sosai yana abu guda ganin kamar bashi da niyyar kyaleni, sai na fashe masa da kuka ina faɗin
"Ni na gaji."
tamkar kukan nawa kai mi yake daɗa kara masa,
dun dole yayi release, yasulale kai na yana mai da numfashi..
ya zare jikin sa ya kwanta gefe na,
duk kanin mu numfashi muke sauke wa, a sannu ya sauka a gadon ya ruko hannuna ya mikar da ni muka shige bathroom a tare mukayi wanka muka fito...
yana saka kaya yafita yace zai je yayi wa su Naseem addu'a dan sai da yasa sukayi bacci kafin ya zo nan, bai kuma yi musu addu'a ba.
ni ko ina saka kaya gado na haye dan nagaji ga kuma baccin da nake ji.
zuwa can yashigo ya haye gadon ya kwanta a gefe na. fuska ta ya leko
yace
"Kyakkyawa ta akwai kari ne?."
yayi maganar cikin zolaya,
baki na turo ina kokarin juya fuska ta taɗaya gefen.
yayi saurin ta ro ni ya matse ni a jikin sa, yayi ta zolaya ta da jana da wasa, har sai da ya sani fashewa da dariya.
sai ya tsaya ya kuramin ido yana kallon yan da nake darawa,
yaja kumatu na yace
"Gaskiya ina da sa'a a rayuwa ta."
sai ya daɗa rungume ni, ya manna bakin sa kan nawa yayi kissing ɗin sa kana ya ɗago, yana yi min kallon cikin ido, kasa jurewa kallon nasa nayi sai na lumshe idanuna....

Washegari da safe haka yaki kyale ni sai da ya sami abin da yake so,
wunin ranar kuwa bai leka ko nan da can ba muna tare, sai yammma yaje gidan sa, bai jima ba kuwa ya dawo.
akwanaki biyun da Ahmad yayi a gidan nan ya nuna min tsantsar so da kaunar da yake yi min.
bayan kwanaki biyun kuwa daya koma yakuma dawo wa,
a lokacin yasa zuciya ta yafara yin sabo da shi.
ko da ya gama yin kwanakin zai tafi har nake jin bada ɗi....

Bayan wani lokaci tuni zuwa wannan lokaci sai da Ahmad ya tabbatar daya dasa wani abu mai muhimmanci a zuciya ta,
sai dai sam naki yarda kan cewa so ne, nafi yar da kan sabo ne kawai.
a yanzu nakan zauna muyi hira da shi sosai,
yanzu har na koya idan ya zolaye ni nima nayi masa,
akuma duk san da ya bukace ni nakan amin ce batare da tirjiya ba....

Yau yakama Ahmad zai dawo gida na,
tun da yamma na shiga kitchen domin na shirya masa abinci da kaina, dan aduk san da nayi masa abinci da kaina yarka santi da nuna yabawa sai ya daɗe yana yaba min.
sai daf magriba na gama nashiga wanka, ina fita na na saka kaya na haye kan sallaya, kasan cewar nayi al'wala.
bayan na idar da sallah mikewa nayi na je na ɗau waya ta, na laluɓo number sa, ganin har magriba tayi bai iso ba, iwar haka ai ya daɗe da zuwa gidan.
har na dannawa number sa kira sai na koma na she, na aje wayar na cigaba da wani da muwa.
har aka kira sallar isha nagabatar, har wajen misalin karfe koma saura kwata bai iso ba.
sai naji duk babu daɗi nakuma ji ina son sanin dalilin daya tsayar da shi har wannan lokacin.
a sannu na turawa number sa kira,
wayar tayi ta ring ba'a ɗaga ba har ta yanke.
a hankali nakuma mai da kiran, shima har na fidda ran daga kiran sai na ga an ɗaga, shiru na yi banyi magana ba,
daga can cikin wayar najiyo muryar Rasheedat tana yin sallama.
na amsa sallamar tare da faɗin
"Ina yini Aunty Rasheedat ya gida."
murya ɗauke da murmushi tace
"Lafiya lau HAMDAH ya yarana suna lafiya, kifaɗa musu ranar weekend zan zo na ɗauke su."
nace To.
dariya ta yi tace
"Kingan shi shiru bai iso ba ko, kinyi tunanin na rike miki shi ne? to babu ruwa na, in yazo ki titsiye shi ya faɗa miki in da yaje yakai dare dan nima yanzu na ganshi, ya dai shiga wanka yanzu, zaki ganshi yanzu insha Allah dan nasan wannan ɓarin jikin da yake alla-alla yake ya isa gare ki."
murmushi nayi cike da jin kunya nace
"A'a wlh nafi zaton yana wajen ne ma."
cike da zolaya tace "A'a faɗi gaskiya dai."
da sauri nace da ita "Sai da safe Aunty Rasheedat."
dariya tayi tace "To Allah ya kai mu..........!

Muna zaune a parlour muna kallo, har su Nasmah sukayi bacci na kwashe su na kaisu ɗaki, sannan na dawo parlour'n na zauna.
tun daga step's najiyo takun sa haɗe da kamshin sa, da sauri na waigo, karaf muka haɗa ido muka sakar wa junan mu murmushi.
yakaraso ya zauna kusa da ni tare da sumbatar kumatu na yace
"Bakiyi bacci ba."
kai na gyaɗa sai kuma na turo baki nace
"Ina ka je kayi dare?, Aunty Rasheedat tace min ita ma yanzu ta ganka."
yace "Zan ce naje gurin wata budurwa ta shine ta rike ni nayi dare."
kaina na kawar tare da ɗaga hanci sama.
yace "In faɗa miki tarika miyin daɗaɗan kalamai shiya sa nayi dare a gurin ta."
"Ya isa."
na faɗa ina mike wa tsaye na sa kafa zan bar gurin, da sauri ya ruko ni ya janyo ni nafaɗo jikin sa, sai ya rungume ni.
dariya sosai yayi, fizge jikina nashiga yi ina faɗin
"Ni ka kyale ni ka tashi ka koma gurin ta kaje can kaci gaba da jin zantuka masu daɗin."
dariya ya kuma yi yace
"A'a ina kuma zakije tun bangama baki labarin yadda hirar tamu ta kasan ce ba."
kunnuwa na na toshe da hannaye na nace
"Bana bukata ka tashi ka tafi kaje kai da kake bukata kaje ka kara ji."
da kyau ya daɗa rungumo ni cikin muryar dariya yace
"Sha kurumin ki Ahmad naki ne ke da Rasheedat kun maye zuciyar babu ɗan ɗigon gurbin da wata zata samu ta tsugunna, babu wacce naje gurin ta zance babu ita ba kuma za'a yi ta ba, ma'aikatan kamfanunnukan Alhaji na ne muka yi zama da su shiyasa na makara har dare ayi min afwa, ba zance naji ba."
baki na taɓe nace
"Ni ina ruwa na ma idan gurin watan kaje, meye damuwa ta."
saida dariyar da yake yayi yazuba min ido kana hankali yace
"Akwai ruwan ki da kuma damuwar ki sabo da kina sona, ga kuma kishi na nan cikin idanuwan ki."
hannunsa na bige daya kai shi karkashin ido na nace
"Babu wani abu a tare da ni kada ma kaga na tambaye ka in da ka tsaya kayi tunanin wani abun ne."
yace "Haka ko?, to kalli cikin ido na kice bakya sona, ki kalli cikin kwayar ido na kice bakya sona, oya kalla ki faɗa yanzun nan."
kawar da kaina nayi na turo baki gaba nace
"Ni ka kyale ni."
dariya yayi sosai har yana buga kafa ya manna min kiss a kumatu ya ɗago tare da faɗin
"Aha yarin ya kina wasa, ni ɗin fa bana wasa bane jarumi ne ni nan da kike gani."
baki na taɓe nace
"Jarumtar me?." yace "Na iya sace zuciya mana, Allah mai girma yaji tausayin bawan sa mai wahala da dakon so a zuciya da ilahirin jikin sa, ya amshi addu'a ta ya sa miki sona a zuciyar ki,

kai gaskiya ni mai sa'a ne."
"Waya faɗa maka kadai na yaudarar kanka dan na tambaye ka in da ka tsaya,
ka laune maganar ta koma wani abu daban, kyale ni natafi na kwanta."
nayi maganar ina kokarin zame wa a jikin sa.
daɗa rungumo ni yayi yashiga zolaya ta,har sai da yasani nayi dariya kana ya ɗago ni cak yayi cikin bedroom da ni.....

Washegari yau natashi da kewar ahalina, har da Mama mai awara,
ga ba ɗaya bani da walwala yau, Ahmad yana cikin ɗaki nafito parlour na zauna nayi jugum, tabbas yau ina cikin kewar su sosai, Allah sarki Mama mai awara
"Ko tana ina?." nayi wa kaina tambayar, hawaye ne suka ciko ido na Allah sarki wata uwa Mama mai awara, tabbas bazan taɓa mancewa da ke a rayuwa ta ba, ke tamkar uwa ce gare ni.
ji nayi an dafa ni a hankali na ɗago na zuba masa ido, a sannu ya zauna a gefe na yaroko hannuna yace
"Me ke damin ki kyakkyawa ta?."
ido na lumshe tare da kuma buɗe wa sai na kuma rike hannunsa gam nace
"Family na ina jin kewar su, har da Mama mai awara matar data rike ni tamkar ƴar data haifa, tayi min gata irin wacce uwa take yiwa ɗiyar ta, badun ita ba awancan lokacin da na rasa raina nida abin da suke cikina, ta saida makwancin ta da duk wani abun da ta mallaka tabiya kuɗi akayi min CS."
hawaye ne suka zubo min sai na yi shiru da maganar dan nasan zan iya fashewa da kuwa.
a hankali ya janyo ni jikin sa ya rungume, yashiga share min kwalla yace
"Kiyi hakuri babu abin da yake tabbata har idan ya zamo fararre, bagashi yanzu kina bada labari ba, yazama tarihi komai mai wuce wa ne har idan yazamana yana da mafari,
kishir ya gobe mukai mata ziyara."
da sauri na ɗago da murmushi yayin da hawaye ke ci gaba da sauka a idona nace
"Da gaske?." kai ya gyaɗa min shima yana murmushi,daci gaba da share min hawaye...
bai gushe ba har saida yaga ya sanya ni dariya...

Washegari kamar yanda yafaɗa motar mu ta hau hanyar Jos, bayan munyi wa su Bappa sallama, kwarai Bappa yaji daɗin jin cewa gurin Mama mai awara zamu je, yayi ta zuba mana addu'a da fatan isa lafiya, yaku ce mu gaishe ta sosai da sosai.
ni da shi muna gaba Naseem da Nasmah suna baya, dan yaki direba ya biyo mu yace tafiyar family ne dan haka direba yayi zaman sa.
da misalin karfe 2 na rana muka iso cikin garin Jos,
daga nan nafara yi masa kwatance har muka iso Narkuta,
wani numfashi na sauke a bayyane lokacin dana ganni dai-dai kan kwalbatin shigan layin gidan Mama mai awara,
nan take tunanin rayuwa ta ta baya tashiga zuwar min, bazan mance ranar dana zo garinnan ba akan wannan kwalbet ɗin na zauna har dare, har wasu mutane suka zo amota suna yimin tayin shiga na biyo su,
idanuna na rumtse da karfi ina kokarin mai da hawayen da ya ciko min ido.

muryar sa najiyo a hankali
"Kibar tunanin nan sam bashi da amfani tuna irin haka sai dai ya sanya maka damuwa da ɓacin rai, ina zamu bi?."
a hankali na buɗe idanuna da tuni hawaye ya gangaro min, nayi masa nuni da hannu nace
"Mu mike nan."
a hankali ya sa kai cikin layin, sai ɗan kalle-kalle nake, garin ya canza anyi sabbin gine-gine, nayi ta masa nuni da hannu har muka iso kofar gidan Malam Musa, dakyar shima na iya gane wa dan an yiwa gidan fenti ga kuma sabbin gine-ginen daya zagaye su.
kallon sa nayi nace "Ina zuwa bari na shiga na tambayi Zainabu gidan da Mama ta koma sai ta nuna mana muje."
kai ya gyaɗa, na buɗe marfin motar na fita.
da sallama nashiga gidan, ga mamaki na wasu mata na gani zaune a cikin gidan suka amsan sallama na karaso ciki, ina ta ɗan raba ido ko zan ga Zainabu,
na gaida matan suka amsa suna faɗin Sannu da zuwa, nace "Yauwa dan Allah Zainabu tana ciki ne?."
ɗaya daga cikin matan tace
"Wata Zainabu?."
nace "Matar Malam Musa." sukace "Au wai ai sun jima da tashi a gidanan na sun koma wata unguwar daban."
da sauri nace "Innalillahi dan Allah wata unguwar suka koma? ko za'a nuna mana ko ayi mana kwatance."
sukace wlh sam basu sani ba, suma haya suke ana gobe zasu tare a gidan su kuma suka bar gidan, sam basu san wata unguwa suka koma ba.
cikin sanyin jiki na juya nayi musu sallama na fita,
jiki ba kwari na shige cikin motar na zauna
duba na yayi yace
"Ya dai tayi miki kwatancen gidan ne?."
kai na girgiza a hankali nace
"Bata nan wasu ne a cikin gidan,kuma wai basu san in da suka koma ba."
wasu hawaye ne masu ɗumi suka zubo min sai nayi saurin sunkuyar da kaina.
a hankali ya dafa kafaɗa ta yace
"Kiyi hakuri idan da rai da rabo wata rana zaku haɗu."
kai kawai na girgiza, a hankali ya share min hawayen yace
"Ya isa haka na roke ki kada ki sake zubda su ina jin zafin su har cikin dai na, Please na roke ki."
ya haɗe hannayen sa biyu.
kai na girgiza masa a hankali na karasa  share hawayen.
a sannu yaja motar muka bar gurin.
muna fita bakin layin unguwar,na juya da kallo na ta gabar wato hanyar Bauchi, ya lura da hakan sai ya saka hannu ya juyo da fuska ta a hankali cikin tausasshen lafazi da son sama min karfin guiwa yace
"Zamuje shima idan Abba ya daɗa huce wa."
yafaɗi hakan ne kawai dan sama min nutsuwa da kwanciyar hankali,

a can kasan zuciyarsa sa kuwa bayan Bappa ne sukayi masa ca,
"Lallai mutum abin tsoro ne, ka haɗa tsihiri da mutuwar ka sabo da kasan duk mai halin irin naka Allah yana musu talala ta hanyar barin su a duniya su shafe shekaru masu yawa, tabbas akwai hisabi ranar gobe kiyama."
duban sa nayi jin yaja kwafa afili nace
"Ya dai?." kai ya girgiza min da sauri yace "Ba komai ina tunanin tafiyar dake gaban mu ne mukwana a cikin gari  kawai, mu huta gobe da safe sai mu juya."
nace "A'a kawai mu tafi."
ya juya ya dubi su Naseem da tuni suka bingire da bacci yace "Sun gaji kiga baccin su nawa, kema kuma nasan kin gaji."
nace "Ni dai mutafi gida kawai."
yace "To shi kenan."
ya haura hanya muka ɗau hanyar Abuja...
kasan cewar da abincin mu muke tafe bamu sha wani wahalar yunwa ba,
ana kiran sallar magriba muna isa ciki Abuja,
yanayin gosulo da muka tarar bamu shiga gida ba sai bayan sallar isha.
koda ya gyara parking na buɗe marfin motar na fito,
ina saka kafata kasa naji wani jiri ya fisge ni, da sauri na dafa jikin motar, har yafita ya zaga yaɗau ki Naseem da Nasmah ina dafe da jikin motar,
yazo in da hake yana gyara rukon su yace
"Muje ko?."
a hankali na mike tsawo na yayi gaba nabi bayan sa a hankali ina jin yan da jirin yake ta cigaba da fizgata, a haka muka shiga ciki direct sama ya haura, niko a parlour'n kasa na zube kan kuje ra, tare da kife fuskata jikin pillow'n kujera, na rumtse idanuna da karfi jin juwan nadaɗa fisga ta.
ya kai su ɗakin su ya kwantar da su kana ya sauko kasa yazo in da nake ya zauna kusa da ni.
yasa hannunsa ya ɗago ni yana faɗin
"Shi yasa nace mukwana a cikib Jos sabo da nasan zaki wahala, kika ce sai dai mu juyo, kin ga irin ta ko."
murmushin karfin hali nayi dan yanayin da nake jin yana son wuce tunani nace
"To baga shi mun dawo ba, ai mun huta basai  goben mun yi ta tunanin kuma hawa hanya ba"
Yaruko lips ɗina  yace "Wannan baki da duk abin da aka faɗa sai yakawo hujja".
dariya nayi nace "To ai rainon ka ne."
shima dariyar yayi yace
"Au haka zaki ce."
gira na ɗaga ina murmushi. gefen fuska ta ya shafa kana ya ruko hannuna yace
"Taso na taimaka miki mu haura ki wasa ruwa zaki ji karfin jikin ki."
a hankali naɗan yunkura ya ɗago ni ya mikar da ni, idanuna na ɗan rumtse kana a hankali nashiga ɗaga kafata, yana tallafe da ni har muka haura sama.
a bakin gado ya zaunar da ni kana ya shiga taimaka min na rage kayan jikina,
ya kuma ruko hannuna muka muka shiga bayi wankan ma sai da ya taimaka min gaba ɗaya jikina ba kwari ga jirin nan yaki bari na, ga masifaffen ciwon kai.
muna fita daga bayin doguwar rigar bacci kawai na zura na haye gado.
bakin gadon ya zo ya shafo gefen fuskata a hankali na buɗe idona na zuba masa yace

"Kyakkyawa ta tashi kiɗan ci wani abu mana zaki daɗa jin karfin jikin  ki."
kai na girgiza a hankali na mai da idanuna na rufe, ya hayo gadon ya kwanta tare da janyo ni kijin sa, a hankali bacci ya ɗauke ni...
can cikin dare jikina yahaɗa zafi rau sai ɓari nake,ina daɗa shigewa cikin jinin sa,
da sauri yabuɗe idanunsa ya daɗa rungumo ni jin yan da jikina ya ɗau zafi yamike da sauri yana faɗin
"Subhanalla kyakkyawa ta zazzaɓi ne haka Innalillahi."
gaba ɗaya ya ruɗe yarika rungume ni yana yimin sannu, ya ɗago ni yana faɗin
"Taso muje asibiti jikin ki yayi zafi sosai."
kaina na kwantar a kirjin sa na rirrike sa a hankali nace
"A'a dare yayi sosai kada muje zai sauka zuwa safiya."
a ruɗe yace "A'a kyakkyawa ta kijin ki yayi zafi sosai muje kawai."
duk yan da yaso mu tafi naki fir.
yana zaune ina rungumo a jikin sa a haka gari ya waye.
da asuba ya kaini bayi da kansa yayi min wanka a daddafe nayi al'wala shima yayi, bai barni na taka da kaina ba ya ɗauko ni ya fito da ni,
ya shinfiɗa mana sallaya a zaune nayi sallar in da shi kuma ya ja mana sallar.
muna idar wa na sulale kan sallayar.
shiko da sauri ya mike yaje ya ɗau wayar sa yakira family Dr su, yace yazo yanzu yayi masa kwatancen gidan.
kana yazo ya ɗaga ni a kasa ya mai dani kan gado.
batare da ɓata lokaci ba Dr ya iso, ya bada umurnin a barsa ya shigo,
har cikin parlour'n sama ya bashi umurnin shigo wa,
kana ya shigo ya saka min hijabi kan rigar baccin da yake jikina, ya ɗago ni ya tallafo ni jikin sa muka fito parlour, ya zaunar dani kan kujera kana shima ya zauna kusa da ni,
a hankali na kwantar da kaina jikin hannun kujera, ina jin Dr yana tambayar me ya sa me ni,
yace masa tafiya mukayi jiya mun wuni a kan hanya,muna dawo wa shine zazzaɓi ya rufe ta.
Dr ya ɗanyi  rubuce-rubuce kana yaɗa go yace "Baza a bata magani ba sai anyi mata test."
Ahmad
yace "To." kana ya dube ni yace
"Bari a ja jinin ki ayi test dan asan maganin daya dace da kisha ki warke da wuri ko kyakkyawa ta."
yayi maganar yana ɗan jan hijabin jikina ya ɗan tattaro shi yaciro hannuna ya ruko hannuna.
Dr ya taso yaja jinina kana ya tafi.
in da aka ja jinin yarika mulmula min a hankali,
shiru nayi ina kwance cikin kirjin sa, a haka bacci ya fara fizgata,
ganin haka sai ya gyara zaman sa da  kyau ya gyara min kwanciya ta cikin jikin sa.
nan da nan bacci ya ɗau ni...

Acikin baccin  narika jin magana, a hankali na buɗe idanuna, maganar Dr ne ya doki kunne na
"Congratulations ranka shidaɗi an sami karuwa Madam tana ɗauke da juna biyu."
wani irin waro idanuna nayi na mike zaune.
Ahmad kuwa mike wa tsaye yayi zumbur yana bin likitar da wani irin kallo mai cike da ɗin bin

mamaki cikin rawar murya yace
"What! mekace!?, kasan me kake faɗa kuwa?."
sai kuma ya girgiza kansa sannan yace
"Kodai kunnuwa na sun jiye min ba dai-dai bane."
murmushi Dr yayi tare da mike wa tsaye takar dar dake rike a hannunsa ya mika masa yace
"Wannan shine sakamakon test ɗin da mukayi, kuma ya nuna tana ɗauke da ciki, amma idan ana kokonto za'a iya zuwa wani asibiti ayi gwaji ta hanyar yin scanning domin tabbatar wa."
takardar da ya mika masa yashiga dubawa har hannunsa na ɓari, wani uban kabbara ya sake, ya juya ya dubi gabar yasulale kasa yayi sujjada............!

Kuyi hakuri na rashin jina kwana biyu kanwa ta ce tayi ɓari so dole nice na zauna a kanta na tsawon kwana ɗaya da wuni ɗaya ban sami damar hawa online ɗin bama bare na shaida muku.

Mommyn Twins ce

26

Ya ɗago tare da ɗaga hannunsa sama yace
"Ya Allah ya Ubangijin rama Allah nagode maka  Nagode maka Allah, ya buwayi gagara misali ya Hayyu ya Kayyum, bana da tsumi bana da dabara maikowa mai komai duk kai kaɗai kake da

su,
hakika Ubangiji na mai girma ka azirtani da abin da bana da wayo da ikon iya bawa kai na, duk arziki na bazan iya baiwa kaina ba kai kaɗai kake da ikon iya bani, Allah Nagode maka! Allah na gode maka!! Allah Nagode maka!!!."
yakuma mai da kansa yayi sujjada,
yana mai cigaba da kwararo addu'a da kirari wa Allah buwayi gagara misali.
kana ya ɗago da sauri yamike yazo ya rungume ni tsam yana faɗin
"Hakika HAMDAH ke alkhairi ce a gate ni, ke fitala ce mai haske duhun dayayi shekara da shekaru, na gode wa Allah daya mallaka min ke amatsayin mata kuma fitila ga rayuwa ta, HAMDAH ke ta daban ce ina sonki ina sonki HAMDAH inayi miki son dayafi wanda nakewa kaina!!."
yadaɗa kankame ni a jikin sa.
Dr da yake tsaye yana bin mu da kallo da murmushin taya murya,
yayi mana sallama yace zai tafi,
ai da sauri Ahmad ya sake ni yace
ya bashi account number ɗin shi, nan take yayi masa transfer ɗin 3 Miliyan.
yace tukuicin sa na sanar da kyakkyawan zance mafi girma, wan da tun da yake ba'a taɓa yi masa albishir da kamar saba.
likitar yarika murna dayi masa fatan isowar baby lafiya ya bar gidan bakin sa har kunne, bayan ya aje mana maganin da yazo da shi.

Ahmad daya kasa zaune ya kasa tsaye yarasa inda zai sa kansa dan farin ciki, yadube ni yana faɗin
"Me kike so kyakkyawa ta me kike so a duniyar nan? kifaɗa min ko mene ne shi ashirye nake nayi miki shi koda zai zamo gurfaniwar dukiyar dana mallaka da dukkanin kadarori na, me kike so nayi miki tukuici
da shi? motoci gidaje kamfanoni acikin kasar mu ko a kasashen waje, faɗa min duk abin da kike bukata zanyi miki shi koma mene ne, faɗa min yanzu kyakkyawa ta."
kai na rausayar gefe jin kai na nadaɗa sara min a hankali cikin yanayin jin zazzaɓi nace
"Ni bana son komai wayyo kaina."
na dafe kaina dake cigaba da sara min.
da sauri ya mike yace
"Bari na ɗauko ruwa kisha magani zai dai na in sha Allah."
da sauri yaje ya ɗauko gorar ruwa cikin fridge yadawo in da nake, ya tsiyaye ruwan cikin cup ɗin da ya haɗo da shi,
kana yaɗau laidar maganin ya curo su daga cikin laidar, kamar yadda yagani a rubuce haka ya cicciro su.
kana ya tallafo kaina yace
"Buɗe bakin ki na saka miki."
da sauri na kawar da kaina yayin da naji zuciya ta ta hautsune jin warin maganin nace
"A'a zanyi amai."
yace "Ya ilahi bazakiyi ba, buɗe baki kisha ga ruwa nan kusa."
cikin zubda kwalla na girgiza masa kai da faɗin

"Zan yi mana kabar shi kawai zan warke a haka basai na sha magani ba."
ido ya waro da karfi ya furta
"Wane ni wlh ban isa ba, kin san kuwa zafin zazzaɓi yana iya zubda ciki, ki tai make ni dan Allah ki ceci rayuwa ta kisha maganin nan ki samu ki warke kada ya janyo min babban asara, na roke ki dan Allah ki sha, ki taimaka min ni kaɗai iyaye na suka haifa ki tai make ni abin cikin nan yafito lafiya, naji a raina inada jinina aduniya."
ya juyo da fuskata yace
"Sha in Allah ya yarda bazakiyi amai ba."
idona na rumtse da karfi na ɗauke numfashi tare da buɗe baki ya zuba min maganin kana ya bisu da ruwa.
da kyar sai da nayi kamar ina yi kafin suka wuce.
ido na ware da karfi jin zuciya ta na wani irin tashi cikin hanzari na tallafe kansa tare da manna bakina da nashi nashiga tsotsar bakin sa.
a hankali a hankali nashiga sauke numfashi, yayin da aman yake kwanciya a hankali.
sai na lumshe idanuna a hankali ina mai cigaba da tsotsar bakin sa,
a hankali kasan tuwar mu da Ya SALEEM a irin wannan lokacin yafara zuwar min, sai na buɗe idanuna da sauri a sannu na zare baki na daga nashi.
shiko ido yakura min da yanayin mamaki sai kuma ya tallafo kaina yana kokarin kuma haɗe bakin mu.
da sauri na kwace kai na na turo baki gaba,nace
"Bana ce maka zanyi amai ba."
murmushi yayi yace
"To baga shi kin mai da aman ba, zo in kara kwantar miki da shi."
kafada na make ina mai cigaba da turo baki gaba.
da sauri ya mike cikin rawar jiki yace
"Ina zuwa bari naje na sanar wa su Bappa wannan dadda ɗan albishir ɗin."
ido na waro nace "A'a kada kaje."
kafin na rufe baki ma yayi gaba.

A kofar side ɗin su Bappa ya haɗu da shi yana kokarin fita.
ganin yan da yake ta washe ba yasa Bappa faɗin Ahmad "Wannan farin ciki haka me ya faru."
cikin matsananciyar farin cikin daya ke jin kansa ciki yace
"Bappa Malam HAMDAH tana da ciki, yanzu likita ya tabbatar min da haka."
Bappa ya faɗaɗa fuskarsa da annuri yana faɗin
"Masha Allah Allah abin godiya alhmdllh Allah mun gode maka, kai lallai wannan abin farin ciki ne, Allah ya ɗaiyiba yaraba lafiya."
Inna Wuro dake ta ciki tana jiyo duk abin da suke ciki,
tayi murmushi mai bayyana farin ciki, ta girgiza kai tare da faɗin
"Yaran zamani kenan wai shi ya ɗauki kafa yazo faɗar matar sa na da ciki."
takuma yin murmushi tana faɗin
"Dole kayi murna Ahmad lallai wannan abin farin ciki ne."

Anan kofa kuwa Bappa yayi ta zuba musu addu'a da fatan isowar abin dake cikin duniya lafiya,
yajuya cike da ɗin bin farin ciki, shiko Bappa ya koma ciki, yana shaida wa Inna Wuro.
tayi dariya tace "Ai duk ina jin ku murna ya hana shi sukuni."
Bappa yace
"Ai dole yayi murna abune sabo a gare sa wan da ya jima yana sumayar sa sai gashi kwasam Allah ya ai ko masa da shi, kin ga kuwa dole farin cikin sa yagaza ɓuya."
tace "Haka ne kam lallai muma munyi farin ciki kwarai aure yayi albarka."
Bappa yace "Haka ne kuwa kwarai da gaske."
haka sukayi ta nuna farin cikin su
da sam barka da fatan isowar baby duniya cikin koshin lafiya...

Ahmad kuwa yana juyawa daga gurin Bappa Rasheedat ya kira a waya cikin farin ciki yasanar mata,
ihun murna Rasheedat ta sake tace "Ina HAMDAH haɗa ni da ita dan Allah."
yace "To bari na kai mata."
ai bata jira ya karasa maganar ba ta kashe wayar da sauri ta zari matafin ta da makullin mota tayi waje.
Ahmad yana tafiya yana daddanna wayar sa nan da nan yashiga posting wa ƴan uwa da abokan arziki, yana faɗin a taya shi murna..

Ina kwance a kan kujera in da ya barni yadawo ya same ni,
ya karaso in da nake da sauri ya sunkuyo ya sumbaci goshi.
ido na lumshe tare da buɗe su a kan a hankali nace
"Yanzu kaje ka faɗa musun ne?."
baki ya washe yace
"Eh mana ai dole duk wani wan da ya sanni yasan wannan labarin."
ya zauna ta gurin kafafu na kana ya ɗago kafafun nawa ya ɗaura su kan cinyar sa, a hankali yashiga matse su.
yana faɗin
"Sannu kinji kyakkyawa ta baki dai jin ciwon ciki ko?, iya ciwon kanne kaɗai?."
ban tanka shiba sai lumshe idanuna danayi..
kira yayi ta shigo wa wayar sa yana ɗagawa yana faɗin yagode yagode, gaba ɗaya bakinsa yaki rufuwa...

Acikin ƴan mintina Rasheedat ta iso gidan tana haurowa parlour'n sama ta taho da gudu ta rungume ni daga kwancen da nake, cikin sananin farin ciki tace
"HAMDAH kai sannun ki da kokari ashe dai zamuga jinin mu Allah ya fito mana da shi lafiya."
ta mike ta sauri ta rungume Ahmad tana fadin
"Aboki wayyo Allah narasa yadda zan sa kaina dan farin ciki,
tabbas yau na daɗa yarda Allah bai mance da mu ba."
dariya yayi yana daɗa rungume ta a jikin sa yace
"Kwarai kuwa Kawa Allah baya bacci."

Haka suka yi ta nuna farin cikin su kamar zasu saka ni cikin jikin su.
suka rika tambaya ta me nake so, Aunty Rasheedat tace me nake jin kwaɗa yin sa ta dafa min.
nace ba komai.
kan kace me labari ya karaɗe yan uwa da abokan arziki.
ranar wuni Aunty Rasheedat tayi a gidan sai dare ta koma.
washegari da sassafe Ahmad yaje gidan su,
yau ƴan gidan sun sha mamakin ganin yan da yashigo da farara hatta Sakeenat yau sai da ya amsa gaisuwar ta.
ɗakin Hajiya Karima ya shige, tana ganin sa ta faɗa fuskar ta da murumshi.
ya nimi guri ya zauna bayan sun gaisa ya dube ta fuska ɗauke da masananciyar farin ciki
yace "Hajiya wani albishir nazo miki da shi."
zama Hajiya Karima ta gyara ta washe baki tana faɗin
"To Ahmadu ɗan Sabil na bada goron kar ɓar albashir fari soll."
yace "Hajiya HAMDAH nada ciki Hajiya ashe nima zan haihu?."
wani irin zabura Hajiya Karima tayi, sai da ta zamo bakin kujera ta buga kirji ta waro ido tare da faɗin
"Me ne ciki!!?."  wani irin murmushi yayi mai kunshe da ma'anoni daban-daban kana yace
Hajiya kema kin ji abin a bazata ko? ai nima haka naji abin kamar almara."
dariyar yake tayi sai kuma ta kama kame-kame tashiga faɗin
"La..laa..ikon..Ikon.. Allah...to ciki..
ciki, kai masha Allah lallai kuwa wannan shine bazata bayan fidda rai ga samu sai ga samun kuma, kai amma nayi farin ciki naji daɗi sosai, ashe zanga jika na, kai Allah yayi albarka yaraba lafiya, Eh Allah ya raba lafiya."
"Amin amin." yafaɗa yana mike wa tsaye yace
"To Hajiya ni zan koma."
tace "To a gaida gida a gai da min me cikin."
yace to kana ya sa kai ya fita..
yana fita Hajiya Karima ta saki wani uban ajiyar zuciya tabigi kirji tace
"Tabɗijam ciki!? kenan hakan na nufi Ahmad zai haihu yasami magajin dukiyar sa, wato wannan shigiyar yarin yar tana kokarin zuguza min shiri shine har da yin ciki, bayan ban taɓa kawo hakan cikin lissafi na ba, nasawa raina bazai haihuwa ba shine zata zo ta yi kokarin haihuwa masa, ina bazai yiwu ba da sakel wlh!...."

Acan cikin garin Bauchi

Abba ne da Ummi tafe cikin mota a hanyar su na komawa gida bayan dawo war su daga asibiti dubiyar wata ƴar uwar Ummi da ba lafiya,
suka biya ta gidan mai domin su sha mai,
tun daga farkon shiga gidan man layi ne har cikin gidan man,
Abba da yake kokarin sako kan motar sa cikin gidan man yaɗan yi jim yana bin layin da ido.

Ummi tace "Abba'n Fauzan wannan layin idan muka shiga ai sai mukai kusan dare ma layin bai iso kan mu ba, duba fa gamasu jaraku da suke acikin motoci sannan ga su motocin kansu, yaushe za'a basu har a bamu."
Abba yace
"Gaskiya kam bari mu koma gida kawai nasa direba yafito ya sha man ko ba a nan ba, tun safe ake layin nan motoci sai dađa zuwa suke zamu ɓata lokaci kam muje gida kawai."
Ummi tace "To in ban da mutane ma ga wasu gidajen mai da yawa wađan da naga babu ko layi wasu bai fi mota biyu zuwa uku ba, baza su je can susha man ba sai suzo nan suyi tayin layi haka."
Abba yace "To ai sauki ake so shiyasa ake wa gidan man layi, ai ba nan kađai ba idan da zaki zaga garin nan kiga gidan mai me irin sunan wannan gidan man zakiga layi kamar haka koma fin haka,
man su na da sauki sosai kuma litar su na da kyau,
an ce wai mai gida jen man ne tace a rika sai da shi a farashin da yanzu suke sai dawar shiyasa duk gidajen man ta zakiga irin wannan layin."
kai Ummi ta jinjina ta đaga kan ta tana duban sunan gidan man. tace
"*HAM'NAS CO PETROLEUM NIGERIA LIMITED* wato mace ce mai gidan man?".
Abba daya juya akalar tafiyar tasu izuwa gida yace "Eh mace ce."
tace "Lallai tayi kokari Allah yasaka mata."
Abba ya amsa da amin amin.
suna isa gida motar SALEEM na shigo wa, a kusan tare sukayi parkin suka fito,
ya tako ya zo in da suke ya shiga gaida su,
suka amsa cike da kuwala Ummi tađan zuba masa ido nan da nan ta hango ƴar karamar ramar da yayi, ta dube shi da kyau sannan tace
"SALEEM baka da lafiya ne kam?."
kai ya girgiza batare da yayi magana ba.
tace "Ai ho nazaci baka da lafiya ne dan naga kađan fađa kađan."
Abba yace
"Wata kila hidimar office ce ta sashi a gaba kin san shima yana sa haka idan ka rasa nitsuwar ka."
Ummi tace "Haka ne Allah yasa mu dace."
suna nan tsaye motar Abbu yashi gidan, koda ya gyara parking yafito duk kanin su gaishe sa sukayi ya amsa, in da ya amsa gaisuwar SALEEM a sama-sama kana yayi gaba Abba ya bi bayan sa.
SALEEM kuwa motar sa ya shige yabar gidan, Ummi kuma ta wuce side đin ta.

Parlour'n da su Abbu suke zama suđan tattauna nan suka wuce, suka zauna suna đan tattauna lamuran su.
Abbu ne yamai da hankalinsa kan TV yana sauraran labaran almuru da ake gudanar wa a wannan lokacin, in da ake sanar wa kan manyan masu kuđi da suke bada taimako da tallafi ga marasa karfi, jinjina kai yayi jin ta in da taimakon ya fito yace
"Kai wannan matar Allah dai ya saka mata wlh tana da kokari sosai, ko wancan satin ma naji kalar taimakon da tayi na dubban nin đarurruwan kuđi ga mara sa karfi,

in dai za'a cigaba da samin irin su a Nigeria ai kasar mu zata cigaba ba ɗan kaɗan ba,
dubi yan da take ta bada mai kamar kyau ta a cikin gari Allah dai ya kara mata buɗi."
Abba ya amsa da "Amin amin ai Yaya ko yanzu ma bakaga layin da ake yi a gidajen manta ba irin su kuma kullum buɗi suke gani ba ci baya ba."
Abbu yace
"Kwarai da gaske Allah ya daɗa buɗa mata."
hirar suka cigaba da yi har sai da aka kira magriba kafin suka nufi masallaci.
bayan sallar isha da Abbu ya tafi side ɗin Mamie hirar matar yayi ta mata da irin kokarin da take,
sukayi ta sanya mata albarka da dukiyar ta.....)

Abuja

Zaune muke a parlour ni da su Naseem Aunty Rasheedat tayi sallama da kaya niki niki a hannun ta, Zulai da Talatu na biye da ita ɗauke da wasu kayan,
Suka dire shi sakiyar parlour,
na dube ta daɗan mamakin ganin ta da manyan laidodi nace
"Sannu da zuwa Aunty Rasheedat."
tace "Yauwa HAMDAH ya nauyin jiki?."
murmushi kawai nayi dan nidai bana jin wani nauyin jiki cikin da bai girma ba ake tambayar nauyin sa.
zama tayi gaban kayan kana ta shiga ciro su cikin manyan laidodin kayan baby ne kala-kala a ciki haɗe da kayan wasa,
da gudu su Nasmah suka je in da take Naseem daya ɗago wani abin wasan baby yace
"Mamy kin kawo mana ne?."
Kuma tun sa ta ja tace
"A'a zan kawo muku naku wannan na baby'n ciki ne, baku san Mommy zata samo mana yaro ko yarin ya ba."
tsalle sukayi cike da murna suna faɗin
"Yeee Mommy zata samo mana yaro."
Nasmah ta dubi  Aunty Rasheedat ta dafa kafa ɗar ta tace
"Mamy yaushe Mommy zata samo mana?."
yatsun ta shida ta nuna mata tace
"Saura wata haka ta samo nama."
tsallen murna tayi tazo in da nake da gudu tace
"Mommy guda haka zaki samo mana yaro."
ido na waro ganin ta ɗaga yatsun ta biyar tana yimin nuni da su nace
"Akuya ce ni."

dariya Aunty Rasheedat da Talatu da Zulai sukayi, Talatu tace
"Ai ba akuya kaɗai suke haifan biyar ba idan Allah ya nufa sai kiga an haifo biyar ɗin."
kai na girgiza nace "Ba amin ba wlh."
dariyar suka kuma.
Aunty Rasheedat tace "Muna so ko goma ne ma Allah yakawo su masu albarka."
ido na kuma waro wa ina faɗin
"Lallai ma."

Ɗakin kayan wasan su Naseem tasa su Sulai suka kwashe kayan da tazo dashi, suka kai cikin ɗakin suka jibge shi a gefe.

Bayan wata ɗaya.........!

Mommyn Twins ce

27

Tun daga ranar da Ahmad yasami labarin ina da ciki, bai sake barina nayi wani abu da kaina ba.
ko wan ka baya bari na nayi shi yake yi min da kansa, ko naki nace ya bar ni nayi da kai na sai ya ce
bai isa na janyo masa a sara ba, shi da kan sa zai min.
koda six yake da ni a hankali yake bi da ni, wai kada ya jijjiga ni da yawa yayi wa kansa a sara..
tun da Dr ya bashi shawarwari game da cikin kan abincin da zan rika ci,sabi da lafiya ta da ta abin da ke cikin. shike nan ya hana ni sakat da cin abinci.
a rana sai yabani naci abinci kusan sau goma, dan yanzu idan ya bani naci anjima kaɗan zai kuma kara min.
yanzu kullum muna tare da shi ko yana gida na ko baya gida na,
idan yana gidan sa da sassafe zai zo bazai koma ba kuma sai dare.

washegari kuwa zai kuma dawowa da sassafen...

Kwance nake a kan dago na tasa ɗan karamin ciki na gaba wan da yanzu watan sa huɗu kenan.
idan bama kasan da cikin ba, bazaka ce da wani halitta cikin cikina ba, dan bai wani fito sosai ba, bakamar irin cikin su Naseem lokacin da ya kai watanni huɗu ya fito sosai kamar wan da yafi watan nin sa.
Ahmad ne ya shigo ɗauke da plt a hannunsa, perpesun kayan ciki ne haɗe da ganyen ogu da dafeffen kwai a gefe, wanda yasha kayan kamshi da na yaji sai tashi da kam shi yake,
ya dire plt ɗin saman table kana ya hayo gadon ya zauna ya tankwashe kafafun sa a gaba na yashafo fuskata yace
"Kyakkyawa ta taso kici perperun gashi na ɗebo miki."
fuska na ɓata nace
"Ni na koshi ba ɗazun nan naci ba, ni bana jin yunwa yanzu."
ido ya waro yace
"To ai ba sai kinji yunwa ba, bakiji abin da Dr yace ba kirika cin abinda zai kara miki jini da kuzari da lafiyar baby na ba, ga perpesun can cikin tukunya ko kwata baki ciba, kuma yanzu nasa Zulai ta kuma girka miki gwaten wake da hanta."
ido na waro nace "Nayi yaya da shi sauran perpesun ma kaje ka basu su ci ni nagaji da ci, kullum-kullum kawai mutum yayi ta ci."
yace
"Dan Allah ki taimake ni kitashi ki ci,cin waɗan nan abubuwan fa sune samin lafiyar ki data baby na, so kike a sami wata matsala? dan Allah ki tashi ki ci kada yayi sanyi."
ya saka hannu ya ɗago ni, ya tallafo ni ya ware kafafun sa ya sani sakiyar cinyar sa, kana ya mika hannu ya ɗau plt ɗin yasaka shi gabana, ya ɗibo perpesun a cokali zai kai bakina.
na karɓi cokalin nace
"Ni zan ci da kaina." yace "To ci
maza dan Allah ki cinye duka."
nace "To Allah kaɗan zan ci dan bana jin yunwa."
yace "To ci dai."
a hankali nasoma ci, ganin na fara ci sai ya daɗa gyara zaman sa da kyau, a sannu ya tura hannunsa cikin riga ta ya kife hannunsa kan ciki na, wani nannauyar ajiyar zuciya ya sauke a hankali yashiga shafa cikin.
bai fi cokali biyar na ciki ba nace nakoshi.
da sauri yace "Please kyakkyawa ta kiɗan kara kaɗan."
nace "Allah nifa na koshi."
duk yan da ya matsa kan na kara ko kaɗan ne naki daya masa sai na sa masa kuka, ai da sauri ya rungume ni yashiga rarrashi na..

Washegari tun da sassafe ya ɗaga ni da kyar na buɗe idanuna dan bacci ne fal a ciki,
yace "Tashi muje kiyi wanka mutafi asibiti yau zaki fara awu, dan likita yace cikin na cika wata huɗu yakamata ki fara yin awu kin ga yau Monday dai-dai kenan."

fuska na ɓata nace
"Ni bacci nake ji kabari ba yau ba."
da sauri yace "A'a ina, duk da dai baccin da awun duk suna da amfani amma dai muje a duba lafiyar baby in mun dawo sai ki cigaba da baccin kinji kyakkyawa ta."
ya karashe maganar da tsi
gar rarrashi.
kai na gyaɗa masa a hankali.
murmushin nan nasa mai narka zuciya ya sakar min kana ya sauke bakin sa kan goshi na ya manna min kiss,
idanuna na lumshi tare da kuma buɗe su, ya ɗago yana kallon fuskanta ta a hankali ya furta
"Ina son ki kyakkyawa ta."
idanuna na kuma lumshe wa a lokaci guda na buɗe, tabbas na gama yarda da son da yake yimin a koda yaushe ina hango sona acikin kwayar idanunsa.
idanunsa cikin nawa cikin sanyin murya yace
"Yaushe zaki faɗa min kema kina so na da bakin ki?."
kasa nayi da nawa idon batare da nace komai ba.
murmushi yayi yace "Ko a iya haka ma na gode."
duban sa nayi da fuskar tambaya jin ya faɗin haka.
murmushi ya kuma tare da ɗaga min gira kana yace
"A faɗa min ɗin ne dai ajin ya hana amma gashi nan ina hango shi."
yasa yatsar sa karkashin idanuna.
kai na nayi saurin kawar wa tare da yunkurin mike wa, ƴar karamar dariya yayi ya taimaka min na mike tsaye yayin da ya soma zolaya ta.
"Ajin nan ya ishe ni haka a ajiye shi a gefe a fito fili a faɗa min ana sona, tun kafin ajin ya tsinke dan wata jiya ta tare ni a hanya tace tana sona, nace ta bari tukun da wan da nake so idan bata ce tana sona ba zan zo na amshi soyayyar ta."
baki na taɓe dan yanzu na gama karantar kalar zolayar sa nace
"Ayya ai da ka amince mata kawai."
da sauri ya leko fuska ta yace
"To ai ke nake jira ƴammata idan baki faɗan kina sona ba sai na koma gurin ta."
"Yi maza kaje ka sanar mata kada ka maka anan."
nafaɗa ina kokarin wuce sa, da sauri ya ruko ni yace
"Bari dai na ɗan kara jira tukun."
ya janyo hannuna muka shiga bayi.
bathtub ya cika da ruwa mai ɗumi,
kana ya tuɓe min kayan jikina, na shige ciki na zauna ina mai jin daɗin ruwan, na lumahe idanuna.
da sauri na buɗe idanun jin motsin sa cikin ruwan sai ganin sa nayi shima a tuɓe,
ya ɗau sosa da sabula yashiga wanke ni shima yana wanke jikin sa a haka akayi wanka,
kana ya ruko ni muka fito bedroom,
koda nazo sa kaya hana ni yayi sai da yagama sumbatar ciki na kafin ya saka min da kan sa.
muna gama shiri muka fito muka dadda an gama wa su Naseem shirin School.
 a saman dinning duk muka yada zangon mu, sai da ya haɗa musu abincin da duk sukace suna

so kafin ya juyo kai na.
perpesun naman zabbi ya zuba min haɗe da tea mai kauri yana kokarin zubo wani abun nace masa
ya isa wannan ɗin ma ba iya cenyewa zan yi ba. ciki na ya shafo
yace "Yanzu fa zaki fara kamata yayi ki fara da mai yawa."
duban su Naseem yayi yakamo kumatun su yace
"Kanin ku yakusa isowa Yaya Naseem da Aunty Nasmah."
washe baki sukayi cike da jin daɗi Naseem yace
"Daddy ina kanin?."
ciki na ya shafa yace "Ya na nan yakusa fito wa."
da sauri Nasmah ta mike tazo kusa da ni tana kokarin jan riga ta sama.
hannunta na bige nace
"Ke meye haka?."
tace "Mommy danga kanin ne fa."
fuska na ɓata nace "Ka dani ko."
dariya yayi sosai kana yaɗan sakaita dariyar, ya dafa kanta yace
"Zaki gan shi?." kai ta gyaɗa tana washe baki.
yace "To ba ri ki ganshi."
juya kujerar da nake yayi yadurkusa kana ya saka hannu yana kokarin jan rigata sama, nayi saurin rike hannunsa nace
"Me ye haka?." juya hannun nawa yayi yarike cikin nasa kana yajan ye rigar da ɗaya hannunsa, yace
"Kibar yara suga ɗan uwan su."
tafin hannunsa ya kife kan cikin yana ɗan shafawa yace
"Nasmah zo ki gani ga kaninku a nan yaron yana nan a nan."
dariya sukayi har suna rige-rigen
taɓa cikin.
Naseem yace
"Daddy ni ban ganci ba."
yace "Yana cikin ciki yakusa fita ku ganshi."
sallen murna suka yi suna faɗin
"Ye damuga yaro, Mommy data samo mana yaro."
kafa na shiga bubbugawa a kasa nace
"Kuma na fasa cikin abincin."
da sauri ya saki rigar yace
"Yi hakuri kyakkyawa ta ci mu tafi o."
sai da yayi ta lallami na kafin na soma ci.
hannu ya saka muka ci tare muna ci yana karawa da dabara yayin da yake ta jana da wasa har naci da yawa sosai.
bayan mun gama muka fito waje in da Talatu ke biye da mu rike da school bag ɗin su.
ko da akazo shiga mota dirjewa yaran sukayi suka ce sam moton Daddy'n su zasu shiga, fuska na ɗaure nayi musu tsawa nace
"Maza ku shige kushiga mota kutafi so kuke kuyi latti."

da sauri yace
"A'a a'a kyale su kushiga muje, Talatu sa musu jakar su cikin mota."
da sauri tace to.
ya buɗe musu motar suka shiga, Talatu saka musu jakar su cikin motar,
kana ya buɗe min nima na shiga, ya zaga gefen direba ya shiga ya ja motar, mai gadi ya buɗe get muka fice a gidan..
sai da yafara bi ta makarantar su da kansa ya sauka ya ruko hannunsu ya shiga da su cikin makarantar kafin ya fito muka nufi asibiti.

Muna shiga cikin asibitin batare da ɓata lokaci ba aka gama kimsa mana komai,
koda nazo shiga ɗakin awu tare da shi muka shiga, yana tsaye yana kallon komai, idan yaga nurse ɗin taɗan danna cikin sai yace wai tayi a hankali kada a sami matsala, a haka a ka gama muka fito muka nufo gida.

Tun daga lokacin idan wata ta zagayo lokacin zuwa awu yayi da shi muke zuwa kuma yana tsaye za'ayi komai....

Haka rayuwa yaci gaba da tafiya,
sosai Ahmad ke kula da ni baya kaunar yaga wani damuwa ko ɓacin rai tare da ni, bazai taɓa samin sukuni ba har sai yaga ya gusar min da damuwa ya sanyani farin ciki....
a yanzu cikina watan sa 7 yafito ɗas da shi, haka zai tasani gaba ya tuɓe min riga yayi ta kallon cikin, yana ganin in da yake motsa wa, yayi ta sumbatar sa, idan nace ni na gaji ya kyale ni.
sai yace ai ba da ni yake ba da babyn sa yake, wai yana mika masa gaisuwa....

Zaune nake a parlour Inna Wuro tashigo rike da manyan kofuna guda biyu, ta iso ta dire su a gaba na tazau na tana faɗin
"Sannu HAMDAH ya nauyin jiki." murmushi kawai nayi. ɗaya kofin ta buɗe ta miko min tace
"Karɓi kisha maganin zaki ne dana bayamma zai taimaka miki sosai."
nace to na amsa nasha da ɗan yawa ta karɓa sauran ta mika min ɗayan shima na sha.
ganin Ahmad ya shigo yasa ta mike wa tana faɗin
"Anjima ki kara sha shi zai zamo ruwan shanki za'a kawo miki wani anjima."
nace to
ya karaso ya gaishe ta ta amsa tana fita daga parlour'n.
ya zauna gefe na tare da ɗaga riga ta sama ya sumbaci cikin kana ya ɗago yana faɗin
"Mene ne Innar ta kawo miki shine ba tayi."
nace "Ɗauka ka sha." buɗe marfin kofin yayi yaɗan kai bakin sa ya ɗan ɗana yayi saurin aje kofin yana yamutsu fuska.
dariya na yi nace "Ka kara mana."
yace "A'a ya ishe ni, amma meye wannan ɗin?."
nace "Maganin zaki ne da na bayamma."
yace "Meye su ɗin."
nayi masa bayani ta yanda zai fahimta.

yace "Oh to karɓa ki kara sha, ai naji tana cewa anjima ki kara sha shine ruwan shan ki."
fuska na ɓata tare da make kafaɗa nace
"Ba yanzu nasha ba."
yace "To an jima kaɗan zaki kara."
nace "To kabari anjiman yayi mana."
yace "To ai gara dai na tuna miki tun yan zu kar anjiman yayi kice da saura."
dariya nayi ina faɗin
"Ai irin anjiman ka ne yanzu sai kace yayi."
shima dariyar yayi yace
"To shike nan a saka time kada lokaci yayi kice bai yi ba."
nace "Eh a saka." yace "Bayan minti 5."
"Tab banyar da ba yayi kaɗan."
"To na kara biyar a kai."
nace "Naki wayon." yace "To ashirin yanzu kam ba kankari."

Ai kuwa duk bayan minti 20 zai sani na sha, ganin ya matsa min sai na gudu sashin su Inna Wuro.
har can ɗin ya bini da kofunan yace wa Inna Wuro ta kara maganin wannan ya kusa kare wa.
nace
"Allah Inna Wuro kar ki kara ni nagaji da sha tun ɗazu yake ta bani."
yace "Ina ance yazama ruwan shan ki ne."
"Shike nan shan ruwan babu adadi ni ciki na zai fashe."
Inna Wuro tayi dariya tace
"Idan ta shanye wannan da rana sai dare  kuma sai a kawo mata wan da zata sha har gari ya waye."
nan ne ya kyale ni amma yace mutafi na karasa shanye sauran.
nace ya tafi zan zo anjima, fir yaki sai da ya tasani gaba muka koma...
tun daga ranar kullum shi yake zuwa da kansa ya karɓo min ruwan maganin, yakuma tasa ni gaba sai na sha...

A bangaren Hajiya Karima kuwa
tsaye take ita da wasu maza guda hiyu, a cikin bedroom ɗin ta, sunyi jungum-jungum kamar waɗan da aka aiko wa da bakin labari,
ɗaya daga cikin mutanen yace
"Hajiya shima kawai a kunce masa tayar mota yabi uban sa inda yaje."
Hajiya Karima tace "Ai matsalar ba daga nan take ba, yanzu fa duk wata shirin mu ya kwaɓe idan aka kashe Ahmad tofa anyi ba'ayi bane, dan kuwa yanzu yasami magaji dole  mufara bi ta kan ita matar tasa mai cikin kafin shi."
ɗayan yace "To Hajiya me kike ganin za'ayi mushiga cikin dare mu harbe banza kawai."
tace "Ina ai bazai yiwu ba dan gidan ta da matakan tsaro iri-iri, akwai jami'an tsaro da masu gadi kuma ko wannen su yana da bindiga, shigan gidan zai bada wuya, dole dai mubi ta wata hanyar, ni a tuanani na kawai mu jira ta haifi cikin sai mu kawar da shi,in yaso duk mu haɗa har

da ita mai azarɓaɓin yin cikin kafin shi Ahmad ɗin.
suka ce haka za'ayi,
nan suka cigaba da tattauna in da lamarin zai tafi musu batare da wata matsala ba.....

A gurguje Please 👌🏼

Bayan wata biyu

Yau tun da gari ya waye nake jina wani iri, sai dai narika daure wa ban nuna masa komai ba.
har wajen karfi sha ɗaya, zuwa lokacin kam nafahim ci nakuda ce kuma sosai nake jin sa.
har kuma lokacin ban nuna masa wani abun na dami na ba na rika daure wa har mukayi wanka yafita, kafin yafita kuwa yayi ta tambaya ta, babu abin da yake damu na me kuma na ke so.
nace masa babu komai...
ina zaune a bakin gado nayi nayi na iya mike wa na kasa, sai na zame kasa nasaka goiwowi na a kasa na kife kaina jikin gado, ina juya kai cikin mawuyacin hali.
"Innalillahi'wa'inna'ilaihirraji'un wayyo Allah na."
nafaɗa da karfi ina juya kai.
sallamar Faty naji daga bakin kofa, da karfi na ɗaga murya na kira ta, da sauri ta shigo nace
"Je ki kira min Inna Wuro da sauri."
hankali tashe ganin halin da nake ciki ta juya da gudu tayi waje.
ina ji ana kiran waya ta har ya katse ban iya ɗauka ba, har sau uku kiran na katse wa sai a na huɗu da kyar na mika hannu na janyo wayar, na ɗaga kiran tare da saka shi amsa kuwa, muryar Ahmad naji yana faɗin
"Kyakkyawa ta kina lafiya ya baby na?, hello kyakkyawa ta bakya jina ne."
wani irin hurɗa cikina yayi haɗe da baya na da sauri nakai hannuna na safe baya na tare da faɗin
"Wayyo Allah wayyo Allah Innalillahi'wa'inna'ilaihirrraji'un."
cikin wani irin birkitaccen murya yace
"HAMDAH me ke faruwa me ya same ki me nene!!?."
salati kawai na cigaba da yi batare da na iya furta komai ba,
jin yan da ya birkice yake ta tambaya ta sai na janyo wayar na kashe...
Inna Wuro ta shigo hankali tashe, ta iso in da nake tana faɗin
"Ikon Allah abun yazo kenan sannu HAMDAH Allah ya raba ku lafiya."
ta dubi Faty tace
"Je ki ce wa Zulai ta ɗaura ruwa a wuta, ki wuce kije ɗaki na ki ɗauko hulba cikin magungunan nan ki kawo mata ta zuba cikin ruwan ta girka, ta ɗura cikin flaks, yi maza yanzun nan."
da sauri tayi waje.
Inna Wuro ta shiga karanto addu'a tana shafa min a cikin  da bayan da nake ta kukan sa...
ya turo kofar kamar wan da aka jefo sa da sauri haɗe da sassarfa ya iso in da nake ya rungumo

ni yana faɗin
"Innalillahi'wa'inna'ilaihirraji'un sai da na tambaye ki ko dawa matsala ce kafin na fita kika ce ba komai, meyasa zaki barni na tafi,
tun ɗazu jikina ya bani akwai abin da yake faruwa da ke shiyasa nakasa samin sukuni kan abin da nake, ya zaki min haka HAMDAH,
sannu kyakkyawa ta sannu kinji."
cikin sananin azabar nakuda na kankame rigar sa ina faɗin
"Wash wash wayyo Allah  wayyo Allah na wayyo baya na."
Inna Wuro kam waje tayi da sauri, zuwa can ta shigo rike da kofi da hulba mai zafi ciki, har lokacin yana rike da ni a jikin sa.
ta mika masa cup ɗin tace "Bata tasha wannan insha Allah zai zo mata da sauki."
da sauri ya karɓa har hannunsa na ɓari, tace "Bata da zafin shi."
ya zauna ya mike kafafun sa ya saka ni sakiyar cibiyoyin sa, kana yasaka min cup ɗin a baki na yana faɗin
"Sha zaki haihu yanzu." Inna Wuro ta sake fita da sauri
ta koma sashin su, ɗakin Bappa ta shiga yana zaune rike da ƴar karamar kwarya a hannunsa yana ta tofe ruwan maganin dake ciki da addu'a,
yana ganin ta ya mike da sauri yace
"Ya dai?." tace "Har yanzu dai."
kwaryar ya mika mata yace
"Kai mata tasha insha Allah zai ta kai ta."
ta karɓa ta fita da sauri.
a in da ta barmu a nan ta tadda mu, da kan ta ta maso ta kafamin kwaryar a baki tace nasha da bismilla.
sai da na shanye duka kafin ta ɗaga kwaryar.
 tana yimin sannu.
wani irin zabura nayi nan take wani gumi yashiga tsastsafo min ta ko ina yashiga ɓari a jikina, yayin da cikina yashiga murɗa na ba ko kakkautawa.
kai kawai naje juyawa yayin da nakasa iya furta komai.
a zabure ya mike yaɗogo ni cak yana faɗin
"Inna Wuro mutafi asibiti kawai."
kan tace me yayi waje yana isa gurin motar sa ya saka hannu ya buɗe gidan baya yasaka ni ciki,
Inna Wuro ta karaso da ɗan sassarfa tashige motar ta zauna gefe na.
da sauri ya shige gidan direba yaja motar da mugun gudu. cikin hanzari mai gadi ya wangale get yasa kai da mugun gudu.
tamkar zai tashi sama haka yake sharara gudu batare da ɓata lokaci ba muka isa cikin asibiti, yana kashe motar yafito da sauri yazago gefen da nake yabuɗe ya cicciɓo ni, yayi dani cikin asibitin, Inna Wuro tabiyo bayan mu,
nurse's suka nuna masa ɗakin da zai shiga dani,
ya wuce ya dire ni kan gado cikin ɗaga murya ganin Nurse's ɗin sun rufu a kaina yace
"Kuje ku kira likita mace tazo ta duba ta."
nan da nan ma'aikatan sukayi waje batare da ɓata lokaci ba Dr mace ta shigo nurse's biyu na

biye da ita.
duk yan da sukayi ya fita yabasu guri domin su gudanar da aikin su sam yaki, da kyar ya yarda ya fita ya tsaya daga bakin kofa yana leka ni.
wani irin nishi na sake tare da faɗin
"Innalillahi'wa'inna'ilaihirraji'un."
dai-dai nan kan ɗan yasoma kunno kai,
ai da gudu ya shigo ya rirrike ni ganin yan da hawaye ke zuba min yace
"Sannu HAMDAH kiyi hakuri ina sonki."
kai na jujjuya tare da rike hannunsa da karfi, nace
"Wayyo Allah na zan mutu."
likitan tace "Kada ki dai na nishin ci gaba."
ai bata rufa baki ba sai ga ɗa yafito fut tare da calla kara.
nurse tana kokarin ɗaukar sa ya ture ta ya ɗauke sa ya rungume a jikin sa yana faɗin...........!

Mommyn Twins ce

28

Yana faɗin "Masha Allah, Allahu Akbar ya iso duniya! ɗana ya iso!!."
yawani sake rungume shi yana juye cike da matsanancin farin ciki mara misal tuwa.
da sauri Dr ta mika hannu ta karɓi ɗan dake ta faman calla kara tace
"Yi hakuri ranka shidaɗe bari a gyara shi, gashi ka ɓata jikin ka da jini, kaɗan bamu guri mu kimsa shi da mamarsa zamuyi mata ɗin ki wannan katon ɗan naka ya karata dole sai munyi mata ɗinki."
kai ya girgiza yana daɗa leko fuskar yaron da ta ke kokarin mikawa nurse.

niko numfashin wahala nake ta sauke wa a raina inayiwa Allah godiya daya raba ni da cikin nan lafiya.
matso ni yayi gaba ɗaya bakin sa yaki rufuwa ya damke tafin hannuna cikin nasa yace
"Sannu kyakkyawa ta Allah dai yayi miki albarka."
kai na rausayar gefe ina mai cigaba da sauke numfashin wahala.
kiss ya sauke min a goshi kana ya juya yafita sabo da maganar da likitar ta sake yimasa kan zasu fara ɗin ki...
ya fito yana ta washe baki,
jama'a sai kallon sa suke ganin yan da yafito jikin sa duk jini,
da sauri Inna Wuro ta iso in da yake tana faɗin
"Ahmad ya haka ya jikin ka da jini."
baki ya daɗa washewa bai damu da jinin dake jikin sa ba cikin sanananin tarin farin ciki yace
"Inna Wuro ta haihu kin ga babyn kuwa bakiji kukan sa ba?."
dariya Inna Wuro tayi tana faɗin
"Masha Allah Allah abin godiya, Allah yaraba su lafiya."
Ahmad yakasa zaune ya kasa tsaye bakin sa yaki rufuwa, mutane kuwa sai daɗa kallon sa suke da jikin sa da ya ɓaci da jini, da yan da bakin sa ya kasa rufuwa.
suna ta shan mamaki wai haihuwa aka yi masa yake ta irin wannan farin cikin haka.
wayar sa ya ɗaga yana ta daddanna wa yama rasa ma wazai kira ya faɗa masa abin farin cikin nan.
Rasheedat yakira ya sanar mata.
ai ko batare da ɓata lokaci ba ta ta iso asibiti da katon akwati, kayan jarirai ne tam ciki, da sabbin jiga-jigan dogayen riguna masu tsadar gaske, da sauran abubuwan bukata wacce mai jego da baby ya kamata suyi amfani da shi idan akayi haihuwa.
ta bawa nurse tace a je a shirya baby, da maman baby,
suna shiga da akwatin.
ta rungume Ahmad tana tsallen murna.
suna tsaye aka fito da jaririn an shiyar sa cikin tsadadden saiti cikin wan da Rasheedat tazo da shi,
har ana rige rigen karɓar sa sakanin Ahmad da Rasheedat da kuma Inna Wuro.
Karshe wa Rasheedat aka mika mawa dan gaban su ta wuce tariga mika hannu.
nurse ɗin tace "Muna tayaku murna an sami ɗa na miji."
Rasheedat tace
"Wayyo Allah masha Allah kawo shi kawo shi."
tana karɓar babyn ta ciro kuɗi masu yawa ɗaurin ƴan 1-1k cikin jakar ta ta mika wa nurse ɗin da ta fito da yaron.
tace tukuicin ta na sanar da abin da aka samu.
da sauri Ahmad yace wa nurse ɗin
"Ya take tana lafiya dai babu wata matsala ko."
tace "Eh babu komai yanzu za'a wuce da ita ɗakin hutu."
kai ya jinjina.
Rasheedat ko
ido ta kurawa yaron cike da matukar farin ciki da ɗoki tace

"Wayyo Allah kyakkyawan yaro, wannan yaron da ala kama da ni zai yi."
dariya Inna Wuro tayi tana lefo fuskar yaron tace
"Tabatakallah masha Allah wannan katon yaro haka duk kai kaɗan ka ka baje cikin kicin nan haka."
Ahmad yasaki dariya mai nuna zallar farin ciki ya mika hannu yace
"Kawo sa na gansa ɗazu ban gansa da kyau ba."
Rasheedat tace "Amma yanzu zaka bani shi ko?."
kai ya gyaɗa mata yana dariya, ta mika masa ɗan daya ke ta rarraba ido kamar ba yanzu yafito duniya ba, idan haske yaɗan dame sa sai ya rufa idon yakuma buɗe wa.
ido ya kura masa babu ko kiftawa sai daɗa washe baki yake,
yarika sumbatar yaron yana juyi cike da shauki mai bayyana zallar jin daɗi da farin ciki..
dakyar ya mika wa Inna Wuro shi tana karɓar sa Rasheedat takuma caɓe shi.
a hannun Rasheedat yayi ta wa yaron hotuna a wayar sa, cikin kankanin lokaci yawatsa shi wa duniya,
batare da ɓata lokaci ba yafara ɗaga kiran yan taya murna..
sun so shiga su duba HAMDAH aka dakar da su akace tasami bacci su bari sai ta farka da kanta...
duk da haka Ahmad a akai-akai yake shiga ɗakin hutun da aka kai ta yana duba ta..

Sunan a cikin asibitin har wajen karfe uku, gaba ɗayan su babu mai gajiya bare jin yunwa.
sai a lokacin wata nurse tazo tace musu ta farka zasu iya shiga yanzu.
ina zaune a kan gadon da aka kwantar da ni, bayan Nurse ta taimaka min na shiga bayin cikin room ɗin wan da yake a tsaftace, nayi wanka da ruwa mai ɗumi na kimsa jikina, ta ciro min ɗaya daga cikin dogayen rigunan da Aunty Rasheedat ta kawo su cikin akwati, na fito fes dani kamar ba ni bace
ɗazu nake a hargetse,
ina zaune ina shan maltina da madarar da nurse's suka kuma haɗa min, su Ahmad suka shigo.
wani sassanyan murmushi ya sake min tun daga bakin kofa.
fuska na ɓata na turo baki gaba.
suka karaso ciki suna yi min sannu,
Inna Wuro tace
"Sannu kinji ƴar nan Allah ya raba lafiya sai fatan samin sauki kuma,
Allah ya kara miki lafiya."
murmushi kawai nayi mata.
da sauri Ahmad ya amsa da amin amin.
Rasheedat ta maso bakin gadon tace
"Sannu HAMDAH sannu da kokari yaya jikin dai?."
itama murmushin nayi mata a hankali nace
"Da sauki."
wani irin murmushi yakuma sakar min tare da kashe min ido, yaɗan matso ya rike hannuna ya matse cikin nasa  yayin da ya gyara rukon babyn da ɗaya hannunsa,
a hankali cikin sassanyan murya mai ɗauke da zallar farin ciki yace

"Madam kinga kyakkyawan yaro na kuwa."
baki na murguɗa masa nace
"Baka tambaye ni gajiyar wuyan da ya bani ba sai ta tashi ma kake ko."
da sauri yace "Sorry kyakkyawa ta na isa gaisuwa ta ta musamman ne."
yayi maganar cikin yin kasa da murya sosai tare da kashe min ido.
da sauri na zare hannuna cikin nashi ganin hankalin su Rasheedat ya dawo kan mu.
yana rungume da yaron a hannunsa sai leka fuskarsa yake Inna Wuro tace
"Ahmad kawo shi a kwantar da shi, yan zu zai bukaci kwanciyar tun ɗazu yake hannu."
yace "A barshi dai zuwa anjima sai a kwantar da shi kamar bacci zai yi ma yana rufe ido."
kai Inna Wuro ta girfiza tare da yin murmushi tace
"Ai yayi baccin yafi a kirga yana farkawa a gajiye yake shi kansa yana bukatar hutu, kada jikin sa ya daɗa masa tsami."
sai da ya sumbaci goshin yaron kafin ya mika mata shi ta kwantar da shi gefe na,
sai a lokacin naga kalar fuskar yaron, kato fari soll da shi kyakkyawa mai kama da ubansa hancin dai nawa ne, dan kalar hancina ne zane a kan fuskarsa, numfashi na sauke a raina nace
"Ka gama wahalar da ni."

Da misalin karfe huɗu likitan ta shigo ta ɗan dudduba ni bayan tambayoyin da tamin ko akwai abin da ke damu na,
nace mata ba komai. tace zamu iya tafi tun da babu wata matsala tare da ni.
bayan magungunan da ta rubuta tace a siya narika sha...
Rasheedat ta ɗauki jaririn shi kuma ya taimaka min muka fito, Inna Wuro na janye da akwatin muka isa jikin mota,
ya buɗe min gidan baya na shiga, kana ya karɓi a kwatin yasaka shi a but,
Inna Wuro ta shiga ta zauna kusa da ni,
ya zaga mazaunin direba in da Rasheedat ta zauna a gefen mai zaman banza tana rungume da jaririn.
a sannu ya ja motar a hankali muka bar cikin asibitin...

Muna isa gida da sauri ya fita ya buɗe min kofa ya ruko hannuna na fito daga cikin motar.
tuni ma'aikatan gidan maza da matan su suka hallaro in da muke, suna yi mana sannu da tambaya ta ya jiki dakuma barka da samun baby,
suka rika leka fuskar yaron dake hannun Rasheedat suna sambarka da faɗin Allah ya raya.
ganin ina yamusa fuska yadube ni cike da kulawa yace
"Kin gaji ko muje ki huta."
yajanyo hannuna muna ɗan yin nesa da inda suke ya ɗaga ni cak yayi cikin side ɗi na da ni.
bai dire ni ko ina ba sai cikin bedroom ɗina a kan gado.
yaɗa go yana bina da wani irin kallo mai cike da tarin so da kauna, a hankali ya kawo fuskar sa daf da nawa, a sannu ya haɗe bakin mu.
wani zazzafar kiss yake ai ka min da zafi-zafi kana ya zare bakin sa yana mai cigaba da yimin wannan kallon,

sai kawai ya rungume ni sam a jikin sa, yace
"Hakika bani da bakin da zan iya yi miki godiya amma ki sani ina sonki ina kaunar ki ke alkhairi ce a rayuwa ta."
sai ya sake ni ya ɗago jin hayanir su Rasheedat a parlour.
Inna Wuro ne tashigo da salla Rasheedat na biye da ita...
nan da nan Inna Wuro ta shiga kiciniyar yiwa yaron wanka, guri ya nima ya zauna yana zaune har aka fara yi masa wankan,
jin yana kuka da ganin yan da Inna Wuro take wanke shi yasa shi faɗin
"Inna Wuro ko dai zafi yake ji?."
dariya tayi tace
"Har ma yasan daɗin jikin sa kenan, ai ko dole a wanke shi sosai acire masa dattin da ya fito da shi."
shiru dai yayi yana kallon sa da alama dai ransa bai yi daɗi ba.
bayan an gama masa an shirya sa cikin wani sabon kaya tuni ya yi bacci cike da jin daɗin wankan da aka masa.
yaso ya ɗauke sa ganin yana baccin ne dai ya hakura ya fita..
Rasheedat ma tafita taje gurin su Talatu da suke kitchen.
Bayan Inna Wuro ta kwantar da shi tace na tashi muje nayi wanka..
wankan towel tayi min sosai nasha zafi kam amma bayan an gama naji daɗin jikina sosai.
Rasheedat ta shigo ɗauke da tray mai ɗauke da kayan abinci kala-kala,
masu in ganta jiki, Inna Wuro ta sani na zauna naci da zafi-zafin sa.
ai ko ina saka kaya nima na haye gado sai bacci...

Da daddare bayan ya maida Rasheedat gida, yadawo yashigo ɗakina yazauna bakin gado ya ɗau jaririn yana ta kallon sa.
Inna Wuro ta shigo ta kuma fita ganin yana cikin ɗakin,
da kyar na sashi yafita dan nasan so take ta kwanta dan tayi shin fiɗar ta a kasa a gefen gado..
washegari Bappa har parlour'n sama ya hauro, Inna Wuro ta kai masa yaron yayi ta masa addu'a da sanya wa rayuwar sa albarka, kana nafito muka gaisa yana tambaya ta ya jiki bana dai jin ciwon komai ko, nace ba komai, yace
"Masha Allah akwai maganin da bawa Innar ku zata girka miki kirika sha."
nace "To Nagode Bappa."
ya mika min ɗan yafita, namike na koma ɗaki..
nakira Ukhtee na faɗa mata na haihu gudun kada taji a wani gurin tace ban faɗa mata ba.
Ukhtee tarika murna tace insha Allah zata zo Nigeria da ita za'ayi suna...

Ahmad ne yashigo rike da su Naseem a hannunsa yana ce da su
"Au bakuga yaron bane?."
kai suka gyaɗa masa suna washe baki.
murmushi nayi ganin su, ɗazu Inna Wuro take cemin sun shigo jiya ina bacci ita ta hanasu tada ni.
gado suka ɗale dukan su har da shi,

ya ɗauki yaron yana faɗin
"To ga kanin ku nan yafito duniya kuzo ku ganshi."
tsallen murna suka shiga yi suna faɗin
"Yeee Mommy ta samo mana yaro."
Naseem yace "Daddy kabani shi na rike shi."
yace "To gyara ka zauna na baka shi."
ya zauna har da tankwashe kafafu, yasaka masa yaron kan cinyarsa yana rike da shi batare da yasake masa shi ba..
Nasmah ma tace itama sai dai a bata, ya ɗago shi itama yasaka mata shi kan kafarta.
murmushi nabisu da shi ganin yan da
suke ta murnan ganin yaron. Ahmad ya dube ni yana faɗin
"Ya dai kyakkyawa ta komai normal ko."
baki na turo nace
"Ba kun sami baby kun share ni ba."
ido ya waro yace "Wane mu ai kece tauraron mu bakya taɓa disashe wa."
murmushi nayi shima murmushin ya bini da shi.

A ɓangaren
Hajiya Karima lokacin da labarin haihuwar nan ya isketa hankalin ta yayi mummunar tashi,
Musamman da aka ce mata na miji aka haifa,
awani ɓarin zuciyar nata kuma shirin da suka haɗa kan kawar da ɗan ta tuno a fili tace
"Lokaci yayi."
ta shirya taje gidan Inna Wuro ta fito mata da jaririn,
ta kafe shi da ido tana dariyar yake da faɗin Allah ya raya..

Ranar da muka cika kwana uku da safe bayan Inna Wuro tayi masa wanka muka shiga bayi nima tayi min, bayan mun fito na shirya cikin riga da zani na atamfa, ina zaune a bakin gado ina cin abinci,
yayin da jaririn ke rike a hannun Inna Wuro.
Ahmad ya shigo, ya leka fuskar yaron yana gai da Inna Wuro,
ta amsa da murmushi tana faɗin
"Gashi nan ai yana so yaji abibcin sa cikin baki, gara dai kabar ta itama ta ci dan ka samu ruwan nono mai yawa."
murmushi mai sauti yayi yace
"Kodai bai sha ba tun ɗazu shiyasa yake nima."
tace "A'a kam wannan acicin yanzu aka cire shi daga bakin nono shidai yafi son ko da yaushe ya kasan ce a bakin shi."
hannu ya mika ya karɓe shi yana ɗan jijjiga shi,
ya dube ni yana faɗin "Madam ayi sauri a ci a bashi yasha dan Allah, Allah sarki ga yana buɗe baki yunwa yake ji."

baki na turo nace "Ai nima yunwar nake ji."
yace "To ai ke babba ce zaki fishi dau riya."
cikin shagwaɓa nace "To Allah sai na fasa cin abincin kuma bazai sha."
ido ya waro yace "Asara biyu kenan, yi hakuri ci abincin ki ni bari na rarrashe shi."
kasa Inna Wuro tayi da kansa cikin yanayin shiga jin kunya.
ya juya yana faɗin
"Inna Wuro bari ayi masa huɗuba."
tace "Yakamata kam yau yau uku."
yayi waje rike da shi yashige ɗaya ɗakin da ke kusa dana su Naseem..
har na kammala cikin abincin bai dawo da shi,
Inna Wuro ta fita tace bari taje tayi wanka, niko na gyara na kwanta har bacci yafara ɗauka ta kafin ya shigo.
a hankali ya hayo gadon yace
"Yi hakuri kyakkyawa ta tashi ki bashi nono kin ji, Allah yunwa yake ji kiga fa sai latse baki yake."
na mike zaune tare da karɓar sa dan nasan yanzu kam yana bukatar nonon sosai.
kiciniyar janye rigata sama na shiga yi, sai ya maso ya taimaka min yaja rigar sama, yasaka hannun sa cikin bra ta ya ciro nonon da kansa ya saka masa shi cikin baki. niko naɗan tallafe masa saboda kada yayi masa nauyi a baki.
ya sun kuyar da kansa ya sumbaci saman nonon ɗan sama da bakin yaron, kana ya ɗago ya saka hannu ya ciro ɗayan, a hankali ya manna bakin sa ya sumbace sa shima,
yace "Nayi missing ɗin ku." sai ya saka hannu yarika shafa nonon,
a sannu ya leko fuskar yaron yayin da hannunsa ke manne kan ɗaya nonon yace
"Yau wa sha sosai ka kara kato."
murmushi nayi tare da duban sa nace
"Wani suna ka saka masa ne?." baki ya washe yace "AHMAD." ido na waro nace "Wane Ahmad fa kace Ahmad kuma."
yace "Eh Ahmad sunan da yanzu nayi masa huɗuba da shi kenan."
kai na jinjina nace "To me za'a rika ce masa kenan?." yace "Babu wani sunan da za'a rika kiran sa dashi face sunan sa Ahmad Ahmad Tijjani Sabil."
baki na rike nace "Taya za'a rika kiran sa da Ahmad bayan sunan ka kenan ai sai a nemo wani sunan da za'a rika kiran sa da shi."
yace "A'a kyakkyawa ta sunan da za'a kira sa da shi kenan asalin sunan sa Ahmad."
baki na turo gaba nace "To har yara ma haka zasu rika kiran sa da shi?."
murmushi mai sauti yayi kana yaja kumatu na yace
"To ai su yara basu ma san sunana ba kuma ko da ace sun sani ma nasa daban ne nawa daban, bare ma basu sani ba Daddy kaɗai suka sani, sai dai idan kece zaki faɗa musu."
da sauri nace "Yaushe." kumatu na yakuma ja yace "Duk san da kika cigaba da kira na da sunan."
nace "To ba sunan ka ba kenan Ahmad."
ido ya waro tare da yin dariya yace faɗar sa bai miki nauyi a baki ba, ko da Ahmad karami kike?."
kai na sunkuyar ba shakka sunan tayi min mugun nauyi, yauce rana ta farko tun farkon haɗuwar

mu da shi har rana mai kamar tayau ban taɓa kiran sunan sa kai tsaye ba sai dai narika yin komai a dungu, bana taɓa iya kiran sunan sa.
hannu ya saka ya ɗago haɓa ta yace
"Me kika ce sake faɗa naji ni Ahmad ɗin?."
kai na daɗa sunkuyar wa ina murmushi, ai ko ba komai shi babba ne, hakan baya rasa nasaba da rashin iya kiran sunan sa da nake kai tsaye, ko ba komai ya girme min nesa ba kusa ba, ga wata babban girman wato da yake a matsayin miji na.
fuska ta ya leko yace "To in ba so kike ki sanar musu da sunan nawa ba, to a canza min suna yanzun nan adai na yimin abu kamar bani da suna arika kirana da sunan babu."
ban yi magana ba sai zare nonon da nayi abakin yaron ganin yayi bacci, na gyara na shinfiɗa shi, sai na yunkura ina kokarin mike wa,
cikin hanzari ya janyo ni na faɗo jikin sa, sai ya rungume ni yashiga ai kamin da zafafan sakwannin sa, masu birkita min lissafi, yashiga nuna min yan da yayi missing ɗi na na wanaki uku.
duk kanin mu numfashi muke sauke wa a hankali ya kawo bakin sa saitin kunne na cikin yin kasa da murya yace
"Kyakkyawa ta wani suna aka bani? oya faɗa min naji."
a hankali cikin yanayin da yagama saukar min da kasala nafurta
"My."
wani irin runguma yayi min kamar zai cusa ni cikin kijin sa yace
"Wlh yayi kai amma gaskiya ni mai sana ne komai kin iya kamar yan da kika iya haifo min wannan kyakkyawan santalenen yaron nan haka kika iya zaɓar min sunan da ya dace da ni, ina son ki HAMDAH
ina yimi ki son da banayi wa kaina."
bakin sa ya dadaɗa mayar wa cikin nawa, nan ma yashi sau ke min wata sabuwar kasalar, tuni idanunsa ya gama sauya wa sai fidda numfashi yake.
gaba ɗaya ya birkice yakuma birkita ni, joystick ɗin sa ya damke da hannun sa da karfi a hankali cikin fizgar numfashi yace
"Zafi yake min ki tai maka min."
ido na waro nace "Ta ina ko ka mance akwai jini kuma akwai ciwo agurin."
kai ya girgiza yace "Na sani bata nan ba."
sai ya cusa hannunsa cikin wando yazaro sa, yana tsaye kem sai zillo yake.
hannuna ya kamo duka biyu ya saka kansa yaɗan matse, fahimtar me yake nufi da sauri nace "Inna Wuro zata shigo fa." yace "Bazata shigo yanzu ba."  a hankali na gyara na shiga kokarin taimaka masa ta hanyar sarrafa shi da hannu da kuma baki na, dan nasan yana buƙatar taimako na a wannan lokacin duba da yanda yake ta matse ido.
sai da na tabbatar da nasama masa nutsuwa kana na zare bakina kan abar tasa, nayi amfani da toilet paper wajen kawar da madarar sa.
sumbatar goshi na yayi tare da faɗin
"Nagode sosai kyakkyawa ta."
idanuna na lumshe tare da kuma buɗe
wa...

Ya juya yana faɗin "Bari naje nayi wanka."
bayan sa nabi da kallo har ya fita, sai na sauke numfashi tare da mai da bayana na jingina da jikin gado a hankali na lumshe idanuna.
fitar sa da kamar minti 30 Inna Wuro ta shigo, ta leko fuskar yaron tace "Bacci yake ne?." nace "Eh."
kofin da ta shigo dashi rike a hannun ta ta mika min tana taɗin
"Gashi kisha maganin da Malam yace a dafa miki ne."
nace To tare da karɓa, nace "Inna Wuro kinji sunan da ya sa wa yaron nan wai Ahmad."
Inna Wuro tayi dariya tace "Ai yanzu yake faɗa min a hanya ta tazuwa nan, nace to kaji Ahmad baban Ahmad, Allah ya raya shi da imani yaɗau ko halin uban sa da kakasan sa."
nace "Wai fa haka za'a rika kiran sa nace a canza masa yace a'a taya za'ayi a rika kiran sa da sunan."
tace "To shi haka yaga yafi tun da shi yace sai a rika kiran sa da hakan kawai."
kai kawai na girgiza kana nashiga shan maganin..

Washegari da sassafe Hajiya Karima tazo lokacin ana shirin yiwa Ahmad karami wanka, a parlour'n sama ta zauna, sai da Inna Wuro tayi masa wanka ta shirya shi kafin ta mika wa Faty da ke zaune tana zaman jiran a gama masa wankan a bata shi.
Inna Wuro tace ta kai wa kakar sa shi a parlour.
sai a lokacin nima na mike na fita parlour'n, Faty tazo daf da ita zata mika mata ɗan mukajiyo maganar Ahmad a sama.
"Da kata Faty!." cak Faty ta tsaya batare da ta mika mata ɗan ba,
ɗan razana Hajiya Karima tayi a ɗan daburce ta ɗago kanta.
ya karaso cikin parlour'n yayin da idanunsa ke kan hannun Hajiya Karima, Rasheedat na biye da shi..........!

29

Da sauri cikin dabara Hajiya Karima ta mai da hannun ta cikin mayafin ta.
murmushi Ahmad yayi ya mika hannu ya karɓi Ahmad karami yana faɗin
"Ke Faty haka ake rukon yaro a garin ku? ya zaki fito da shi a sanyin nan babu wani isasshen

kaya a jikin sa, bani shi nan budurwar kauye kawai."
Faty tace "Kai Yaya Ahmad ba ga kaya ajikin sa ba."
yace "Ke yaushe kika san yan da ake rainon ɗa haka zakije gidan ustaz ɗin nan kina fidda masa ɗa babu kaya a sanyi ko."
dariya tayi tana rufe fuskarta.
baki na buɗe nace "Wani Ustaz ɗin?." yace
"Ita ta sanshi ai."
da sauri tayi waje tana faɗin "Ni babu ruwa na."
ya dubi Hajiya Karima yana daɗa faɗaɗa murmushin sa yace
"Hajiya so take tasa angon ki ya kamu da mura wannan kayan ai baiyi a fito da shi ba."
baki Hajiya Karima ta washe cikin ɗan kame-kame tace "Eh haka..haka ne."
wani murmushin yakuma sake wa kana ya juya ya shige cikin bedroom ɗina.
zuwa can yafoto da shi cikin wani katon towel ya karaso inda take ya mika mata shi yana faɗin
"Hajiya ga angon naki."
baki ta washe tace "A'a kaga Ahmad ɗan Ahmad jika ga Tijjani sabil, kaman kai lokacin kana jariri."
baki ya washe yana zama kan kujerar da ke fuskantar ta yace
"Hajiya da gaske haka nake lokacin ina jariri anya nakai sa kyau lokacin kuwa?."
tace "Sosai yan da ka ganshi haka kake kai da gashi har yanzu kyan naka na nan bai gushe ba."
kallo na yayi tare da ɗaga min gira.
niko baki na taɓe a ɓangaren Aunty Rasheedat ma haka a bin yake itama bakin ta taɓe sannan tace
"Hajiya kice kun sha kallo lokacin can."
fuska Hajiya Karima ta ɗan suke tana yimata kallon kasa-kasa.
itako Rasheedat wani murmushi ta sake tare da jijjiga kai.
Ahmad kuwa idanunsa a kan ɗan da kuma hannun Hajiya Karima. tana kokarin mike wa da sauri shima ya mike yana faɗin
"Hajiya badai tafiya zakiyi ba?."
dariyar yake tayi tace "Gidan wani biki nake son zuwa direba ma yana waje yana zaman jira na, dama nazo ne naga jikar nawa gashi nan sai baccin sa yake Allah ya raya mana shi muga girman sa."
karɓar ɗan yayi a hannun ta yace "Amin amin gun gode Hajiya."
yayi mata sallama ta fita. tana fita ya matso in da Rasheedat take ya zauna tare da jan towel ɗin da ya naɗe yaron ciki yace
"Ɗau ke shi ban da towel ɗin."
ta ɗago shi da iya abin ɗaukar sa da ɗazu aka fito da shi ta rungume shi a jikin ta tana sumbatar goshin sa.
shiko Ahmad mike wa yayi rike da towel ɗin a hannunsa yanufi kasa..
numfashi Rasheedat ta sauke dan tasan komai akayi akwai wani abun.
ta dubeni da murmushi ganin yaron ya farka yana mutsumutsu tace
"HAMDAH bashi nono kin ga ya farka."
nace "Allah Aunty Rasheedat yaron nan yafiye tsotso Allah ni bacci ma nake ji kuzau na da shi

kawai ki bashi madara ya sha."
na mike tsaye na nufi bedroom ɗina. dariya tayi tace
"Madara kuma ah da sauran sa tukun kidai tai maka ki bashi ɗin."
ta biyo ni tana cigaba da faɗin
"HAMDAH karɓe shi kibashi kin ga zai yi kuka."
Inna Wuro da take cikin ɗakin tana gyara, ta karɓe shi ta miko min shi...

Rasheedat na fita daga ɗakin lokacin Ahmad ya hauro, da fuskar tambaya ta dube sa, sai ya ruko hannun ta ya janyo ta cikin bedroom din da suke kusa da shi.
suna shiga tace "Aboki me ke faruwa ne ina kakai towel ɗin?."
numfashi ya sauke yace "Nasa aje a yar da shi ne, tazo da wani irin guba mai amfani da fatar jiki yana saurin yiwa yara musamman jarirai illa acikin mintuna kalilan, shine a hannunta duk da yana cikin kwalba
amma yana da hatsarin gaske, taso yin amfani da shi wajen sakawa yaron a jikin sa, bayan ƴan mintina kuma zai shige cikin jikin sa daga nan kuma sheke nan, fatan jariri bashi da karfi koda kwalbar kaɗai ya taɓa jikin sa za'a iya samin matsala, shiyasa na saka masa towel ɗin nan ta in da koda kwalbar ya taɓa shi ma zai tsaya a iya jikin towel ɗin ne."
Ido Rasheedat ta waro cike da tsananin tsoro tace
"Aboki ya kamata kayi wani abu fa, matar nan babu ɗigon imani tare da ita, zata iya bin tawata hanyar tun da taga yanzu bukatar ta bai biya ba, nikam nafara jin tsoro."
murmushi yayi  yace "Babu abin da zata iya yi."
tace "To amma dai zaka faɗa wa HAMDAH ko dan tasan me ake ciki tadaɗa sanya ido sosai, kada ranar da baka nan kuma tazo."
yace "A'a baza'a faɗa mata ba idan aka sanar mata hankalin ta zai tashi dan ba ni da ɗan kaɗai take hari ba har da ita, idan taji kuma hankalin zai tashi za'a iya samin matsala."
cikin kaɗuwa tace "Har da ita?."
kai ya jinjina kana yace
"Muje babu komai."

Ana gobe suna da daddare Ahmad ya shigo, Inna Wuro na ganin sa ta fita, ɗan madaidaicin akwatin da ya shigo da shi ya aje kan table,
sai da ya sumbaci goshina sannan ya sumbaci Ahmad karami dake bacci.
yaɗa go kana ya zuge zip ɗin akwatin wasu kaya ne na alfarma a ciki, dogayen riguna ce irin na amare haɗe da jaka da takalmi da sarka da ƴankunne da abun hannu na gold,
tsayuwa kwatan ta muku kalar tsaruwan kayan ma ɓata lokaci ne, ya haɗu yayi kyau ya tsaru iya tsaru wa.
da sauri na mike na ɗago ɗaya daga cikin  rigunar na manna shi a jikina nace "Wannan fa kai gaskiya sunyi min kyau sosai."
murmushi yayi yace "Yanzu naje na amso su a airport jiya nasa a siya
yau aka saka a jirgi."
murna yahani tsayuwa naji daga wata kasar yasa asiya, naɗago sarkar da sai wal-wal yake yana ɗauke ido nace

"Kai gaskiya wlh duk sun yi kyau sosai fa."
dariya yayi yace "Ashe nima na iya zaɓe kenan."
nima dariyar nayi nace "Gaskiya yayi kyau sosai ka iya zaɓe kam."
wayar sa ya ɗauka ya daddanna yace
"Zo ki gani." gefen sa na zauna ina leko cikin wayar.
hotunan wani katon hall ne wan da tsaruwan sa yakai ya kawo yace
"Anan za'ayi toron bikin mu dana suna gobe da karfe sha ɗaya na rana za'a fara za'a tashi karfe 11 na dare."
da mamaki nace "Ina a gida za'ayi taron."
yace "Ina ai ba iya taron suna ba ne kaɗai har da taron bikin mu, yanzu haka ina da ba'ki waɗan da suka zo daga kasashe masu nisa sosai suna masaukin da a ka tanadar musu wasu kuma zasu iso cikin dare wasu gobe da safe."
kai na jinjina jin da gaske yake nace "Allah ya kaimu, Ukhtee ma ta kusa iso wa wata kila jirgin su ya sauko karfe 9."
yace "To bari a sa direba ya shirya zuwa taro ta, ya kamata ya isa airport kafin saukowar su."
kira ne yashigo wayar sa ya mike yana faɗin
"Wani abokin Daddy na ne ɗan Nigeria ne mazaunin Ingila, jirgin su ya iso kenan bari naje nasa a taro shi, bani number Ukhtee na baiwa direba ya tafi yanzu time zai yi."
nace to. ina bashi yafita da sauri.
da misalin karfe 9 kuwa jirgin su Ukhtee ya sauko, direba ya ɗauko ta zuwa gida, har farfajiyar gida naje na taro ta, muka rungume juna muna ihun murna.
ranar kusan kwana muka yi muna hira...

Washegari tun sassafe Hajiya Rahama tazo da me makeup dan jiya mun yi waya da ita, bayan nayi wanka na zauna a ka shiga tsantsara min kwalliya,
ana gamawa nasa Ukhtee ta zaɓo min ɗaya saga cin kayan da jiya Ahmad ya kawo min, na saka na zauna me kwalliyar tashiga naɗe min ɗankwalin kayan a kai tana gama ɗaurin, aka miko min takalli da ɗan madaidaicin pos wan da suma acikin akwatin aka ciro su, nasaka takalmin narike pos ɗin a hannu sai ɗan karamin gyale wan da aka rataya min shi a hannu, karfe 11 da minti goma a ka gama yimin komai, kowa ya tsaya kallo na kamar basu taɓa ganina ba, sai faɗi suke Masha Allah. Aunty Nasiba da Faty da Ukhtee sai hotuna suke ta yimin. hannu na wacce tayi min makeup ɗin ta ruko muka tako gaban mirror mirror'n tayi min nuni da shi tare da faɗin
"Bismilla." ina sauke idanuna kan mirror sai da naɗan girgiza, sosai na kure kaina da kallo ta cikin mirror.
sai nake gani kamar ba ni bace, "Masha Allah." nafaɗa a kasan raina, ni kai na nasan nayi kyau ba na wasa ba.
kiran Ahmad ne ya shigo waya ta na ɗaga yace
"Ki fito gani a waje time yayi fa har yaɗan go mun bar mutane acan."
nace to, nayi wa Ukhtee magana da larabci kan ta karɓi Ahmad karami dake nannun Hajiya Rahama wan da shima aka shirya sa cikin kayan alfarma wan da ɗazu Aunty Rasheedat ta aiko dashi tace a sa masa.
muka fito gaba ɗayan mu, tsayuwa nayi ina kallon kayan dake tare cikin parlour Inna Wuro da

wasu ba'ki suna zaune suna kallon kayan, nan Inna Wuro take faɗa min dangin Ahmad ne suka kawo.
nace mata zamu tafi gurin taron ne ko zata je, tace min a'a ita kam tana gida.
wasu daga cikin mutanen cikin parlour'n suka mike suka ce suma zasu.
a parlour'n kasa na iske mutane tam wasu ma ban san su ba.
nan muka ɗunguma mukayi waje.
motoci ne ajere a tsakar gidan da suka kai guda goma,
motar sakiya an bita da wani kwalliyar furanni ta sama da gefe-gefen ta, kuma kaf cikin su tafi kowani mota kyau.
da sauri wani soja dake tsaye jikin motar ya buɗe marfin gidan baya, can na hango Ahmad yana leko ni.
a hankali na karaso jikin motar, da sauri sojan yayi baya ya daɗa buɗe marfin motar, a sannu na shiga nayi wa Ukhtee magana nace ta shi gaba.
sojan ya mai da marfin ya rufe.
kana ya buɗe mata itama ta shiga,
acikin motar na tadda su Naseem sun sha wanka na alfarma kayan su iri ɗaya Nasmah har da makeup a fuskar ta, sun yi kyau sosai.
shima Ahmad ɗin wani kaya ne a jikin sa na alfarma agogo da takalmin kafar sa sai sheki suke.
ido Ahmad ya kura min babu ko kiftawa yabuɗe baki da hanci gaba ɗaya yana kallo na.
iska na hura masa a fuska nace
"Ya dai?." firgigit yayi sai ya damko hannuna yace
"Kyakkyawa ta kin gan ki kuwa kin ga yan da kika daɗa kara kyau."
murmushi nayi nace "To ai kai ma kayi kyau."
baki su Naseem suka shiga washe wa suna faɗin
"Mommy tayi kyau." nace "Kuma kun yi kyau."
Ahmad suka gaisa da Ukhtee yana yi mata ya gajiyar hanya.
jama'a kowa ya shishiga mota a ka ja motocin a jere aka ɗau hanyar hall ɗin.
tun daga farkon shiga layin da zai sadaka da hall ɗin jami'an tsaro ne ke tsaitsaye har bakin get ɗin,
baka jin komai sai tashin sautin kiɗa,
a hankali aka wangale get ɗin motoci suka kusa ciki,
cikin katon farfajiyar gurin cike yake da motoci, a haka aka rika faka motoci layi-layi.
sauran motocin da muka zo da su duk mutanen ciki suka fita suka nufi cikin hall ɗin, muna zaune cikin motar har waɗan da suka zo daga bayan mu suka shige ciki.
zuwa can Rasheedat ta fito daga cikin hall ɗin, cikin shigar ta na burge wa irin shigar manyan mata matan manyan mutane.
ta karaso jikin motar in da wasu sojoji guda huɗu suka mara mata baya,
ta buɗe gefen da nake fuska ɗauke da murmushi tace
"Ku sauko ku ake jira."
a hankali na zuro kafafu na waje na mike tsaye,
ɗaya daga cikin sojojin ya zaga da sauri ya buɗe gefen da Ahmad yake, shima ya fito, sannan a ka buɗe wa Ukhtee tafito rungume da Ahmad karami.
Naseem da Nasmah ma suka fito.

cikin harshen turanci Rasheedat tace wa Ukhtee ta bata ɗan bayan sun gaisa tayi mata maraba da zuwa kasar mu...

Naseem da Nasmah suna gaba ni da Ahmad muna biye da su, in da Rasheedat da Ukhtee ke bayan mu, Rasheedat nata gefen Ahmad Ukhtee kuma tana ta gefe na.
haka Rasheedat ta tsara yan da zamu tafi a jere,
takuma bawa Naseem da Nasmah wasu fulawa masu kyan gaske suka rike a hannun su.
a hankali muka fara takawa, yayin da sojoji huɗun nan suke biye da mu rike da bindigogin su, sun ɗaga bindigogin sama kamar masu jiran kiris.
a sannu muke takawa har muka isa bakin kofar da zai sada mu da ai nahin cikin hall ɗin.
a sannu muka kusa ciki, wani irin wal-wal haka hasken camara ke haska mu, a take aka sauya kiɗa aka saki wani zazzakar waka mai kwankwasa zuciyar masoya, ga mamaki na sai naji sunan mu ake ambata cikin wakar,
gaba ɗaya cikin hall ɗin yaɗau ki tafi raf-raf-raf, yayin da MC yashiga zuba kirari.
"Gafa taurarin sun danno farin wata sha kallo an gai da ango da amarya."
sai ya shiga bin wakar da ke tashin yana faɗin
"Ga HAMDAH sarauniya mata ga Ahmad sabil uwa ga Ahmad kaga mai farar aniya."
a hankali nake ɗaga kafata da naji tana yi min nauyi dan jama'ar da na gani cike a gun.
yayin da aka cigaba da haska mu da camara.
har muka isa mazaunin da aka tanadar mana,
kuje rune guda huɗu a jere sai wasu biyu ƴan madaidai ta a ta kasa da namu wato step ɗin dake kasa da mu.
a biyun tsakiya muka zauna ni da Ahmad Rasheedat ta zauna a gefen sa in da Ukhtee kuma ta zauna a gefe na,
Naseem da Nasmah kuma a biyun da ke kasan mu.
muna zama kuwa camara suka cigaba da haska mu,
ƴan jaridu ma aikatan gidajen TV ne ta ko ta ina a gurin sai ɗauka suke.
nan da nan akafara gudanar da biki, yayin sa ƴan wasan hausa da mawaka kowa ya fito yana nuna bajin tar sa.
taro yayi taro anyi ɓarin kuɗi,
ma'aikatan hotel da akayi odar su hotel daban-daban da suka girka kalolin abinci kala-kala. sai zubawa ake ana kaiwa tebur-tebur.
MC yace ana bukatar ango da amar ya su fito,
Rasheedat ta ɗan karkato in da yake tayi masa magana, sai ya riko hannuna ya mike kana ya mikar da ni, a hankali muka sauka muka shigo cikin filin.
wani kiɗan aka kuma sakewa shima da sunan mu cikin wakar.
yana rike da hannuna dukan mu muna tsaye, kai na na sunkuye,
yaɗan sunkuyo da kansa dai-dai fuskata yace
"Bazaki yi rawa ba."
kafaɗa na make cike da jin kunya nace
"Ban iya ba." yanayin yan da muke maganar da shi hakan yabada wani irin kala, ai ko hall ɗin ya kaure da ihu da tafe.
cike da jin kunya na kife kaina jikin kafaɗar sa.

hannu ya zura cikin aljuhu yaciro ɗaurin kuɗi ƴan 1-1k sababbi katakar yashiga lika min, yana murmushi ban ɗago ba kai na najikin kafaɗar sa,
sai da naji maganar Rasheedat daf  da ni tana faɗin,
"Ba zakuyi rawa ba." sai na ɗago tare da girgiza mata kai ina murmushi.
liki tashiga yi mana tarika ciro kuɗi cikin jakarta tana wasa mana, ta dage tarika tika rawa.
nan manya manyan mutanen dasuka taho daga kasashe daban-daban suka rika shigowa filin suna lika mana kuɗi, wasu kuɗin kasar mu wasu kuma na kasashen da suke...
kai tsaye ake nuna shagalin bikin dan daga can jikin bangon hall ɗin katuwar majiki ne ke haska duk abin da ke faruwa..
biki yayi biki
naira tayi kuka agurin....

A can cikin garin Bauchi Masa'ud ne kwance cikin ɗakin sa da waya rike a hannunsa, yana kalle-kalle a yanar gizo,
ido ya kurawa wani bikin da yaga ake gudanar wa,gani har ya shari kusan minti 5 bai ga shigowar ango da amarya ba sai ya wuce.
yana yin gaba kuwa yakuma cin karo da wannan bikin da ake hasko sa kai tsaye.
da mamaki yakurawa amaryar ido tare da maimaita sunan da yaji MC yana kira "HAMDAH!."
yafurta da karfi, yayin da hannunsa yashiga ɓari idanunsa a kan fuskarta, duk da ta kara girma da kuma kwalliyar dake fuskarta tabbas bazai taɓa iya mance fuskar nan ba.
da sauri ya mike yayi waje har yana cin karo.
tun daga bakin kofar side ɗin Mamie yashiga kwaɗa mata kira
"Mamie Mamie Mamie."
kasan cewar yau weekend ne su Aunty Rafee'at da Aunty Jaleeta sun zo gida dukan su da ƴaƴan su,
Na'ima ma tazo da nata ɗan, duk suna hallare a sashin Mamie har da Ummi.
da sauri Mamie ta ɗago jin irin kiran da yake gwaza mata sai kuma gashi ya faɗo cikin parlour'n kamar an jefo sa, ko gaban sa baya gani.
tace
"Kai Masa'ud wani irin hauka ne haka, bazaka shigo ba tun daga waje kake lafta min kira irin haka kamar wani sabon makaho."
da sauri ya karaso in da take kamar zai faɗi a kan ta hannunsa na ɓari yace
"Mamie kigani Mamie HAMDAH HAMDAH ce."
sai kuma ya sake wa Mamie wayar da sauri ya juya ya fizge rimut ɗin da ke hannun Nusaiba ya daddan na  sai gashi ya kamo ɗaya daga cikin  tashoshin da ake haska bikin kai tsaye..............!

Mommyn Twins ce

30

Masa'ud da gaba ki ɗaya jikin sa ya kama tsuma kamar zai tashi sama yace
"Mamie kun ganta wlh itace HAMDAH ce ga ta nan itace wannan."
yakai hannu yana taɓa jikin TV dai-dai fuskar ta.
gaba ɗaya cikin parlour'n suka mai da hankalin su kan TV. Aunty Rafee'at ta mike da sauri tazo jikin TV tana karewa wanda Masa'ud ke nunawa kallo, da karfi ta furta
"Wlh ita ce wlh HAMDAH ce wannan, masa musu su gani Masa'ud masa su ganta."
tayi maganar tana ture shi gefe.
Ummi da tayi mutuwar zaune tana kallon abin mamaki, sai ga hawayen farin ciki yana fitowa daga idon ta.
yayin da bakin ta ke ta furta kalmar
"Alhamdulillah³."
Mamie kuwa abun kamar a mafarki take ganin sa yayin da zuciyar ta ke ta son tunano mata abubuwan da suka faru abaya, yayin da wani abu ya taso yake ta son danni hakan.
kokawa tashiga yi sakanin zuciyar  da wannan abun da ke ta faman son danne hakan, lallai ba shakka wannan HAMDAH ce, duk da girma da cika da sauyin da ke tattare da ita, koda shekaru ɗari tayi basa tare bazasu kasa gane jinin su ba.
wasu zafafan kwalla ne masu ɗumi suka zubo mata, takasa iya furta komai kamar yadda ta kasa janye idanunta daga kan TV.
hannunta na rawa ta shiga nuna TV da yatsa yayin da bakin ta yakasa iya furta komai, sai zafafan hawayen da suka cigaba da wanke mata fuska.

Da gudu Aunty Jaleela taje ta rungume Aunty Rafee'at tana faɗin
"Wlh ita ce HAMDAH ce Aunty Rafee'at da gaske ita ce."
Nusaiba da Fauzan ma suka mike suka rungume su suna faɗin
"Aunty HAMDAH ce wlh ita ce."
parlour'n ya kaure da hayaniya da ihun murnar da su Aunty Rafee'at suke..

A ɓangaren Na'ima kuwa tun san da ta sanya idanunta kan HAMDAH dake cikin TV, tayi wani irin daskarewa
a zaune a gurin, wani irin bugawa kirjin ta yayi da mugun karfi har sai da takai hannu ta dafe kirjin nata, cikin tsananin firgici da kaɗuwa.
su Abbu da suke zaune cikin parlour'n  da suke zama shi da Abba, jin hayaniyar dake fita daga cikin side ɗin Mamie yayi yawa sai suka mike da sauri suka fito.
dai-dai lokacin motar SALEEM yashigo gidan, daga cikin mota ya hangi yan da su Abbu suke sauri suka nufi side ɗin Mamie.
cikin hanzari ya faka motar yafito yarufa musu baya.
a kusan tare suka shiga parlour'n Mamie.
 Abbu ya buɗi baki da zumbar tambayar abin da kefaru idanunsa ya sauka kan TV dai-dai lokacin da aka hasko katon hoton HAMDAH wan da ya maimaye fuskar TV gaba ɗaya,
inda ɗan jarida yake faɗin
"HAMDAH kenan  shahararriyar ƴar kasuwan nan wacce aka fi sani da *HAM'NAS CO PETROLEUM NIGERIA LIMITED*
ayau ne ake gudanar da shagalin bikin su da kuma murnar samun karuwan ɗa da sukayi, ita da mijinta shahararren attajin nan shahararren ɗan kasuwan nan wacce duniya ta sanshi wato *AHMAD TIJJANI SABIL* ."
sai a ka ɗauke hoton ta kana aka kuma sakin wani katon hoto, tana tsaye rike da jariri Ahmad na tsaye a gefen ta ta dama yaɗan leko fuskar ta suna yi wa juna murmushi, in da Rasheedat ke tsaye gefen ta na hagu, Naseem da Nasmah suna tsaye a gaban su suna dariya,
ɗan jaridar yaci gaba da faɗin
"Kai tsaye ake gudanar da shagalin bikin, gamu nan a filin taron, biki yayi biki jigajigan shararrun ƴan kasun nan kuma ma'aurata Ahmad Tijjani Sabil da amaryar sa HAMDAH wacce akafi sani da *HAM'NAS* Co petroleum Nigeria limited,suna cike da murna da farin cikin kuma samin karuwa da farin cikin karuwan family'n su, muna nan zamu cigaba da kawo muku yan da bikin take kasan cewa a filin taron kai tsaye kucigaba da biyo mu."
shagalin bikin aka cigaba da nunawa...

Kamar a mafarki kamar abun almara haka dukkanin su suke kallon.
yanayin da Mamie ta shiga shi Abbu ya shiga, sai nuna TV yake da yatsa, Abba kam baya yayi ya jingina da jikin garu yayin da idanunsa shima ke kan TV.
a ɓangaren SALEEM kuwa wani irin wawan burki yaja yatsaya cak daga bakin kofa, yayin da zuciyar sa tayi wani irin tsalle tamkar zata faso kirjin sa ta fito,
wani irin rumtse idanunsa yayi da mugun karfi yakuma ware sa a kan TV,
dai-dai lokacin da Ahmad ya rungumo ta ita da baby'n su suna dariya, yayin da wani bature yake yi musu liki.
da karfi ya kai hannunsa ya dafe kahon zuciyar sa,da yake wani irin tafarfasa, wani tari ne ya suɓuce masa yashiga yin sa babu ko kakkautawa yana mai cigaba da damke kirjin sa,
baya yashiga yi hannunsa na dafe a kirjin sa.
Masa'ud ne yalura da halin da yake ciki da sauri ya isa in da yake,  yana faɗin
"Ya SALEEM sannu ka shake ne bari na kawo maka ruwa."

hannu ya ɗaga masa kana yayi waje dafe da kirjin sa yana mai cigaba da tarin...
zumbur Na'ima da zufa yashiga keto mata ta mike tsaye ta tsaɓe ɗan ta tayi waje da sauri, mai adaidaita ta tsare yakai ta gida, tana shiga gida hankali tashe takira kawar ta Raliya a waya tana ɗagawa tace
"Raliya kina ina." jin yan da tayi maganar hankali tashe yasa Raliya faɗin
"Aminiya me ya faru? ina gida yanzu dai nake shirin fita."
tace "Kizo gida yanzu-yanzu akwai matsala."
Raliya tace "Wacce irin matsala kin tsinkar min da gaba."
cikin tsananin tashin hankalin da take ciki tace
"Ashe yarinyar nan bata mutu ba tana nan a raye, ashe ita ce mai kamfanin *HAM'NAS* mai *HAM'NAS* Co Petroleum Nigeria Limited."
Raliya tace
"Wai wa kike magana ne kam ban gane ba."
tace "HAMDAH HAMDAH nake faɗa."
da karfi Raliya tace "Wacce HAMDAH ke bari gani nan zuwa."
tana kashe wayar ta zari makullin mota tayi waje,
tarika kai wa da kawowa a parking space har Raliya ta iso. Raliya
tace "Wai me kike faɗa min ne kina nufin kice min HAMDAH bata mutu ba tana raye kuma anan kusa?."
da sauri Na'ima tashiga mota tana faɗin "Shiga shiga zakiji komai a hanya kada mu ɓata lokaci."
Raliya na shiga ta figi motar da mugun gudu suna fita a gidan Na'ima
ta dubi Raliya hankali a mugun tashe tace "Aminiya HAMDAH na da rai ko kin san ita ce me kamfanin *HAM'NAS* sai gata ɗazu ana nuna ta a TV ita da wannan mai kuɗin Ahmad Tijjani Sabil amatsayin miji da mata, Raliya ina cikin muguwar tashin hankali gurin boka zamu je yanzun nan, shi da yace baza a sake jin ɗuriyar ta ba kwasam sai na ganta cikin daula, dole na sake sabon shiri ya daɗa jefa ta can da nisa, taya ne ma ta kasan ce haka ina wlh da sake wai HAMDAH ce tazamo mai kuɗi kuma wai har ta auri hamshakin attajiri, wani bokan ne yabata sa a haka."
kirji Raliya ta buga tace
"Wai da gaske HAMDAH ce mai kamfanin *HAM'NAS* amma taya akayi haka? kai amma ni ina da kokon to kan lamarin."
Na'ima tace "Ga abu a fili a TV naganta da idanuna ba faɗa min akayi ba, muje gurin boka bamuyi haka da shi ba maza-maza yakashe ta kawai idan ba mutuwa tayi ba bazan taɓa samin sukuni ba."
gudu Na'ima take shararawa har suka iso dajin da bokan yake,
a gindin bishiyar da suke faka motar su a duk san da suka zo gurin bokan a nan suka faka motar suka fito.
da sauri suka nufi in da bukkan bokan yake, tun kan su haura kan tudun da zai sada su da bukkan suka rika jiyo gurnani da wani irin kara mai firgitar wa,cike da fargaba Raliya ta dubi Na'ima tace
"Ko kinji abin da nake ji?."
cikin bushewar zuciya
Na'ima tace "Naji yanzu haka wani gaggarumin ai ki yake muje a shigar da namu gaba ɗaya ayi

akashe ta na huta."
suna haurawa saman tudun babu shiri suka ja wani wawan burki, gaba ɗayan su jikin su ya ɗau ɓari.
bakon suka hango kwarkwasa sun maye jikin sa tun daga saman sa har kasa ko fuskar sa ba'a iya ganin, sun cike ko ina a jikin sa, kunne ido baki hanci ta ko ta ina sun baibaye sun rufu a jikin sa yam-yam.
shiko sai wani irin kara da gurnani yake, sai ya yanki jiki ya faɗi akasa ya goga fuskar sa a kan duwatsun da suke gurin yayi ta goga wa jini yana fita, yakuma mike wa yakuma faɗuwa kamar wan da ake ɗaga shi ana buga shi da fuska, kwarkwasar nan kuma suna nan a jikin sa.
da mugun gudu suka juya ganin wasu kwarkwasan suna gangaro wa in da suke, nan take bokan nan yakuma yin sama kamar wan da aka ɗaga shi sai gashi cikin wutar da yake hurawa domin yin wani asirin sa ko shan ɗumi.
yayi ta birgima yana bige-bige da kara haɗe da gurnani mai firgitar wa cikin wutar.
Raliya da Na'ima har suna rige-rigen shiga motar har gindin motar kwarkwasar na suka biyo su Na'ima ta ja motar a guje suna waigen bayan su da duba kasan kafar su ko kwarkwasan sun biyo su..
sai da sukayi nisa sosai kafin Na'ima ta dubi Raliya tana haki tace
"Raliya boka ya mutu yanzu meye mafita?."
Raliya tace "Gurin wani bokan zamu je ai basu kare ba."
daga nan suka nufi gurin wani bokan
da Raliya ta faɗa mata ita ma wata kawar tace ta nuna masa gurin sa.
suna zuwa bayan sun gama zayyane abun da ya kawo su, bokan yace
ta ajiye miliyan 10 wan da za'a fara ai ki da shi, dan ai kin nata babba ne.
babu wani dogon nazari ko tunani ta ajiye masa check ɗin miliyan 10.
yace suje nan da kwanaki biyu su dawo...

A ɓangaren su Ummi kuwa kowa ya tsurawa TV ido in da ake kan cigaba da gudanar da biki, yayin da su Ummi Mamie Aunty Rafee'at Aunty Jaleela Ya Masa'ud Fauzan Nusai ba, duk kanin su hawayen farin ciki ne ke zuba kan fuskokin su.
Abba da Abbu kuwa ido suka zubawa TV kawai, har kuma lokacin suna tsaye da ƙafafun su, duk kanin su kuma sun kasa iya furta komai sai zuciyoyin su dake ta ambaton sunan Allah dayi masa godiya.
a hankali suka rika jin zuciyoyin su tana washewa tamkar ana ɗaga musu wani nannauyar dutse data danne musu zuciya.
Abba Abbu Mamie a tare suka dafe kirjin su da suka ji kamar an fincike wannan abu mai nauyi an cire sa gaba ɗaya,
a tare suka sauke nannauyar numfashi...
a ɓangaren SALEEM da tun fitar sa daga parlour'n ɗakin Masa'ud ya shiga ya kwanta kan gadon sa, dafe da kirjin sa har kuma lokacin yana dafe da kirjin nasa, wacce take yi masa wani irin mugun zafi, a take shima yaji kamar an fige masa wani abu mai nauyi cikin zuciyarsa, sai dai zafi da zugin da zuciyar tasa take masa...

Acan cikin parlour'n kuwa Mamie ne tayi  wani irin mike wa tare da furta "Wlh HAMDAH ce tabbas ita ce, Alhaji baka ganta ba?."
tayi maganar tana duban Abbu.
Abbu yashiga gyaɗa kai yana nuna TV da yatsa tare da faɗin
"Tabbas ba shakka ita ce."
wani hawayen farin ciki ne yakuma zubowa kan fuskar Ummi, ganin yan da sukayi firgigit tamkar waɗan da suka farka daga bacci, tasan dole watarana gaskiya zatayi halin ta.
Abba kuwa cikin matukar nadama yake kallon ɗiyar tasa daga cikin TV.....

Abuja
Har wajen magriba ana ta kan gudanar da shagalin bikin, salla ce kaɗai take ɗaga wasu agun.
da misalin karfe 11 na dare aka rufe taron bayan an cike waɗan da suka zo bikin da kayan da Ahmad yasa a tanada domin duk wan da ya ziyarci bikin,
duk wan da yazo bikin idan macece turamen manyan zani guda biyu da kuɗin ɗinki naira dubu goma acikin jaka mai ɗauke da katon hoton Ahmad karami a jiki.
idan kuma na miji ne tsadadden shadda ne shima guda biyu haɗe da kuɗin ɗin kin sa a cikin jakar.
a gajiye muka fito daga cikin hall ɗin mota ta kwashe mu.
ga mamaki na sai na ganmu a airport,
da fuskar mamaki na dubi Ahmad nace
"Rakiya muka zo ne?." da murmushi kan fuskarsa sa yace "Mu aka zo raka mu."
nace "Ina?." nayi maganar ina waro ido.
kumatu na yaja kana yace "Lagos zamu, gobe za'ayi bikin buɗe Company ki na can, wan da ɗana ya hanaki samun sukunin buɗe shi."
baki na buɗe zanyi magana sai aka buɗe marfin motar,gefen sa da fege
na, sai nayi shiru na fito kawai.
direct cikin jirge muka shige anan na tadda wasu daga cikin mutanen da suka halar ci bikin mu waɗan da suka zo daga wasu ƙasashe har da wasu ɗaiɗai ku ƴan nan kasar mu,
a can kujerar gaba na hango Bappa yana zaune, acikin jirgin nake faɗa wa Ukhtee in da zamu je, na tausaya mata ganin yana yin ta na san tafaji sosai.
a jere suka zauna da Aunty Rasheedat da Naseem da Nasmah, in da muka zauna ni da Ahmad a kujerar bayan su, yana rungume da Ahmad karami...
muna isa motoci suka kwashe mu suka kai mu masauki, ni da Ukhtee ɗakin mu ɗaya Naseem da Nasmah kam ma ban ga idanunsu ba.
a gaye muka shiga rage kayan kijin mu,
ganin Ahmad karami ya nata mita nasan cewa wan ka yake bukata, na tuɓe sa naje nashiga dashi bayi nayi masa wanka cikin bathtub dan dole sai dai nan ɗin tun da ba bu bawo da zan masa a ciki, na naɗo sa a towel ɗin sa na sauya masa wani kaya, dan gani kawai nayi an biyo mu da akwatin mu.
sai da yayi bacci kafin na shimfida shi, lokacin Ukhtee tafito daga wanka, nima na shiga nayi

wan ka, yau kam babu wani hira muna kwanciya dukan mu sai bacci..
washegari ban farka ba sai wajen karfe 9.
ko da na farka na tadda Ukhtee har tayi wanka, ina dira a gadon Ahmad na buɗe ido, sai da na fara yi masa wanka kafin nima nayi. kayan
breakfast ɗin da aka shigo da shi tun ina bacci, bayan na shirya na zauna muka yi breakfast ɗin, sai san nan naje na ɗau wayata da na kashe ta tun jiya isowar mu na kunna.
ai ko ina kunnawa sai ga kiran Ahmad ya shigo, yace
"Kyakkyawa ta an tashi lafiya ya gajiyan jiya."
nace "Gajiya ya washe."
yace "Alhmdllh Nagode wa Allah, ina Ahmad ya tashi kuwa ga su Naseem har yanzu basu farka ba." nace
"Shikam ina tashi shima ya farka gashi nan yana ta rarraba idanu."
dariya yayi yace "Sa masa wayar kusa da shi naji numfashin sa."
wayar na kawo kusa da shi nace "Daddy na magana." murmushi yayi mai sauti yace "Shafa min kansa." nace To.
yace "Anjima karfe 12 za'a tafi gurin nan, karfe 2 za'a gama yau zamu koma gida."
nace "To Allah ya kaimu."
yace su Naseem sun tashi bari ya yi musu wanka zasu shigo nace to...

Da misalin karfe 12 da kwata gaba ɗayan mu muka hallara a farfajiyar hotel ɗin.
nan motoci suka rika kwasan mutane suna tafiya da su.
kamar yan da muka tafi wancan filin taron jiya motar mu ɗaya da shi yau ma haka,
tun daga wajen kamfanin har cikin sa an zagaye shi da adon fulawa, a katafare filin da ke cikin kamfanin aka gudanar da taron, wan da mai girma Gwamnan Lagos shine babban bako a gurin taron da sauran mukarraban sa.
an gudanar da taron cikin lumana da kwanciyar hankali in da ake nuna taron kai tsaye a kafafen sadar wa.
anan gurin aka tantance ma'aikatan da suka nimi yin ai ki a kamfanin, aka kara akan wan da dama can aka tantace su kwararru masana ai kin...
karfe 2:30Pm aka watse a taron kowa ya kama gaban sa, a ranar wasu suka koma kasashen da suka fito wasu kuma sai zuwa gobe.
da misalin karfe uku jirgin mu ta ɗaga zuwa Abuja.
muna isa yau washegari Ukhtee tace zata koma, Ahmad yayi mata cuku-cukun komawa sai dai ba'a sami jirgin da zai tafi Saudi kai tsaye ba dole na dubai zata bi, daga can sai ta shiga jirgin Saudi.
har airport muka yi mata rakiya Ahmad na ta yi mata godiya, bayan cike ta da yayi da goma na arziki.
lokacin da ake sanar wa kan fasinjoji su shigo cikin jirgi sai muka rungume juna muka fashe da kuka, da kyar Ahmad ya ɓanɓare ni a jikin ta jin ana ta cigaba da sanar wan, ta wuce cikin jirgi muna ɗagawa juna hannu...
a mota yayi ta lallaɓe na har sai da yaga nayi dariya, ya dube ni fuska ɗau ke da sihirtaccen murmushi mai bayyana zallar so da kauna yace "Ina son ki kyakkyawa ta."
idanuna na lumshe kana a hankali na kwanto da kai na jikin kafaɗar sa a hankali cikin yin kasa

da murya nace
"Nima ina son ka My."
wani irin wawan burji ya ja,  da sauri na buɗa idanuna na ɗago kaina da sauri cikin hanzari na dafe gefen kujerar moton jin yan da nayi gaba kamar zan garu da gaban motar.
a gefen titi yayi parking, ya wani irin jan yo ni ya rungume tamkar zai cusa ni cikin jikin sa, yace "Nagode kyakkyawa ta Nagode da jin fitar wannan kalma daga bakin ki, ako da yaushe zaman jiran sa nake naji yafito daga bakin ki,
ina son ki! ina son ki!! ina son ki!!!, ako da yaushe kamar daɗa kara min son ki ake."
sai ya shiga sumbatar fuskata takota ina, yarika manna masa kiss,
ya ruɗe yagama zauce wa, sai kokarin daɗa nuna min yanda yake so na da kuma kauna ta yake.
sai da na janye jikina da karfi nace Ahmad na gida zai iya yiwa Inna Wuro kuka.
kafin ya ja motar muka bar gurin,
yana tukin sai ya juyo ya sumbaci kuma tu na, aha muka isa gida.
ranar bai matsa ko nan da can ba yana like da ni, karshe Inna Wuro fita tayi ta bar mana side ɗin gaba ɗaya sai dare ta dawo....

Bauchi

Ranar da aka gudanar da toron buɗe Company HAMDAH duk ka family'n su suna gindin TV, Aunty Rafee'at da Aunty Jaleela suna daga gida jen su suna waya a gida, cike da  murna suna tambayar suma suna kan kallo ko.
Ummi farin cikin ta har ya gaza ɓuya duk tarin kawai cin ta.
washegari da sassafe Ummi ta tashi da shiri, Abba ya shigo ya same ta tana ta shiri, da ɗan mamaki ya dube ta yace "Shirin me kike ta yi haka?."
tace "Gurin ɗiya ta HAMDAH zani."
ta faɗa a takai ce ta cigaba da shirin ta.
Abba yaɗan yi gyaran murya kana yace
"Yan zu muka gama magana da Yaya Idris ya kama ta ki bari mu shir ya tafiyar duka."
da sauri Ummi ta ɗago ta dobe shi tace
"Babu abun da zai hanani tafiya yau sai ikon Allah, idan kana tunanin cewa ma zaka kuma dakatar da ni ne, kamar lokacin da kayi hakan a lokacin da take bukatar taimako da mafaka, na amin ta nayi maka biyayya to ka sani a yanzu bazan taɓa hanuwa ba, zan fita naje na nimo ƴata tun da har Allah ya nuna min tana nan da ranta, sai dai daga nan kakuma cewa kada na dawo maka gida,
ko ban same ta ba na tabbata banyi asara ba."
shiru Abba yayi yana kallon ta yayin da jikin sa gaba ɗaya yayi sanyi,
tabbas yasan Ummi mata ce mai hakuri da kawai ci, duk da shi ya kori HAMDAH da kansa ko dai-dai da rana ɗaya bata taɓa nuna masa ɓacin rai ba, kuma bata gushe kan biyaytar da take masa ba.

yana tsaye tagama shirin ta ta ɗau mayafin ta, taɗau jakar ta tayi waje.
ya biyo bayan ta yana faɗin
"To ki tsaya direba ya kai ki." bata ko saurare shi ba.
a sakar gida suka haɗu da Abbu ya tambaya ina zata, Abba ya faɗa masa, Abbu ya jinjina kai cike da yabawa da hakuri da kawai ci irin na Ummi yacewa Abba kada ya dakatar da ita da tafiyar, tafiyar nata shine zai samar mata da nutsuwar data rasa shekarun baya da suka wuce tun barin HAMDAH gida, wan da ta rika dauriya da juriyar iya danne shi ta barwa ranta...

Ummi na fita a dai-dai ta ta tsara ya kaita tasha daga nan ta shiga motar Abuja, idan bata man ce ba anan taga taron bikin farko da su HAMDAH sukayi, kuma taji ƴan jaridun suna faɗin daga Abuja,
taɗau haryan Abuja da tunanin idan ta neme ta bata same ta ba zata wuce Lagos in da taga an gudanar da taron buɗe kamfanin ta.........!

Mommyn Twins ce

31

Koda Ummi suka iso Abuja ta sauka a tasha, tunanin ta in da zata fara ta shiga yi.
mene ne abin yi tayi tambaya a babban gari irin wannan tana ganin kamar babu mafita a yin hakan,
to amma ai HAMDAH ta sanu a yanzu wata kila baza ta sha wuya wajen samo ta ba.
da ire-iren irin waɗan nan tunanin ta tsare mai abun hawa, ko da mai taxe ya tsaya ya leko ta yana faɗin
"Hajiya ina zuwa?." tace "Malam ko kasan gidan wata da ake cewa HAMDAH?."
ɗan shiru yayi alamun tunani kana yace

"Gaskiya ban sani ba wace unguwar take?."
tace "Ban san unguwar da take ba." yace "To in banda abin ki Hajiya zaki tsari mai abin hawa baki san in da zaki ba, a gari irin wannan zaki tambayi wata batare da sanin adireshin ta ba ai ba lallai ki iya samin ta ba ko a kauye ba'a haka bare a birnin tarayya."
yaja taxes ɗin sa yayi gaba. Ummi tace
"In sha Allah zan same ta ko batare da adireshi ba."
wani ta kuma tsare wa shima irin tambayar da tayiwa wancan shi tayi masa,kusan irin amsar da wancan ya bata irin shi shima wannan ya bata.
ta tsari masu taxe da suka gai kusan guda goma duk kusan amsa iri ɗaya suke bata idan tayi musu tambaya kan sun san gida wata da ake cewa HAMDAH...
har yamma tana tsaye a bakin titi, wani mai taxe yazo zai wuce da ido kawai ta bishi dan har ta gaji da tsare masu abun hawa, ta fara tunani ta sami masauki ta huta dan ma Allah ya taimake ta tayi salla cikin tashan lokacin da suka sauka.
har ya ɗan gota ta sai ya dawo da baya yace
"Ina zuwa Hajiya?. a ɗan gajiye ta dube shi tace "Masauki mafi kusa da nan."
yace "Hotel kenan?." tace "Eh." yace "To shigo muje." taɗau jakar ta tashige cikin motar da bismilla.
har sun fara tafiya sai me taxe ɗin ya ɗan waigo kana ya mai da idanunsa ga titi yace
"Babban hotel kike so a kai ki ko me ɗan dama-dama?." tace "Me ɗan saukin kuɗi dai wanda bazan kashe yafi dubu hamsin ba."
kai ya jinjina kana suka cigaba da tafi,
sun iso daf da hotel ɗin me taxe yace "Yau wa gamu mun iso bari na karasa da ke can basai kin tsallaka ba sai ki shiga."
tace to. baki ya washe "Amma Hajiya a garin nan fa komi dare ana samin mota duk garin da kike son zuwa zaki sami mota, ai da zai fi miki akan ki kashe kuɗi mai yawa gara ki shiga mota ki wuce gaba ɗaya,
ko da shike manya basu fiye son zaman mota da yawa ba wai shima wahala ce agurin su, kai talaka kam gara ka wuce ɗin ka adana kuɗin da zaka nimi masauki kayi wata bukatar da shi."
yakara sa maganar yana cigaba da washe baki.
Ummi tace "Allah ya rufa mana asiri duniya da kiyama, amma ba wani gari zanje ba iya ka ta nan garin idan ban dace ba kuma sai na wuce Lagos,
ni gidan wata nake nima tun ɗazu na iso garin nan gashi har yamma tayi, ina ta tambaya ban dace ba."
yace "Tambayar gidan wata a cikin garin nan, gaskiya zai yi wuyar samu in ba wai kasan adireshin gidan bane, to ke baki da lambar ta ne ki kirata tayi miki kwatance?."
Ummi tace "Bani da lambar ta."
yace "To gaskiya zaki sha wuya ne kawai wajen neman ta, manya ne waɗan da aka sansu akasar sune idan kashigo niman su cikin garinnan bazaka sha wuya wajen samun su ba, tun da sun sanu yawanci zakiga an san su, gaskiya zaifi ki koma gida ko kuma ki kira aturo miki lambar ta sai ki neme ta, amma ya sunan ta ko sunan wani wan da take kusa da su wata kila manya ne tanan zaki iya dace wa?."
tace "HAMDAH sunan ta." yace "Wai to Allah yasa ki dace."
tace "Amin ngd." dai-dai nan yagyara fakin ta sauka ta biya sa kuɗin sa, taɗau jakar ta ta

gangara hanyar da zai sada ta da cikin hotel ɗin.
har ta kai bakin get ɗin hotel ɗin taji ana faɗin
"Hajiya Hajiya Hajiya." ta juyo dan gani ko da ita ake sai taga mai taxe ɗin nan ne yayi ribas ya dawo da baya, kanta ta nuna alamun ita yace Eh.
sai ta juyo ta nufi in da yake.
kansa ya leko ta window motar yace
"Hajiya kika ce meye sunan wan da kika zo neman ta?."
tace "HAMDAH." yace "Babu wani inkiyar ta HAMDAH ɗin ne kaɗai?."
shiru Ummi ta ɗan yi tana son tuno sunan da taji an kira ta da shi a TV da kuma wan da ta taɓa gani a wani gidan mai.
mutumin yace "Dama akwai wata ce me irin sunan nan sai dai tana da inkiya, mutane da dama basu san ta da ai nahin sunan taba sai inkiyar nata,sau ɗaya nataɓa jin ainihin sunan nata shine nake tuna nin ko ita ɗin ce."
Ummi tace "Tabbas akwai sunan da ake kiran ta da shi amma naman ce."
yace "To wata kila ba ita bace ni wanda na sani idan kuma ban mance ba HAMDAH baji an faɗa amma sunan da aka fi sanin ta dashi shine wan da take amfani da shi kan kamfanoni da gidajen mai asibitoti da sauran su, shine *HAM'NAS* ita kuma matar Ahmad Tijjani Sabil ne."
da sauri Ummi tace "Kwarai kuwa tabbas ita ce so nake na tuna "*HAM'NAS* ɗin na mance, dan Allah bawan Allah kai ni gidan nata."
yace "To a gaskiya dai ni ban san gidan ta ba gidan Ahmad Sabil ɗin kaɗai na sani kuma ance gidan ta da ban ne, sannan kuma gidan sa a gaskiya akwai matakan tsaro ko na kaiki ma ba lallai bane a barki kishiga in ba wai an san da zuwan ki bane."
ɗan shiru yayi sai kuma yace "Amma dai shigo mu je tun da kin ce ita ce samun gidan ta bazai bada wuya ba sai muyi tambaya."
godiya Ummi tashiga yi masa da addu'ar samun nasara a rayuwar sa.

Tun daga gurin suka fara tambaya har suka sami wan da yayi musu kwatance har unguwar da take da kuma lambar gidan.
suna isa dai-dai gida mai lambar da aka faɗa musu ya tsaya yace da ita sun iso, ta sauka tayi ta masa godiya kana ta bak
shi 5k, ya karɓa shima yana yi mata godiya, kana yaja motar sa yayi gaba.
ido ta zubawa katon gidan wan da tsaruwan sa ya kai ya kawo a ranta take faɗin.
anya kuwa gidan ne, anya ma kuwa HAMDAH suka gani a TV ko dai idanunsu ne ke yi musu gizo, ko dai wata ce me irin sunan ta suka gani suke tunaɗin ɗiyar su ce?.
kai ta jinjina yayin da jikin ta ya ɗanyi sanyi da tunanin afili ta furta
"Sai na ga wannan ɗin idan na tabbatar da ba ita ba bace sai na tafi na cigaba da niman ki HAMDAH."
a hankali ta karaso bakin get ɗin ta kwankwasa har sau uku, kana mai gadi ya taso ya buɗe karamar kofa ya leko kansa yace
"Wane ne?." tace "Nice." yace "Gurin wa kika zo?." tace "Gurin HAMDAH." ɗan shiru yayi kana yace "Tasan da zuwan ki ne?."
Ummi tace "Bata san da zuwa ta ba."
yace "To ba a bamu masaniyar cewa wata zata zo ba ki nimi izinin shiga kafin idan aka sanar

mana sai ki shigo."
yana kokarin mai da kofar yarufe
tayi saurin cewa "Dan Allah kace mata Mamar ta ce ta zo."
yace "Maman ta haba Hajiya mun saba jin irin wannan."
ya mai da kofar zai rufe da sauri tamaso bakin kofar tana faɗin
"Ganin ta kawai zan yi idan ba ita bace bama ni zan tafi." wani
security ne ya mike daga in da yake zaune ya zo bakin kofar yana faɗin "Mene ne wa tazo gurin sa?."
maigadi yace "Wai gurin Hajiya ta zo wai ita mamar Hajiya ce, nace mun saba jin irin wannan masu neman taimako su rika fakewa da ƴan uwan ta ne sai sun shiga kaji babu abin da ya haɗa su."
jami'in tsaron yace "Ita ta gayyaci ki ina katin shaidar."
Ummi tace "Bata san da zuwa ta ba kuce mata mahaifiyar ta ce tazo."
sauran security suka mike daga in da suke tsaye cikin faɗa suka ce
su rufe kofar takira a sanar musu tukun abar ta ta shigo.
maigadi ya rufe kofar.
yana faɗin "Mutane babu godiyar Allah kaduba wannan matar kwata-kwata batayi kama da mabukata ba amma hali irin na mutum kabari a bawa na kasa da kai wai kai ma sai ka nimi kari."
Faty da ta fito daga side ɗin su zata je gidan makotan su gurin kawarta, ta nufo bakin get tana hango yan da security suke magana da faɗa-faɗa da alama dai da wani wanda ya nimi shiga gidan suke,
ta karaso bakin get ɗin, mai gadi ya mike ya buɗe mata get tasa kai zata fita, sai ta hango Ummi a tsaye a gefe tayi jigum.
sai ta leko tace wa maigadi
"Wace ce wannan ɗin?." mai gadi yace "Wai gurin Hajiya tazo kuma mu Hajiya bata bamu masaniya kan cewa wata zata zo ba, wai cewa tayi ita mamar Hajiya ce."
Faty ta dube ta kana ta karasa fita waje."
kana mai gadi ya mai da kofa ya rufe.
har Faty tazo zata gota ta sai ta ce mata sannu.
Ummi ta amsa da yauwa, kana ta wuce.
Ummi kuwa gefe da get ɗin ta nima guri ta zauna, a ranta take ayyana bazata tafi ba har sai taga wannan HAMDAH'N idan ba HAMDAH'N ta nane
sai ta tafi...

Har Faty ta gama zaman ta gurin kawar ta tafito lokacin yamma tayi sosai,
tayi mamakin gani matar nan har lokacin zaune a gurin.
har tazo bakin get zatayi knocking sai ta juyo ta dubi Ummi daɗan fuskantar tausayi ganin ta zauna shiru, tace "Wai Adda HAMDAH kika zo gurin ta?."
da sairi Ummi ta juyo tare da gyaɗa mata kai, Faty tace "To ki kirata ki sanar mata kina bakin get zata sa mai gadi ya barki ki shigo, in ba haka ba security baza su barki ki shigo ba."
Ummi tace "Bani da lambar ta, amma dan Allah kice mata mamar ta ce ta zo."
kai Faty ta gyaɗa da mamakin matar jin tace wai ita mamarta,ita kuma wannan kalar nata salon

kenan ko ba komai in ta faɗi haka ai za'a barta tashiga, gata kuma zubin ta baiyi kama da irin masu zuwa suna karyace-karyacen nan dan a barsu su shiga cikin gidan ba.
kai Faty ta jinjina.
sai tayi knocking maigadi ya buɗe ta shige ciki.
Ummi ko zama ta kuma gyara wa.
ganin lokacin sallar magriba saura kaɗan ga unguwar shiru babu ko motsin mutane, tun da ta zauna ita dai bata ga wani mutum yazo ya wuce ba sai dai motoci ɗai-ɗai ku su zo su wuce, unguwar shiru kamar babu bil'adam, sai sautin kukan karnukan gadi.
a hankali Ummi ta mike tazo jikin get ɗin ta kwankwasa.
mai gadi ya buɗe ido ya waro yace
"Har lau kece?."
a fusace security suka tambaye sa waye?
yace musu "Matar ɗazun ɗin nan ce." a fusace ɗaya daga cikin su ya mike yafito yace mata maza-maza ta bar bakin get ɗin nan tayi nesa da gidan nan tun bai sa bindiga ya harbe ta ba, ya ɗaga bindiga yana faɗin tayi sauri ta bar eriyan nan.
ai ko da sauri ta ɗau jakar ta tasoma tafiya, cike da takaicin wai ita ce ake yiwa korar kare irin haka, amma babu komai zata jure koma mene ne har idan zata samo ɗiyar ta...

Acikin gidan kuwa Faty na zaune a parlour ganin Bappa ya mike yana faɗin
"Lokacin salla ya kusa bari na shiga Masallaci."
da sauri ta mike tace
"La na mance wata mata tun ɗazu ta zo tana bakin get security sun hanata shiga, wai cewa tayi ita mamar Adda HAMDAH ce, na mance naje na faɗa mata ko zata sa a barta ta shigo wata kila taimako ta ke nima."
tsayuwa Bappa yayi kana yaɗan yi shiru yace
"Tace ita maman ta ce?." kai ta gyaɗa tana mike wa da faɗin
"Bari naje na faɗa mata Allah ta ban tausayi tun ɗazu take zaune a waje."
Inna Wuro tace "To shine tun tuni baki je kin faɗa mata ba kika zauna shiriri ta, ace tunruni tana waje ai ko kuɗin mota aka bata zata ji daɗi."
waje Faty tayi tana faɗin "Yan zu zanje na faɗa mata ai wata kila har yanzu tana waje dan ko shigo wa ta ma a waje na barta."

Ina daga parlour'n sama najiyo muryar Faty a parlour'n kasa, Ahmad na zolayar ta budurwar Ustaz tana ce masa ita bata ma sanshi ba,
ta hayo saman tana dariya.
na sako kai na zan sauko ita kuma zata shigo parlour'n sama tace
"Yauwa Adda HAMDAH dama gurin ki zan je, tun ɗazu wata mata tazo tana bakin get security sun hanata shiga tace wai ita mamar ki ce, su kuma suka ce karya take so take abarta ta shigo kawai."
ido na waro tare da dafe kirji nace
"Wai ita mama tace?." kai Faty ta gyaɗa min. da sauri nace "Tana ina?." tace "Tana bakin get."
da saur na wuce ta ina faɗin

"Ina so na ganta babu wan da ta taɓa zuwa tayi karyar cewa ita mama na ne, sai dai suce su ƴan uwa na ne, ina so na ganta."
nayi maganar ina karasa sauka daga step da sauri, gaba ɗaya jikina ya ɗau kyar ma,
cikin hanzari na nufi kofa da sauri haɗe da sassarfa nayi waje.
da sauri  Ahmad ya mike rungume da Ahmad karami yana tambayar Faty ta faɗa masa ko mene ne, bayan na yabi da sauri su Naseem suka biyo sa...
tun daga farfajiyar gidan naɗaga murya ina faɗin
"Mai gadi ina matar take."
har na karaso get ɗin, da sauri msi gadi ya mike yace "Hajiya an kore ta ta tafi."
murya a hargitse nace "Kuje ku kira ta yan zu ku dawo da ita ina so na ganta."
cikin hanzari biyu daga cikin security sukayi waje suka lelleka kana suka dawo suka ce, basu gan ta ba.
ganin yan da gaba ɗaya lokaci guda na ruɗe cikin tsawa Ahmad yace
"Kuje ku nemo ta yanzun nan kuzo da ita."
ai ko da sauri sukayi waje.
niko tsayuwa na gyara ina mai da numfashi kamar wacce tayi tsere.
Bappa ya karaso in da muke yana tambayar matar ta tafi ne?.
Ahmad ne ya iya bashi amsa nikam gaba ɗaya na ruɗe sai kyarma nake haka kawai naji ina so na ganta.
munkai tsawon minti 15 tsaye a gurin kafin aka turo kofa,
ganin security ne yasa ni ɗaga murya nace
"Ina take?." yace "Gata nan Madam sai da muka fita can farkon eriya kafin muka iske ta."
yayi maganar ne yana shigo wa ciki, niko leken bayan sa nake ina alla-alla naga matar.
a sannu ta sako kafar ta cikin gidan da sallama yayin da ɗayan security ke biye da ita.
kamar almara kamar a mafarki nake binta da kallo yayin da na wawwaro idanuna waje cikin matukar mamaki.
ido na kuma waro wa da karfi na furta
"Ummi Ummi na!!."  da gudu nayi in da take na rungume ta ina faɗin
"Ummi dama kece Ummi kece."
sai kawai na fashe da kukan farin ciki ina daɗa rungume ta.
ita ma rungume ni tayi tana bubbuga baya na yayin da hawaye ke zuba a idon ta tana faɗin
"Kiyi hakuri HAMDAH kiyi hakuri........!

Ummi ta rika bubbuga baya na tana faɗin nayi hakuri, yayin da hawaye ke cigaba da zuba a idanunta.
da sauri na saki Ummi na juyo hawaye na zuba a ido na, na saki murmushi hawaye na zuba cikin matukar farin cikin ganin yau gani ga mahaifiya ta, na dubi Ahmad nace
"My ga Ummi yau gani ga Ummi na, Bappa Ummi na ne Ummi na ne."
sai na kuma rungumar ta ina hawaye haɗe da murmushi.
wani irin farin ciki ne ya lulluɓe zuciyoyin su Ahmad yace "Barka da zuwa Ummi hakika mun yi farin ciki da zuwan ki."
Bappa ko Masha alhmdllh alhmdllh yake ta faɗa yayin da fuskarsa ke bayyana jin daɗi.
security kuwa gaba ɗayan su kowa yayi zuruu.
Ummi ta share hawaye da gefen mayafin ta tace
"Duk da sun kore ni na ayyana a raina bazan yi nisa da nan ba sai na ga HAMDAH da take cikin gidan nan dan jiki na na bani kece kiyi hakuri HAMDAH."
na sake ta tare da faɗin "Ummi kiyi hakuri."
sai kuma na juyo in da security suke nace
"Uwa ta kuka yi wa wulakanci kuka hana ta shiga gidan duniya bana kiyama ba."
Ahmad ya ɗaga murya cikin tsawa yake ce da su,
"A wani dalilin zaku hata ta shiga bayan ta sanar da ku ko wace ce ita!?."
suka haɗa baki wajen cewa "I'm sorry sir sabo da ba'a sanar mana da zuwan nata bane, kuma bamuyi zaton mamar Madam bace da gaske mun ɗauka waɗan da suke alakanta kansu da ita ne kawai dan a barsu su shiga."
Ahmad yace "Sai kuma baza ku iya kira ko zuwa ku sanar a kwai bako a waje ko ansan da zuwan sa ba? wani irin banzar aiki kuke ne!,
an ajiye ku kurika wulakanta mutane ne a bakin get."
Bappa yace "Sam bai dace ba ya kama ta idan irin haka ta faru, har idan ba'a sanar muku da zuwan bako ba, to idan yazo ba ku kore sa ba, ku nimi masaniya kan cewa an san da zuwan nasa ne sabo da wata rana zaku iya korin ɗan gidan abun kuma ba zai yi kyau ba,
to ba gashi yanzu kunyi a kan uwar mai gidan ba."
Ummi tayi murmushi cike da Dattaku tace
"A'a babu komai wlh, ai abakin ai kin su suke, kuma hakanne zai nuna tabbacin jajircewa kan aikin nasu, basu yi laifi ba sai dai kawai a kiyaye gaba."
security suka shiga bawa Ummi hakuri kamar zasu zuba goiwowin su kasa, tace wlh har cikin ranta babu komai kuma bataji haushi ba dan a bakin ai kin su suke.
na ja hannun Ummi cikin farin ciki muka yi ciki in da na karɓi jakarta na rike a ɗaya hannuna.
da sauri Inna Wuro ta fito dan Faty taje ta sanar mata Ummi na ta zo, a tare duk muka ɗunguma mukayi cikin parlour,
Bappa yace shi zai shiga Masallaci bari su yi salla zai shigo su gaisa,
a parlour Ahmad ya mika min Ahmad karami yace shima bari ya je yayi salla.
gaba ɗaya baki na yaki rufuwa farin cikin da nake jin kaina ciki tamkar anyi min albashir da aljanna.

a kan kafar Ummi na dire Ahmad karami, Ummi ta rike sa ta na faɗin "Yaya sunan sa?." nace Ahmad.
tace Masha Allah Allah ya raya da imani."
su Talatu suka shigo parlour'n suna kwasar gaisuwa da tayani farin cikin zuwan Ummi na.
Ummi ta kurawa Naseem da Nasmah ido da suke ta tsalle gefen ta sunayi wa Ahmad karami wasa, ta dube su da murmushi tace
"Yaya sunan ku?."  kusa da ni Naseem ya zo ya kawo bakin sa kunne na yace "Mommy ita yaya sunan ta."
ido na waro tare da saurin toshe kunne na wai shi a dole magana a hankali zai yi kada kowa yaji amma kamar ihu yayi min cikin kunne.
dariya duka parlour'n a ɗauka, nace
"Mama na ne fa kun gaishe ta kuwa, sunan ta Ummi."
murmushi Ummi tayi yayin da ta kasa janye idanunta kan yaran, ta janyo hannunsu tana faɗin
"Bari na faɗa muku sunana kuma sai ku faɗa min naku, suna na Ummi ku ya sunan ku?."
Naseem ya washe baki yace sunan sa Naseem ita kuma sunan ta Nasmah.
ai ko Nasmah ta shiga bubbuga kafa kasa wai ita zata faɗi sunan ta da kanta.
Ummi tace "To faɗa min naji ban ji nashi ba."
ta washe baki tace Nasmah.
ai ko surutun su suka shiga cike ta da shi, suka rika bata rabaran da bata san tushin sa ba, har da labarin gobe Dadday'n su yace zai ɗauke su da kanin su ya kai su ya kara siyo musu lilon doki.
Nasmah ta wawwaro ido tace
"Kuma muna da wani har guda haka kuma Daddy'n mu yace zai kara mana guda haka."
tayi mata nuni da yatsun ta huɗu da kuma biyu wan da za'a kara musu.
Naseem yace "Zo kiga lilon dokin mu yana kusa da ɗakin ɗawisu ne fa."
yayi maganar shima yana wawwaro idanu
Ummi tace "To sai gobe zan je na gani."
Nan da nan nasa su Zulai suka cike ta da kayan ci da sha..

Su Bappa da Ahmad suka shigo su ka zauna bayan sun gaisa da Ummi akayi ta hira.
gaba ɗaya nakasa zaune na kasa tsaye farin cikin ganin Ummi na yasa bakina ya kasa rufuwa farin ciki na yagaza ɓuya, ina jikin Ummi na naki matsawa ko nan da can,
a ɓangaren Ummi ma haka abun yake farin cikin da take jin kanta ciki yau bazai misaltuba, sai kallon ɗiyar tata take, yan da ta kara girma ta zamo cikakkiyar mace, ga ƴaƴan da take ganin su a gaban ta wai duka ƴaƴan HAMDAH ce, Allah mai iko buwayi gagara misali.
Bappa ya mike yace a barta ta huta ya fita, Inna Wuro Faty Talatu Zulai duk suka yi mana sai da safe suka tafi.
cike da girmamawa Ahmad ya mike ya lura Ummi nauyi take ji yasa ta kasa cin komai a gaban su, ya dubi su Nasmah yana faɗin
"Naseem Nasmah kuzo muje mu bar Ummi ta huta."
ya ja su suka haura sama.
nace "Ummi muje sama kiyi wanka kici abinci ki huta."
tace "A'a nan ma ya ishe ni ba sai na  haura ba."

murmushi nayi dan nasan ganin Ahmad ya haura ne, na mike na ɗau jakarta nace
"To ki shigo nan Ummi." nayi maganar ina nufar ɗaya daga cikin bedroom ɗin cikin parlour'n.
ta biyo bayana rike da Ahmad karami da yayi bacci,
ɗakin a gyare yake tsaf dan kullum sai su Talatu sun gyara ɗakunan duka.
Ummi ta rika bin cinin ɗakin da kallo kana ta shinfiɗa Ahmad kan gado ta shige bathroom ni kuma na fito parlour,
abincin da aka kawo mata bata ci ba na kwashe na kai mata ɗakin,
ina zaune ta fito tayi wanka haɗe da al'wala, na shinfiɗa mata sallaya, ta gabatar da salla.
tana idarwa na zuba mata abinci tana ci muna hira sai da naga taci abincin sosai kafin na mike nafita.
na haura sama na tadda tuni su Naseem sunyi bacci Ahmad yana kwance a gefen su.
yana gani na ya mike ya janyo ni jikin sa, goshi na ya sumbata kana ya ɗago da murmushi yace
"An ga Ummi shine za'a mai da ni marayan gasken-gaske ko?."
dariya nayi tare da jan ɗan karamin gyamun sa nace
"Maraya kuma kana da ni da Aunty Rasheedat kake kiran kanka maraya."
hannunsa ya sakalo ta kugu na ya daɗa haɗe jikin sa da nawa kana yace
"To a sallame ni dan yau nasan ba lallai naji ɗumin jikin kiba."
murmushi nayi nace "Ai kuwa kamar ka sani gurin Ummi zan kwana."
yace "Na sani ai kuma na yafe dan nasan a yanzu Ummi ta fini bukatar ganin ki kusa da ita,amma fa zan yi fama sosai na rashin ki kusa da ni."
nace "Kaje gurin Aunty Rasheedat mana nima bana so na barka kai kaɗai."
yace "A'a ai da ni za'ayi murnar ganin Ummi'n nan." yayi maganar yana jan kumatu na.
dariya nayi kana a sannu na kai lip's ɗi na kan nashi, sai da na ai ka masa da kwararan sakwanni na wan da nasan zai sami bacci cikin nutsuwa kafin na zame jikina na koma gun Ummi...

Ina shiga na tadda tana waya tana faɗin
"Yanzu haka ma ina cikin gidan a ɗaki ina shirin kwanciya Yaya."
na karaso ciki da sauri tun da naji tace Yaya nasan Abbu ne take wayan da shi.
daga cikin wayar cikin matukar farin ciki Abbu yace
"Ina HAMDAH ina HAMDAH take?." Ummi da bakin ta ya kasa rufuwa tace "Ga ta nan bari na bata."
ta mika min wayar tana faɗin "Abbu'n ku ne." a gefen ta na zauna tare da kara wayar a kunne nayi sallama,
Abbu ya amsa yana faɗin "HAMDAH HAMDAH kece?." wasu zafafan hawaye ne naji sun zubo min a hankali naji saukar hannun Ummi kan fuska ta tana share min, sai na saki murmushi mai sauti nace
"Ni ce Abbu ina yini."
Abbu yace "Alhmdllh ita ce." hele najiyo daga cikin wayar da hayaniya idanuna na lumshe nakuma buɗe wa jin muryoyon ƴan uwa na, Abbu yace
"Masha Allah alhmdllh sannu sannu HAMDAH sai mun zo maganar waya bazata wadatar da mu ba."
muryar Aunty Rafee'at najiyo tana faɗin

"Abbu bani inji muryar ta." tace "HAMDAH." nace "Na'am Aunty Rafee'at." sai kawai ta fashe da kuka, nima kukan na fashe da shi.
Abbu ya karɓi wayar yana faɗin
"To yanzu kam hankali na daf da kwanciya Rafee'at Jaleela kowa ya tafi gida sai kuma ranar tafi."
cikin shessheka Aunty Rafee'at tace
"Abbu Ina gobe ne zamu tafi."
yace "A'a sai jibi kuje gobe a shirya jibi a tafi."
farin cikin da na tsinci kai na ciki bazai misaltuba jin muryoyin ƴan uwa na.
Abbu ya kashe wayar, Ummi ta rika rarrashi na ganin naci gaba da kukan har sai da taga na daina kukan.
ranar kusan kwana mukayi muna hira da Ummi...
washegari da kaina na shiga kitchen muka shirya abun breakfast iri-iri, na kwashi na Ummi na kai mata cikin bedroom ɗin da take, na ɗau na Ahmad na kai masa sama, sai da na tayasa wanka kafin ya barni na sauko.
ni dai a ɗakin Ummi nayi wanka dan na sauko da kayan da zan sa da na Ahmad karami, Ummi da kanta tayi masa wanka ta shirya shi.
su Naseem ne suka shigo da shirin tafiya school Ahmad na biye da su,
cike da girmamawa ya tsunkuya ya gaida Ummi da tambayar ta gajiyar hanya, ta amsa fuska a sake. nan ma Ummi tayi ta kallon yaran har suka fita, tabbas yaran suna mata mugun kama da SALEEM musamman Naseem yafi kama da shi sosai,
a ranta take faɗin ko dai sune cikin da ta tafi da shi, sai kuma ta kakkaɓe zuciyar ta da wannan tunanin, bayan ga ubansu nan tana gani,
ai dama HAMDAH kama suke da SALEEM dan ƴaƴan ta sun yi kama da shi ba abun mamaki bane.
na lura da kallon da Unmi take ta yiwa su Nasmah, nasan tarin bambayoyi ne tare da ita musamman kan yaran, sai dai har yanzu bamuyi wannan hirar da ita ba.
bayan munyi breakfast tare da Ummi, muka fito parlour.
Inna Wuro ta shigo, dan yanzu bata kwana cikin side ɗin nan tun da mukayi bakwai sai dai da safe ta shigo tayiwa Ahmad karami wanka,da yamma ma haka. bayan sun gaisa da Ummi nima na gaishe ta, nace
"Inna Wuro shine yau baki zo kinyiwa Ahmad wanka ba."
dariya tayi tace "Ai ni yanzu na sake wa matar sa tayi masa wankan arba'in ɗin."
hire sasoi muka yi ta yi, ina like kusa da Ummi na, a ranar da yamma Aunty Rasheedat ta zo yiwa Ummi barka da zuwa, bata bar gidan ba sai dare suka koma da Ahmad.
Ummi ta yaba da halinta kwarai da gaske tayi ta mamaki da na ce mata matar Ahmad ce....

Kamar yadda Abbu yace bayan kwana biyu da zuwan Ummi suma suka ɗau hanyar zuwa Abuja,
koda suka iso Ummi ta haɗa mu da su a waya nayi ta musu kwance har suka iso.
koda suka iso suka ce gasu a bakin get nan da nan nasa security suka buɗe musu get,
ina jin shigowar su da sauri na fito,
motoci biyu suka taho da shi na Abba da Abbu.

Aunty Rafee'at ne ta fara fitowa daga cikin mota, wani irin kallo muke bin junan mu da shi, Aunty Rafee'at kuwa kallon yan da na kara girma da cika take, da gudu ta taho nima nasa gudu muka rungume juna.
Aunty Jaleela Ya Masa'ud Nusaiba Fauzan Mamie Abbu Abba duk suka fito,  sai na saki Aunty Rafee'at nayi gurun su, yan da na shiga rungume su sai ya tuna min da lokacin da suke zuwa Dass gurin Inna haka zanyi ta rungume su ina yi musu oyoyo, sai kawai na fashe da kukan farin ciki, duk kanin su sai da suka yi kwalla.
jiki a sanyaye na matso in da Abba yake tsaye, yana duba na cike da nadama a gaban sa na tsaya ban iya rungume shi.
sai ya miko min hannu alamar na zo, jiki a sanyaye na maso in da yake,
kai na yashafa tare da bubbuga kafaɗa ta.
kai na sunkuyar jin hawaye ya ciko min ido sai ga hawaye sharr.
Mamie ta matso in da nake ta janyo hannu na tare da girgiza min kai,
Ya Masa'ud ya leko fuska ta yace
"Kai ƴar gidan Inna har kin fi Jaleela girma yanzu."
dariya nayi hawayen na zuba.
Aunty Jaleela kuwa harararsa tayi tana murmushi, ciki duka mukayi har da su Bappa da suka fito,
muna shiga na kira Ahmad na sanar masa isowar su batare da ɓata lokaci ba suka iso shi da Aunty Rasheedat...
cike da sha'awa su Aunty Rafee'at suka yi ta ɗaukar su Naseem da suke ta zuba musu surutu.
Mamie ko ido ta rika binsu da shi lokacin da ta janyo su jikin ta, Naseem ta yi ta kallo ganin suffofin SALEEM lokacin yana karami tare da shi...
Su Abbu sun sha mamakin ganin Ahmad Sabil sun jinjina lamarin da ganin tabbas da gaske shi miji na ne....

Bayan gaishe-gashe daya gaba ta, cin abinci ya biyo baya,
daga nan kuma sallar la'asar aka tashi yi, in da su Abbu suka tafi masallaci, su Mamie kuma suka shiga ɗakunan da suke cikin parlour'n kasa sukayi salla.
bayan anyi sallar aka kuma dawowa parlour.
bayan an zazzauna Bappa yayi gyaran murya ya soma magana...........!

Bappa ya soma da addu'a bayan addu'a ya ɗaura da faɗin
"Alhamdulillah muna godiya wa tabakara maɗaukaki mabuwayi mai izza, wan da ya nuna mana wannan rana, muna niman tsari da sharrin masu sharri Allah ya kaɗe mana fitina, muna godiya wa Allah da ya nuna mana wannan rana, Allah ya daɗa kaɗe mana fitina duniya da kiyama."
kowa ya amsa da amin amin,
Bappa ya gyara zama tare da ci gaba da faɗin
"Abubuwa sun faru da dama bama fatan hakan ta kuma faruwa Allah ya kaɗe fitina, ya iyar mana abun da baza mu iya ba, Allah yayi mana maganin makiya da masu hassada kamar yadda ya nuna musu karshen sharrin su,
hakika addu'a makarin Mumini ne, a na son musulmi a duk in da yake a duk halin da yake ya kasan ce mai ruko da addu'a, domin addu'a takwabi ne mai kaifi ya kan tsare fitina da sharri da kaifin sa, hakika wannan abu da ya faru ya nuna ɗan sakacin addu'a kaɗan duk da Allah yayi taimako an farga da wuri, Allah ya da ɗa tsare mu ya yi mana katangar karfe da azzalumai."
Abbu ya jinjina kai cike da gamsuwa yace "Amin ya rabbil izzati, hakika addu'a takwabi ne mai kaifi hakika lamarinnan ya jijjiga mu ba kaɗan ba duk da bakin mu baya iya
furta wa amma zuciyoyin mu tana kuna."
ya ɗan sakai ta maganar tare da duba na kana yaci gaba da faɗin
"Kiyi hakuri HAMDAH duk da bamu kuma yunkurin niman ki ba amma zuciyoyin mu suna tare da ke a ko da yaushe."
kai Bappa ya jinjina dan ya san cewa ai kin sihiri kenan shi yasa ake so a koda yaushe mutum ya zamana yana cikin sarki da addu'a idan aka jefe ka da shi bazai yi wani tasiri a tattare da kai ba...
Abbu yace "Muna mai ci gaba da baki hakuri hakika mun ai kata rashin kyautawa wa rayuwar ki, a matsayin mu na iyayen ki da kike da hakki a kanmu da muka gaza sauke shi na wasu shekaru mu na roko da ki yafe mana."
da sauri na shiga girgiza kai yayin da hawaye ke zuba a ido na
kwalla na share nace "Abbu bakuyi min komai ba, Abbu ka rokar min Abba ya yafe min dan naga kamar har yanzu bai yafe min ba amma wlh ni ban taɓa ai kata zina ba."
wani kuka ne ya tsuɓuce min na fashe da kukan, Aunty Rafee'at ta rungume ni itama ta fashe da kuka.
cikin matuƙar nadama Abba yake faɗin
"Ki gafarce ni HAMDAH tsananin kunyar ki ce ta hanani iya furta komai, tabbas nayi danasanin yanke hukunci cikin fushi, ki gafarce ni ki gafarce ni HAMDAH ina mai da na sanin yanke hukunci cikin fushi,
dana kore ki HAMDAH ina kika shiga ina kika shiga HAMDAH nayi da na sani nayi na dama HAMDAH ina kika je wani rayuwa kika yi?."
Abba yayi maganar cikin nuna nadama sosai kamar zai zubda kwalla.
in da yake na rarrafo tare da rike hannunsa gam kana a hankali nashiga basu labarin abun da ya faru, tun ranar da na sa kafa na bar gida da
rayuwar da na fara fuskanta,

da rayuwar da mukayi cikin daji ni da su Naseem da,
irin gwagwarmayar da na sha a rayuwa har na kai matsayin da na ke a yanzu.
tun da na fara bada labarin
gaba ɗaya parlour'n ya kacame da koke-koke su Aunty Rafee'at har da jan shassheka, Ummi Mamie gaba ɗayan su kuka suke wei-wei kamar kananun yara,
Abba Abbu Bappa Ahmad duk kanin su sai sharar kwalla suke.
Abba yana sharan kwalla yana faɗin na yafe masa,
kai na shiga girgiza wa
nace "Baka yi min komai ba Abba."
Mamie tana kuka ta rungume su Naseem da tun ɗazu take jin wani yanayi a kansu a kasan ranta take faɗin a she dai jinin ta ne su shiyasa tun da ta sanya idanunta kan su take jin su a cikin jikin ta.

su Abbu suka shiga yiwa Bappa godiya da irin kokari da jajirce wa kan lamari na da yayi yake kuma kan yi shi da matar sa wato Inna Wuro.
Bappa yace ai yiwa kaine, da ɗa da dukiya bana mutum ɗaya bane kuma ba'a yi musu keta.
sun yaba kwarai da gaske da irin kokarin da Mama mai awara ta yi a kaina suka kuma ɗau alkawarin niman ta suyi mata godiya.
Ahmad ma godiya suka yi ta masa suka kuma yi jinjina ga Rasheedat matar da ba kasafai ake samun irin su a duniyar mu ba....

A ɗaya side ɗin da babu kowa ciki wan da yanzu su Talatu suke kwana ciki, nasa su Talatu suka fita suka koma side ɗin su Inna Wuro suka shiga ɗaya daga cikin ɗakunan side ɗin wan da ba kowa ciki,
wannan side ɗin kuma nayi wa su Abbu da Abba Ya Masa'ud Fauzan masauki ciki.
ɗaya daga cikin
ɗakunan kasa kuma aka shigar wa Mamie kayan ta ciki, ɗaya ɗakin kuma Aunty Jaleela da Aunty Rafee'at da Nusaiba.
a ranar raba dare mukayi muna hirar bayan rabo da ahlina abu mafi soyuwa a rayuwa ta,
Ahmad kuwa gidan sa ya tafi yace ya barni na gana da ƴan uwa na, bayan ya gama zolaya ta wai na share shi na nuna masa wariya...
kwanan su Abbu uku suka soma shirin komawa gida bayan na kaisu na nuna musu duk kanin kadarori na da suke cikin garinnan,
sauran na wasu gararruwan kuma a computer na nuna musu..
ranar da suka cika kwana biyar suka juyo Bauchi, amma banda Ummi dan ta ce ita tana nan sai ta yimin zaman arba'in tukun.
Abba ko da wasa bai yi yunkurin hana ta ba, sai dai ma karfafawa zaman nata da yayi, yace ta zauna tayi min wankan arba'in kamar yadda ake yiwa mai haihuwar fari dan na cancanci haka, duk da na sami ingantaccen kulawa gun Mama mai awara a haihuwa ta ta farko wan da ya kamata ace uwata ce ta bani wannan kulawar,
to amma guri bai kure ba, ta zauna nakuma kara samu agurin mahaifiya ta...
Ahmad yayi musu goma na arziki dan mota guda ce ta raka su da kayan tsaraba, bayan wan da

nima nayi musu..
lokacin da suka iso gida Masa'ud ya shiga ɗakin sa, yayi matukar mamaki haɗe da razana ganin SALEEM cikin ɗakin a kwance ya dukunkune cikin bargo sai rawar sanyi yayi, lokaci zuwa lokaci kuma sai yayi wasu tagwayen tari ya dafe kirjin sa da karfi yana matse idanunsa.
a bin da ya daɗa bashi mamaki shine kayan jikin sa, kayan da yazo da shi gidan ranar da zasu tafi Abuja gurin HAMDAH, "Kenan tun ranar yana ɗakin nan?."
Masa'ud yayi maganar a ransa, da sauri ya karaso bakin gadon yana faɗin
"Subhanalla Ya SALEEM baka da lafiya ne?."
da ido kawai ya bishi barate da yayi magana ba.
ganin yan da ya kuma rumtse idanunsa yana daɗa damke kirjinsa,
da sauri Masa'ud ya fito dan yaje ya sanar wa Mamie halin da SALEEM ɗin yake ciki.
a sakiyar gidan ya haɗu da su Abbu da alama masallaci zasu tafi,
da sauri ya karaso in da suke yace
"Abbu Ya SALEEM bashi da lafiya yana kwance a ɗaki na."
da sauri Abba yace "Subhanalla me ya same shi?."
ya juya da sauri ya nufi ɗakin nasa Masa'ud ya rufa masa baya.
Abbu kam tsayuwa yayi yaɗan yi dimm kana ya girgiza kai yawuce masallaci abin sa..
Abba na shiga ɗakin ganin halin da yake ciki yashiga tambayar sa abin da ke damun sa,
ba wani kwakkwaran amsa ya samu a gurin sa ba dan tun da ya tambaye sa, me ke damun sa ya nuna masa kirjin sa bai kuma cewa komai ba duk tambayar da yake masa.
Abba ya ɗaga waya ya kira Dr Farooq yace ya zo yanzu.
batare da ɓata lokaci ba Dr Farooq ya iso.
bayan sudduba shi da yayi ya rubuta masa magani, Abba ya bawa Masa'ud kuɗi yaje ya siyo maganin ya kawo masa....

Abuja

Ina samun kulawa sosai wajen Ummi na, dan dole Ahmad ya tarkasa ya koma gidan sa sai dai yazo ya duba mu ya koma.
yanzu bani da wata damuwa a rayuwa ta hankali na ya daɗa kwanciya, na daɗa yin ɓul-ɓul da ni na kara haske da sheki na kara kyau,
kullum ina tare da Ummi na hankali na a kwance..
Hajiya Lubabatu na kira nayi mata aiken kuɗi ta turo min kayan gyara irin na masu jego.
kafin na cika arba'in kuwa idan ka ganni sai ka kara kallo na, shi kan sa Ahmad idan yazo yakan zauna ne yata kallo na, wai shi ya godewa Allah da ya kawo masa Ummi tamkar kara min kyau take,
dariya kawai na ke masa.
ranar dana ciki arba'in Ummi ta fara shiri washegarin ranar Ummi tace yau ba kwana sai Bauchi, na sha kuka na har na gaji, nace sai dai mu tafi tare,
tace a'a na bari sai jiki na ya daɗa karfi jaririn ma yadaɗa kwari sai nazo zan fi jin daɗin zuwan...
direba ya shirya kayan ta cikin mota da kayan tsarabar ta da Ahmad yayi mata, da wan da nima nayi mata.

muna tsaye a parking space dukan mu gidan sai hawaye nake sharewa, cikin tura baki nace
"Allah Ummi sati ɗaya zan kara na zo."
tace "A'a HAMDAH kibari ɗan nan ya daɗa yin kwari kada kirika kwasar sa kina yawo da shi bai yi kwari ba, kibari nan da wata uku lokacin yayi kwari sosai sai ki zo."
ido nawaro nace "Ummi har wata uku Allah ni dai a'a."
Inna Wuro tayi murmushi tace "To in ban da abin ki HAMDAH wata uku yanzu nawa yake kamar gobe ne agurin Allah."
Ahmad kuwa sai washe baki yake adole yaji daɗi an ce ba yanzu zan tafi ba.
Ummi ta shige mota direba ya ja muna ɗaga mata hannu har suka fice daga gidan.
na juya jiki a sanyayi cike da kewar ta...
ina shiga parlour Ahmad dake biye da ni ya rungume ni ta baya,
baki na turu gaba ina yi masa hararar gefen ido.
murmushi mai sauti yayi kana, ya cusa fuskarsa a gefen wuyana na ya sumbaci fatar wuyana a hankali yaɗan ja numfashi yace
"Kyakkyawa ta yaufa a shirya shirin karɓar bakwanci na."
baki na kuma turo wa tare da fizge jikina nace
"Ni ka kyale ni."
dariya yayi cikin zolaya yace
"Zo muje oh na rarrashe ki Ummi ce ta hana ki tafiya ko?."
baki na murguɗa nace "Ina har murna kake." yace "Allah sarki Ummi Allah ya tsare miki hanyar ki, taji tausayin Ahmad da Ahmad shi yasa tace ki kula da su kafin, muje a fara bani nawa kulawar yanzu."
kafa na shiga bubbuga wa, ya janyo hannuna muka haura sama yana dariya..

Bayan sallar isha, tsaye nake gaban mirror ina feshe jikina da turare bayan fitowa ta daga wanka,
Ahmad ya shigo ya iso ya rungume ni ta baya, daga cikin mirror ya kura min ido yayin da ya sako kan sa kan kafaɗa ta yana yimin kallon cikin ido, sanin manufar sa sai na ɓata fuska na zame jiki na ina tura masa baki.
murmushi mai sauti yayi ya ruko ni yana faɗin
"Wai ba ɗazu nayi rarra shin nan ba to zo na kara yanzu kam na Musamman ne, shi yasa nasa su Naseem sukayi bacci da wuri."
cak ya ɗaga ni ya dire ni kan gado,
ganin ya shiga zare kayan jikina da sauri nace
"Ban fa warke ba ni dai ka bari."
sai da ya zare doguwar rigar baccin jikina kafin ya ɗago har jikin sa na rawa yace
"Please kyakkyawa ta, kwanaki arba'in da ƴan kai kiji tausayi na mana."
cike da shagwaɓa nace "Allah My zafi zai min kamar bai warke ba."
yace "To bari na gwada na gani idan bai warke ba sai na hakura, a hankali zanyi kinji ki daure."
kai na gyaɗa masa,
har jikin sa na ɓari yashiga shafani da sumbatar sassan jikina,
ya birkice ya birkita ni sai na shiga mai da masa martani.
sai da ya jagula ni na jiku sosai kafin ya ɗago ya zare pant ɗin jikina, nan ma sai da yayi ta

wasa da HQ ɗina kafin ya haye kaina.
idanuna na rumtse san da ya shige ni da tunanin jin zafin gurin ɗin kin da a kamin, sai naji akasin hakan.
tamkar yau yafara sanina haka yayi ta sambatu yayin da yake ta sama da kasa a kaina.
ya sharin tsawon lokaci mai tsawo a kaina yana abu guda, nayi ta daure wa domin ganin ya sami nutsuwa dan nasan yayi missing ɗi na sosai.
sai da ya sami ingantacciyar gamsuwa kana yayi lamo a kaina, duk kanin mu numfashi muke sauke.
a hankali ya ɗago yayi kissing ɗin goshi na yace
"Nagode sosai kyakkyawa ta Allah yayi miki albarka."
idanuna na lumshe tare da kuma buɗe su kan fuskarsa tare da yi masa murmushi, shima murmushin ya maida min kana yace
"Ina son ki kyakkyawa ta."
a hankali ya zare jikin sa ya mike ya ɗago ni muka shige bayi.....
washegari da safe ina manne da waya a kunne na muna waya da Ummi,
Fauzan ya karɓi wayar muka gaisa da shi.
ina kashe kawar Ummi, kiran Mamie na ahigo wa itama sai da muka gaisa har da Nusaiba, dan tun da suka koma kusan kullum sai munyi waya da su da su Aunty Rafee'at.....

Bauchi a ɓangaren Na'ima kuwa
tana zaune cikin bedroom ɗin ta waya ce kare a kunnen ta tana magana da aminiyar ta Raliya, tana faɗin
"Aminiya nikam anya bokan nan ai kin sa na ci kuwa, nifa banga yan da ake ta faɗa kamar yankan kuwan ba, gashi bini-bini sai yace abada dubu ɗari kaza miliyan kaza kin san har account ɗi na yafara yin kasa kuwa,
ba wannan ba ma ban damu da koda kuɗin zai kare idan har zan sami biyan bukata duk abin da na mallaka zan iya ɓatar da shi har idan za'a kashe wancan shigiya annobar yarin yar, dan wlh ta zame min annoba, jiya muna kwance da shi da daddare yana bacci yana kiran sunan ta, kin san  yanzu baya fita ko offece kullum yana ɗaki,
daga zaran bacci ya ɗauke sa zai fara kiran sunan ta, idan naji haushi na bubbuga shi ya tashi yana farka wa zai ruko ni yana faɗin
HAMDAH, ke Aminiya ina cikin babbar matsala dan Allah yanzu muhaɗu agurin boka, ko nawa yake so na kara masa ni zan basa, nifa nafi son ai kin da za'a yi sha yanzu maganin yanzu, bana son ai ki mai jinkiri shi yasa nake son ai kin boka na kan dutu, ban so mutuwar sa ba da yana nan da duk haka bata faru ba,
dan Allah aminiya mu haɗu yanzun nan gidan boka gani nan fitowa."
ta kashe wayar ta mike ta zari mayafin ta da makullin mota tayi waje.
SALEEM na zaune gurin hutawar sa ya hango ta ta shige mota tayi waje,
da ido yabi ta har tayi waje, a zahirin gaskiya kuwa hankalin sa ba ya tare da shi, ya milla yayi nisa daga gare sa,
a hankali ya kai hannunsa ya dafe kirjin sa yayin da ya fara tari a hankali babu kakkautawa.
wani irin zafi da zugi zuciyar sa yake masa, a hankali ya mika hannu yaɗau ɗaya daga cikin

wayoyin sa da suke aje kan table ɗin gaban sa wan da ya ɗaura kafafun sa a kai,
yayin da hannunsa ɗaya ke dafe a kirjinsa.
Dr Farooq ya kira bayan sun gaigasa  Dr Farooq yake tambayar sa yaya jiki?.
bai amsa tambayar ya jikin da yayi masa ba sai cewa yayi
"Ka faɗa min sunan wani maganin da zan sha."
Dr Farooq yace "Wan can ɗin baiyi maka amfani bane?, to gaskiya kazo asibiti kawai zai fi a duba ka da kyau a baka magani, Please Ya SALEEM ka zo yanzu."
bai yi magana ba sai sauke wayar da yayi a kunnen sa,
a sannu ya mai da bayan sa jikin kujera tare da lumshe idanunsa har lokacin hannunsa ɗaya na dafe a kirjin sa.
Dr Farooq yakira sa har sau biyu bai ɗaga wayar ba, yana jin wayar tana vibrate bai ko buɗe idanunsa ba.
sai da yaji alamar shigowar message kafin ya buɗe lumsassun idanunsa ya ɗau wayar yana duba sakon da ya shigo masa,
Dr Farooq ne ya ai ko masa da sakon cewa dan Allah yazo asibiti kada ya ɓata lokaci.
bayan da ya gama karanta sakon sa sai ya mike ya kwashi wayoyin sa yanufi side ɗin sa.
sai da yayi wanka ya shirya kana ya ɗau makullin motar sa ya nufi asibitin, ko da ya iso asibitin.
bayan tambayoyin da Dr Farooq yayi masa kan ciwon nasa, ƴan takaitartun amsoshin da ya basa da shi yasamu damar yi masa gwaji kan abun da yayi hasashe bisa amsoshin da ya basa..
lokacin da Dr Farooq yaga result ɗin test ɗin ya jijjiga ba kaɗan ba,
ganin yana daf da kamuwa da ciwon zuciya,
hankalin sa a matukar tashe yake basa wasu shawarwari kan yan da zai gudanar da lamuran sa domin gujewa kamuwa da ciwon zuciya,
ya tausaya masa kwarai da gaske,
ya ɗaurasa kan magani.
har gurin motar sa ya rako sa, ya yana daɗa jaddada masa yan da zai kula da shan maganin sa, SALEEM yana kokarin shiga mota Dr Farooq yakuma duban sa yana faɗin
"Dan Allah Ya SALEEM ka kula da shan maganin ka, kuma dan Allah ka rage tunani idan Allah ya tai maka zai tsaya iya haka Allah ya sauwaka."
ya amsa da amin kana ya shige mota...

A ɓangaren Na'ima kuwa
zaune suke a gaban sabon bokan su, sun naɗe kafa gaban sa kamar masu niman gafara,
sun kura ido suna kallon yan da yake ta wani surkullen sa, yayi zane kan kasa ya bubbuga ya share ya kuma zana wa.
bokan ya ɗago ya dube su yace "Zata mutu mutuwar wulakanci amma aljanun da zamu tura su sun ce suna bukatar jini rakuma kosassu guda goma kafin suje suyi ai kin."
kirji Raliya ta buga tace
"Rakuma guda goma kosassu ayanzu fa kuɗin ko wani ɗaya zai kai miliyan uku."
bokan yayi wani irin dariya yace "Bazaku iya ba ku tashi ku tafi."

da sauri
Na'ima ta gyara zama tace "Boka zamu iya."
wayar ta ta ɗaga taduba balance ɗin account ɗin ta taga babu wani yawa sosai dan duk ta gama basa kuɗin.
ta yi masa transfer ɗin duka kuɗin zuwa account ɗin shi, kana ta aje makullin motar da tazo da shi a gaban sa tace
"Asai da motar a haɗa da kuɗin idan basu kai ba zan nemo cikon,
ni dai dan Allah boka ayi min kokari bana so a sami matsala, a kashe ta kawai shine samin kwanciyar hankali na, ko bacci mai daɗi bana samu yanzu."
boka yace "An gama baki da matsala yau za'a sai da motar idan kuɗin ya cika, da daddare za'a bawa aljanu jinin rakuman a daren nan zasu kashe ta, dan kuma bai cika ba zamu neme ku."
suka mike suna ta zuba masa godiya a motar Raliya suka fito saga cikin dajin..
suna tafe Raliya ta juyo ta dube ta tace
"Aminiya amma yanzu idan boka yace a kawo ciko a ina zaki samu cikon?."
Na'ima tace "Agurin SALEEM ai da ma daga gurin sa suke fita, zan sa a ɗauke Ameer a nimi kuɗin fansa a gurin sa dai-dai kuɗin siyan rakuman, idan ya bayar sai na bawa boka cikon kuɗin narike sauran."
dariya Raliya tayi tace
"Kai Aminiya daɗina da ke kwakwalwar ki na ja, idan aka sace ɗan sa kam ai da gudu zai kawo kuɗin babu gargada."
Na'ima tayi wani murmushi mai cike da tarin makirci....

Abuja

Kullum a cikin lissafin tafin watannin ukun da Ummi tace na kara kafin nazo nake, sai nake ganin lokacin yayi min nisa. da kyar naga wata biyu yayi.
kullum idan muka yi waya da Ummi sai na ce mata
Allah Ahmad yayi wayo sosai yayi kwari nace kuma bari taji dariyar sa, sai nayi ta masa wasa yayi ta kyalkyalewa da dariya nace taji shi ko.
tace taji amma dai na bari na cikita wata ɗayan tukun..
idan Ahmad yaji muna waya da Ummi yarika yimin dariya kenan sai yace wai Ummi ta fiso na zauna na kula da su..
ranar da wata ɗayan nan ya cika, tun da na farka da asuba ban kuma iya komawa bacci ba,
a kwatunan kayan mu na sauke waɗan da na shirya su tun sati ɗaya daya wuce.
ranar Ahmad baya gida na, na kira sa a waya nace masa mu fa mun gama shiri, yace na jira sa gashi nan zuwa.
ina zaune a parlour ya shigo su Nasmah suka rungume sa suna yi masa oyoyo, sai da ya ɗaga ko wannen su sama kafin ya dire su yana bin su da dariya.
in da na ke ya karaso ya ɗauki Ahmad karami dake kan kafata yarika cillashi sama yana

kwalkwale dariya,
ganin yan da ya shagala da wasa da yaron yana kuma biyewa su Naseem da suke taya sa wasa wa yaron, na turo baki gaba
nace "My rana fa zatayi kana so muyi tafiyar dare ne."
zama yayi gefe na tare da manna min kiss a kumatu yace
"Kyakkyawa ta ki bar tafiyar nan yau."
ido na waro nace "Me ne!?."
janyo keken da ake saka Ahmad karami a ciki yayi yasaka sa ciki kana ya tura sa gefe ai ko da gudu su Naseem sukayi kansa suna yi masa wasa yana ta ɓalle musu da dariya.
janyo ni jikin sa yayi ya sakalo hannayen sa ya zagaye ni da shi,
a hankali cikin tattausan lafazi yace
"Ki saurare ni kiji abin da zan faɗa, ai tafiyar ba naki ke kaɗai bace har da ni da su Bappa,jibi ina da wani zaman da zamu yi kuma mittin ne mai muhimmanci, nayi miki alƙawari idan mukayi mittin jibi washegari zamu tafi."
kai na langwaɓar gefe zan yi magana yace
"Kar kice komai kika iya jiran wata uku kwana uku ne zai gagara iye kyakkyawa ta?."
yadda yayi maganar a marairaice tare da langwaɓar da kansa gefe,
sai ya bani dariya murmushi nayi nace
"Amma Allah kwana ukun nan kam idan yazo babu fashi."
yace "In Allah ya yarda."
kai na girgiza nace "To Allah ya kaimu."
daɗa rungumo ni yayi yana faɗin
"Amin Amin." ganin yana shirin haɗe bakin mu nayi saurin kawar da kaina gefe, nace
"My yarannan fa suna nan." ido ya kashe min yace "Su da suke wasan su hankalin su baya nan."
fuska ta ya juyo tare da haɗe bakin mu, idanunsa a kan yaran garin hankalin su na kokarin dawowa kanmu sai ya zare bakin sa ya sake ni,
ya mike yana faɗin
"Kuzo muje musha  ice-cream."
ya ɗauki Ahmad karami ya dube ni yace
"Madam muje ko."
a sannu na mike kasan cewar da mayafi a jikina muka nufi gurin mota.
ya buɗe wa su Naseem gidan baya suka shiga, kana ya mai da marfin ya rufe sannan ya matso ya buɗe min gefen mai zaman banza, sai da na shiga kafin ya miko min Ahmad karami.
kana ya zaga ya huɗe driver seat ya shiga, yana kokarin ta da motar da sauri wani security ya iso,yaɗan leko gefen da nake cike da girmamawa yace
"Barkan ku da warhaka."
Ahmad ya ce yauwa, yace "Madam dama wata ce ta zo, wai tazo niman taimako ne ansan da zuwan ta ne."
kai na girgiza nace
"Okay bari idan muka fita wajen sai a taimaka mata."
yace to ya juya da sauri mai gadi ya wangale get, Ahmad ya ja motar muka fito a hankali.
matar tana ɗan rakuɓe a gefe kallon ta nayi daga sama har kasa, gaba ɗaya kayan jikin ta sun

koɗe hatta hijabin jikin ta tagefe duk a yayyage, silifas ɗin kafar ta ya cinye kusan rabib kafar ta a kasa yake, tana rungume da bakko a hannunta.
Ahmad yayi hon da ɗan sauri ta nufo in da muke,
ido na kurawa matar,
da sauri na kai hannu na mussuke idanuna da kyau na zuba su a kanta, dai-dai lokacin da ta karaso jikin motar tagefen da nake tana faɗin
"Alhaji Hajiya a taimaka min da ko kuɗin mota ne na koma garin mu."
wani irin waro ido nayi da karfi na furta
"Mama!". ta ɗago da sauri ta na duba na,
juyo wa nayi gun Ahmad ina faɗin
"My ita ce Mama mai wara ita ce wlh."
sai kuma na juyo in da take ganin tana bina da kallon rashin sani nace
"Mama baki gane ni bane nice fa HAMDAH ce fa Mama."
da sauri na ɗago Ahmad karami na ɗaura kan kafar Ahmad na buɗe marfin motar da sauri na fita.
ido ta kura min tana nuna ni da yatsa murya na rawa tace
"HAMDAH kece HAMDAH kece haka ke kika zamo haka HAMDAH?."
rungume ta nayi a tare fashe wa da kuka cikin muryar kuka nace
"Nice Mama, Mama nayita niman ki har na ɓata."
ita ma tace "Nima nayi ta neman ki HAMDAH ashe darabon ganawa."
Ahmad ya fito daga cikin motar, na sake ta tare da share hawaye na na nuna mata shi nace
"Mama miji na ne shi." murmushi tayi tana share hawaye tace
"Shine SALEEM?." kai na girgiza mata. Ahmad da take ta binmu da murmushi yace "Sannu Mama." tace yauwa.
tace "Ina Naseem da Nasmah?." nace "Gasu nan cikin mota."
Ahmad ya buɗe musu suka fito na kamo hannun su na kawo su gaban ta nace
"Ga Mama wacce tasha ɗawainiyar ku tun kuna ciki."
hannunsu ta ruko tana faɗin
"Masha Allah Naseem Nasmah kune kuka girma haka."
Naseem da ya washe baki yace
"Ai Daddy yace mun gima ga kanin mu a hannun Daddy ni Yaya Naseem ne."
dariya dukan mu kayi, Mama ta dubi Ahmad karami da ke rike a hannun Ahmad sai washe baki yake kamar wan da yasan abun da ake faɗa,
tace
"Masha Allah kanin ku kenan yaya sunan sa?."
Nasmah tace "Ahmad."
nace "Mama mu shiga ciki."
tana rike da hannun su Naseem muka shige cikin gida, Mama ta rika bin katafaren gidan da kallo tana jinjina kai.
a parlour'n kasa muka zazzauna, Ahmad cikin girmamawa yashiga gaishe ta da taya mu murnar kuma haɗuwa, ya dube ni yana murmushi yace
"Yau maganar Mama ya kare ko." dariya nayi ina ɓoye fuska ta a jikin ta.
kira ce ta shigo wayar sa ya mike yafita yana faɗin sai ya dawo.

da kaina na fita naje side ɗin su Bappa na sanar musu da zuwan Mama mai awara.
a tare muka shigo parlour'n da su.
sunyi farin ciki kwarai da gaske haɗuwar mu da ita, cikin yanayin damuwa Mama ta dube ni tana faɗin
"HAMDAH ke da na ce miki ki jira ni ina dawowa shine kika tafi."
nace "Mama nayi ta jiran ki da banga kin dawo ba shine nace zan biki kawai, a hanyata na tafi Yola na shiga motar ɗan yankan kai."
ido Mama ta ware tabuga kirji tace
"Ɗan yankan kai kuma?."
kai na gwaɗa kana asannu na shiga bata labarin abun da ya faru daga lokacin da na shiga motar ɗan yankan kai ɗin nan har zuwa rana mai kamar ra yau.
mama ta rika hawaye cike da tausayawa halin da muka shiga bayan ta,
da ga bisa ni kuma tarika murmushi jin nasarorin da na samu bayan wuyan da muka sha.
nace mata na zo Jos domin neman ta wacce nake da tabbacin zan sami labarin ta wajen su wato Zainabu da mijinta Malam musa mai maganin macizai, na tarar da sun tashi a gidan da dana sansu.
Mama tace "Nima lokacin da nadawo dan da ɗauke ki mu tafi na tarar da bakya nan, nayi tunanin naje Bauchi ko kin koma gun iyayen ki ne, nayi tunanin ban san ta in da zan fara niman ki ba tun da bakara min gari bane,
haka na koma Yola nayi ta rayuwar kunci ɗan gonar gado na da nake gadara da shi matar yaya na ta saida wai gadon ƴaƴan ta ne."
kwalla ta share kana ta cigaba da bani labarin rayuwar da ta fuskanta a can, da kuma abun da ya kawo ta garinnan, tace niman ai ki tazo yau satin ta guda kenan, bata sami ai kin ba duk gidan da ta shiga wasu su kore ta wasu kuma suce basa bukatar ƴar aiki suna da su,
haka tayi ta kwana a kan titi shine ta fara yawon bara dan ta sami kuɗin mota ta koma Yola taje ta karasa rayuwar ta acan.
rungume ta nayi tare da fashe wa da kuka, mukayi ta kuka.
su Bappa ne suka yita bamu baki har mukayi shiru,
kana Bappa yayi ta kwararo addu'a yace
dama duk abun da yayi farko zaiyi karshe Allah ya tsayar mana haka.
duk kanin mu muka amsa da amin amin, sai da sukayi hira sosai da Mama mai awara kafin suka koma side ɗin su...
ɗakin da Ummi ta zauna na kai Mama nace tashiga bayi tayi wanka,
tare muka shiga na nunnuna mata in da zatayi amfani da bathroom ɗin kafin na fita.
waya nayi a *HAM'NAS* Store Camplex
nace a kawo min manyan dogayen riguna haɗe da atamfofi da mayafai da takalma marasa tudu, nafaɗi lambar takalmar da kuma adadin yawan kayan da nake so.
batare da ɓata lokacin ba motar ShopRite ɗin ta iso, da kaya niki niki cikin babbar jaka.
na shiga da shi cikin ɗakin da Mama take, lokacin har tayi wanka tayi salla tana zaune a kan sallaya,
a gaban ta na aje jakar na zazzage kayan, na cire atamfofin gefe nace ta kwada dogayen rigunan ko zasu yi mata in basuyi ba aje a canzo.
ta gwada zukayi mata Mama ta rika samun albarka tana hawaye.

na kira tela yazo ya ganta kana ya ɗibi zannunwan ya tafi da su,bayan na sanar masa cikin kwana biyu nake bukatar su...
muna zaune da Mama a parlour bayan mun gama cin abincin dare na kira Ummi bayan mungaisa nace
"Ummi ga Mama mai awaran da nake faɗa miki wacce ta rike ni tamkar ke da kika haife ni."
Ummi tayi ta murna tace na bata wayan su gaisa, nace to tare ma zamu zo.
bayan sun gaisa Ummi tashiga zuba mata godiya,
Mama tace ai ba ita kaɗai bace Mama ta itama Mama ta ce.
Ummi taji daɗi kwarai da gaske tayi  mana fatan isowa Bauchi lafiya...
bayan kwana biyu tela ya kawo ɗin kin Mama, na haɗa na shirya mata wasu daga cikin kayan cikin ɗan madaidaicin akwati..

Kamar yadda Ahmad ya faɗa bayan kwana uku motocin mu suka haura hanyan zuwa Bauchin Yakubu.
motan mu daban ni da Ahmad da su Naseem duk muna baya in da direban sa ke janmu.
motan su Bappa daban, Bappa na gaba shida direba Inna Wuro da Mama da Faty suna baya.
har da su Uncle Mahmoud motan su daban shi yake jan motar sa da kansa shi da matarsa da ƴaƴan su ne ciki dan shima yace ba za'a barsu a baya ba.
sai motar security motar su guda, a hanya muka haɗu da su na fahimci biyo mu suke.
a jere motocin suke tafiya, motan su Uncle Mahmoud ne a gaba na su Bappa na biye da su in da moton security ne ke biye da mu......
da misalin karfe uku muka iso cikin garin Bauchi,
wani irin lumshe idanuna nayi tare da kuma huɗe wa a cikin garina mahaifata,
na shaki iskar dake kaɗa wa ina mai farin ciki da jin daɗin gani na cikin garin.
murmushi Ahmad yayi tare da jan kumatu na yace
"Yarinya tana murna tazo kauyen su."
dariya nayi nace "Nan ɗin ne kauyen me Abuja yafi shi da shi."
yace "Lalala birnin tarayya ne fa babu haɗi ai."
nace "Ba wanin nan."
yace "To dai nuna mana hanya ina zamu karmuje mu ɓata."
dariya nayi tare da soma yi masa kwatance ya kira Uncle Mahmoud ya haɗa mu da shi narika yi masa kwatance har muka shigo unguwar mu.
a bakin get Uncle Mahmood yayi hon mai gadi ya buɗe ya shiga muka bisa a bayan sa, a farfajiyar gidan motocin mu suka faka.
numfashi mai karfi na sauke gani na a cikin gidan mu.
su Aunty Rafee'at ne da su Mamie da Goggo Hauwa suka fito daga sashin Mamie da sauri suka nufo gurin motocin,
da saauri na ɓalle marfin motar na fito da sauri muka rungume juna cikin matukar farin cikin ganin junan mu,
su Abbu suka iso gurin suna yi wa su Bappa sannu da hanya, kana a ka ɗunguma aka shiga side ɗin Mamie, security kuma aka shinfiɗa musu babban tabarma a gindin bishiyar anbulera dake gefe da tsakar gidan.

muna zazzaune a parlour sai gaisawa ake, tuni Mamie ta sa su Aunty Rafee'at suka cike mu da kayan ci da sha wan  da aka tanadar domin mu, aka ɗibi wasu aka kaiwa security.
niko ina tsakiyar su Aunty Rafee'at da Aunty Jaleela da Ya Masa'ud, da ƴan kanne na Nusaiba da Fauzan.
Naseem da Nasmah suna like a jikin Ya Masa'ud wai har sun gane shi kenan sai surutu suke zuba masa, wannan yace Uncle kaza wannan yace Uncle.
Ahmad karami kuwa yana hannun Mamie tana yi masa wasa yana dariya.
ana ta hira cike da jin daɗi da nishaɗi.
nan suka yi ta yiwa Mama mai awara godiya da irin kokarin da tayi a kaina...

Acan gidan SALEEM kuwa labarin zuwan su HAMDAH ne ya iske Na'ima,
a bujajan ta taso dan gane wa idon ta karya ne ko gaskiya, dan yau tayiwa boka alkawarin kawo masa cikon kuɗin sa, dan wan da suka shirya zai sace Ameer baya nan shine aminiyar ta Raliya ta bata aron cikiton kuɗin da zata bawa boka, idan aka karɓi kuɗin fansar Ameer ta biya ta,
shikuma yayi mata alkawarin yau ɗinnan da daddare zai tura aljanu su kashe HAMDAH...

Sallama muka jiyo daga sama, duk kanin mu muka mai da hankali bakin kofa,
kamar an jefo ta haka ta faɗo cikin parlour'n, wani irin kallon-kallo muke yi da Na'ima da tayi mutuwar tsaye bakin kofa.
dogon tsaki Aunty Rafee'at ta ja kana tace
"HAMDAH kalli wannan hoton ki gani."
tayi maganar tana nuna min hotunan mu da ta sa Fauzan ya ɗibo a side ɗin Ummi.
dariya nayi ganin hoton tun ina Dass wani lokaci Inna ta bani kuɗi naje na ɗau hoton,
kai na girgiza tare da faɗin
"Allah sarki Inna ta."
Ahmad da hankalin sa ke kanmu yana binmu kallo cike da sha'awa da burge wa ganin yan da muke da junan mu yace
"Madam muga hoton."
ɓoye sa nayi a baya na ina dariya, Aunty Jaleela ne ta fizge hoton tana faɗin
"Bashi yaga munin kawai." ta mika masa hoton.
nace "Allah Aunty Jaleela ko a da ma na fiki kyau."
Ya Masa'ud yace "Bare kuma yanzu har girma kin fita ƴar gidan Inna."
dariya na fashe da shi nace "Yau wa Ya Masa'ud faɗa mata dai."
Aunty Rafee'at tace
"Oh Masa'ud zaka fara haɗin naka ko."
tayi maganar tana dariya cike da kewar faɗar mu da Aunty Jaleela da muka saba.
Aunty Jaleela kuwa hararar sa tayi tace "Ni sa'ar ka ce Masa'ud?."
Ya Masa'ud yace
"Aunty Rafee'at matsa na mari bakin yarin yar nan."
dariya muka yi dukan mu har da Ahmad da hankalin sa ke kanmu,
yana kallon hoton yana dariya, idan muka haɗa ido da shi sai ya nuna min hoton yayi dariya,

baki na rika murguɗa masa nima ina dariyar...
Na'ima tana tsaye kamar wacce a ka kafata idanunta a kaina, Kamar a mafarki haka take ganin komai.
Ummi ce ta dube ta tace
"Shigo mana Na'ima ya kika tsaya a gurin."
ta janyo ɗan da ke rike a hannunta suka karaso cikin parlour'n hankali a mugun hargitse....

Hospital
Dr Mukhtar ne zauna cikin offece ɗin sa, kamar daga sama yake jiyo hayaniya cikin asibitin, da sauri ya mike ya fito, sai ganin ƴan sara suka yayi cike a cikin parlour'n asibitin shi, ko wannen su daga mai wuka sai mai adda sai walkiya suke, suna faɗin
"Ina likitan yake."
ido ya wawwaro cike da tsoro yace
"Bayin Allah lafiya?."
wani bakware ne yayi kansa da adda yace "Na sassare ka idan ka kuma mana tambayar da bata gamshe mu ba, kai ne likitan?."
kai ya gyaɗa jikin sa na ɓari.
yarinyar da suke tare da ita ya janyo ta yace
"Kasan wannan?." Ido Dr Mukhtar ya kura mata yana ta son tuno in da ya taɓa sanin ta.
mari ɗan saran yayi masa da adda a fuska da karfi yace
"Ka gane ta?."
a gigice yashiga gyaɗa masa kai dan marin yasa shi tuno ta da sauri.
yace "Eh..Eh.. na gane ta."
murmushi bakwaren yayi yace
"Ai da har na soma tunanin nasa yara su ankarar da kai su tsastsaga min kai."
fuska bakwaren ya murtuke yace
"Ina ɗana da ta zo ta siyar muku da shi anan, sabo da ku kananun ƴan isaka ne shine zaku karɓi ɗana ku bata kuɗi, zan nuna muku naku iskancin kaɗan ne idan ɗana bai fito ba duk wan da yake da hannu kan lamarin sai na bubburma masa wuka."
da sauri Dr Mukhtar yace "Wlh billahil lazi baya gurina yana gurin wata ne."
kwashe sa wani yayi yakaɗa keyar sa yace
"Wuce muje ka nuna mana in da take."
suka tasa shi gaba suka ɗaura shi kan mashinan da suka zo da shi,
gidan su Raliya suka fara zuwa kasan cewar bai san gidan Na'ima ba.
suka taki sa'a Raliya tana gida, yace musu tare suka zo suka karɓi yaron shi bai san gidan ta ba ita tasan gidan ta.

nan suka saka Raliya ita ma gaba bayan sun gama gwaza mata maruka.
suna zuwa gidan Na'ima mai gadi ya shaida musu ba ta nan,
Raliya ta kira ta a waya tace mata tana cikin gidan su SALEEM, nan suka ɗau hanyar gidan...
koda suka zo shiga gidan ganin su da makamai sai security suka hana su shiga gidan...
jin hayani ya a waje da karar wasa wukake da adduna yasa muka fito dan ganin me ke faruwa,
jin abun da ɗan saran nan yake faɗin
"Wlh sai ya sassare ta idan bata fito masa da ɗan sa ba."
yasa Abbu cikin rashin fahimta yace wa security su bar sa shi ya shigo yaji gurin wa yazo."
tare suka shigo da Raliya da yarinyar da yake ta janta, da kuma Dr Mukhtar.
ido Na'ima ta cicciro cikin tsananin tsoro da firgicin ganin yarin yar da ta karɓi yaro a gurin ta
tayi karyar cewa ita ta haife sa,
ga kuma Raliya da Dr Mukhtar..
Abbu yace
"Gurin wa kuka zo a gidan nan."
bakwaren ya dubi yarinyar cikin muryar ƴan iska da suka gama holewa da kayan maye yace
"Bazaki nuna ta ba sai na daddatsa ki."
da sauri yarin yar ta ɗago hannunta na rawa tashi nuna Na'ima tana faɗin
"Gata nan ita ce wannan."
baki ya karkata cike da rashin mutumci yace
"Okay ɗan nawa kenan wannan dan tsabar rashin daraja da kika san bazaki iya haifa ki rike ba
shine bazaki kawo min shi ha, ance miki ni abin kunya dami na yayi zan kaiwa tsohuwa ta ta
rike min shi, taho nan yaro nine ubanka."
ya miko hannu zai ruko hannun ɗan da ke hannunta.
cikin rashin fahimta kowa ke kallon su Abbu yace
"Me kake nufi kana nufin kace shi wannan ɗan naka ne?."
yace "Eh mana ɗana ne mana."
Abbu ya jinjina kai cike da al'ajabi yace
"To ɗan dakata kaɗan." wayar sa ya daddan na yakira lambar Ya SALEEM yana ɗagawa Abbu
yace
"Duk in da kake duk abun da kake kabari yanzu yanzun nan kazo ina neman ka."
daga cikin wayar Ya SALEEM yace
"Gani nan kusa da gidan ma."
yana kashe wayar motar sa tana karaso wa bakin kofar gidan,
ganin cincirindon kwarawa ƴan tsara suka haɗe da hukuma a kofar gidan su, yasa shi fita cikin
motar da sauri yanufi cikin gidan.
yana sa kafa cikin gidan muka haɗa ido da shi.
cak ya ja ya tsaya yayin da zuciyar sa tayi wani irin tsalle har sai da yakai hannunsa ya dafe
kirjin sa da sauri.
niko cikin hanzari na janye idanuna a kansa, yayin da naji kirji na yayi wani irin bugawa..
Abbu yace "Ka tsaya kuma ka karaso mana kai muke jira."
a sannu ya shiga ɗaga kafar sa har ya karaso gurin.
Abbu ya dubi Ya SALEEM da kyau yace
"Kasan wannan?." ya nuna ɗan saran

kai ya girgiza batare da yace komai ba.
ɗan saran cikin yanayin Muryar maye yace "Ai da ma bai Sanni ba, kamar yadda nima ban san shi ba, kamar dai yadda ban san wannan matar da ta siya ɗana ba."
ya karashe maganar yana tangaɗe da ɗaga addan da ke hannunsa sama yana nuna Na'ima da shi.
Abbu ya girgiza kai kana yace
"To kaji wai ɗan ka ɗan shi ne, dama nace kazo ya faɗa a kunnen ka bazai bamu sako mu faɗa maka ba."
sai a lokacin Bappa yayi magana dan sai yanzu ya fahimci in da batun ya dosa, yace
"Kai yaro kace ɗan ka ne wannan ta ya aka yi ya zamo ɗan ka bayan ga uba da uwan yaron anan?."
mari ya kai wa yarin yar yace
"Faɗa musu yan da kika yi kika siyar min da ɗana, a miko min shi na tafi ina da shara yau."
duban ta Bappa yayi yace "Ke yarin ya ya akayi haka, da gaske ɗan sane?."
hawaye ta shiga share wa tana jan hanci tace
"Eh ɗan sa ne, dama..dama..dama lokacin ina da ciki ne da zan haihu shine iyaye na suka kore ni suka ce ba a gidan su ba, shine naje asibitin wannan."
ta nuna Dr Mukhtar dayake ta tsilli-tsilli da ido,
kana ta cigaba da faɗin "Shine na haihu sai waɗan nan suka kirani."
ta nuna Na'ima da Raliya sannan ta cigaba
"Shine suka ce suna son ɗan in dai yadda shi zan yi, shine wannan ta bani kuɗi ta karɓe sa."
ta karasa maganar da nuna Na'ima.
Bappa ya dubi Dr Mukhtar daya sunkuyar da kai kasa yace
"Abun da ta faɗa haka ne shin a asibitin ka akayi haka?."
Dr Mukhtar ya shafa gefen fuskar sa daya kunbura in da bakwaren ya mare sa da adda, ya gyaɗa kai tare da faɗin
"Eh haka ne a asibiti na ta haihu kuma ni na karɓi haihuwar, kuma wannan shine ɗan."
ya nuna ɗan dake rike hannun Na'ima.
salati kowa ya sake cike da ɗinbin mamaki, masu tafa hannu suna tafa wa masu salati suna yi.
Abbu ya dubi Na'ima yace "Mika musu ɗan su."
jiki a sanyaye cike da taren jin kunya ta tura musu ɗan.
bakwaren ya ja hannun ɗan yana faɗin
"Taho nine nan uban ka, ke kuma wuce muje ko na tsastsaga ki anan,
dan rashin mutunci da kika ce a zubar da cikin ba cewa nayi miki ki haifa ki bani ɗana ba,
karamar ƴar iska kika iya yin cikin ɗan ne baza ki iya rukon sa ba,
shine zaki siyar min da shi ance miki ni abin kunya ya dame ni ne, rike ɗan titin ne bazan iya ba tun da na iya yin cikin sa."
Bappa yace "To Allah ya shirye ka."
yace "Amin Baba amin baba."
ya kaɗa keyar yarin yar yana layi da waina addar hannunsa sama suka fita,
yaja ƴan uwan sa ƴan sara suka yi gaba.
Dr Mukhtar ma yaja kafa ya fita tsimi-tsimi Raliya ta bi bayan sa...

Baya Ya SALEEM yayi yayin da hannunsa ke dafe da kirjin sa.
a hankali ya shige cikin ɗakin Ya Masa'ud.
Mamie ta dubi Na'ima da take jin wani irin tsanar ta rai ɓace tace
"Shi yasa ko dai-dai da rana ɗaya ban taɓa jin son ɗan nan ba ashe sabo da ɗan shege ne ba jinina bane."
Mamie ta juya ta nufi side ɗin ta rai ɓace.
shewa Aunty Rafee'at tayi tashiga tafa hannu, ta zo gaba Na'ima tana yi mata wani irin kallon sama da kasa
tace "Ai dama karshen muna fuki jin kunya, duk wanda yace ruwan wani bazai tausa ba nasa ko lum-lum bazai yi ba, zakaran da Allah ya nufa da cara kuwa ko ana ga muzuro ga shawo sai ya yi,
wacce kika lankaya wa tayi ciki da auren ta kika kazan ta mata ciki, gata a gaban ki ta zame miki abun kallon abin kwatance,
ɗan shege zaki kawo mana cikin family bama bukatan bare a cikin mu,
fita mana agida makira algunguma kaɗan kika fara gani,
sai duniya tayi juyin masa da ke."
Aunty Jaleela tace "Kamar yanzu kuwa zaki fara ganin aya, sai kin gwammaci mutuwa da rayuwar ki, fita a kace fita mana agida."
suka kaɗa ta har waje.
niko ina tsaye ina kallon abin kamar a Film,
Bappa ya girgiza kai yace
"Duk wan da ya nufi wani da sharri a kwan a tashi kan sa yake koma wa, Allah ka tsare mana imanin mu."
aka amsa da amin kana muka juya muka koma ciki.
kowa yana jinjina lamarin.
har muka zazzauna ana alhenin abun.
Bappa yana ɗago kansa idanunsa sukayi arba da wasu hotunan Inna guda biyu acikin glass ɗaya, dake like jikin garun parlour'n,
huf ya mike tare da nuna hoton da yatsa yana tafiya in da yake, cikin rawar murya Bappa yace
"Adda A'i."
da mamaki kowa ke kallon sa su Abbu suka mimmike tsaye,
ya juyo da sauri yana faɗin
"Wannan hoton a ina kuka samu?."
Abba suka haɗa baki wajen cewa
"Innar mu ce ka santa ne?."
da sauri Bappa ya fita gurin mota yaje ya buɗe kana yabuɗe jakarsa dake cikin motar ya ciro wani hoto kana ya dawo cikin parlour da sauri,
ya mika musu hoton wan da yake iri ɗaya da ɗaya daga cikin hotunan,
da mamaki su Abbu suke kallon hoton iri ɗaya da wan da yake jikin garun parlour,
Bappa yace "Dai-dai da rana ɗaya ban taɓa ajiye hoton a wani guri daban ba ko da yaushe yana cikin jakata sabo da girma da matsayin wacce take cikin hoton a guri na,

Adda ta ce ita ta sha nono ta bar min,
lokacin da Bappan mu ya rasu ina ɗan kara mi, sai ƴan uwan Baban mu suka ɗauke ni suka tafini, kasanceaar ni na miji ne, suka barwa Maman mu Adda A'i,
kamar yadda kuka sani mu fulani bamu fiye zama guri guda ba, musamman fulani makiyaya, haka mukayi ta yin nesa da in da mamar mu take,har muka sallaka Nigeria,
tun da aka tafi da ni bansake haɗuwa da Maman mu da Adda A'i ba,
bayan wasu shekaru masu dama aka zo ma na da sakon rasuwan maman mu da kuma wannan hoton, aka bani duk da lokacin da muka rabu da ita ina yaro ne sosai amma bai hanani gane ƴar uwa ta ba,
lokacin da girma ya same ni na dawo Nigeria da kaina ban san kowa ba bansan ta inda zan fara neman ƴar'uwa ta ba, rugar mu da na rike sunan sa nayi ta bincike a kansa har naje rugar, duk wanda na tambaya sai ya cemin baima santa ba,
a haka na fauwalawa Allah komai nacigaba da addu'a Allah ya haɗu mu da ita, haka na rika ajiyar hoton nan harrrana mai kamar tayau,
ashe dai da rabon mugana ina Adda A'i take tana ina?."
Abbu yace "Allah yayi mata rasuwa."
salati Bappa yayi sai ga hawaye a idon sa, kowa sai da yayi kuka tuno da Inna..........!



Bappa yace "Allah mai girma da
ɗaukaka ashe dai jikata ce HAMDAH, a she dai jika ta ce nake zaune da ita cikin rashin sani, alhamdulillah masha Allah, hakika ɗan adam baya fidda rai da rahamar Allah, ashe wata rana zan haɗu da jinina ga jiko ki na ga ƴaƴa na, kuzo nan ƴaƴa na Allah yayi muku albarka."
ya janyo su Abbu jikin sa yana ta sanya mu
su albarka,
Abba ya nuna goggo Hauwa yace "Wannan ita ce kanwar mu."
Bappa yace "Taho nan kema."
Goggo Hauwa ta mike tana sharar kwalla taje in da yake su Abbu suka ce tabbas Inna tana faɗin tana da kani amma bata san in da yake ba sun rabu tun suna kana na.
tabbas nima Inna tasha faɗa min tana da ɗan'uwa sai dai tun suna kana na aka raba su yanzu bata san in da yake ba..

Uncle Mahmood farin ciki ya gama lullube shi yau shima gashi cikin ahlinsa.
haka akayi ta farin ciki yayin da farin cikin ya gusar da alhinin da Na'ima ta sakawa mutane...
Ahmad ya dube ni kasan cewar yanzu a kusa da shi na zauna, yace
"Ina taya ki murna na karuwar ahlinki, sai naji ina ma ace nine iyayena da ƴam'uwa na suke zagaye da ni haka."
kai na rausayar ina mai jin tausayin sa, na sauke hannuna kan nashi dake saman hannun kujera nace
"Allah ya haɗa ka da su a jannatir firdausi."
murmushi yayi tare da faɗin amin amin....

A ɓangaren Na'ima kuwa tana fita a gidan, a hargitse cikin matsanancin tashin hankali ta tsari mai napep.
tayi gidan bokan ta,
tana zuwa ta shaida masa abun da ke faruwa.
bokan yace taje ta kawo cikiton kuɗin aiki yanzu ta dawo a rufawa kowa baki su mance da abunda ya faru, a kuma kashe HAMDAH.
tace to ta fita abujajan ta dawo gida,
domin ɗaukar kuɗin da Raliya ta bata aro ta kaiwa boka.
tana shiga gida ta dadda SALEEM a parlour da magunguna da gorar ruwa a gaban sa da alama yanzu yagama shan maganin.
tana kokarin wuce sa tashiga ɗaki, ya dakar da ita ta hanyar kiran sunan ta
"Na'ima." ya kira sunan ta batare da ya dubi in da take ba.
sai da hantar cikin ta ya kaɗa, jin yan da ya kira sunan nata a sama,da jin amon sautin sa da babu wasa ciki.
a fusace ya mike tamkar fusataccen zaki yayi kanta,
tana ganin haka ta shiga ja da baya tana kokarin gudu,
da sauri ya cakfo ta tare da shako wuyan ta har saida idananun ta suka fiffito waje,yayin da numfashin ta yake kokarin barin jikin ta.
wasu tagyayen maruka yashiga shinfiɗa mata nan da nan fuskarta ya canza kala.
sai kuma ya sake ta da sauri tare da dafe kirjin sa da hannayen sa biyu, yashiga yin tari a hankali ya durkusa kasa.
Na'ima ko yana sakin ta da sauri tayi baya tana maida numfashi tare da shafa wuyan ta da fuskar ta daya sauya masa kamanni...
hannun sa ya ɗaga yayin da taren ke ci gaba da zuwar masa ya nuna ta tare da faɗin
"Fita tafi na daina ganin ki, ki sani har aba na haramta kaina gare ki, fita min a gida tafi na daina ganin ki,
kije Allah ya haɗa ki da hukubar duniya dana kiyama."
numfashin sa ne ya soma fizga yayin da maganar tasa tashiga harɗe wa.
wani kururuwa Na'ima ta sake tace
"SALEEM kasan abun da kake faɗa kuwa, kana nufin ka sake ni sakin da baza ka sake dadowa dani ba har abada,
haba SALEEM kada ka min haka wlh duk abun da nayi sabo da son ka nayi, ina son ka bana

kaunar wata ta raɓe ka sabo da son da nake maka,
wayyo Allah SALEEM meyasa baka cewa HAMDAH ka haramta kanka har abada da ita ba,
wayyo Allah na nashi uku
dan Allah SALEEM kada ka min haka."
dagudu ta juya ta shiga ɗakin ta, laidar kuɗin da Raliya ta bata aron sa ta ɗauka tana faɗin
"Boka kai zaka iya min komai kai zaka fitar da ni cikin wannan hali, dole SALEEN ka cigaba da zama dani dole boka yasa ka zauna da ni."
tafito da sauri, har lokacin yana durkushe dafe da kirjin sa.
tayi waje da gudu, tana duba mai abun hawa, babu ko alamar su a unguwar.
da kafa ta rika tafiya tana sauri kamar zata tashi sama bata ko ganin gaban ta burin ta kawai ta isa gurin boka,
har ta fito babban titi zata sallaka ta koma ɗayan gefen dan ta tari abun hawa,
wani mai babban mota ne ya sako kai bata ankara ba sai ji kake keeeee motar tayi ciki da ita..
salati mutane suka fara akayiyo kan titin a can karkashin motar a ka ciro ta, gaba ɗaya halittar ta ya canza sabo da sabar jin ciwo, bata ko motsi tana kwance kamar gawa.
wasu suna faɗin ta mutu wasu suna faɗin bata mutu ba,
aka kwashe ta aka garzaya da ita asibiti mafi kusa da gurin....

Da daddare duk yanda Ahmad yaso yatafi masaukin da yasa a tanar masa shi da security sa, su Abbu suka hana suka ce ya zauna a cikin dangi dan shima ya zama ɗan uwa,
duk da sun san gida kamar nasu kam yayi wa Ahmad Tijjani Sabil kankanta.
parlour'n da su Abba suke zama su tattauna nan akayi masa masauki, kasan cewar akwai bedroom's ciki har guda uku, shi ɗaya Bappa ɗaya Uncle Mahmood ɗaya.
sashin Inna na gidan kuma akayi wa security masauki ciki,
inda mu mata kuma muke cikin sauran sashin wato sashin Ummi da Mamie, dan su Aunty Rafee'at ma anan gidan yau sukace zasu kwana....

Washegari duk a sashin Mamie muka hallara kamar jiya, anan mukayi breakfast, ana zaune ana ta hira,
Bappa yace a kira masa Ya SALEEM kowa na nan shine kaɗai ba ya nan,
ya kama ta yazo ya gan sa dan ganin da yayi masa jiya ko a hanya ya gansa yanzu bazai gane sa ba.
Ya Masa'ud ne ya kira sa a waya
ya ɓata lokaci mai tsawo kafin yazo.
yashigo sanye da kananun kaya a jikin sa Black jeans da yellow t-shirt.
kallo ɗaya nayi masa na ɗauke kai,
ya ɗan rame ya kara haske gashin kan nan nasa nanan yalan-yalan baki sutuf sai sheki yake, sai dai ya ɗan hargitse da alama bai sami damar tace shi ba ya fito.
fuskar nan tasa a ɗaure tamau yanayin nan nasa da yanayin suffarsa yana nan yana biye da shi.

Bappa yace "Zo zauna nan kusa da ni SALEEM kaga yan da Allah yake ikon sa ko ashe ku jinina ne."
Ya Masa'ud ya washe baki yace
"Ya SALEEM ashe shine kanin Inna da take faɗan nan, jiya kawai sai gashi da ɗayan wancan hoton Inna."
ya nuna hoton ta dake like a jikin garun parlour'n yana mai cigaba da washe baki cike da farin ciki.
shiko Ya SALEEM bai yi magana ba sai zama da yake a kuje rar gefen Bappa, duk maganar da ake baya jin su gaba ɗaya hankalin sa na kan su Naseem da suke jikin Ahmad.
waya ta na ɗaga nashiga daddan na ta,
ina jiyo gaisuwar da yake yiwa su Bappan kamar mai ciwon baki.
su Aunty Rafee'at suka gaishe sa, ya amsa kamar wanda aka sashi dole.
baki na taɓe a kasan raina nace ashe dai hali na nan.
Ahmad ya mika masa hannu da murmushi kan fuskarsa yana faɗin
"Barka da safiya."
"Barka." kawai yace a dakile batare da ya dube sa ba bare ya sa ran zai karɓi hannun nasa suyi musabaha.
Naseem da ya kafe Ahmad da ido yana kallon yan da ya mika wa Ya SALEEM hannu, sai ya washe baki shima ya miko masa hannu tare da faɗin "Baika ka da wai haka."
dariya duk aka saka ganin yan da yayi kamar wani babba, shima dariyar yayi yace
"Daddy haka ake yi." kai Ahmad ya gyaɗa masa yana dariya.
Ya SALEEM kuwa tun da Naseem ya miko masa hannu yakafe tafin hannun nasa da ido, har ya janye hannun yana binsa da kallo yayin da jikin sa da zuciyar sa suke wani irin fizga da jin yaran a cikin jikinsa.
Ya masa'ud ne ya miko masa hannu yace
"Zo mu gaisa my boy." ai ko da gudu suka dawo jikin Ya Masa'ud Nasmah tana faɗin
"Hai dani Uncle." hannayen su duka ya rike yana yi musu dariya yace "To munyi gaisuwar."
jiki na suka dawo Naseem yace min "Mommy ya sunan shi?."
ya nuna Ya SALEEM.
yi nayi kamar banji sa ba, ina cigaba da danna waya ta.
ganin ban kula shi ba sai ya shiga bubbuga kafa kasa yana faɗin "Mommy ya sunan shi ni ban sani ba."
batare da na ɗago daga kallon wayar da nake ba nace
"Uncle." Nasmah tace "La shima Uncle ne." sai suka juya suka ci gaba da tsalle-tsallen su a sakiyar parlour'n.
Ahmad ya mike tsaye sakama kon shi gowar kira wayar sa, ya ɗaga kiran yayi waje.
Nasmay ce ta bi bayan sa tana faɗin
"Daddy nima dan bika."
yace "Waya zanyi Nasmah ina zuwa."
tace to sai ta dawo.
goggo Hauwa ta dube su cike da sha'awar yaran ta dube ni tace
"Allah sarki HAMDAH wai nikam ina cikin da kika tafi dashi ne kam, ko wuya ya sashi zuba ne, tun jiya nake ta son na tambaya."

Aunty Rafee'at tayi murmushi tare da kallon yaran tace
"Gasu nan Naseem da Nasmah takwaran Inna da Abbu."
wani irin ɗago wa Ya SALEEM yayi yana mai ware idanunsa a kan yaran yana binsu da wani irin kallo.
goggo Hauwa ta janyo yaran tana faɗin
"Ikon Allah ikon gaske Allah mai girma ashe dai kune ƴaƴan SALEEM."
da sauri na ɗago tare da faɗin "Su ba ƴaƴan sa bane ƴaƴa na ne!."
Ummi tace "Ke HAMDAH baki da hankali ne."
da sauri Mamie ta tari numfashin ta tace
"Da hankalin ta karya ta faɗa ne?."
mike wa nayi na dubi su Nasmah nace
"Ku wuce muje nayi muku wanka."
ai ko da gudu suka riga ni fita na bi bayan su muka nufi sashin Ummi.

A parlour'n kuwa murmushi Abbu yayi kana yace
"Yarin ya ta faɗi gaskiya ƴaƴan ta ne tafi kowa iko da su ita tasan wuyan su, sannan kuma ai da bakin sa yace ba cikin sa bane, ta ya za'ayi su zamo nashi."
wani irin mike wa Ya SALEEM yayi yanufi kofa yayi waje.
Abbu ya bi bayan sa da kallo yana jinjina kai..

Muna shiga side Ummi kuwa bedroom na shige da su muka haye gadon Ummi, nace "Ku zauna a nan kuyi wasan ku."
nima nayi kwanciya ta.
kwanciya ta bada jimawa ba kiran Ahmad yashigo waya ta ina ɗagawa yace
"Kyakkyawa ta kina ina nashigo ban ganki ba?."
"Ina side ɗin Ummi."
yace "Shine kika bar Ahmad yana kuka zo ki karɓe sa."
nace to. kana na mike na fito.
ina fita na hango sa shima yana fito wa daga sashin Mamie rike da Ahmad karami a hannunsa sai dariyar sa yake,
tsayu nayi dai-dai kofar Ya Masa'ud ya karaso tare da miko min shi yace
"Karɓe shi ki bashi nono."
baki na turo nashiga yarfe hannu ina ɗan bubbuga kafafu na a kasa cikin muryar shagwaɓa nace
"Dama ba kuka yake ba kace wai yana kuka yaro yana wasan sa, baya jin yunwa."
yace "A'a kyakkyawa ta bashi nono yasha tun ɗazu da yasha ina lura baki kuma kara masa ba, yana da hakuri ne kawai shi yasa baiyi kuka ba."
"Allah ni nagaji da shan nonon nan har zafi yake min fa."
yace "Yi hakuri muje na hura miki shi zai daina zafin, muje na gani, idan ya daina sai ki bashi ya sha."
yayi hanyar side ɗin Ummi, na ɗaga kafa zanbi bayan sa, sai naji tari cikin ɗakin Ya Masa'ud kofar ɗakin na tura ina faɗin
"Ya Masa'ud wannan irin shakewa haka kasha ruwa mana ko..."

nayi maganar ina leka cikin ɗakin,
cak na haɗe ye ragowar maganar tawa ganin ba Ya Masa'ud ɗin bane Ya SALEEM ne yana dafe da kirjin sa, ina sako kaina idanunmu ya sarkafu da juna, da sauri na janye nawa baya nayi da sauri nabi bayan Ahmad...
muna shiga ya zauna kan kujera na zauna gefen sa,
yaja riga ta sama ya ciro nonon cikin bra ya ɗaura shi kan kafa ta, yasaka masa cikin baki yaleko fuskarsa yace
"Sha a hankali bada zafi ba."
hannun na ya ruko ya haɗe cikin nasa,
ya dube ni tare da faɗin
"Kyakkyawa ta gobe zamu koma ko."
ido na waro nace "Gobe kuma." kai ya gyaɗa yana murmushi baki na turo nace
"Ni da zan yi wata uku." yace "Wata uku? ina ban isa ba, in kin daɗe kiyi sati ɗaya, gobe ni zan koma akwai abin da zanyi sati ɗaya zakiyi kuma kinci kwana biyu a ciki."
"Haba My sati ɗaya yaushe naje na yi ziyara har Dass fa zani, ni da nake so ma na wuce har Maiduguri garin su Ummi, sati 1 ai ba zai min ba."
"Kidai je Dass amma banda Maiduguri kibari zamu je musu na musamman,sati ɗaya babu kari, bari naje naga gari."
yayi maganar yana mike wa.
nace "Nidai sati 1 ya min kaɗan,wata ɗaya zanyi."
yace "Ni dai natafi ganin gari."
"Idan ka ɓata babu ruwa na." waje yayi yana dariya da faɗin
"Idan har na ɓatan ke zaki fara nima na."
na kwantar da Ahmad karami kan kuje ra,
bayan sa nabi lokacin har yayi waje da sauri haɗe da sassarfa na iso in da yake naruko hannunsa ina dariya nace
"Ko neman ka bazan yi ba idan ka ɓata."
shima dariyar yayi tare da jan kumatu na yace
"To sake ni naje na ɓatan." kafaɗa na make ina kwantar da kaina a kafaɗar sa nace "A'a to ai ina son ka idan da bana son ka ne sai na barka ka tafi kaje ka ɓatan."
kiss ya manna min a gefen fuska a hankali yace
"Ko zamu tafi tare ne Allah nayi missing ɗin ki."
dasau ri na ɗago kai na ina kokarin barin gurin da sauri ya ruko hannuna ya janyo ni yace
"Muje ni?." kai na girgiza ina dariya nace "Jeka kawai." "Zo kiji wani magana." yafaɗa yana kokarin haɗe jikin sa da nawa, yayin da hannunsa ke sarkafe cikin nawa dukkan mu dariya muke ina ɗago wa muka haɗa ido da Ya SALEEM,dake tsaye jikin motar sa da waya kare a kunnen sa da alama waya yake.
kai na nakawar tare da mai da dubana kan Ahmad nace "My ina fashin salla fa."
"Zo muje na gani da ido na."
da sauri na fizge hannuna na juya ina yi masa dariya na koma ciki.. a
ɓangaren Ya SALEEM kuwa da sauri ya shige motar sa ya bargidan da mugun gudu kamar zai tashi sama....

Washegari da safe Ahmad da Uncle Mahmood da iyalen sa suka juya, sabo da ai kin sa.
washegari nima na tafi Dass  in da Ya Masa'ud da Fauzan da Nusaiba suka yi min rakiya.
ranar da muka isa Dass nasha kuka gani na ɗakin Inna ta bata nan ciki.
na zaga gida jen ƴan uwa da abokan arziki tun da nazo muna tare da kawata Rabi da yanzu ƴaƴan ta biyar,
ranar da zamu dawo Bauchi ta raka ni lambun Baba na lambu, muka same sa yana ta ai kin ban ruwa wa kayan lambun sa,
ko da ya ganni bai gane ni ba sai da Rabi ta tuna masa ni.
yace "Allah sarki HAMDAH kece kika zamo haka sam ban gane kiba."
nayi murmushi bamu bar gurin ba sai da muka tuno da baya,
na cire mayafi na nasha ɗammara na karɓi tiyo nayi ta bin layi layi ina zubawa shukan ruwa, cike da nishaɗin tuno da baya.
kuɗi na bashi masu yawa nace ya kara jari da su.
yayi ta min godiya yacire min kayan miya yacika min babban laida da su yace naje na sha miya..
Rabi da Mamar ta duk sai da nayi musu alkairi, musamman Rabi da naga kalar yaruwar da take kuɗi masu yawa na bata nace taja jari da su tasami abin dogaro da kai ita da ƴaƴan ta, nakuma bada kuɗi domin a sasu a makaranta dan duk basu makaranta kuma sun fi su Naseem girma, muka juyo Bauchi..
ranar da na cika sati Ahmad yakira ni wai sai dai na taso yau nace
dan Allah ya barni na kara wani satin.
da kyar ya amince nayi kwana goma, shima ɗin sai da ya haɗa da Ummi da kanta ta shirya mana kayan mu, ta sa aka kai mana cikin mota.
Ya Masa'ud ne ya shigo ina gyara mayafi na Ummi tana ta cewa nayi na fita kada muyi tafiyar dare, kada na bi na su Aunty Rafee'at mu ɓata lokaci.
hannun su Naseem ya kamo yace
"Wai ku zo." ya janyo hannunsu har sun kai bakin kofa nace
"Ya Masa'ud wake kiran su?."
"Ya SALEEM ne." yayi maganar suna fita daga parlour'n.
da sauri na bi bayan su Ya SALEEM ɗin yana tsaye jikin motar sa su kuma suna daf da isa in da yake.
sauri na kara na iso su narike hannayen su tare da janye su nace
"Ya Masa'ud kar ka kaisu sauri muke."
sai na juya gurin mota na buɗe na saka su ciki nima na shiga na mai da murfin motar na rufe.
yabi motar da ido.
su Bappa suka fito da duk mutanen gidan in da su Bappa suka shige motar da suka zo ciki.
Ummi tazo gefen da nake ta buɗe ta mika min Ahmad tana yi mana fatan isa gida lafiya,
muka yi bankwana da ƴan uwa har muka fita yana nan tsaye a gurin..........!

Bayan wani lokaci..
ranar wata laraba zaune nake a parlour'n kasa, najiyo sallamar hajiya Karima.
na amsa tare dayi mata barka da zuwa, ta amsa tana zama kan kujera,
wasa ta shiga yiwa Ahmad karami da ke zaune a kasa kan carpet rike da pida a hannunsa yana shan madara.
na gaishe ta ta amsa fuska sake tana tabbaya ta ya kwanan gidan da yaran.
nace kowa lafaya.
ta dube ni da kyau tare da gyara zaman ta tace
"HAMDAH nazo ne dama na nimi gafarar ki da kuma sulhu,
hakika nasan abin da na ai kata a baya ban kyauta ba, na gane kuskure na Ahmad ɗana ne, kullum cikin ladabi da biyayya yake agare ni,
me zai sa naso ganin bayan sa, i naso ki rufa min asiri kada ki faɗa masa komai, duk da nasan ko da kin faɗa masan ma bayar da zaiyi ba, sabo da irin ki sun sha faɗa masa baya yarda,
ina so na gyara kuskure na shi yasa nazo na sanar miki yanzu duk na zubda makamai na, me zai sa na so kashe Ahmad wanda yaɗau keni matsayin uwa, sharrin shaiɗan ne, yanzu  zuciya ta ɗaya yake,
kuma zan same sa cikin dabara na nimi gafarar sa."
ɗan shiru  nayi ina duban ta
yan da take maganar  gaba ɗaya yanuna zallar gaskiyar ta take faɗa,
kai na jinjina kana nace
"Babu komai hajiya Allah ya tsare mu da sharrin shaiɗan."
na mike  ina mai jin daɗin maganar ta ina ayyanawa a raina yanzu zan zo na kira Ahmad na sanar masa, Hajiya ta yada makaman ta, nasan shima yanzu zuciyar sa zata sami salama. na tufi kitchen domin na samo mata ɗan abin taɓawa, matar nan tana bani mamaki idan ka ganta tamkar mutumiyar kwarai amma zuciyar ta baki, gara da yanzu Allah ya ganar da ita tana da rabo...
kayan ci da sha na shirya su a kan tray kana na ɗauka na nufi kofa.
da sauri nakarasa fita daga cikin kitchen ɗin jin ana tafa hannu,
turus na naja na tsaya nan bakin kofar kitchen ganin Ahmad tsaye cikin parlour'n yana tafa hannu tare da dumfaro Hajiya Karima dake rike da Ahmad karami ta kawo fida daf bakin sa tana kokarin saka masa shi cikin baki, cak ta saida hannunta bata sauke hannun ba bata kuma kara sa dashi cikin bakin nasa ba, yayin da hannu yake rawa.
ya karaso gaban ta yana mai cigaba da tafa hannu ya dube da kyau tare da faɗin
"Da kyau Hajiya ya kika da kata kuma bashi ya sha mana."

da sauri na karaso in da suke na dire tray ɗin saman table nace
"My Hajiya ta gane gaskiya tace yanzu babu komai cikin ranta."
"Shiru HAMDAH." yayi maganar tare da ɗaura yatsar sa kan lips ɗin sa, kana ya dubi Hajiya Karima da gaba ɗaya ilahirin jikin ta ke ɓari sai ta shiga kame-kame tana faɗin
"Ah..la... Ahmad..kuka yake shine na ɗauke sa na bashi madarar sa, da na gani a nan."
hannayen sa ya naɗe a kirki yayin da idanunsa ke kan ta yace
"To sha fara sha kafin kiba shi ya sha, sha yanzu!!!."
yayi maganar cikin tsawa sosai,
daga ni har ita sai da mukayi wani irin zabura.
yadube ni kana ya soma magana cikin fusatacciyar murya sosai.
"Duk abun da ta faɗa miki yauda ra ce bazata taɓa sauyawa ba."
kana ya mai da duban sa kan ta yace
"Kin jima kina cutar dani, kin yi sanadiyar rasa mahaifa na,ni kaina kina bibiyar rayuwa ta, hakan baiyi miki ba har da ɗana cikin jadawalin ki!
to ki sani rayuwa ta dana ɗana ba a hannunki yake ba ke baki isa kiyi mana abinda Allah bai hukunta ba, mutuwar mu ba a hannunki yake ba,
basai kin kashe mu ba ki jira idan lokacin mu yayi zamu tafi dole ba makawa,
me wannan jaririn ya tsare miki da zaki zuba masa guba cikin abin shan sa, muddin ina numfashi bazaki taɓa kuma cin galaba kan ahalina ba!!,
duk wani motsin ki a tafin hannuna kike yin sa, lokaci na ɗebar miki,
domin hukun taki kan abun da kika jima kina ai kata shi, kuma lokacin yayi dan haka."
wani irin razana nayi da sauri na sunkuci Ahmad karami dake ta raba ido kan kafarta, na rungume shi ina duban bakin sa ko har ta bashi madarar.
kofa ya kalla tare da faɗin
"Kushigo."
da mamaki na maida duba na kan kafor, wasu mutane ne guda huɗu suka shigo, yace "Kutafi da ita."
suka dube ta suna faɗin
"Oya mike."
duk wani roko da magiyar da take wa Ahmad bai saurare ta ba yace a tafi da ita, suka saka mata ankwa sukayi gaba da ita...
Numfashi na sauke tare da duban Ahmad da ya zube kan kujera tare da shafa kansa.
jiki a sanyaye na zauna kusa da shi, na dube shi jiki a sanyaye nace
"My na ɗauka da gaske Hajiya ta tuba da bakin ta take faɗa min ɗazu har tace zata nimi gafarar ka." shafo gefen fuska ta yayi, yace
"Kyakkyawa ta ai tayi hakan ne dan ki yarda da ita har ta cimma burin ta, Hajiya bazata taɓa sauyawa ba sabo da son duniya ya rigada ya gama rufe mata ido,
kuma abun da bata sani ba sam bazata taɓa zamo silar rasa rayuwa ta dana ɗana ba, idan tayi hakuri ma zan tafi na bar mata duniyar dan ba mai tabbata a duniyar nan."
ya mika hannu ya karɓi Ahmad karami dake ta zame wa yana son zuwa gurin sa,
ɗan kwanciya nayi a gefen jikin sa ina mai jin son sa da tausayin sa yana shiga na, ɗan ɗago kaina nayi ina duban fuskar sa kana nace,
"My wai ya akayi ne kake san duk shirin ta, ya akayi ne ma kasan ta zuba guba cikin abun shan

Ahmad?."
murmushi yayi tare da sumbatar goshin Ahmad karami, kana ya ɗan karkato ya ja kumatu na sannan yace
"Ai ki na ne fa a kan wasu bare kuma ni kai na, jami'in sirri."
da mamaki na ke duban sa cikin kuma rashin fahimta nace "Jami'in sirri?."
kai ya gyaɗa yana murmushi tare da ruko hannuna yace
"Eh ni SS ne kece mutum na huɗu da kukan koni waye Daddy na da Mommy na da kuma Kawa."
cikin matukar mamaki nake duban sa, ban taɓa zato ko sammani ba, ban taɓa ganin wata alama a tare da shi ba, lallai kuwa waɗan nan jami'an sun san ai kin su, in ba wai sun so ka san ko su waye bane ko shekara dubu zakayi da su baza ka taɓa sani ba,
tunanin hirar da Bappa ya taɓa min akan sa na lokacin da yaje rugar su ya kama ɗaya da gacikin makiyayin su, wan da basu san cewa shi ɗan fashi bane, ashe dai dama aikin sa ce ya kai shi can.
maganar sa ce ta katse min tunanin da nake
"Kiyi min alkawarin ko bayan raina Ahmad zai gaje ni."
da sauri na dube shi jin abin da ya faɗa mai haɗe da kalmar ko bayan ransa.
murmushi ya yi tare da kawar da maganar da wata zancen da ban.....

*Bayan wata biyar*

Zaune muke a parlour dukan mu cike da walwala da jin daɗi,
sai dai tun waye war garin yau na sinci kaina cikin matsanan ciyar faɗuwar gaba da son yin kuka.
haka nayi ta daure wa ina ta son gusar da fargabar da bansan dalilin yin sa ba. Ahmad karami da yanzu yafara tafiya sai gujegujen su suke a sakiyar parlour shi da su Naseem,
ina kwance jikin Ahmad sai binsu da dariya muke cike da shauki.
ɗan muskutawa nayi na ɗago kaina ina duban fuskar sa nace
"My last month ɗin nan zan yaye yaron nan."
yace
"A'a kam gaskiya ba yanzu ba ki bari ya kara wata biyar nan gaba sai a yaye shi."
ido na waro nace "Cap wata biyar wannan katon yaron da kowa yagan sa yake cewa har yanzu ban yaye shi ba, wani irin girma kake so yayi kafin a yaye shi, ni dai Allah ya ishe ni da tsotso."
"To masu faɗan ai basu san watannin sa bane dun sun gansa da girman jiki wannan ɗan jaririn suke cewa a yaye shi,
wani shan nono ma yake yaron da zai wuni yana wasan sa bai zo in da kike ba."
baki na turo tare da bubbuga kafafuna kan kujera nace "Ni dai kam watan nan na kare wa zan kai wa Aunty Rasheedat shi ta yaye shi."
yace "To ya isa ba sai anyi min rigima ba zan yi tunani amma dai kafin nan taso muje kiji wani

magana."
kafaɗa na make ina dariya nace
"A'a faɗa a nan basai mun shiga ciki ba naki wayon, ina dai yanzu muka fito."
a hankali ya raɗa min "Kari zanyi."
dariya nayi ina make kafaɗa..
wayar sa ce tayi kara ya ɗaga.
bayan yagama magana ya sauke wayar kana ya dube ni da murmushi yana faɗin
"Alhamdulillah wasu kuɗaɗen da Daddy ya bada kwangilar wasu kamfanoni guda uku kafin ya rasu, ba a fara aikin ba ya rasu sai a ka dakatar da aikin, waɗan da a ka basu kuɗin basu dawo da shi ba sai yau, lauyan sa ne ya kirani yanzu nazo na karɓi kuɗin."
mike wa zaune nayi ina faɗin
"Masha Allah an godewa Allah."
ya mike yana faɗin "Bari naje yanzu wai ni a ke jira."
nace "To a dawo lafiya."
har yakai bakin kofa ya jiyo ya kuma dawowa cikin parlour'n, in da su Naseem suke ya isa ya sunkuya dai-dai tsawon su, ya shafa kan ko wannen su yace
"Allah yayi muku albarka kuyi rayuwa mai kyau da inganci, kowa ya bani sallamar sa anan fita zanyi."
yanuna musu gefe da gefen kumatun sa.
cikin washe baki Nasmah ta sumbaci gefen kumatun sa na dama Naseem kuma ɗaya gefen, ganin abun da suka yi Ahmad karami shima ya maso ai kuwa ya yanka masa cizo a kuma tu.
dariya dukkan mu muka yi,
kumatun ya shafa yana faɗin
"Ash Ahmad sallamar taka kenan?."
karaso wa in da suke nayi ina dariya nace
"Oh Ahmad haka aka ce maka suka yi ne." yaɗa ga shi sama ya na juyi da shi sai washe baki yake, daga bisani ya dire shi kasa.
yayi ta biye wa yaran suna ta wasa sai da nace masa, ya tafi ko ya mance a na jiran sa.
nan ma har ya kai kofa yakuma juyowa, ya kira yaran tare da buɗe hannayen sa suka zo da gudu ya haɗa su duka ya rungume su.
ido na ɗan kura musu yayin da fargaba mai haɗe da faɗuwar gaban nan ke daɗa taso min.
maganar sa naji yasani saurin mai da hawayen da naji suna kokarin zubo min.
"Zo mana kyakkyawa ta." yafaɗa yana min alamar nazo kusa da shi, jiki a sanyaye na taka zuwa in da suke, sai ya janyo ni duk ya haɗa ya rungume mu, a tare muka sauke ajiyar zuciya ni da shi.
duk kanin mu shiru mukayi muna cikin jikin sa, yayin da zuciya ta ke wani irin bugawa.
jin yanayin nason firgita ni sai na ɗan mosa, a hankali ya sake mu yana binmu da murmushi.
da sauri na maso jikin sa na ruko hannunsa na kankame shi gam, murya na rawa tuni hawaye yafara zubo min nace
"My tsoro nake ji." Naseem da Nasmah ya kalla yace
"Kuje kasa kujira ni gani zuwa yanzu."
suka amsa da sauri suka nufi parkour'n kasa, da sauri ya janyo ni ya rungume ni tare da haɗe bakin mu, da karfe na daɗa rungume shi ina daɗa cusa baki na cikin nashi. yayin da nake jin

numfashi na ke yin sama-sama, da sauri na janye bakina sai kawai na saki kuka ina jujjuya kaina.
da sauri ya rirrike ni cikin muryar dariya yake faɗin
"Ke lafiyar ki kyakkyawa ta meye kuma na kukan kuka baya baki wuya ke, to ya isa faɗa min me ya saki kukan."
baki na turo ina jan shesshe ka.
"Mene ne me ya same ki?."
kai na girgiza dan nima ban san dalilin kukan nawa ba.
hawayen yashiga share min yana faɗin
"To bana son wannan kukan ko nan gaba dan Allah kiyi min alkawarin zaki daure, addu'a yafi komai tasiri a kan koma me, aduk san da kika ji tsoro ko fargaba ko faɗuwar gaba ko wannan kukan kiyi kokarin danne su ta hanyar faɗin
Innalillahi'wa'inna'ilaihirraji'un,
wannan kalmar yana samar wa zuciya nutsuwa,shagwaɓaɓɓiya ta."
ya karashe maganar cikin sigar zolaya tare da jan kumatu na.
yaci gaba da faɗin
"Ni bari naje kar su gaji da jira na, kiyi min shiri mai kyau anjima, yau ina sa ran da zaran na jefa kwallo na ya isa raga, Ahmad nason kani ko kanwa."
yayi maganar yana kashe min ido,
baki na kuma turo wa cikin muryar shagwaɓa nace
"Ka mance gun Aunty Rasheedat kake."
kai ya dafe yace "Oh wlh gaba ɗaya na mance amma dai zan dawo kafin dare ayi min shiri kawai."
haka yayi ta jana da wasa da kuma salon zolayar sa mai sani nishaɗi har sai da yaga na ware har da dariya ta kafin ya sake ni, ya juya zai fita Ahmad karami dake wasa gefen mu ya saki wani irin kuka, yana mika masa hannu.
da sauri ya dawo ya ɗauke sa yashi rarrashin sa, sai da yayi shiru kafin ya mika min shi yana faɗin
"Je ka gurin Mommy kada ka sake kuka, kada ki barshi ya sake yin kuka ki tsaya masa ya kasan ce cikin farin ciki, mu je ayi min rakiya ko."
na bi bayan sa muka sauka kasa, nan muka tadda su Naseem duk mukayi waje tare.
ko da muka isa parking lot ya karɓi Ahmad karami yayi ta masa wasa yana kyalkyale dariya su Nasmah ma haka, sai da ya gama yiwa yaran wasa kana ya mika min Ahmad yace bari yaje ya sanar wa Bappa Yakamata ya sami labarin da wuri.
muna tsaye a parking space yaje ya dawo,yake sanar min Bappa ya taya sa murnar fitowar makudan kuɗa ɗen sa.
yashige mota muna ɗaga wa juna hannu har ya fita,
numfashi mai karfi na sauke san da motar sa ta ɓace wa gani na, jiki a sanyaye na juya muka koma ciki....

Da misalin karfi 6 da yanma,

har zuwa wannan lokacin ina dai nan ne amma gaba ɗaya yanayin baya min daɗi,
kiran Ahmad ne ya shigo waya ta da sauri na ɗaga tare da yin sallama.
ya amsa yana faɗin "Kyakkyawa ta mun gama komai na karɓo kuɗin gasu a mota, sai dai banki yanzu sun tashi zan kai su gida gobe zan sa a kaisu banki."
"Masha Allah mun gode wa Allah, amma  My kai kaɗai kake tafi babu security?."
yace "Tare da su muke, ina zuwa."
ya faɗa tare da ɗan yin shiru,
jin abun da yake faɗawa security yasani faɗin,
"My mene ne?." yace "Wasu mota ne guda biyu suke bayan mu tun ɗazu na lura kamar biyo mu suke, ina son sanin ko su waye ne."
jin yana kokarin kashe wayar da sauri nace
"My kada ka ci gaba da tafiya da su ku canza hanya ni dai hankali na bai kwanta ba kaji dan Allah."
yace "To yan da kika ce haka za'ayi kyakkyawa ta."
ina tsaye cikin ɗaki rike da waya sai kaiwa da komo wa nake da kyar na samu na iya zama, tafiya da kuɗi masu yawa a mota irin haka a kwai hatsari sai dai saukin ma ɗaya yana tare da jami'an tsaro.
da sauri na ɗaga waya shigo war kiran sa yace
"Kyakkyawa ta na iso gida ta hanyar canza hanya kamar yadda kika faɗa."
numfashi mai karfi na sauke nace "Kai alhmdllh amma wlh duk a tsorace nake har naji hankali na ya kwanta."
yace "To je kiyi salla kiyi mana addu'ar dace wa da rahamar Allah nima masallaci zan tafi yanzu."
nace to...

Da misalin ƙarfe goma na dare ina kwance sakiyar yara na yayin da waya ke kare a kunnena kamar kullum, a duk san da Ahmad baya gida na to muna tare da shi a waya, ko yanzu hira da shi muke ta waya.
hamma nayi haɗe da mika tare da yin salati nace "My bacci." yace "To sai da safe kiyi baccin ki mai daɗi."
murmushi mai sauti nayi nace "Kai ma haka."
na kashe wayar,na bi yaran da addu'a nima na shafa na gyara kwanciya ta, wani irin faɗuwar gaba naji da sauri na dafe kirji na, a hankali na fara nanata kalmar Innalillahiwa'inna'ilaihirraji'un³.
gaba ɗaya bacci ya kairace a idona ina dai kwance shiru.
can wajen karfe 2 na dare har lokacin ina kwance idanuna kuma biyu,
da sauri na janyo waya ta dake tsuwa karkashin pillow, ganin mai kiran nawa yasa ni saurin mike wa zaune na kai wayan kunne na tare da faɗin
"My." yace "Baki bacci ba kyakkyawa ta?." nace "Na kasa nakasa yi My."
numfashi ya ɗan sauke tare da faɗin "Ko na zo ne." kai na girgiza da sauri nace "A'a dare yayi sosai."
yace "To ki tashi kije kiyi al'wala kiyi nafila ko da raka'a biyu ne kiyi addu'a zakiyi Baccin."
nace to. yace "Ina su Naseem?."

"Ga sunan suna bacci."
"Shafa min kansu duka ki sakawa Ahmad wayar a kunne."
nace "Yana bacci ai." yace "Eh sa masa."
a hankali nayi yanda yace na saka masa wayar a kunnen sa, magana ya soma yi a hankali yace
"Ahmad Ahmad Tijjani Sabil, kada ka bari wannan sunan ya mutu, kada ka sake duniya ta mance da wannan sunan duniya ta cigaba da faɗar waɗan nan sunayen, kamar yadda nayi tsayuwar daka domin ci gaba da ɗaukaka sunan Tijjani Sabil da har yau duniya basu mance da shi ba,suna kuma yi masa addu'a a koda yaushe,
Allah ya dauwamar da albarka cikin rayuwar ka kai da ƴan uwan ka."
da sauri na ɗago wayar a kunnen sa ganin yana motsi, nace
"My me kuma ya kawo wannan maganar a daren nan?."
murmushi mai sauti yayi yace
"Kiyi hakuri kyakkyawa ta."
nace "Na me fa?." yace "Ba komai rayuwar ce dai dole sai da hakuri, Ahmad yana son ki da kaunar ki."
numfashi na sauke zuwa yanzu maganganun sa na tun waye war garin yau da kuma yanzu sun fara da mi na, suna son su haɗe su cunkushe da yanayin fargaba da faɗuwar gaban da na ke ji.
nace "My nima ina son ka da kaunar ka."
yace "Nagode kyakkyawa ta, kin san me?."
nace "Sai ka faɗa." yace "Ɗazu ban zo da kuɗin nan gida ba a hanya na kira manajan banki yazo sai mukayi canjen mota na bashi nawa wan da kuɗin yake ciki na karɓi nashi, shi ya tafi da nawa gidan sa gobe zai shige da shi banki."
nace "Ai ma hakan yafi gara da ka bashi kaga idan zai tafi ban kin sai ya tafi da shi yafi sauki ma."
jin ya ɗanyi shiru baiyi magana ba nace
"My kai ma bacci kake ji ka kwanta sai da safe."
yace "A'a naji karan buɗe get ne."
nace "A cikin daren nan?." "Ai nima shine na gani bari naje na ga ko waye mai gadi ke buɗe wa get da daren nan ina zuwa."
ya kashe wayar tare da duban qRasheedat dake kwance a gefen sa, ya mike ya sauko a gadon ya fito.
a hankali yake tafi ya har ya fito, ga mamakin sa sai yaga an kakkashe wutan gefe da gefen gidan har zuwa lungunar dake cikin gidan duk wutan a karkashe, iya wutan dake can bakin get da kuma na hanyar shiga side ɗin sa da na Rasheedat ne kawai a kunne.
can ya hangi security kwakkwance a gurin zaman su duk suna bacci ko wannen su ya yada bindigan shi gefe suna ta sharar bacci.
gefe can kuma karnukan gadi ne suna zazzaune sai fidda harshe da ciccire ido suke.
motsi yaji a ta gefen sa in da babu hasken wuta a gurin, a hankali ya mai da duban sa gurin ya kurawa gurin ido sosai, inuwar mutum ya hango tsaye a gurin. da sauri ya waiga ɗaya gefen sa nan ma yakuma hango inuwar mutum, a hankali yayi baya yarika tafiya da baya da baya cikin hanzari ya koma ciki, da sauri ya shige bedroom ɗin sa,
ya isa jikin gado ya saka hannu sa kasan gado yaja sai ga drower ya bayyana yaciro bindiga

ciki ya mai da drower ya ɗago yana gyara rukon bindigan a hannunsa.
Rasheedat ce tayi juyi tare da ware idanun ta a kansa, da sauri ta mike zaune tana faɗin
"Aboki lafiya?." yace
"Ɓarayi sun shigo gidan nan." ido ta waro da sauri ta duro a gadon tana faɗin
"Ina security suke har ɓarayi suka sami damar shigowa gidan nan?."
yace "Akwai matsala suna nan abin mamaki duk kanin su bacci suke."
ya juya da sauri yana kokarin fita tasha gaban sa da sauri tace
"Aboki ina kuma zaka je?, a'a kada ka fita, kayi waya wasu jami'an suzo, kasan da abin da suka zo,
hakika da abin da suka taka tun da har kaga suka iya samin karfin guiwar shigo wa gidan nan duk tulin tsaron da ke gidan nan."
yace "Nasan abun da ya kawo su kuɗin nan ne kuma baya gidan nan ma zan je naji da su."
ya juya da sauri.
da gudu ta bi bayan sa ta rungume shi ta baya tana faɗin
"Aboki kada ka fita ka tsaya na buɗe maka kofar baya ka fita ta can dan Allah kada kaje."
juyo wa yayi ya rungume ta yace
"Kawa ki zauna duk abunda zakiji kada ki fito, kiyi min addu'a kinji."
kai ta shiga girgiza wa tare da sakin kuka tana faɗin
"Aboki kada ka je na roke ka ka fita ta kofar baya."
jikin sa ya zare daga nata, lokacin da aka fara harbi cikin gidan, ya tallafo fuskarta yace
"Kiyi min alkawarin ba zaki fito ba duk abun da kika ji, kizauna cikin ɗakin nan ki kulle kanki bazan taɓa barin su sushigo ciki ba zan kare ki da yardar Allah,sannan kuma bulet bazai iya ɓula ginin gidan nan ba ko da ace sun yi yunkurin yin harbi cikin nan, kada ki fita kizauna a nan."
harbi aka cigaba dayi cikin gidan ta ko ta ina, Rasheedat ta daɗa kankame shi tana faɗin kada ya fita.
da sauri ya sake ta ya fita.
ita ko kuka ta kuma sake wa ta durkushe a gurin, sai kuma ta mike da sauri ta isa ta kulle kofar, ta koma bakin gado tana cigaba da kukan..

A hankali cikin sanɗa Ahmad ya fito
yayin da ya gyara rukon bindigan sa da kyau.
harbin yashiga mai da musu daga inda yake laɓe suka rika musanyar wuta sakanin sa da ɓarayin.
kara ɗaya daga cikin ɓarayin yayi lokacin da harbin Ahmad ya same shi, ya zube a gurin,
kaimi ɓarayin suka kara akan harbin da suke, cike da tafasar zuciya cikin hanzari Ahmad yafito daga in da yake laɓe, yana fita daga gurin kuwa wani yayi saitin sa ya sake masa harbi a gefen kirji.
dafe gurin yayi cikin jin azaba da raɗaɗin shigan bulet jikin sa,
cikin tsananin tafasar zuciya da kunar rai yayi gaba da gaba da su in da yakuma samin nasarar harbin mutum biyu a kafa,
cike da tsananin mamaki ya tsaida harbin da yake ganin amintaccen mai  gadin sa, yana nuna shi wa wasu ɓarayi huɗu da suke tsaye da hannu,suka juyo tare da saita shi da bindiga.

kafin ya dawo da ga mamaki mai haɗe da tunanin daya tafi, sai ji kake tau-tau saukan harbi a cikin sa har sau biyu, kara yayi tare da damke cikin sa da jini ke tsiyaya, yayi tangal-tangal kafin ya isa kasa ya harbe su gaba ɗayan su su huɗun nan har da mai gadi cikon na biyar, a tare suka zube kasa mutattu.
yana kwance a kasa yana sakin wani irin numfashin wahala wan da yafi kama da na fitar rai...

Ina zaune a kan sallaya bayan na idar da nafila kamar yadda Ahmad yace min nayi zan sami bacci,
gaba ɗaya ilahirin jiki na babu karfi tamkar an zare min laka.
na janyo wayata lokacin karfi biyu da rabi,
na danna number Ahmad tare da kara wayar a kunne na, yayi ta ringing har ya yanke bai ɗaga ba, kuma mai da kiran nayi shima har na cire rai da ɗaukar nasa dan nafara tunanin bacci yayi.
wani irin razana da zabura nayi jin muryar sa yana faɗin
"Kyakkyawa ta sun harbe ni sun harbe ni......!

Mommyn Twins

36

A kiɗime na mike tsaye ina faɗin
"My me ya same ka suwaye suka harbe ka My me ya same ka My kayi magana dan Allah!!!."
numfashi yaja da kyar cikin sarkewar murya yace "Nasan bazan rayu ba sun illatani da yawa, kiyi hakuri kyakkyawa amma ki sani da son ki zan mutu ina son ki ina son ki."
ya karasa maganar da jan wani irin. numfashi hade da yin salati.
kuka sosai na fashe da shi ina faɗin
"My kar kayi min haka dan Allah kada ka tafi ka barni dan Allah, ka jira ni zan zo yanzu babu abun da zai same ka zan zo yanzu gani zuwa My kana jina ka jira ni kaji, babu abun da zai same ka."
cikin yanayin jin azaba da fitar numfashi yace
"HAMDAH kada ki zo kinji kyakkyawa ta akwai wan da basu mutu ba a cikin su bazan juri ganin sun nimi illatar da ke ba, na rokeki kibarni natafi cikin salama bada kunar ran abun da zasu yi miki ba, kada ki bari Ahmad yayi kukan maraici."

maganar tasa ce ta sarke yayin da yaja wani irin numfashi mai haɗe da ajiyar zuciya kana salati yabiyo baya.
"Myyyyyy!!!."
na kira shi da karfi jin alamar faɗuwar wayan kasa,
nakuma sakin wani irin kuka mai tsuma rai.
da gudu nayi waje a kiɗime ina kuka da kiran sunan sa ina faɗin kada ka tafi ka barni.
a haka nafito sakar gida yanayin dare shiru babu motsin kowa, sai hasken daya haske ko ina na gidan.
masu gadi suna can bakin get,
kuka mai karfi na sake san da na kuma kiran wayan sa a karo na uku ba'a ɗagawa, direba nashiga kwallawa kira cikin muryar kuka mai haɗe da tsantsar tashin hankali, da iya karfi na nake kiran direba.
da gudu su security da direba suka iso in da nake a tare suna tambayar ko lafiya akwai wata matsala ce.
ban iya basu amsa ba sai cewa direba nayi
"Bani makullin mota." direba yace
"Ina kuma zuwa hajiya da daddaren nan yanzu fa karfe uku saura shin lafiya?."
cikin muryar kuka da karfi nace
"Ka bani makullin mota nace."
jin hayaniya yasa su Bappa fitowa daga sashin su Mama mai awara ma haka ta fito daga ɗayan side ɗin dasu Talatu, da sauri suka karaso in da muke hankali tashe Bappa da Inna Wuro da Mama suka haɗe baki wajen cewa
"Lafiya me ke faruwa?."
ganin yan da na birkice gaba ɗaya Bappa ya ruko hannuna yana faɗin
"HAMDAH ki nutsu mene ne a cikin sashin naki ina yaran suke?."
cikin jan shassheka nace
"Bappa Ahmad Ahmad zasu kashe shi."
cikin matukar shiga firgici Bappa yace
"Su waye zasu kashe shi ina Ahmad ɗin yake kin baro shi a ɗaki ne?."
a zaton sa Ahmad karami ne.
nace "Yana gidan sa Bappa sun harbe shi."
kuka ne yaci karfi na nashi kokarin kwace hannuna Bappa yarike ni gamgam yana faɗin
"Innalillahi wa'inna'ilaihirraji'un
ki nutsu HAMDAH ki tsaya tukun ba zai yiwu kifita a daren nan ba, ki bari hukuma suje dan zuwan naki akwai hatsari."
Bappa ya dubi security yana faɗin
"Kuje gidan ku kai masa ɗauki."
da sauri suka juya cikin zafin nama cikin hanzari suka shige motocin su suka nufi gidan Ahmad.
Bappa ya dube ni ganin yan da nake rusar kuka yace
"Jami'an sa ne dama shi ya ajesu a gidan nan batare da saninki ba zasu je su kula dashi,
babu komai in sha Allah babu abun da zai faru, ki kwantar da hankalin ki yanzu zasu je suzo miki da shi."
da kyar suka lallaɓa ni na yarda muka koma ciki...

Acan cikin gidan Ahmad
tuni wani makocin sa yayi waya wa jami'an tsaro dan gaba ɗaya unguwar ta ɗauka, sai dai babu wan da yayi yunkurin fita dan jin yan da karan bindiga ke tashi, sai dai kowa yana tsaye a kan kafafun sa a cikin gidan sa.
kan kace me sojoji sun iso unguwar suka zagaye gidan, koda security suka iso sun tadda sojoji a gurin, nan suka haɗe da sojojin.
wasu daga cikin jami'an tsaron suka shiga cikin gidan.

Rasheedat na ɗaki tana ta rusar kuka, jin harbin bindigan ya tsaya ba'a kuma yi ba daga bisa ni tajiyo jiniyar sosoji, sai ta buɗe kanta tafito hankali.
wani irin kaɗuwa tayi
ganin Ahmad kwance cikin jini, tayi kansa tana ihu da kiran sunan sa,
tana faɗin "Aboki sai da nace maka kar ka fito ka fita ta kofar baya wayyo Allah na karkayi min haka Aboki."
polisawan da suka iso yanzu suma motar su guda su suka dakar da ita batare da sun barta ta taɓa shi ba,
sabo da yanayin ai kin su da kuma gudanar da aikin su da suke a lokacin.
ta zube a gurin tana rusar kuka mai ban tausayi.
abun mamaki duk hayaniyar da ake ɗinan security suna ta sharar bacci karnukan gadi kuma suna zaune in da suke tun ɗazu basu ko mosa ba bare suyi haushi.
motar ambulance da ta iso yanzu cikin hanzari polisawa suka ɗauki Ahmad suka saka shi cikin motar,
in da wasu daga cikin police ɗin duka shige cikin motar
da mugun gudu motar ta fice a gidan.
sauran gawawwakin ɓarayin dake kwance har da mai gadi suma a ka zuba su cikin wata mota aka tafi da su,
ɓarayi biyu kuma da suke da rai wan da Ahmad ya harbe su a kafafun su a ka zubasu cikin wata mota suma a ka tafi da su...
kan kace me a cikin daren unguwar gaba ɗaya ta gama hargitsewa hankalin kowa ya tashi da jin abun da yafaru, matasa suka fito kowa da makamai nan karamar zanga-zanga ya kaure, sai da hukuma sukayi da gaske.
a take a lokacin labari ya iske mahaifan Rasheedat hankali tashe suka iso gidan a cikin daren, Alhaji Bashir mahaifi ga Rasheedat kani kuma wa Alhaji Tijjani Sabil,Bappan Ahmad kenan, hankalin sa yayi mummunar tashi a take yabi bayan motar da aka tafi da Ahmad, in da mahaifiyar Rasheedat kuma ke tare da ita agidan....
sai da aka kira sallar asuba kafin security suka farka duk tulin bubbuga su da sojojin da suka zo sukayi domin su  farka baisa sun farka ba sai a lokacin,
karnuka ma suka kama haushi da tsalle kamar zasuci babu.
hankalin security'n yayi masifar tashi da jin abun da ya faru wan da suna cikin gidan basu kuma san da faruwar hakan ba.

koda ƴan jaridu suka nimi jin ta bakin su sun shaida musu cewa
su sam basusan da faruwan komai ba sun dai sinci kansu cikin yin bacci mai nauyi, bayan da mai gadin gidan ya rabamusu lemun gora a daren ranar yakuma shaidar musu da cewa ogan su ne ya bashi ya basu wato Ahmad ɗin kenan,
shan su kuma bada jimawa ba bacci mai nauyi ya ɗauke su, wan da basu farka ba kuma sai yanzu.
ɗaya daga cikin security ya bada tabbacin cewa
shi bai sha lemun da wuri ba ya aje nashi sai daga baya yasha, lokacin da bacci ya fara fizgarsa bai kai ga ɗaukar sa ba ya yaga mai gadin yaje in da karnuka suke yana fesa musu wani abu, sai dai baccin da ya zo mishi babu zato ya hanashi tashi ya bincike mai gadin kan abun da yake yiwa karnukan...
har gari yayi haske sosai sojoji na zagaye da gidan, tuni gidajen TV dana rediyo suka fara sakin labarai kan rahoton da suka samu.....

A parlour mukayi salla dukan mu har da su Bappa, dan Bappa yaki matsawa ko nan da can daga in da nake.
ganin gari yayi haske kuma har zuwa lokacin security basu zo da Ahmad kamar yadda Bappa ya faɗa ba.
gashi duk kiran wayar sa da nake baya ɗagawa,
na saka musu kuka nace ni sam zan tafi zanje da kaina gidan.
wayar Bappa ce tayi kara, ya ɗaga tare da yin sallama.
"Innalillahi wa'inna'ilaihirraji'un."
abun da Bappa ya furta kenan, zumbur na mike tsaye ina kallon Bappa, Bappa ya kawar da kansa tare da sauke wayar a kunnen sa, yayin da laɓɓan sa ke motsawa alamun salati yake.
ɓari jikina ya soma murya na rawa nace
"Bappa mene ne wa yayi maka waya?."
kai ya girgiza yayin da idanunsa suka kawo kwalla, sai ya kawar da kansa daga kallo na yace
"Babu komai je ji sa babban mayafi ki zo sai muje gidan Ahmad ɗin kawai tun da har yanzu basu zo ba."
ya dubi Inna Wuro yace
"Je ki rakata tasa mayafin."
sai ya sauya harshen sa izuwa fulatanci yayi mata magana cukin harshen fulatanci,
Inna Wuro ta saki salati tana dafe kirji, sai kuma tayi saurin sauke hannunta a kirjin sabo da maganar da Bappa ya kuma mata da fulatan ci, ta ruko hannuna yayin da hannunta ke ɓari ta janyo ni muka haura sama.
muna shiga muka tadda su Naseem duk sun farka, tace na cire hijabi da kayan baccin da ke jiki na na sa wani kayan.
jiki a sanyaye yayin da hawaye ke bin fuskata nayi kamar yanda tace, nasaka babban hijabi, kana ta ruko hannun su Nasmah ni kuma na ɗau Ahmad karami muka sauko kasa.
tun kan mu karaso parlour'n kasa su Mama suna ganin mu kowa ya shiga sun kuyar da kai suna share hawayen su cikin dabara sai kowa ya mike da sauri akayi waje gaba ɗaya.

da sauri na ɗaga murya nace
"Kukan me kuke yi?."
da sauri Bappa yace
"Kuka kuma sam ba wan da yayi kuka a cikin mu."
cikin rawar murya da kuka ke son kwace min nace
"Na ganku da idona na, ganku kuna kuka ku faɗa min kukan me kuke yi?."
Mama tayi murmushi wan da yafi kuka ciwo tace
"A ina kuma HAMDAH mu sam bamuyi kuka ba muje direba yana jiran mu."
ta ruko hannuna muka karasa fita waje...
koda muka iso parking lot Bappa yace su Zulai su zauna da su Naseem a gida.
a tsakiya suka sani Mama da Inna Wuro, Ahmad karami na rike a hannu na, Bappa kuma ya zauna a gefen mai zaman banza, direba yaja muka fita.
ina zaune shiru hawaye na zuba a idona na, ido na kurawa titi ganin mun ɗau wata hanyar daban ba hanyar gidan Ahmad ba.
a bakin wani katon asibiti direba yayi hon, aka buɗe masa ya sakai ciki ya faka motar muka fito, asibitin zagaye yake da sojoji da ƴan sanda, can na hango Abba Bashir yana sunkuye da alamar kuka yake, wasu mutane na tsaye a kansa. Inna Wuro ta karɓi Ahmad karami dake hannuna, Mama kuma ta ruko hannuna gam ta janyo ni muka nufi cikin asibitin.
da kyar nake iya ɗaga kafafu na da sukayi min mugun nauyi,
maganar Mama na jiyo tana faɗin
"Ba a ja da ikon Allah duk abun da kaga ya sami bawa da sanin ubangiji, Allah kuma baya barin wani dan wani yakan kuma jarabci mutum ta ko wace hanya domin ya gwada imanin sa,
yana da kyau mu kasan ce masu karɓar kaddara mai kyau ko mara kyau aduk san da tazo mana,
Allah yafi mu son bayin sa duk son da muke musu, hakuri kuma shine magani nasan ki da hakuri da iya karɓar kaddara ina fata yau ma ki kasan ce a haka, kice Innalillahi wa'inna'ilaihirraji'un kici gaba da nanata shi cikin ranki."
"Innalillahi wa'inna'ilaihirraji'un³."
nafaɗa da karfi har sau uku dai-dai lokacin da muke sakai cikin parlour'n asibitin, Mama ta daɗa rike hannuna gam jin yan da ilahirin jikina yaɗau ki ɓari tace
"A hankali zaki faɗa ko a cikin ranki ki nusu HAMDAH."
muna shiga jami'an tsaro suka dakatar da mu suka ce mu tsaya anan, wani soja ne ya fito daga cikin wani room yakaraso in da muke yace "Zata iya shiga yanzu."
Bappa ya dube ni cikin rauni yace
"Kullu nafsin za'ikatulmaut duk mai rai mamuci ni, muma bamu da tabbacin zamu iya kaiwa nan da dakika ɗaya, Allah yayi wa Ahmad rasuwa ki daure kiyi masa addu'a."
wani irin dimm haka naji kunnuwa na sunyi min mugun nauyi jiri haɗe da bakin duhuwa ya gilma min,
kallon bakin Bappa nake domin tabbatar da abun da yake faɗa dan ni dai a yanayin da nake jin kaina ciki da yan da maganar tazo min a sama sai ji da gani nake kamar ba gaskiya bane, bakina kuma yayi min mugun nauyi na kasa iya furta komai.
sojan yace
"Madam bismilla sai hakuri fa."

yayi maganar yana nuna min hanya Inna Wuro ta mika min Ahmad karami, kana sojan yayi gaba na bisa a baya ina jan kafata da kyar.
muna isa jikin kofar room ɗin ya murɗa handle ɗin ya shiga, kana yaɗan ja gefe ya bani hanya na sako kai na ciki.
kana ya mai da kofar ya rufe, sojoji ne tsaitsaye cikin room ɗin haɗe da likitoci,
ido na kurawa kan gadon da nake hango mutum kwance an lulluɓe shi daga sama har kasa, jikin a bun da aka lulluɓe sa da shi da ɗigo ɗigon jini tagurin kirjin sa da gefe da gefen cikin sa.
wani dake tsaye ta gurin kansa ga dukkan alama babbane dan da zaran yayi magana sai sauran jami'an tsaron su sara masa.
ya ɗaga hannu tare da yi min alama dana karaso, a hankali naja kafafu na zuwa bakin gadon, ya dube ni tare da faɗin
"Allah ya baki hakuri mun kira ki ne abisa cika masa burin sa na karshe, kiyi hakuri bamusan rai zaiyi halinsa ba tun a daren jiya yanemi da a kira ki sai dai ganin halin da yake ciki yasa muka kasa iya ai watar da hakan burin mu kawai likitoci su samu nasarar kuɓutar da shi daga halin da yake,ga wannan a hannunsa muka samu bayan cikawar sa, ko da muka duba sai muka ga a kanki yake maganar shine muka neme ki kafin mu ɗaga shi a nan mu damka miki sakon sa a hannun ki."
ya mika min takarda wan da gefe da gefen takar dan duk da ɗigon jini,
hannu na na ɓari na karɓi takardan na dunkule shi cikin hannuna.
mutumin ya dubi nakusa da shi yace
"Ku buɗe mata shi ta gansa." ya yaye abun da aka rufe shi da shi daga kansa zuwa wuyan sa.
da gaske Ahmad ne a kwance wan da tun ɗazu ban gaskata abun da suke faɗa min ba sai gani nake kamar ba gaskiya bane.
wani irin tsalle zuciya ta yayi tamkar zai faso kirji na yafito,yayin da ilahirin jiki na ya ɗauki ɓari.
a hankali nashiga jan kafata ina daɗa matsowa bakin gadon yayin da idanuna ke kan fuskarsa, yana kwance idanunsa a rufe yayin da fuskarsa ke bayyane da kayataccen  murmushin sa, tam kar akirasa ya amsa.
kai na shiga girgizawa nashiga kokarin motsa laɓɓa na, na mika hannu izuwa jikin sa, nashiga girgiza shi tare da sakin kuka mai taɓa zuciya cikin muryar kuka sosai tamkar numfashi na zai fita nashiga faɗin
"My bana son irin wannan wasan!, My kafarka dan Allah kadai da min irin wannan wasan,ka tashi mana nice fa gimbiyar ka kyakkyawar ka, ka tashi ka gani gani ga Ahmad ɗan ka ɗan da ka fara samu a duniya, shin ka mance alkawarin da ka min da bakin ka kace min bazaka taɓa bari nakara yin kuka ba, kar kayi min haka kar ka tafi ka barmu dan Allah My dan Allah ka tashi so kake Ahmad ya zamo maraya, ka buɗe idanun ka ka faɗa min kalmar da kake faɗa min kullum kana sona nima ina son ka My ina sonka ina sonka My, My ka tashiiiiiiii kar ka mutu dan Allahhhhhhhhh!!!."
kuka yaci karfi na sai kawai na kife kansa tare da ɗaura Ahmad karami a kansa na saka fuskata kan nashi nashiga goga fuskata cikin nashi ina wani irin kukan danake jin ina ma ace yanzu nima na mutu na bishi, Ahmad karami ya saki kuka yana cakumar sa...
mutumin da ya sa aka buɗe min shi ya girgiza kai tare da share kwalla, kana yace
"I'm so sorry Madam hakika muma munji ɗacin rasa gwarzon jami'in sirri kamar Ahmad, sai dai abun farin ciki duk da bulet har uku da suka same sa a gurare daban-daban wan da ko da ace

harbi ɗaya ne  bazai iya taɓuka komai ba, amma da bulet ɗin a jikin sa ya kashe mutane biyar yayi wa biyu mummunar raunin da bazasu iya morar raruwar su ba, hakika wannan abun alfahari ne, Allah ya baki hakuri."
sukace na tashi a ɗaga shi fir naki sai ma daɗa kankame shi da nayi.
da kyar babban sun ya iya janye ni a jikin sa,ina mike wa a jikin sa sai ji nayi tamkar an fisgo ni sai kawai na yanki jiki na zube a gurin nan take hankali na yabar jiki na ban kuma sanin abun da ake ciki ba....

After 5 hr.
Sai a lokacin na farka daga doguwar sumar dana tafi,
a hankali nashiga buɗe idananuna dasuka yi min mugun nauyi, maganar Ummi na najiyo a kusa da ni, da sauri na yunkura zan mike, Ummi tayi saurin rike ni tana faɗin
"Yi a hankali HAMDAH."
nace "Ummi ni tashi zanyi." Mamie dake zaune a gefe da waya a kunnen ta tana faɗin
"Mun  iso sai dai har yanzu bata farfaɗo ba."
sai kuma tayi saurin kashe wayar ta mike tazo ta rike ni tana faɗin "Zaki iya tashi?."
kai na gyaɗa, tace "To tashi." suka taimaka min na mike zaune,
kokarin durowa a gadon nake Ummi tace
"Da kata HAMDAH ina zaki ko fisari kike ji?."
kuka na fashe da shi nace
"Ni gun Ahmad zan je." hawaye Ummi ta share Mamie tace "Kiyi hakuri HAMDAH, ki tsaya ki daɗa samin sauki tukun."
kai na shiga girgiza wa ina faɗin "A'a ni gurin sa zanje ni dai zanje."
duk yan da suka kai da lallaɓi na fir naji nace nidai gurin sa zani, haka suka hakura suka kyale ni.
na sauko a gadon da gudu nafita a room ɗin, nashiga waige-waige room ɗin da aka kwantar da Ahmad na nufa a guje na tura kofar na shiga, turus nayi cikin ɗakin ganin babu kowa ciki. sai kuma na juya a guje tare da kuka sakin kuka nayi,
su Ummi da suka biyo baya na da suka ruko ni.
Mamie ta rike ni gam tana faɗin
"Ki nutsu HAMDAH." nace "Ni gida zan tafi an mai da Ahmad gida  nidai gida zanje."
Su Mama Inna Wuro Ummi Mamie duk kanin su hawaye suke cike da matukar tausaya min, Ahmad karami na goye a bayan Mama yana bacci sai sauke ajiyar zuciya yake.
Mamie tace "To muje gidan...
ko da muka iso gida direba na dai-dai ta parking na fito da gudu nayo cikin side ɗi na,tun daga parlour'n kasa nake faɗin
"My kana ina My kadawo gida ko."
har na haura sama ban fasa kiran sa ba, na shige bedroom ina ta waige-waige.
Ummi data biyo baya na da sauri ta ruko ni tana faɗin
"HAMDAH kidawo cikin hayyacin ki, ki nutsu kiji ni, Ahmad ya rasu mutuwa kuma ba karya bace, yanzu addu'a kaɗai yake bukata shi da ma yayi kyakkyawar tafiya ki nutsu ki sawa zuciyar ki salama ki fauwalawa Allah komai, hakika akwai ciwo amma ki daure, ki daure jin ƴata

ƴar albarka Allah ya baki ikon cin jarabawar ki."
"Ummi yanzu shima ya tafi kenan bazan sake ganin sa ba kenan Kamar Inna."
kwai Ummi ta shiga girgiza wa tana kwalla.
rungume Ummi nayi tare da sakin wani irin kuka, bata hanani yin kukan ba sai bubbuga bayana da take itama tana kwalla.
su Mama suka janye ni a jikin ta suka zaunar dani bakin gado na zube a gadon ina mai ci gaba da rusar kukan..

Basu hanani kukan ba sai da nayi sosai kafin suka fara rarrashi na, da ban baki har nayi shiru,sukayi ta bani baki haɗe da nasihohi nidai ina nan zaune amma hankali na baya gurin, nan Ummi suke shaida min tare suka zo da su Abbu suna gidan Ahmad can in da ake zaman makoki...

Bayan kwana uku..........!

Mommyn Twin ce

37

Haka zan rungume Ahmad karami nata kuka cike da tausayin sa da kuma tausayin kaina,sai Mamie ko Ummi sun karɓe sa, tun ranar da Ahmad ya rasu Ahmad karami yaki shan nono, Ummi tace a ɗaga shi kawai a nonon tun da ya makai na yaye...
A ko da yaushe su Ummi suna tare da ni basa taɓa barina na zauna ni kaɗai,yau su Aunty Rafee'ta suka zo ita da Aunty Jaleela da Ya Masa'ud da Goggo Hauwa,
da yamma suka ɗunguma suka je gidan Ahmad domin yi wa ƴan uwan sa da Aunty Rasheedat ta'aziyya har da su Mamie.
kamar yadda suma ƴan uwan nasa suke zuwa har dama ƴan uwan Aunty Rasheedat domin yimin ta'aziyya.
Abba Bashir da mahaifiyar Aunty Rasheedat su tun ranar rasuwar ma suka zo nan..

tare da su Abbu su Ummi suka dawo dan yau an gama zaman makoki...
ranar bakwai da safe Alhaji Bashir da mahaifiyar Aunty Rasheedat da ita Aunty Rasheedat ɗin da wasu daga cijin dangin su, da shaidu da kuma laiyoyi, da manyan malamai suka zo.
duk kanin mu muka hallara a parlour'n kasa.
Aunty Rasheedat na rungume da Ahmad karami a jikin ta, ta kura masa ido sai kawai ta fashe da kuka, ni ma kukan na fashe da shi dan nasan abun da nake ji a raina itama shi take ji.
rarrashin mu akatayi tare da yi mana nasiha har sai da zuciyoyin mu suka sami salama, kana a ka soma gudanar da abin da ya taramu wato rabon gado.
duk kanin dukiyar Ahmad da kaddarorin sa na nan gida Nigeria da kuma na kasashen waje da wan da aka kashe shi domin sa wan da ya damkawa manajan banki, duk aka haɗo kansu.
batare da ɓata lokaci ba malamai suka fara gudanar da rabon gado kamar yadda shariya ya shar'anta, duk kannnin mu uku a ka dan kawa kowa abin da ya gada ni Aunty Rasheedat da kuma Ahmad karami, nayi mamakin tulin dukiya da kandarorin da Ahmad karami ya gada, daga mahaifinsa nakuma yi mamakin tulin taren dukiya irin na Ahmad.

Washegari su Abba Abbu Mamie Aunty Rafee'at Aunty Jaleela Ya Masa'ud suka koma Bauchi, yarage saura Ummi na,
Ummi tana iya bakin kokarin ta wajen ganin ta gusar min da damuwa ta dan ko nan da can bata matsawa koda yaushe tana tare da ni.
yanzu Mama ma ta dawo side ɗina ita ma muna tare..
lokacin da mukayi arba'in Ummi tace zata koma gida,
washegari bayan ta gama shiri ta je sashin su Bappa bayan sun gaisa take sanar masa yau insha Allah zata koma sannan ta ɗaura da faɗin
"Bappa ina so na tafi da HAMDAH tadanje tayi kwana biyu."
Bappa yace
"Kwarai kuwa kinyi tunani me kyau tafiya da ita ɗin shiyafi saboda acan zata zauna cikin yan'uwanta da iyayenta tunaninta zai ragu akan zamanta anan ɗin, Allah yatsare yakiyaye hanya."
Ummi ta amsa da Amin...
ina zaune dasu Naseem da Nasmah suna gefena sai rikici suke min kamar kullum Naseem daya ware baki zaiyi kuka yace "
Mommy ina Daddy kince zai dawo."
 kwalla nashare nace "Naseem nace muku daddy zai dawo daddy yayi tafiya zai dawo."
Nasmah tace "Mommy nikam kikaini gun Daddy kinji Mommy."
kaina girgiza yayin da hawaye yake zuba a idona inajin yadda yaran suke bori Naseem yasaya yana fadin nikam ki kiramin Daddy, yami kamin wayata, yana ci gaba da faɗin na kira masa Daddy.
 kuka nafashe dashi na rungume yaran ajikina ina mai matuqar missing na Ahmad.
 Ummi ce tashigo ganin ina kuka tayi saurin isowa tana faɗin
"HAMDAH lafiya?." kaina girgiza ina fadin "Ummi Ahmad yatafi bazan iya qiranshi a waya ba Ahmad yatafi kenan bazai dawo ba, bazan sake ganin sa ba, suma so suke su gansa."
 kuka sosai nafashe dashi Ummi ta rungume ni tana rarrashi na, kana tace na tashi nahaɗa kayana zamu tafi Bauchi tare, baza ta iya tafiya ta barni cikin halin da nake cikin nan ba.

babu musu namiqe danni ma nasan  tafiyar zai fi min bazan iya jure Ummi tatafi tabarni Anan ba.
ita ta tai makamin  mukashirya kayanmu tasa su Talatu suka fita dasu,
gabadaya yan gidan suka rako mu parking lot,
nace Mama ta komo part ɗina tun da ba kowa ciki kafin mu dawo,
suna tsaye har
muka shiga mota, muna ɗagawa juna hannu muka fice a gidan.
muka dauki Hanyar Bauchi...
koda muka iso Bauchi naji daɗin ganina acikin yan'uwana domin kota'ina najuya sune basu kaunar ganin wata damuwa tattare da ni,
kowa yana iya bakin kokarin sa wajen ganin farin ciki ya samu gare ni.
Su  Aunty Rafee'at da Aunty Jaleela kusan kullum sai sun zo gida sai dare su koma, Ya Mas'ud baya motsawa konan da can kullum muna tare idan ya dawo daga gurin ai kin sa, haka zai zauna muta hira.
yan'uwana suna matuqar qoqari wajen ganin sun sani farin ciki sun kuma ɗebe min kewa...
A hankali na fara sake wa, da muwar dake dankare cikin raina yana ta washe wa, yanzu kam alhmdllh na sake hankali na kuma nata kan daɗa kwanciya..

Zaune muke a parlour'n Mamie Aunty Rafee'at tafito daga kitchen rike da flaks da ɗan madaidaicin tray mai ɗauke da cup spoon da sugar,  ta karaso cikin parluor'n,
duba na tayi tana faɗin "Bari na kai masa na dawo."
nace "Wa zaki kai masan Abbu ne?." tace
"Ya SALEEM." kai na jinjina tare da faɗin "Anan kuma yanzu yake shan shayin sa yabaro gidan sa yazo nan ina matar tasa take?."
baki Aunty Rafee'at ta taɓe tace "Ƴar wahala tana can asibiti kwance ita bata mutu ba batayi rai ba, tana kan karɓar hukuncin ta."
Ya Masa'ud yayi dariya da faɗin
"Ai yanzu Ya SALEEM gwauro ne tuni ya kaɗa matar tasa, yana gidan nan bashi da lafiya."
shiru nayi ina jinjina lamarin a raina.
Aunty Rafee'at ta fita domin kai masa shayin ta dawo muka ci gaba da hirar mu na tuna baya ana ta dariya, da tuna yaranta ta da da nayi ta yin sa,
cikin muryar dariya Ya Masa'ud yace
"Ƴar gidan Inna iyaye shirme."
baki na washe nace
"Allah Ya Masa'ud da ne nifa yanzu na girma."
yace "Ah sosai ma kuwa dube ki fa kinfi na hannun dama nan nan girma yanzu."
yayi maganar yana kallon Aunty Jaleela da ke gefen sa ta gefen ido.
hararar sa tayi tana faɗin
"Zamu sami matsala da kai Masa'ud ban son raini."
nace "Ya Masa'ud baka sani ba jiya Uncle Habu da ya zo yace wai dama nice gaba da Aunty Jaleela ko."
dariya duk muka yi cikin muryar dariya Aunty Rafee'at tace

"Kai Masa'ud ka kiyayi kanka da haɗa rigima, ke kuma HAMDAH a ina Uncle Habun ya faɗi haka?."
dariya nayi nace "Ai ita tasan lokacin."
fuska Aunty Jaleela ta haɗe tana hararar mu tare da faɗin
"Ni ba sa'ar ki bace daga ke har Masa'ud ɗin."
"To gyanbo duk kin girme mu kice har da Aunty Rafee'at ɗin ma ke har da ma Ya SALEEM, wlh yanzu yasa na kai masa bulalar zane ki, ni kuma nace ya huta tun da bashi da lafiya yana zaune na tsumage ki."
kafaɗar sa Aunty Rafee'at ta buga tace
"Tashi ka bar nan tafi damuwar ka."
ya mike yana dariya yafita. Aunty Jaleela ta ɗaga murya tana faɗin
"Yan zu ma zaka iya ɗauko bulalar."

Bayan sallar Isha mazajen su Aunty Rafee'at suka zo ɗau kar su, har gurin mota na rako su, Ya SALEEM na hango zaune kan kujera
Dr Farooq na zaune kusa da shi,
tun da nazo gidan sai yau na saka shi a ido na, ban ma san yana gidan ba sai ɗazu da su Aunty Rafee'at suke faɗa,
kai na na kawar daga kallon sa na mai da hankali na kan su Aunty Rafee'at.
Dr Farooq yaɗan ɓata lokaci a gurin sa ga dukkan alamu duba shi yake game da rashin lafiyar sa da aka faɗa, dan har su Aunty Jaleela suka tafi yana gurin sa, sai can ya mike ya taho in da muke suka shige mota ina yi musu sai da safe,
Dr Farooq yace
"Ƴar gidan Inna yaushe zaki zo mana?."
nace "Kuna zaune zaku ganni."
dariya yayi da faɗin
"Babu rana kenan ko da shike manya fitar su na da wuya sai dai a zo musu basu suzo ba."
"Akwai rana kai idan tazo shine zaku gannin ai."
yace to Allah yasa...
ina tsaye har suka fita.
a hankali na juyo zan ko ma ciki, Ya Masa'ud ya fito rike da Hannun su Nasmah, suna ta zuba masa surutu, in da Ya SALEEM yake suka isa, murmushi mai sanyi ya sake ganin yaran ya miko hannu yana kokarin ruko hannun su, murya na ɗaga nace
"Naseem Nasmah kuzo nan muje ku kwanta."
cak ya tsaida hannunsa kana ya ɗago a hankali ya kalli in da nake,
da hannu na kuma yi musu alama da su taho ina ci gaba da faɗin
"Ku wuce muje ku kwanta nace."
suka juyo suka taho in da nake na ruko hannun su muka wuce sashin Ummi...

Washegari da safe duk muna side ɗin Mamie Ya Masa'ud ne kawai baya nan yatafi gurin aiki.
waya ta dake gefe na su Naseem suka ɗauka wai sam sai na cire musu a key sun yi game, sai

da na cire musu kafin suka dai na fitina ta.
can anjima sai ganin su nayi sun shigo daga waje,
nace "Ku ina waya ta?."
Nasmah tace " Na guyin Uncle." nace "Wani Uncle ɗin?." tace
"Uncle ɗayan." "Wani Uncle ɗayan yaushe Ya Masa'ud ɗin ya dawo daga gurin aiki."
Naseem yace
"Ba yace shi Daddy ne ba Uncle ba."
yayi maganar yana rike haɓa da ware idanu.
Nasmah ta gyaɗa kai tare da faɗin
"Eh yana guyin Daddy."
da sauri cikin ɗaga murya nace "Ku rufa min baki shi ba Daddyn ku bane Daddy'n ku ya rasu."
cikin tsawa Ummi tace "Ke HAMDAH baki da hankali ne kin san me kike faɗa kuwa, wani irin tarbiyya kike son basu, to wannan shine uban su na asali shi da kike faɗan ubansu  uban su ba ubansu bane uban arone,
baki da ta in da zakiyi ki sauya musu uba."
Mamie tace
"A'a Ummin Fauzan wai ke laifin ta kike gani ne, sam bata da laifi kuma bata faɗi karya ba, Ahmad yayi musu abun da shi ya kasa iya yi musu a matsayin sa na uban nasu ai shi ya kamata a kira sa da uban aro,
basu san shi ba Ahmad suka sani a matsayin uba kuma har gobe zasu cigaba da ganin sa a matsayin uba,
tun da shi ya gaza a cikin rayuwar su."
mikewa nayi na nufi kofa na fita.
can na hango shi zaune in da jiya
na gansa yana zaune kan kujera ya ɗaura kafafunsa kan wata kujerar dake gaban sa, idanunsa a lumshe ya naɗe hannayen sa a kirji yayin da bayan sa ke jin gine jikin kujerar.
har na nufi sashin Ummi najiyo karar waya ta,
da ɗan sauri na juyo, sai naji karar daga inda yake yake fitowa,
kiran ya katse wani ya kuma shigowa, nasan me kiran bai wuce manajan gidan mai na ba dan ɗazu mun fara magana da shi bamu gama ba.
a hankali na juyo na nufi inda yake jin wani kiran ya kuma shigo wa a karo na huɗu, a sannu na iso in da yake daidai lokacin wani kiran yakuma shigowa,
kallon inda sautin wayar tawa ke fitowa nayi, sai ganin wayar nayi a cikin kirjin sa ya rungume shi har lokacin idanunsa a lumshe.
kai na naɗan kawar daga kallon sa kana na mika hannu jin wani kiran ya kuma shigo wa, ina kokarin zaro wayar daga kirjin sa.
a hankali ya buɗe lumsassun idanunsa ya zuba su a fuska ta yayin da idanun mu ya sarkafu dana juna,
da sauri na janje idanuna daga nashi kana nayi hanzarin zare waya ta da ga kirjin sa, na juya da sauri jin zuciya ta yana wani irin tsalle haɗe da bugawa,
su Naseem na gani sun fito daga side ɗin Mamie da sauri naje na ruko hannun su na janyo su muka shige side ɗin Ummi.
tun daga ranar ban sake barin su  sufita ba bare su haɗu da shi, idan ina side ɗin Mamie ne ma

to muna tare da su bana taɓa barin su su matsa ko nan da can, bare ma su fita ya gansu har suje in da yake.
niko tun da na zo gidan gaisuwa bai taɓa haɗa ni da shi ba bare maganar baki...

bayan wata ɗaya

Zaune nake a parlour'n Ummi muna hira na waiga gefe da gefe na banga su Nasmah ba, da sauri na mike nashige bedroom ɗin Ummi nan ma basa nan da sauri nafita na yi waje ina kiran sunan su,
can na hango su rike a hannun Ya SALEEM sun fito daga side ɗin Mamie sun nufi get,
da sauri na biyo bayan su ina isa in da suke da sauri na ruko hannayen su ina faɗin
"Ku wuce mu tafi." juyo wa yayi batare da yasaki hannayen su ba yaɗan zuba min lumsassun idanunsa, yana bina da wani irin kallo tamkar yau ya fara sani na,
niko
hannun su nashiga ja ganin bashi da niyyar sakin su, yana rike da su gam niko sai daɗa jan su nake, a hatsale cikin kunar rai da tuno a bin da yayi min a baya nace
"Sake min yara ina zaka kaimin su."
nayi maganar cikin bushewar zuciya,
da mamaki yake kallo na nasan mamakin yadda na iya tsayuwa nake gaya masa magana babu shakka ko tsoro yake, niko a yanda nake jin zuciya ta zan iya gaya masa fiye da haka danni yanzu bana jin tsoro ko shakkar sa,
baki ya motsa kana ya soma magana kamar mai jin bacci
"Idan kika ji musu rauni sai nayi maganin ki, sakar musu hannu."
 zan tafi da ƴaƴa na bazaki sake ganin su ba, bare kicigaba da nisantasu gare ni."
da sauri nace "Su ba ƴaƴan ka kane ban kuma yarje maka kafita min da su ko nan da kofar gida ba, babu in da zaka je min da su, ka sakar min ƴaƴa na."
nayi maganar ina mai daɗa jan su.
da sauri ya saki hannun su tare da fizgo ni  har sai da na garu da jikin sa,
yarike hannaye na gam a hankali cikin yanayin nan nasa ya soma magana yayin da sautin maganar tasa ke fita da ɗan sautin numfashi irin na mara lafiya,
"Ƴaƴa na ne idan kika kara nesan tani gare su."
ya taune lips ɗin sa tare da girgiza kansa.
kokarin kwace kaina mashiga yi ina faɗin
"Su ba ƴaƴan ka bane ba kuma zasu taɓa zamowa naka ba."
maganar Mamie mukaji a bayan mu tana faɗin
"Sake ta ai ba karya ta faɗa ba, kai da kan ka kafaɗi cewa su ba naka bane tun suna ciki ba'a gama yi musu halitta ba, baka kuma isa yanzu kadawo kace naka ba ne, sake ta maza."
sake ni yayi ya juyo in da Mamie take kamar zaiyi magana miskilancin nasa ya hana shi iya cewa komai, sai dai bugun zuciyar sa daya karo.
da sauri na ja hannun su Nasmah muka wuce ciki...
ina shiga na soma haɗa kaya na, koda Ummi ta shigo taga ina haɗa kaya ta tambaye ni, nace mata gobe zan tafi ana nema na game da harkoki na da gaggawa, washegari kuwa da sassafe

nabar garin Bauchi..........!

38

Sai da na dawo Abuja kafin hankali na ya kwanta nayi masa nisa da yaran bazai sake ganin su ba bare ya sami bakin faɗin cewa su ƴaƴan sa ne.
yanzu harkoki na da na Ahmad karami kaɗai nasa a gaba, duk da ko mai bai canza ba ma'aikatan da suke ai ki karkashin Ahmad su suka cigaba da gudanar da aikin a karkashi na.
Bayan wani lokaci
sabuwar rayuwa na gina wa kaina, abisa rashin Ahmad na nutsar da zuciya ta na fauwala wa Allah komai na rungume kaddar rashin sa, idan na tuno da shi da rayuwar da mukayi dashi wani lokaci na zauna nayi kuka wani lokaci nayi dariya, sannan nayi masa addu'a, nakuma sawa raina nagama aure kenan a duniya bazan kuma maimaita kuka na uku a cikin aure ba, kamar yadda nayi a baya, da farko nayi kukan kazafi da wahalar rayuwa dalilin auren Ya SALEEM, daga bisa ni nayi kukan rabuwa da Ahmad a lokacin da na yi sabo da shi, yanzu kam zanyi rayuwa ta ce cikin salama ni kaɗai sai ƴaƴa na...👌

A gajiye na dawo gida daga gurin mittin ɗin da muka gudanar yau da ma'aikata na,
a parlur na tadda Mama goye da Ahmad,
"Mama barka da gida Ahmad ɗin ne goye a baya har yanzu zai sa miki ciwon baya fa."
nayi maganar ina zama kan kujera,
Mama tayi murmushi tare da faɗin
"To ya zanyi tun da ai kin aure nake, ai wannan angon shi maganin sa goyo idan ba haka ba yarika haɗa kashi kenan da kiriniyar sa,
ɗazu wai shi zai sauko kasa da kansa kaɗan ya rage yayi dungure."
dariya nayi nace
"Tab da yau keya yasha kasa kenan."
tace "Ai kuwa."
Talatu ce tashigo parlour rike da  da tray mai ɗauke da kayan motsa baki ciki, ta dire shi kan table ɗin gabana tanayi min sannu da dawowa, na amsa tare da yi mata sannu da aiki.

na gyara na soma cin abin da ta kawo min.
waya ta ce tayi kara murmushi nayi ganin Aunty Rafee'at ce ke kiran na ɗaga tare da yin sallama,
ta amsa jin yanayin muryar ta da sauri nace "Aunty Rafee'at lafiya ya naji muryar ki haka?."
tace "HAMDAH Ya SALEEM bashi da lafiya muna asibiti ne jikin sa ya tashi sosai."
ɗan shiru nayi jin yanda take maganar kamar zatayi kuka cikin rauni sosai.
nace "To ikon Allah jikin har haka ne to Allah ya sawaka."
bata kuma iya cewa komai ba sai kashe wayar tayi,
fuska na yamutsa a kasan raina nace
"Fatan saukin ma dana maka albarkacin ƴan'uwan taka ce."

A can sashin su Bappa kiran Abba ne ya shigo wayar Bappa bayan sun gaisa, Abba ke sanar masa da SALEEM ba lafiya sosai yana asibiti.
hankalin Bappa yatashi sosai dajin lamarin, lallai ciwon babba ne tun da har aka kwantar da SALEEM a asibiti.
yace gobe yana zuwa insha Allah,
washegari da safe Bappa ya ɗau hanyar Bauchi.
koda ya isa asibitin da aka kai SALEEM yasa aka kai shi, hankali sa ya tashi matuka ganin halin da SALEEM yake, yana kwance baya ko motsi na'urori suna ai ki a jikin sa.
cikin matukar tashin hankali Bappa yake tambayar su Abbu me ya ke damun shi me likita yafaɗa game da ciwon nasa.
Dr Farooq ne ya shigo da wasu likitoci su huɗu suka dukufa a kansa kowa da kalar gwajin da yake masa, Dr Farooq yaɗan yi baya tare da faɗin "Ya salam." a cikin zuciyarsa, ya juyo ya kalli su Abba da Abbu da Bappa dasuke tsaye jungum-jungum, kansa ya kawar ganin sun kura masa ido suna so suji ta bakin sa.
ɗaya daga cikin Doctors ɗin ne ya ɗago tare da share zufa ya kalli sauran ƴan'uwan sa sukayi magana sakanin su kana ya juyo gasu Abbu yace
"Kuyi Hakuri a gaskiya yana cikin hatsari sosai zuciyarsa sa yana daf da bugawa, amma zamuyi iya bakin kokarin mu daga nan zuwa kwana biyu har idan ba'a sami wani sauyi ba, to gaskiya sai dai a ɗaga shi a kasar nan a cikin kwana kin nan."
salati Bappa ya sake hankali tashe yake faɗin
"Bugun zuciya kuma Innalillahi wa'inna'ilaihirraji'un, garin yaya akayi haka yau she yafara ciwon zuciya da har zuciyar ke kokarin bugawa?."
Dr Farooq ya gyara tsayuwar sa yayin da likitocin suka fita,
Bappa ya matso jikin gadon da SALEEM ke kwance idanunsa a rufe yayin da yake fidda numfashi ɗaya na bin ɗaya, Bappa ya dubi su Abbu yace
"Tun yaushe yake cikin wannan halin kuma mene ne musabbabin sa?."
Dr Farooq ne yace "Tun ranar da HAMDAH ta bayyana tafiyar ta na wannan karon kuma shi ya haifo da wannan babban matsalar,
kuyi hakuri tun wancan lokaci ban sanar wa kowa bane sabo da ina sa ran zai iya samin sauki ta hanyar shan magani da kuma rage tunani,

sai dai a yanzu komai ya kwaɓe kuma na lura da tun ranar da HAMDAH tabar garin nan washegari dana kuma yi masa gwaji sai naga ciwon nasa ya ɗare na da, sai dai abin da na lura baya amfani da shawarwarin da na ɗaura shi a kai yawan tunani da kuma damuwa shi ya janyo sa izuwa wannan matakin."
da mamaki su Abbu suke jin maganar su sam basu taɓa sammanin haka ba,
Bappa ko kai ya jinjina yana mai cigaba da kallon SALEEM dake kwance numfashin sa yana sama yana kasa.
Dr Farooq yace "Sakamakon allurar da akayi masa shi yasa yasami baccin nan, zamu jira zuwa ya farka muga abin da ya dace, zamu ɗan bashi guri yasa mi baccin da kyau."
duk suka fita a ɗakin domin barin sa ya sami baccin...

Bayan wasu ɗan awanni ya farka daga baccin da yake, sai dai har yanzu babu abun da ya sauya daga halin da yake ciki,
bayan likitoci sun shiga sun daɗa dudduba shi suka fito, Dr Farooq yace wa su Abbu zasu iya shiga su gansa yanzu,
yana kwance har lokacin amma idanunsa a buɗe suke yanzu, sai dai babu in da yake na'urori ne ta ko ina ke ai ki a jikin sa.
suka karaso in da yake suna yi masa sannu,
Bappa yace "Sannu SALEEM ya jikin?." kwayar idanunsa kaɗai ya juya ya ɗan kalli Bappa kana ya ɗan lumshe su tare da buɗe su a lokaci guda,
Bappa ya gyara tsayuwar sa da kyau ya kalli sa kana yace
"Akan wani dalili kake son salwantar da rayuwar ka, kunshe damuwa cikin rai mai cutar wa bazai taɓa haifar da maslaha ba, ka dubi halin da ka jefa kan ka ciki, muma ka jefa mu.
SALEEM kana son komawar auren ka da ƴar'uwan ka, a kan hakan kake son salwantar da rayuwar ka ta hanyar ɓoye hakan acikin zuciyar ka."
"SALEEM." Bappa yakuma kiran sunan sa, kana yace "Kana son komawar auren ku da HAMDAH?."
shiru yayi tare da yin kasa da idanunsa yana wani taune leps ɗin sa,
Bappa yakuma faɗin "SALEEM kana son mai da matar ka?."
nan ma bayyi magana ba sai ɗago idanunsa da yayi ya kuma kallon Bappa, yayin da bugun zuciyarsa ya karo,
Bappa yagirgiza kai tare da yin murmushi irin nasu na manya kana yace
"Miskili kafi mahaukashi ban haushi, to ka faɗawa zuciyar ka ta sami nutsuwa za'a bata abin da take so,
basai tayi bindiga ta fashe ba."
idanunsa ya lumshe tare da jan numfashi mai ɗan tsawo a bayyane, a hankali ya ɗago hannusa izuwa kan kirjin sa ya kife tafin hannunsa kan kirjin nasa dake harbawa da sauri-sauri.
Abbu yace "Bappa shin ka mance abin da ya mata ne kayi hakuri da abin da zan faɗa Bappa, idan aka mata haka sam ba'a kyauta mata ba, kada mu kuma maimaita kuskuren baya,
ya kuma cutar da rayuwar ta,
sam bai cancance ta ba."
Abba yace "Hukun cin da Bappa ya yanke shine kaɗai mafita, shin zamu cigaba da zuba ido ne

muna ganin sa cikin halin mutuwa ko rayuwa."
Bappa yayi waje su Abbu suka bi bayan sa,
koda suka fita Bappa ya dube Abbu kana yace
"Ka sani SALEEM bashi da laifi duk abun da ya faru sharrin ma sharranta ne."
Abbu yace "Da kuma halin sa, in da sharrin wasu har da ma halinsa, kada mu shiga hakkin yarinyar nan."
"Kada ku kuma cewa komai a kan gamanar nan na gama yanke hukunci." Bappa ya faɗa yana tafiya hanyar masallaci dake cikin asibitin."

bayan kwana biyu da tafiyan Bappa dasassafe yaqirani yace nazo Bauchi yanason ganina da gaggawa,
natsorata dajin qiran da Bappa yamin na gaggawa sai naqira wayan Ummi danjin mekefaruwa naji wayar Ummi akashe,
jin wayar Ummina akashe Hankalina yayi mummunar tashi atake nazari mayafina naja yarana mukayi waje tunkafin na isa parking space nake qiran Driver, ya iso da gaggawa nace masa maza yanzu mutafi Bauchi,
yana tambayar lafiya hajiya ban saurareshi ba na saka su Naseem cikin mota kawai nima nashiga.
nace masa tafiya mai sauri zamuyi ba ɓata lokaci yaja motar,
cikin awa huɗu da rabi muka iso cikin garin Bauchi saboda gudun da driver yake shararawa.
koda muka iso gida hankalina yayi mugun tashi ganin babu Kowa a gidan numbern Bappa naqira nace Bappa
"Na iso ina mutanen gidan?."
yace kizo asibitin Dr Farouq gamunan anan,
dasauri nafita nashiga motan piiiiiiiii naja motan ko Driver bantsaya qiraba bantsaya ko ina ba sai asibitin.
ina daidaita parking na fito su Naseem suka biyoni dasauri ina shiga cikin asibin naga Mamie da Ummi Aunty jaleela Aunty Rafee'a Fauzan Ya Mas'ud Nusaiba
suna gani na suka mike duka suna faɗin
"Zuwan yau she kenan?."
murmushi nayi kana na karaso in da suke, na dube su ina faɗin
"Ina su Abbu da Abba ina Bappa?."
Ummi tace "Suna cikin ɗaki in da aka kwantar da SALEEM."
numfashin mai karfi na sauke jin kowa yana lafiya, nace
"Kai wlh har hankali na ya kwanta na ɗauka wani mummunar abune ya faru ashe dai kowa lafiya."
Ummi tace "Eh to gamu nan dai kowa lafiya amma SALEEM gashi can a kwance babu in da yake."
baki na taɓe tare da faɗin "Allah ya sawaka."
na juya ina kokarin zama kan kujera,
Ummi ta ce "Baki shiga kin duba shi ba kike kokarin zama a nan, je ki duba shi kafin ki zauna."
fuska na ɗan yamutsa tare da mike wa na nufi kofar da take nuna min.

da sallama na tura kofar,
su Abbu suna tsastsaye suka amsa min sallamar,
idaduna ne ya sauka kan gadon dake cikin room ɗin
Ya SALEEM na kwance idanunsa a lumshe  numfashin sa yana sama da kasa na'urori suna ta ai ki a jikin sa.
 a hankali na karaso cikin ɗakin. tare da soma gaida su Abba, suka amsa suna yi min sannu da hanya.
Bappa yace "Kin iso?." nace "Eh na iso."
yace "To madalla." ya dube Ya SALEEM da ke kwance tare da duba na yace "Kiyi masa sannu da jiki."
naɗan dube shi tare da faɗin
"Ya jiki?." idanunsa ne suka motsa
daga lumshen da suke a hankali yashiga kokarin buɗe su, har ya ida buɗe su a kai na.
a yanayin da yake ciki bana sa ran zai iya amsa ya jikin da na masa dan gaba ɗaya yagama fita hayyacin sa,
kai na na kawar daga gare sa, a hankali ya mai da idanunsa ya kuma lumshe su tare da sauke numfashi mai sauti.
Bappa ya dube ni tare da faɗin
"Zo nan HAMDAH ina da magana da ke."
yayi maganar yana juyawa tare da fita a ɗakin.
nabi bayan sa muka fita can farfajiyar asibitin,
gefe muka samu Bappa ya zauna kan dakali lima na zauna gefen sa.
ya dube ni da kyau yana faɗin
"Kun zo lafiya dai ko ya hanya?."
nace "Lafiya lau." yace "To madalla."
zaman sa yaɗan gyara kana yace
"HAMDAH."
ya jira suna na, na juyo gare sa tare da amsa kiran nasa.
yace "Mene ne matsayi na a gare ki?."
ɗan jim nayi dajin maganar nasa kana nace
"Ko a da da bansan kai waye a gare ni ba, matsayin uba nake ganin ka bare yanzu da ya kasan ce kai ɗin uba ne kuma kaka a gare ni."
yace "Madalla naji dadɗin jin hakan ina kuma alfahari da ke, da biyayyar ki nasan bazaki taɓa bani kunya ba, HAMDAH ina son ki sani yau na mayar da auren ki da ɗan uwan ki."
wani irin dadammm kirjina ya buga da mugun karfi, na wani irin mike wa a razane a kuma zabure, ina bin Bappa da wani irin kallo.
Bappa ya ruko hannuna tare da maidani zaune, yace "Ki nutsu kiji abin da zan faɗa miki,
ɗan uwan ki yana cikin mawuyacin hali halin mutuwa ko rayuwa, kuma duk a ta sana diyyar ki ne, kin ganshi kuma kin ga halin da yake ciki, ke kaɗai zaki iya tsamo shi daga cikin halakar dayake dumfaro shi na bugawar zuciya, likitoci sun bamu tambacin har idan yau yagaza samin abinda yake muradi a cikin zuciyar sa, to ba shakka zuciyarsa zata iya bugawa ya mutu,
ke yake muradi a zuciyarsa sabo da gudun kada mu rasashi shi yasa na mai da auren ku da shi yau,

nasan wannan hanyar ce kaɗai zai iya kuɓutar dashi daga cikin halin da yake."
kai na shiga girgiza wa ina faɗin
"Sam bani ce cikin zuciyarsa ba, Bappa Ya SALEEM ya tsane ni baya kauna ta Bappa me yasa zaka mai da ni cikin halaka rayuwa da shi tamkar halaka ce, ina murnar rayuwa ta tasami salama ashe dai a cikin kunci da wuya zan tabbata,
Bappa bana son komawar auren nan dan Allah ka raba auren nikuma zanyi nesa da ku bazaku sake gani na ba tun da bakwa son ganin farin ciki na,
aure na da Ya SALEEM tamkar rugujewar farin ciki nane, wata a zabar zan kuma fuskanta ta sanadiyyar sa a karo na biyu."
kuka ne nafashe da shi tare da haɗe hannaye na ina faɗin
"Dan Allah dan Allah Bappa karaba auren nan wlh bana so."
numfashi Bappa ya sauke kana yace
"Kiyi hakuri ki ceci ɗan uwan ki kada ki bari ta sana diyyar ki ya mutu, babu abun da zai faru da rayuwar ki Allah bazai bawa azzalumai masara tsoron Allah nasara a kan ki ba,
ɗan uwan ki na bukata ki ke da ƴaƴan shi."
kai narika girgiza wa ina faɗin
"A'a a'a Bappa dan Allah, ba ƴaƴan sa bane su ba ƴaƴan sa bane."
na mike zumbur da sauri naje na ruko hannun su Naseem na jasu da sauri nanufi mota, muka shiga muka bar asibitin...

Motar Bappa yabi da kallo kana ya mike yashiga ciki,
a bakin kofar ɗakin da SALEEM ke ciki ya haɗu da su Abbu har da su Mamie suna tsaye kowa yayi jungun-jungun, jiki a sanyaye Bappa ya iso in da suke yana faɗin
"Ya'ya lafiya?." Abba yace "Ina HAMDAH take......



Bappa yace "Ta tafi bata tsaya ta saurare ni ba, bata kuma taɓa yimin haka ba, HAMDAH, bata taɓa ketare magana ta ba, hakika tana cikin tsoro da tuno rayuwar ta ta baya tana tsoron kada ta kuma shiga halin da ta shiga a baya."
cikin rawar murya da zubda kwalla Ya Mas'ud yace "Bappa numfashin Ya SALEEM yana

kokarin barin jikin sa."
salati Bappa yayi da sauri ya shige cikin ɗakin in da likitoti suke tsaye ca a kansa.
tuni kowa ya fara kwalla su Aunty Rafee'at har da jan shassheka,
Mamie tayi baya duk daure zuciyar ta da take sai da hawaye suka zubo mata,
ta zauna a gefe tana mai cigaba da zubda kwalla.
da sauri Ummi ta nufi kofar fita tayi waje,
direba ta saka ya kaita gida da sauri tana isa,
direct sashin ta ta wuce tun daga parlour take jiyo shesshekar kuka, da sauri ta karasa cikin bedroom.
ina zaune cikin ɗakin nahaɗa kai da guiwa sai rusar kuka nake,
a sannu ta karaso kusa da ni ta zauna gefe, a hankali ta dafa kafaɗa ta tare da kiran suna na tace
"HAMDAH na tabbata kinsan kuna da ɗacin rabuwa irin na mutuwa, HAMDAH ga uwa can tana kukan rabuwa da ɗan ta da yake kokarin barin duniya a ta sanadiyyar ki, shin bazaki zamo mai yafiya a rayuwa ba, shin kin san falala da tarin lada a gun duk wan da ya ceci wani daga faɗa wa wata halaka, ɗan uwan ki ne fa shi shin ashe bazaki zamo mai share mana hawaye ba, ni mahaifiyar ki ina mai rokon ki da kije ki ceci ɗan uwan ki, ba zanyi miki dole ba amma ki sani har idan SALEEM ya mutu duk ahali zamu rataya miki alhakin mutuwar sa a kanki,
sannan baza mu taɓa dai na ganin ki a matsayin wan da takasa taimakon ahalin ta ba."
Ummi ta mike tana sharar kwalla ta nufi kofa zata fita,
da gudu na mike naje na ruko hannun Ummi, cikin muryar kuka nace
"Ummi na kiyi hakuri kar kuyi fushi da ni Ummi ina jin tsoro ina jin tsoro ne."
kai ta girgiza min tare da share min hawaye ta ruko hannuna gam-gam
cike da karfafa guiwa tace
"Babu abun da zai faru da yardar Allah kisawa zuciyar ki hakan, zamu tsaya miki da karfin ikon Ubangiji babu abin da zai kuma faruwa."
kai nashiga gyaɗa wa alamun gamsuwa yayin da hawaye ke ci gaba da zuba a ido na.
ta janyo hannuna ta haɗo da na su Naseem muka fita.
koda muka iso asibitin hannuna Ummi ta kuma ruko wa tana ɗauke da Ahmad karami Naseem da Nasmah suna gaban mu, muka shiga asibitin.
su Mamie da Aunty Rafee'at Aunty Jaleela Nusaiba Fauza suna tsastsaye a bakin kofar ɗakin da Ya SALEEM yake ko wannen su kuka yake da hawayen sa,
jiki a sanyaye muka karaso in da suke, hankali tashe Ummi ke tambayar su lafiya. cikin zubda kwalla
Aunty Jaleela tace "Ummi Ya SALEEM baya numfashi."
tuni hawaye yafara zuba a idanun Ummi,
niko jiki na ne ya ɗau ki ɓari, Ummi ta kuma ruko ni gam ta janyo ni muka shige cikin ɗaki.
doctors ne ke tsaye a kansa suna ta fafutukar ceto numfashin sa,
Bappa Abba Abbu Ya Mas'ud suna tsaye a gefe.
Bappa sai anbaton sunan Allah yake Ya Mas'ud ko sai sharar kwalla yake, lokaci zuwa lokaci Abba ke kai hannunsa karkashin idanunsa yana share ɗan guntun kwallar dake fito masa, a ɓangaren Abbu ma haka.
ɓarin jiki na ne ya karu lokacin da idanuna ya sauka kan Ya SALEEM dake kwance ko matsi

baya yi babu alamun numfashi tattare da shi,
sosai jiki na ke kakkarwa, zuciya ta tayi rauni tausayi mai haɗe da kawa zucin ɗan uwa suka lulluɓe ni, ko ba komai Ya SALEEM jina na ne dole naji makamancin hakan a tattare da ni, domin ɗan uwa yawuci wasa koda ace kuwa a kullum yana kuntatawa rayuwar ka, ka gansa a gaban ka tamkar mutacce dole zuciyar ka ta girgiza.
da sauri na fizge hannuna da gudu na fasa sakanin doctors ɗin na faɗa a jikin sa tare da girgiza shi ina faɗin
"Ya SALEEM kar ka mutu ka tashi dan Allah ka tashi kar ka mutu Ya SALEEM Ya SALEEM Ya SALEEM".
na karasa da kiran sunan sa da karfi ina mai jijjiga shi.
tuni Naseem da Nasmah suka saki kuka suna kiran Daddy Daddy.
sosai nake gargiza shi ina kiran sunan sa yayin da nake rusa kuka mai karfi,
a raina ina ayyana shike nan babban yayan mu ya tafi ya barmu, duk miskilancin halin sa da rashin dariyar sa muna son sa a haka, ga ƴan uwa na da mahaifiyar sa tana kukan rashin sa, hakika rashin wani naka na da zafi, shike nan shima ya tafi bazai dawo ba, kamar yadda Inna da Ahmad suka tafi tafiyar da babu dawowa..
wani kuka ne nakuma sake wa da karfi ina faɗin
"Ya SALEEM kai kar ka tafi dan Allah kada ka tafi ka barmu ka tashi Ya SALEEM ka tashi."
nayi maganar ina mai girgiza shi da karfi.
fuska ta na kife cikin kirjin sa ina jujjuya fuskar tawa da gogashi cikin kirjin nasa ina mai ci gaba da kukan.
a sannu ya sauke wani irin numfashi mai tsawo kana yashiga motsi da idanunsa.
cikin matukar mamaki likitotin ke kallon ikon Allah, mutumin da numfashin sa ya tafi bugun a gogon hannun sa ne kaɗai yake iya  tabbatar musu da yana raye shima bugun hannun nasa yana daf da tafi dan sai ya ɗau tsawon mintina masu dama kafin ya ɗan buga sai ka lura sosai kafin ga gane hakan shima,
da sauri su Bappa suka maso suna mai mamakin hakan suma, dan gaba ɗaya sun gama cire rai da shi suna jiran jin ta bakin likitotin  kawai.
da sauri na ɗago kai na jin yana motsa jikin sa na kurawa fuskar sa iso, ganin idanunsa suna motsi a lamar yana son buɗe su.
da sauri nace "Ya SAKEEM buɗe idanun ka Ya SALEEM ka buɗe ka huɗe kada ka tafi ka harmu."
a hankali yashiga buɗe idanun nasa har ya ida buɗe su a kan fuska ta,
 a sannu ya ɗago hannunsa ya sauke sa kan nawa ya rike shi gam, a hankali ya juya fuskarsa in da su Naseem suke yayi musu alama da hannu da suzo in da yake, suka matso bakin gadon suka kwantar da kansu a jikin sa, numfashi mai sauti ya sauke yana mai daɗa damke hannuna tare da shafa kan yaran da hannunsa guda.
gaba ki ɗaya ƴan cikin ɗakin farin ciki ne bayyane a kan fuskokin su,
hatta likitotin, ɗaya daga cikin Dr ya dube ni da murmushi yace
"Sannu da taya mu ai kin da ke kokarin gagarar mu."
"Itace maganin ai."
ɗaya Dr dake kusa da shi ya faɗa yana ɗan dariya...

Ya Mas'ud yafita da sauri sai gashi da su Mamie sun shigo har suna rige-rigen shigo wa.
fuskar Mamie ɗauke da murmushi mai bayyana tsantsar farin cikin ganin sa ya farfaɗo daga sammanin mutuwar da suka saka masa.
kowa sai sannu yake masa, sai dai babu wan da ya amsa shi, hakan bai dami kowa ba dan kowa yasan hakan halin sa ne.
hannu na dake cikin nasa na ɗan motsa ina kokarin janye hannun nawa,
dan irin kallon da yake min yasa ni jin wani iri cikin jikina, ga kuma idanun kowa a kanmu.
gam yada ɗa rike hannun nawa bai kuma fasa bina da irin wannan kallon ba.
Aunty Rafee'at da bakin ta ya kasa rufuwa dan murna ta juyo ta kalli mijin ta Dr Farouq, shima murmushi yayi tare da ɗan dungurin ta cikin kasa da murya ya ce
"Kin ga yayan ki ko so nason kashe shi ga kallon da yake mata kamar bashi bane ɗazu ke kokarin mutuwa."
hararar wasa tayi masa tace
"To an faɗa maka so karya ne."
yace "Ni zan bada shaida ba karya bace gashi ina kan fama da shi a kan ki."
ya karasa maganar da kashe mata ido,
dariya tayi tana ture kafaɗar sa...

Hannu na na zare cikin nasa da ɗan sauri cikin jin kunya ganin su Abbu sun matso kusa da shi suna yi masa sannu,
shiko idanunsa na kaina, yana yi min wani irin kallon cikin ido.
baya nayi ina mai jin kunya.
bayan wasu ɗan mintina likitoti sukace a ɗan bashi guri ya huta bayan sun masa allurai...
a ranan da yamma Ya SALEEM yace shi zai koma gida, Dr Farooq yace ya bari ya daɗa jin kwarin jikin sa,
yace shi sam zai tafi dan shi lafiyar sa lau,
sai da su Bappa suka sa baki kafin da kyar ya yarda.
kwanan sa uku a asibitin kullum a can muke wuni dukan mu, idan na shiga ɗakin yi masa sannu da jiki haka zai kafe ni da ido yata kallo na kamar bai taɓa sani na ba.
su Nasmah kam ko da yaushe suna jikin sa, sai dare idan zamu koma gida suke rabuwa da shi.
ranar da ya cika kwana huɗu yace bazai kuma kara kwana cikin asibitin ba, dun dole a ka bashi sallama.
nuka koma gida kowa hankalin sa kwance da farin cikin samun lafiyar sa.....

A ranar Abbu ya sa a ka kirawo ma'aikatan gidan Ya SALEEM dukan su waɗan da suka yi aiki lokacin ina gidan, wato waɗan da suka bada shaida kan sunga wani yana zuwa guri na lokacin da Ya SALEEM yayi tafiya.
dukkan mu a parlour'n Mamie muka haɗu,har da Ya SALEEM da Abbu yayi masa dole yabaro ɗakin sa na cikin gidan yazo gurin taron.
ganin ma'aikatan ya sani tuno wa da abunda ya faru a baya sai nake ganin kamar yau hakan ta faru.

bayan addu'a da Bappa yayi Abbu yayi gyaran murya kana ya dubi ma'aikatan ɗaya ba yan ɗaya,
Baba Mai gadi Sani direba Habu mai shara sai Salele wan da shi a lokacin bai bada shaidar ba sai dai kasan cewar yana aiki a lokacin yasa shima a ka gayyato shi.
Abbu ya dube su da kyau yace
"A wancan lokacin kunyi kokarin bata mana family kuka kuma yi sana diyyar raba aure da tarwatsa mana family, dukkan ku bazan kyale kowa ba zan ɗau mataki a kanku zakuyi bayani a gaban kotu, har da kai da girman ka mai gadi baka ji kunyar bada shaidar karya ba."
baba mai gadi yashiga jan hanci da matsar kwalla yana faɗin
"Allah ya huci zuciyar ka Alhaji ayi hakuri wlh sharrin shaiɗan ne, amma da fari na ki karɓar kuɗin da Hajiya ta bamu kan muyi shaidar, tace har idan bamu yi abun da tace to to abakin aikin mu shine naji tsoro na karɓi kuɗin, amma wlh duk abun da ya faru karya ne Hajiya ce ta shirya komai tace mu faɗa."
Bappa yayi salati yace
"Akan kuɗi akan kuɗi kuka tarwasa aure kuka jefa yarinya cikin ukubar rayuwa Allah bazai kyale ku ba."
Salele yace "Wlh Alhaji lokacin can data bani kuɗi kan nayi shai da naki sai tace har idan na faɗa sai tayi min sharrin da bana sammani, sai tace har dani ta taɓa kama ni ɗakin Hajiya HAMDAH shi yasa naji tsoro ban faɗa ba."
Abbu yace "Yanzu kam komai ya zo karshe ita wacce ta shirya muku makircin bagata can kwance a asibiti Allah ya fara nuna mata iyakar ta ba, ai ba ayi wa Allah dabara, kukuma mai gadi da Habu da Sani yau za'a kurfanar daku gaban Shari'a kotu zata yanke muku hukun ci dai-dai da abin da kuka ai kata."
rokon Abbu suka shiga yi da magiya Abbu ya ɗaga waya ya kira yace a zo a tafi da su,
aka washe su akayi gaba da su. har aka gama magana
Ya SALEEM baice komai ba yana dai zaune yana kallon kowa da ido, har taron ya watse shima ya mike ya fita.
su Aunty Rafee'at kam sai murna wai yau asiri ya karasa tonuwa...

Da daddaren ranar da aka sallame shi, ina zaune a bedroom ɗin Ummi,
Ummi ta shigo rike da tray mai ɗauke da kayan motsa baki ciki tace
"Ke HAMDAH taso ki kaiwa yayan ku."
nace "Ni kuma Ummi a bawa Fauzan ya kai masa Allah bacci nake ji."
"Maza tashi ki kai masa Fauzan ɗin ne zai kai masa ke aikin me kike, in kin dawo kyayi baccin."
mike wa nayi ina faɗin
"Allah Ummi bakiji yan da na gaji ba bai ma fa ce zaici komai ba."
"Sai ya faɗa ne mutu min da bashi da lafiya."
karɓar tray ɗin nayi nanufi ko ina bubbuga kafa,

kai Ummi ta girgiza tana faɗin
"Allah ya shirya ko yaushe zaki girma oho."

A bakin kofar ɗakin sa na cikin gidan na tsaya, nayi sallama ya am sa ɗan tsayuwa nayi kaɗan dan ban mance dokar sa na idan kayi sallama ka ɗan tsaya kafin ka shigo ba,
guntun tsaki naja.
to ma wai sai nice zan kawo masa abinci.
wani tsakin na kuma ja ina shige wa cikin ɗakin, da sallama.
ya kuma amsa wa, ya ɗago tare da zuba min ido.
yana zaune bakin gado sanye da jallabiya, gashin kan sa ya na ɗiga da ruwa da alama fitowar sa daga wanka kenan.
su Nasmah suna kwance a kan gadon sa suna bacci,
nayi mamakin ganin su cikin ɗakin na ɗauka suna gun Ya Mas'ud ne.
a sannu na karaso cikin ɗakin na dire tray ɗin saman table ɗin gefen sa,
har lokacin idanunsa a kaina, mike wa nayi ina  kokarin barin gurin.
naji ya ruko hannuna, a hankali na juyo na kalle sa muka haɗa ido, cire idanuna nayi daga nasa a hankali nace
"Ya jiki?." bai yi magana ba har zuwa ɗan wasu sekonni bai kuma sake hannuna ba, zuwa can ya motsa laɓɓan sa yace
"Naji sauki." hannuna na zame cikin nasa naɗan matso bakin gadon ina kokarin ɗaukar su Nasmah najiyo maganar sa,
"Ki bar su a nan." a hankali na juya nafita a ɗakin dan kallon da yake min yafara min yawa...

Washegari da safe bayan nayi wanka na shirya cikin doguwar rigar les nafito parlour, Ummi tana ta kiciniyar haɗa breakfast, tana gani na tace
"Yauwa HAMDAH zo ki kaiwa yayan ku breakfast ɗin sa."
baki na turo na rasa me yasa Ummi take son lallai sai ni zan rika kai masa abinci.
tace "Kiyi sauri mana kin san zai sha magani yakamata ya fara cin abinci kafin ya sha."
ɗaki na koma naɗau gyale nafito na karɓe tray'n data shirya masa kayan breakfast ɗin ciki na yi waje.
da sallama na shige ɗakin suna kwance kan gado shi da su Naseem sai zuba masa surutu suke, shiko sai murmushi yake binsu da shi.
na dire tray'n naɗa go ina faɗin
"Ina kwana, ya jiki?."
lumshe idanunsa yayi tare da buɗe su a kai na ya kura min ido sosai,
ganin haka da sauri na juya zan fita naji maganar sa
"Wa zai bamu breakfast ɗin idan kika tafi?."
baki na murguɗa a kasan raina nake faɗin "Jimin samin guri ko da ni nake bashi da zai wani ce wai idan na tafi wazai bashi, badun banson ran Ummi na ya ɓaci ba an faɗa masa zan zo ɗakin ne ma."
ɗan gajeren tsaki naja karaf muka haɗa ido da shi, farr nayi da ido na dan nasan yaji kuma nasan baya son tsaki.
ganin yana bina da kallon tuhuma na tsakin dana masa, sai na kaɗa kwayar ido na tare da

murguɗa baki.
na dawo cikin ɗakin naɗan sun kuya nasoma haɗa musu abin karin,
da sauri na ɗago jin hannun mutum a kafaɗa ta na juyo cikin hanzari,
sai ganin sa nayi daf da ni,
ganin yan da mukayi daf da juna a hankali nayi baya da kafata ina kokarin matsawa baya.
sai ya ruko kafaɗu na gaba ɗaya,
ya jefa idanunsa cikin nawa yana yi min wani irin kallo, da sauri rumtse idanuna dan sam bana iya jure wa kallon nan nasa,
a sannu yashiga motsa laɓɓan sa yayin da nake jin idanunsa suna yawo cikin jikina
"Yau she kika zamo haka?."
cikin tsiwa na ware idananuna a kan sa nace
"Tun shekaru biyar zuwa shi da da suka wuce."
shiru yayi tare da sauke idanunsa kasa da alamun jikin sa yaɗan yi sanyi da abun da na faɗa, na faɗi hakan ne kuma domin na tuna masa da baya da kuma abun da ya faru a baya, tun kuma bayan faruwar haka na daina jin tsoron sa.
a hankali ya sake kafaɗa ta ni ko na juya na fita...

Bayan kwana uku kullum ni Ummi take sawa na kai masa abinci ina kai wa kuwa zan juya, ko gaisuwa bana tsayawa yi masa zan fita, kullum su Naseem suna gurin sa a can suke kwana.
yanzu shirye-shiryen koma wa Abuja nake dan sai kira nake samu daga ma'aikata na.

Da daddare har na kwanta Ummi ta shigo tace na tashi na kai masa abinci, na mike na ɗau hijabi na saka kan kayan baccin da ke jiki na na nufi ɗakin sa.
yana zaune bakin gado su Nasmah suna kwance a gefen sa suna bacci,
na juya zan fita ya dakatar da ni ta hanyar rike min hannu,
na juyo gare shi zan yi magana, yakai waya kunnen sa tare da faɗin
"Mamie su Nusaiba su zo."
jim kaɗan Nusaiba da Fauzan suka shigo, yana rike da ni bai sake ni ba kuma baiyi magana ba, yace da su su ɗauki su Nasmah su kai su gun Mamie.
suka kwashe su suka fita da su.
ya ɗan dube ni yace
"Ahmad fa?." "Yayi bacci."
nafaɗa ina mai mamakin yadda akayi yasan sunan sa.
a hankali ya saki hannuna ya mike ya taka zuwa bakin kofa ya rufe da key.
da sauri nace
"Ban fita bafa ka buɗe zan fita."
juyo wa yayi ya zo bakin gado ya zauna kana ya miko hannu ya ruko hannuna sannan yafizgo ni na faɗo jikin sa,
hannayen sa duka biyu ya saka ya zagaye ni da su, kokarin fisge jiki na nake da kyau ya daɗa gyara rukon da yamin, kana ya mike dani a jikin sa ya haye gado can kuryar gado ya dire ni.
da sauri na mike zaune nace
"Ka bani key na buɗe na fita."

kwanciya yayi a gefe na a hankali yake faɗin
"Nasan Ummi zata kula da Ahmad ki kwanta a nan bacci zaki taya ni."
cike da tsiwa nace "A sabo da me zan kwan ta anan ni ka bani key na tafi."
ya tsarsa ya ɗaura kan baki tare da faɗin
"Shiiiit ban son hayaniya kwanta nace."
yayi maganar yana tsare gira alamun ba wasa suffarsa na Ya SALEEM ɗin da na sani a da ya bayyana,
sai naji suffar tasa da kwarjinin sa ya cike ni,
kasa nayi da kai na batare da na kwanta ba ban kuma iya cewa komai ba.
a hankali ya mika hannu ya sauke kan nawa yaɗan matse a hankali cikin yin kasa da murya irin na mai jin bacci yace
"Kwanta mana HAMDAHHHH ko ke bakya jin baccin ne."
har cikin ƙwaƙwalwa ta najiyo sautin muryar sa da yan da yakira suna na, karo na farko a haɗuwar mu da shi na biyu ya kira ni da suna na a kuma irin yanayin da yake kira na a da, a duk san da ya kira ni da suna na sai naji kamar shi kalar yadda yake faɗin sunan da ban ne dana kowa.
ya janyo ni tare da gyara min pillow na kwanta gefen sa, a hankali yakuma furta
"A kwai maganin da zan sha cikin dare ina so ki tashe ni ne dan na sha."
mamaki ne ya kama ni wani magani ne kuma ake shan sa cikin dare ban taɓa jiba.
a hankali ya lumshe idanunsa, ido na ɗan kurawa fuskarsa yaɗan rame ya kara haske hancin nan nasa ya daɗa fitowa zarr sajen sa zuwa zagayayyen ɗan gemunsa a kwance suke luf-luf sai sheki suke, san da idanuna ya sauka kan lips ɗin sa da sauri na lumshe idanuna bana so na shagalta da kallon sa.
ɗan numfashi ya sauke kana a hankali ya ɗago hannunsa batare daya buɗe idanunsa ba ya zare hijabin jiki na sannan ya saka hannunsa ya zagaye ni,
nan ma wani numfashin yakuma sauke wa, jin a iya nan ya tsaya bai kuma yin motsi ba,
nakai tsawon awa guda idanuna biyu ganin dai baccin yatafi da shi sai nima na lumshe idanuna babu jimawa bacci yayi gaba da ni...

Washegari nayi nayi ya buɗe min kofa da asuba na tafi yaki, dana matsa yace kada na cike shi da surutu, a ɗakin duk muka yi salla.
koda gari yayi haske Knocking ɗin kofar da ake ne yasa shi mike wa yaje ya buɗe kofar, Naseem ne da Nasmah sai Mamie da Abbu Abba Ummi da kuma Bappa.
ina ganin su da sauri na gyara zama ta, tare da sun kuyar da kaina kasa cikin jin kunya, Allah ma yaso da hijabi a jikina.
suka karaso cikin ɗakin suna yi masa ya jiki, yace
"Da sauki." cike da jin kunya nashiga gai da su Bappa, suka amsa suna tambaya ta ya mai jiki.
nidai bance komai ba dan kunya yaga isa ta, Ahmad dake rike a hannun Ummi
yashiga mika wa Ya SALEEM hannu yana tsalle a hannun ta alamun zaije gurin sa, cikin gwalaɓen sa yake faɗin Daddy Daddy.
wasu zafafan kwalla ne suka ciko ido na, cike da tausayin ɗan dan nasan gani yake kamar mahaifinsa ne Ahmad.

murmushi Ya SALEEM yayi ya mika hannu ya karɓe sa yana cigana da yi masa murmushi har sai da fararen jerarrun hakoran sa suka bayyana,
ina ganin su Abbu sun fita nima da sauri na mike nabi bayan su, su Nasmah kuma suka zauna a gurin sa.
har dare su na gurin sa har da Ahmad.
a daren ranar ma dana kai masa abinci, hana ni tafiya yayi yasa aka kwashi su Naseem da sukayi bacci a ka kaisu gun Mamie dukan su,
washegari ma har sai da su Abbu suka shigo duba shi kafin na fita, ina mai jin kunyar su...

Yau kam na ɗaura aniyar bazani ɗakin sa ba, da wuri nayi shirin kwanciya ta na haye gado, Ummi ce
ta shigo tarike baki tana faɗin
"Ikon Allah wai ke sai an ce ki kai masa abinci kafin ki kai masa, kwanciyar ki kikayi wazai je ya kula da shi, amma dai kin san ba lafiya yake da shi ba ko."
da sauri nace
"Ummi shi yaro ne da sai an kula da shi dan bashi da lafiya, nima kai na ciwo yake min a bawa Fauzan ya kai masa."
tace "Ungo naki tashi maza in kin je can ɗakin nasa kya sami magani ki sha, yo dan tsiya wazai kullar miki da shi kina matar sa abincin da nake masa ma taimakon ki nake ai kin san dai aikin ki ne, shashancin banza maza tashi ki kai masa."
baki na turo gaba na mike kamar na saka ihu ina buga kafa nayi waje,
nacika har wuya haushin sa ya kamani
"Sai kace wani karamin yaro."
nayi maganar a fili ina jan tsaki.
ina shiga ɗakin na dangwara masa abincin najuya da sauri, har na ɗaura hannuna jikin handle ina kokatin buɗe kofar na fita, najiyo muryar sa haɗe da ɗan tari tari yace
"Zo ki bani magani na a can na sha."
naɗan juyo ina kallon in da yake nuna min saman bedside,
kamar na tafi abina ganin yan da ya damie kirjin sa yana ɗan jan numfashi da taunar lips ɗin sa, sai na juyo a hankali naje na ɗau magani haɗe da gorar ruwa da cup dana gani a gun,
na zo gaban sa na mika masa maganin kana na siyaye ruwan cikin cup na mika masa, ina tsaye ya sha ya miko min cup haɗe da maganin.
ido na shiga rabawa cikin ɗakin ganin ban ga su Nasmah ba nasan har ya sa an kaisu gurin Mamie.
ina aje maganin na juya zan fita nakuma jiyo muryar sa yana faɗin
"Zo ki rufe ni."
koda na juyo naga yakwan ta yaɗan dunkule guri guda da alama sanyi yake ji, baki na taɓe a raina nace
"Ba dole kaji sanyi ba a sanyin nan singlet da gajeren wando ne ajikin mutum gakuma AC na aiki."
na iso bakin gadon na ja blanket na rufe masa jiki, zan juya sai jin hannun sa nayi cikin nawa ya janyo ni na faɗa jikin sa,ina kokarin mike wa ya gyara min kwanciya gefen sa tare da rufe ni da

bargon ya janyo ni jikin sa sosai har muna gogar juna.
"Sanyi nake ji." yayi maganar yana tura hannayen sa duka biyu cikin
riga ta yana mai daɗa janyo ni jikin sa, tafin hannun sa sun ɗau zafi rau sai daɗa cusa su yake cikin jiki na yana niman mafakar da zai aje su,
gaba ki ɗaya jikin sa yayi zafi har ina jin zafin yana rasa ni, shiru nayi ina jiyo sautin bugun zuciyarsa, sai fidda numfashi yake da ɗan sauri sauri.
a ɗan tsorace ganin halin da yake ciki nace
"Ya SALEEM ko na kira su Abbu ne jikin ka yayi zafi sosai, ko za'a koma asibiti."
cikin ɗan jan numfashi yace
"A'a su ba zasu iya yimin maganin komai ba ke ce maganin ina jin sanyin sosai kiyi wani abu na daina ji."
ɗan shiru nayi ina tunanin maganar nasa,
kankame ni yayi sosai a jikin sa kana ya cigaba da magana
wan da maganar tasa a hankali yake fita haɗe kuma da sautin numfashi,
"Ki taima min wajen samar min da ɗumi a jiki na na tabbata ke kaɗai zaki iya."
shiru na kuma ina tunanin ta ina zan fara kamar yadda yace ɗin, sake ni yayi
a sannu yaɗan yunkura ya zame singlet ɗin jikin sa, kana ya ɗago ni ya zare rigar baccin dake jiki na, yarage sai bra da kuma wandon rigar.
da fari nayi kokarin dakatar da shi daga cire min rigar da yake yunkurin yi, sai dai ganin yadda yake rawar sanyi da faɗin sanyi yake ji, sai na hakura da kuma ganin bayyi yunkurin cire min bra ba.
rungume ni yayi kamar zai cusani cikin kijin sa yarika mannani da jikin sa, yayin da ya saka fuskarsa gefen wuya na yana juya fuskarsa da manna shi a fatar wuya na.
yarika yin haka har muka kwanta kan katifa,
ya kan kame ni gam-gam ko kyakkyawar motsi ba na iya yi,
magana ya soma cikin jan numfashi
"HAMDAHHHH kar kiyi nesa da ni dan Allah kada ki kara yin nesa da ni, na tabbata kika sake bari na babu ko shakka yanzu kam mutuwa zanyi,
ban san yanda zan misalta miki yadda nake ji cikin zuciya ta ba,
amma ki sani zan iya mutuwa idan kika kuma bari na,
kiyi min alkawarin bazaki sake bari na ba, zaki zauna dani duk wuya duk rintsi ina mai baki hakurin abun da ya faru,
amma ki sani bada sona hakan ta faru ba."
ture sa na shiga yi ina faɗin
"Idan bada son ka ba tilasta ka akayi, ka wulakanta ni ka tozartani kayi min kazamin kazafi da tabo mai muni, ka kazantamin ƴaƴa na kasa mahaifina yayi min korar kare kasa Ummi na ta zubda hawayen ta, kasa na shiga duniya rayuwa ta takusa salwanta har da na ƴaƴa na da basujiba basu gani ba,
Ya SALEEM bazan taɓa yafe maka ba, ka sani ka rabu da ni babu wani yafiya saka nin mu, wannan komawar auren kaddarar zan karɓe sa zuwa san da zaka gama samin lafiya zan yi tafiya ta nayi nesa da nan bazaka sake gani na ba,
kaje ka zauna da matar ka mai gaskiya wacce bata karya bata kuma kawo maka wani gardi gida da cikin shege gida ba da auren ta, ni kuma zan zauna da nawa halin a haka da kuma

ƴaƴan da basa da uba sai uwa a duniya."
da karfi na ke ture sa ina son kwatar kaina, ganin ko kyakkyawar motsi bana yi cikin hannunsa.
sai kawai na saki kuka ina cigaba da ture sa da faɗin
"Ka sake ni ka rabu da ni."
lips ɗin sa ya taune da karfi tare da rumtse idanunsa yayin da sautin bugun zuciyarsa ya karu.
fuskar mu ya haɗe guri guda, yana goga fuskar sa kan nawa, yaɗan fisgo numfashi kana yace
"Kiyi hakuri dan Allah ki mance da kukkanin abun da ya faru cikin duhu babu haske, ki kuma daina dan ganta min ƴaƴa na da mara sa uba."
nayi matukar mamakin jin fitar kalmar hakuri daga bakin Ya SALEEM wai ni yau yake baiwa hakuri, cikin tattausan lafazi da sigar lallaɓi da kuma neman gafara haɗe da sulhu.
ganin numfashin sa yana yin sama-sama da sauri na haɗiye kukan ina faɗin
"Ya SALEEM na kira su Abbu ko Dr Farooq?."
kai ya girgiza min yana ta kokarin janyo numfashin sa, tsoro ne ya kamani sosai ganin yan da yake yi sai na shiga jera masa sannu a kiɗime.
kansa ya ɗan ɗago da kyar yana kallon cikin kwayar idona yakuma yanyo numfashi da kyar kana yace
"Ke ce maganin idan kika yafe min nasan zan warke."
da sauri nace "Nayafe maka nayafe maka Ya SALEEM."
wani murmushi ya sake har sai da hakoran sa suka bayyana, a hankali ya sauke lips ɗin sa kan nawa ya tsotsi baki na sosai kana ya zare bakin sa tare da faɗin
"Nagode."  kwanciyar sa yaɗan gyara batare daya sake ni ba, har kuma lokacin numfashin sa bai dai-dai ta ba,
lamo nayi a jikin sa ina jiyo bugun zuciyarsa,
a sannu a hankali bugun zuciyar tasa da kuma numfashin sa suka fara dai-dai ta, har sukayi normal.
idanunsa a lumshe kamar mai yin bacci fuskarnan tasa yayi fayau da shi.
numfashi naɗan sauke ganin ya sami salama daga halin da yake ciki hatta zafin jikin ma babu shi yanzu,
a hankali nashiga kokarin zame jiki na, sai ji nayi ya daɗa rike ni gam
da sauri na kalli fuskarsa idanunsa a lumshe, sai na mai da kaina a raina ina ayyana idan baccin sa yayi nisa zan tafi abina, ban san san da bacci ya ɗauke ni ba sai kiran sallar asuba najisa a kunne na.
ko da na buɗe idanuna baya gadon, jin karar buɗe kofa yasani kallon kofar bathroom,
jikin sa na ɗiga da ruwa da alama wanka yayi, a sannu ya tako bakin gadon
ya dube ni da kyau kana yace
"Taso kije kiyi al'wala kizo muyi sallah."
yayi maganar yana ruko hannuna tare da mikar da ni zaune,
ganin yan da yake bina da wani irin kallo da sauri na kalli in da yake binsa da kallon, cikin hanzari na janyo blanket narufe kirji na, na gama mance wa babu riga jiki na sai bra,
baki na ɗan turo tare da janyo riga ta na saka kana na mike na shige bayin,
sai da na wanke baki na da burosh ɗin sa kana nayi wanka sannan na ɗauro al'wala na mai da kayan da na cire na fito.
a kan sallaya na same sa yana zaune yana azkar,

yana gani na ya mike tare da ɗaukar hijab ɗina dake bakin gado ya mika min na saka, kana na tsaya bayan sa yaja mana sallar ko da muka idar addu'a sosai ya rika kwararo mana na neman kariya da samin falalar Ubangiji.
muna shafawa na mike
"Zo mana." ya faɗa yana mike wa kan sallayar bakin gado ya zauna, a hankali na tako in da yake,
sai ya ruko ni yace "Zo ki rufe ni na fara jin tsanyin."
sakiyar gadon ya haura nima na hau ina kokarin jan bargo na rufe shi, sai ya janyo ni na faɗo jikin sa.
ya zagaye ni da hannayen sa, a sannu ya mirgina ni zuwa kasa shi ya dawo sama na,
hijab ɗin jikina ya zare kana a hankali kamar maiyin raɗa yace
"Zaki taya ni hira?."
kai na girgiza da sauri nace
"A'a." idanunsa ya lumshe tare da kuma buɗe su cikin nawa sannan yace
"Please ki gwada dai."
kai na girgiza a lamar a'a dan yafara sanya min kasala da narkakkun idanunsa, sai naji baki na yayi min nauyi.
asannu yashiga kissing ɗina da shafa ni, yakuma tare ni ta in da bazan iya motsawa ko yunkurin dakatar da shi ba,
cikin kankanin lokaci ya kashe min jiki da salon sa, har ya sami nasarar zare rigar jiki na, a sannu ya kife fuskarsa sakankanin ababen kirji na  ya zura harshen sa yana latsar tsakiyar su da gefe da gefen su,
gantsare wa nayi jin yan da harshen sa ke yawo sakankanin nonuwa na,
hakan dana yi kuwa ya bashi dama wajen zura hannunsa ta kasan baya na, ya ɓalle maɓallan bra na a sannu cikin wani irin salo mai wuyar fassara ya zare bra'n.
wani nannauyar numfashi ya sauke, yakafe ababen kirji na da ido,
wan da suke tsaye kyam sun cika tip-tip tamkar babu ɗan da ya taɓa sha, kana ya ɗago hannunsa da tuni suka kama ɓari ya sauke su kan ababen kirji na, wani irin cafka yayi musu tare da kuma sauke numfashi, nan yashiga shafa su da matse su kana ya kafa bakin sa kan ɗaya yayi masa kyakkyawar cafka tamkar zai cinye shi.
yarika tsotsar sa yana kuma matse ɗayan,
sai da ya tsotse su son ransa kana yaɗa go yayin da gaba ɗaya jikin sa ya ɗauki ɓari ya zare wandon jiki na, ina kwance ko yatsa ta bana jin zan iya ɗagata dan gaba ɗaya ya gama kashe min jiki da salon sa.
jallabiyar jikin sa ya zare haɗe da boxes,
nan ya cigaba da latse jiki na tundaga kan nonuwa na har zuwa kan HQ ɗina jin yanda yake juya tongue ɗin sa cikin HQ ɗina yasani bankare wa tare da cusa hannuna cikin sumar kansa.
"Ya SALEEMMM ka bariiiiii." nayi maganar jiki na na ɓari, sama yayi da hannunsa batare daya ciro bakin sa ba ya zura min yatsar sa cikin baki ba shiri na cafke yatsar nashiga tsotsar sa.
sai da yagama birkita ni ya kuma birkita kansa kafin ya ɗago yayi min rumfa yana karanto addu'a.
da sauri ya shige ni a tare muka sauke numfashi a fili,
kamar dai da suna na yarika kira yayin da yake sama da kasa a kaina kamar jarumin dokin

daya sami katon fili yake sukuwar sa son ransa,
Ya SALEEM jarumi ne bana wasa ba ina daɗa tabbatar da hakan ne a duk san da ya kusan ce ni, a yauma na daɗa gaskata hakan dan kuwa na gurzu a hannunsa bana wasa ba, sai da na nimi daya yi hakuri ya kyale ni.
bayan yasami sauke abin da ke cikin matar sa yayi lamo a kaina yana maida numfashi,
a hankali ya zare jikin sa ya kwanta gefe tare da janyo ni ya rungume ni a jikin sa sosai, yayin da yake jin sa wasai tamkar an zare masa ciwon da ke damin sa.
idanuna na lumshe ina mai sauke numfashin gajiya,
a hankali ya shafi gefen fuskata a sannu na buɗe idanuna muka haɗa ido da shi,
lallausar murmushi ya sakar min kana ya mike ya shiga bayi,
yana mai jin zuciyarsa wasai,
siffofin HAMDAH ne kaɗai ke yi masa yawo a ido yan da yaganta ta kara cika ko ina ya ciko tip-tip da shi sai tsole idon mai kallon sa yake.
yana wankan yana sakin murmushi lokaci zuwa lokaci,
yadda ya sami HAMDAH bayyi zaton samin ta a haka ba sai kuma tayi masa ba zata dan yadda ya jita sai yake jin taɗare sanin sa a da' bayan yayi wanka ya fito, ya karaso baki gadon yaruko hannuna yana faɗin
"Taso kiyi wanka."
ina mike wa da sauri na koma na zauna ina mai mamakin kaina  dajin abin da nake ji a duk san ya ya kusan ceni a wancan lokacin,
hakika Ya SALEEM na daban ne.
"Yaya dai."
yafaɗa yana mai ruko ni da sauri, hannu na yarfe nace
"Jiri nake ji."
kansa ya ɗan dafe tare da faɗin
"Oh sorry na mance zauna bari na samar miki abin da zaki ci."
tea ya haɗo mai kauri ya mika min na sha kana ya taimaka min na mike naje nayi wanka, yana tsaye har na gama duk motsin da zanyi idanunsa a kan bottom da breast ɗina.
ina fita na saka kaya da sauri na fita a ɗakin, gudun kada su Mamie suzo naji kunya......

Kwana na goma yau na ɗaura aniyar komawa saboda kiran danake ta samo daga can,
banbi ta kan Ya SALEEM ba na sami Bappa na sanar masa dan nasan inta shine kam bazai barni na koma ba.
Bappa yasame shi da maganar yace bazan tafi ba ko zan tafi ba yanzu ba,
sai da Bappa ya nutsar da shi da kyau game da ayyuka na, da kyar ya amince na tafi...
kwana na uku da dawowa ya biyo ni,
ranar da yazo yace shi bazai bakwana a side ɗina ba,Bappa yayi dariya yace yasan abinda yake damin SALEEM kishi ne kawai kishin ma da da wan da ya mutu,
a side ɗin ba'ki ya kwana, washegari kuwa can naje na taya sa kwana.
washegarin kwanan sa na uku tun da yafita da safe sai yamma ya dawo yana dawowa yace, mu tattara mu koma gidan sa dan shi bazai zauna cikin gidannan ba,
Bappa yace gidan nasa a ina yake kuma yaushe ya siya, yace tuntuni yana da abinsa yau kuma

yasa aka zuba komai na amfani.
a daren ranar aka raka mu sabon gidan sa,
babban gida ne sosai dan girman sa ya kai wan da muka baro,
an shirya komai na more rayuwa.
wancan gidan kuma nace su Abbu su dawo ciki su zauna da su Bappa cikin wata ɗaya nasa aka rushe ɗaya side ɗin gidan da Mama da su Talatu suke zaune ciki aka gine shi iri ɗaya da ginin side ɗina,
Abba da Ummi suka dawo ɗaya Abbu da Mamie suka zauna a ɗayan.
 kana aka gine wani gefe guda ɗan dai-dai Mama ta koma ciki,
gidan mu na Bauchi kuma a ka kulle shi, aka barshi na saukar mu idan muka zo Bauchi ko wani hidima idan ta tashi acan muna da masaukin sauka ciki,
gidan Ya SALEEM kuma ya barwa Ya Mas'ud dan shi bai dawo Abuja sabo da aikin sa, yace idan yayi aure yasaka matarsa a ciki......

Bayan wata uku da komawar mu sabon gida Aunty Rafee'at ta haihu, muka tafi bauci duka har da su Ummi.
bayan suna da kwana biyu, mukayi shirin koma wa, motar su Ummi ya riga namu tashi dan Ya SALEEM
ya fita bai dawo da wuri ba, ya na dawo yakwashe mu,
muna fita daga layin unguwar mu kira ya shigo wayar sa bayan ya sun gama magana da wan da ya kira shi ya dube ni cikin kula yace
"Wani aboki na ne nayi masa alkawarin haɗuwa da shi idan nazo yanzu yake tuna min da hakan, bari mubi gurin sa sai mu wuce daga can."
nace to, yajuya akalar tafiyar izuwa gurin abokin nasa,
a bakin get ɗin wani asibiti yayi hon a ka buɗe get ɗin yasa kai ciki,
yana dai-dai ta parking muka fito, yana ɗauke da Ahmad yayin da yake rike da hannun Naseem, niko ina rike da Nasmah muka nufi  cikin asibitin,
a bakin kofar da zai sada mu da cikin asibitin muka haɗu da abokin nasa,
gaisawa irin na abokai suka fara tare da ɗan zolayar juna,
abokin nasa ya dube ni yana faɗin
"Madam da so kike ki tafi da shi baki bari mun haɗu ba ko."
dariya nayi tare da gaishe sa ya amsa yana yiwa su Naseem wasa,
ya dube Ya SALEEM yace "Muɗan je daga can kada wari ya dame ku anan."
Ya SALEEM yace "Wari kuma ina ma'aikatan naka suke da bazaka sa su gyara maka cikin asibitin ba, ai hakan sai ya iya karawa masu jinya ciwo."
yace "Wlh kai dai bari wata mara lafiya ce ke wannan warin ba datti ba,yanzu haka da nake faɗa maka ta kora min kostoma, duk wani wan da zai kawo majinyaci nan da zaran ya shigo yaji wannan warin sai ya juya da majinyacin sa,waɗan da suke nan kafin ta fara wannan warin suma suka tattara sukayi gaba,
hatta ƴan'uwan ta kasa zama sukayi a kanta sai kuɗi suke turawa na jinyar ta, to suma inaga yanzu sun gaji ne dan wata biyu kenan rabon da suturo da kuɗin,

nima yanzu nagaji sallamar ta zanyi nasa a tattara ta akai ta duk in da tace a kaita dan zata kashe min kasuwa."
kai na jinjina cike da tausayin matar, nace "To me ya same ta haka wani irin cewo ne gare ta?."
yace "Wlh hatsari tayi tasami kariya a kafa da hannu an ɗaure kafan bayyiba karshe ruɓa yayi dole sai an yanke kafar shine yake wannan warin, ƴan'uwan ta kuma su kawo kuɗin ai kin sun gagara gashi nan ta ishe mu da wari."
Ya SALEEM yace "Kuɗin har nawa ne haka?."
yace "Miliyoyin uku."
kai na girgiza ceke da jin tausayin ta nace
"Ayya ko zamu iya ganin ta?."
ido ya waro yace  "Wa wai kushiga inda take?, ai bazaku iya ba tana cikin ɗaki kofa a kulle wari yana fito wa har nan ta ya zaku iya shiga inda take."
nace "Zan iya muje na gaishe ta, Allah ban ganta ba amma tausayin ta ya cika ni."
"To muje in zaku iya."
yafaɗa yana shige wa gaba muka bi bayan sa.
sai da ya shiga office ɗin sa ya ɗauko turare haɗe da facemax ya bamu muka saka kana yayi gaba yana fesa turare muna biyo shi har muka isa bakin kofar ɗakin da take ciki.
sai da ya shiga ya fesa turare mai yawa kafin yace mu shigo,
muka kusa kan mu ciki, duk da turaren da ya fesa bai hana ɗakin tashi da wari ba, kamshin turaren daban warin shima da ban.
ido na kurawa matar dake zaune a kan gado kuda suna binta, ina ta son tuno in da na santa.
hannun ta na ɓari ta shiga nuna mu tana faɗin
"HAMDAH SALEEM." sai kuma ta fashe da kuka, da mamaki nake kallon ta nace
"Na'ima ke ce?." kuka sosai take tana faɗin
"Dan Allah dan Allah HAMDAH ki yafe min kinga yanda Allah yayi dani ko kowa guduna yake, nakuma san alhakin ki ne ke bina, ki yafe min na roke ki, SALEEM dan Allah ku yafe min, HAMDAH ina ɗan da kika haifa na roki gafarar sa ko shima zai yafe min.
Naseem da Nasmah na nuna mata nace "Gasu nan." hannu ta miko tana faɗin
"Kuzo ku yafe min ko zan sami sassauci gurin mutuwa."
da sauri Ya SALEEM ya janyo su jikin sa tare da binta da mugun kallo yace
"Kul kada ki sake ki taɓa min yara."
ya sasu gaba sukayi waje ina kiran sa bai ko saurare ni ba.
kuka Na'ima ta kuma fashewa da shi tana cigaba da niman gafara ta,
kwalla na share nace "Na yafe miki Allah ya yafe mana duka, Allah kuma ya baki lafiya."
godiya ta shiga min ba kakkautawa,
na fita ina yi mata Allah ya sawaka,
a cikin mota na tadda su Ya SALEEM sai tofar da yawu yake rantsa a ɓace.
a take a gun na karɓi account ɗin Dr nayi masa transfer ɗin kuɗin da ake nema ayi mata aikin, nace "Ayi mata aikin dan Allah cikin gaggawa dan naga alama tana jin jiki sosai."
yace "Insha Allah za'a yi sa cikin gaggawa tun da ga kuɗi ya samu."
ina shiga motar Ya SALEEM ya figi motar da gudu bai ko tsaya yi wa abokin nasa sallama ba.
har mukayi nisa babu wan da yayi wa wani magana,har lokacin kuma fuskarsa babu annuri, kamar an zabure sa cikin faɗa ya kalli inda nake yace

"Matar da taso hallaka rayuwar ki dana ƴaƴan ki wai ita kike jin tausayi, ko yau ta tashi sai ta nimi abin da zata hallaka ki da shi, ita ba abin tausayi bace, wai har kuɗi kika biya ayi mata jinya, to bari kiji har idan kinsan kuɗin maraya kika ɗauka kika bada ayi mata aiki dashi, kiyi gaggawar maida masa abin sa dan nasa ne ba naki ba."
murmushi nayi nace "Ayya Ya SALEEM wlh ta ban tausayi ne, idan muka yafe mata Allah shi ma zai gafarta mana, kuma ba kuɗin Ahmad na bada ba kuɗi na ne, kai ma kayafe mata dan Allah."
a fusa ce yace "Bazan taɓa yafe mata ba kin san girman laifin da ta aikata min kuwa! ta raba ni da ke da kuma ƴaƴa na, shi ne kike cewa na yafe mata!!."
ya karasa magaran cikin karaji.
kai na girgiza nace "To ba gashi mun dawo gare ka ba yanzu, babu abun da baya wucewa."
ganin bai kuma magana ba sai huce yake, nasan ransa ya ɓaci sosai, a hankali na ɗan matso tare da kwantar da kaina jikin kafaɗar sa.
nasaka hannuna nazagaye shi,
numfashi ya sauke a fili kana yayi kasa da idon sa ya kalle ni, murmushi na sakar masa, yawani lumshe idanunsa tare da kuma sauke numfashi.
da sauri na tashi a jikin sa nace
"Ya SALEEM ka buɗe idon ka karkasa mu faɗi."
ya buɗe idon a kaina tare da sakar min murmushi mai sanyi.....

Bayan shekara ɗaya
zaune nake a parlour natasa katon ciki na gaba Ya SALEEM ne suka shigo shi da Naseem da Nasmah da Ahmad.
tun kan ya karaso yake bina da murmushi yaran ko da gudu suka iso in da nake zasu zube kaina, da sauri Ya SALEEM ya ɗaga kafa ya taro su yana faɗin
"Kai ku tsaya kada ku danne baby ciki mana,
ku zauna a nan." ya zaunar da su gefe kana ya zauna gefe na tare da shafo ciki na ya ce
"Wai yaushe zaki haifo mana babyn mun masu mu gansa fa."
baki na turo nace "Nima na matsu na sauke na huta."
Naseem yace "Mommy yaushe zaki zamo mana baby." baki na turo banyi magana ba
Ya SALEEM yaɗan yi karamar dariya yace
"Bashi amsa mana,yauwa Naseem me kake so a haifo mana mace ko na miji?."
baki ya washe yace "Namiji."
yace "To Aunty Nasmah fa me kike so a haifo mana?."
tace "Daddy na mace."
ya ce "To duk naji naku saura na my Ahmad ɗina, kai me kake so?."
yace "Mace na miji."
dariya mukayi dukan mu nace "To kai duka kake so mace da na miji kenan."
rungume shi Ya SALEEM yayi yana faɗin
"I love You my son Allah ya kawo su masu albarka irin ku."
dariya nayi ina kwantar da kaina jikin kafaɗar sa,
gefen fuska ta ya shafo yace "Inayi miki son da baki ba zai iya furta wa ba, idanuna na lumshe

ina sakin murmushi,
nikam nasan nayi dace a rayuwa ta da kallamar sona Ahmad ya mutu gashi a yau gorzo jarumin maza ABDALLAH IDRIS ABDALLAH yana faɗa min girman son da yake min a zuciyar sa wan da baki bazai iya furta wa ba sabo da girman sa.
hakika ni HAMDAH nagodewa ALLAH...............!

TAMMATBIHAMDILLAH

Ina godiya wa tabaraka ma ɗaukaki mabuwayi mai izza da ya nuna min wannan rana da littafin nan ya kawo karshe,
ina yiwa ɗaukacin masoya fatan alheri....